DUBA MIN BAYA FAKON BIRI,,,,,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

1

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DON MIN AMANACE HAKKI, , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIOVISUAL HAKKIN S ZARI NE WANAN.

Akori kura motar kauye ta kwashi kaya ta kwashesu takaisu gangaren yan ,,,,,

Wanan wakar da mukeyi da dare idan muna wasan hasken farin wata na dandali na tuna a yau da muke bayan wanan tsohuwar akori kuran motan data dauko mu muda kayan mu har yar akuyata durgu yar illori mai zuba min diya da inna ta saye da sunana .

Don inna na fadin hbakinsa

yana da albarkan kiyo ta fahinci hakan ne tun lokacin yayena da aka sake min kaza da sunana wanan kazan a yau itace ta rikede ta zamo min akuya dan nake kiyo mai sake min diya tasowan namu mane aka sayar da mazan inna ta dunkule kudin tazo muna dashi nan katsina da zamu zo.

Asali kuma tasowan mu zuwa katsina shine dalilin fadan baba da matan gida wanda fadan yarane ya kawo wanan hatsaniyar dama gori muna shansa duk da muna yara amma haka za a sake muna magana da sunan diyan agolan gida.

Sukace damu idan dan magana ya hadamu dasu sani in fika angola da rabon gidan gidan gado tun bansan ma,anan hakan na har yakai na fahinci me suke nufi da kalman hakan a garemu.

Watau mu da mahaifan mu mun algaje gida baba yazo masu gida ya zauna yana yar mace yana kokarin fin masu gidan karfi shine habaicin nan ya hau kan mu dan abu kadan za,ace damu sani in fika,,,,,,

Ko asalin wanan fadan da har yakai muka bar kauye a yau ya samo asline daga mama tambaya matar da ta zamo masifafa a cikin wanan gidan kusan kowa na tsoron ta gidan bama gidan ba ince kaf kauyen kusan kaf suna tsoron mama tambai don haka wasu ke kiranta dashi asalin sunan tambaya.

Don irin matan nam ne da iyayye ke tambaya wurin bokaye ko malaman tsubbu da sukan zo su addabi al,umma saboda suna da surki da aljannu ko wani saddabaru shine mutane ke mata lakani da tambai din a fahintar bahaushe.

Wanan matar itace dai silan barin kauyen da muke zaune a ciki inda mahaifan mu suka haifemu mu ukku yan mata wanda take muna lakani wani lokacin da haihuwan yuyuyu da babu gara daku don kunfi babu gun iyayyen ku.

Muna dai rayuwane naba dadi a wanan dajin don can yake surkukin daji tsakanin Jibiya da Niger inda ya hada mahada da kasashen biyu watau niger da nageria asali mu mahaifiyar mu yar niger ce mahaifin mu kuma dan Nageria don kusan rayuwansu dayane a wajen don haka alakan aurataya yake yawan shiga tsakanin mazauna wajen don kusan ko wani halakan zimunci na bahaushe ya samo asaline ta dalilin aurataiya a duniya.

Matan gidan mu basu kaunar mahaifiyarmu damu don kawai kishin saure da yawancin matan hausawa sukeyi tsakanin matan wa dana kani ko wani dan uwa a dauki kishin duniya anawa juna har yafi na kishiyar da kuke miji daya zafi wani lokcin ma abin yakan zamo harda jifa a tsakanin don basu kaunar mijin daya ya dara na daya samu wanan shine yakan jawo wanan bakin kishin a tsakani a koma ana jin haushin juna na ba gaira ba dalili.

To nagidan mu da akewa lakanin da babban gida a kauyen mu ya samo asaline ta irin albarkan noman da baba ke samu wanda har ya dara samun mazansu yasa suka dauki kishi da kyashi da hassada suka dorawa iyalin baba watau mu ke nan a yanzu.

Don baba ya dara mazajen nasune kuma ta hanyar dan aikin da yakeyi na likitancin dabbobi a kauyen kasancewa shivyayi karatun shi don mahaifinshi bai

yarda ya barshi cikin yan uwa ba ilimi ba don yan uwan baba na haihuwa da suke uba daya suna garin katsinane da zamasu.

Hanyar uwace nan a kauyen dan shi kusan hannun mahaifiyarshi yayi rabin rayuwanshi ko zaman mu a kauye gadonta yakeci yasa yake zaune a gidan da suke ganin kamar zaman banza yakeyi shi agolan gidane ba dan gida ba.

Amma mazajensu sun sani kason mahaifiyarshi ya gada a gidan yasa yake zaune dasu a cikinsu har yakai ga tara iyalin kansa da suka dauki karan tsana suka saka muna .

Don duk sun hade muna kai ko dayan mu ya dan fita by mistake yanzune za a hattaroshi don hakane bamu fita ko ina muna sashen mu dake can karshen gidan wanda yakai har baba ya bude muna hanya ta baya amma duk da hakan bamu tsira ba a wajensu.

Don don gulma zaki gansu sun biyo wai hanyan yafi saurin fita idan tafita ya kamasu kwatsam muna zaune zamuga sun fado muna ba ko magana wani lokacin hakan zasu tatsamu su wuce zuwa inda zasu.

Dan dama dama in yan arzikin na a kai wani lokacin zasuyi muna magana kansu fita din amma ido na aikin gulma suna rabashi wurin kallon wani bakon abu da idan anshiga gida za a karas wa sauran jama,an gidan da cewa muga kaza munga kaza a sashensu wace ai ko kuma a ailo inna ta sam masu abu kaza da suka gani.

Saboda mahaifinmu yana shiga daji a kullun wajen yin sana,an sa don hakane baka raba sashen mu da kayan marmari irin na kauye harma dana birnin don yana yawan shiga katsinashi sosai ya saro kayan amfaninshi ya dawo kauyen don hakane muka dan bambamta da sauran mutanen gidan da suka dora kyashinsu a kan mu.

Fada akayi akan mama tambai ta aiko inna ta san mata dankali hausa data gani shine inna tace bata aiko da wuri ba ta sulala ko saidai dafafen ta diba mata yan kwarori wanan ya kawo fada har yakai ga gama na tsawon wata da watani a tsakaninsu wanda dole kowa ya bita don tsoronta da akeji muka koma rayuwa mu kadai a gidan da mun fito kuma su bugemu mu koma da kuka lungun mu.

Har yakai sai babane zai fita yayi fadan hakan don inna kan gaskiya tana tsoronsu sosai ita kan sun manna mata tsoronsu kuma tanayin hakan.

Yasa bamu shan ruwa ya sauka muna a ciki ba,a dawo dashi ba abin yana bakantawa baba rai yasa da zaran karfe hudu yayi baba na gida da iyalinsa yana hada yan kayayakinshi ko yana wani abin don idonsa yana kan mu ko yaushe.

Kanwata habibi da aka aika shago ta biyo ta cikin gida don yafi kusa nan dan mama tambai ya maketa kuma ya zubar da gishirin a kasa ya turmuze da kafa anyi dace koda ta shigo da kuka daidai lokacin baba na gidan don dawowanshi ke nan

yana aje tsohuwar mashin dinsa suzuki yana kokarin baiye dan kulin buhun kayan shi daya dauro a baya mukaji kukanta tashigo ga baki ya fashe yana jini.

Nan ya tashi ya bisu ya samu dan mama din ya doka ita kuma ta dauko tabarya tayi masa rotse a kai Allah ya gyara a ranan da baba ya mutu don jini ya balle a goshinsa daidai inda ta buga masa tabaryan saida akaje kemis aka gyara masa.

Wanan yasa abin yai tsanani don yace sai ya halaka mama ita kuma tace kafin ya halakata sai tayi sanadinsa har iyalinsa sun bar duniya hakan yasa mazan gidan suka shiga cikin zancen.

Ganin abu yaki ci yaki karewa yasa baba yaje birni gidansu na gado ya tayar da wa yanda ke haya a part dinsa ya gyara da sunan zamu koma ciki da zama.

Rana daya bai fadawa kowa ba sai ji sukayi wanan akori kuran ta tsaya kofan mu ana loda yan kayan mu a ciki labari ya kai masu suka dauki tafe da shewa mama har guda ta rangada taci gari dole uwar naki baba zai bar mata gida don dole.

Yan uwanshi maza basuso hakn ba don mutum yana da ranansa saboda zaman baba a cikinsu akwai taimako mai karfi a tsakaninsu wanda yake masu su matan basu sani ba.

Su baba Ado sukazo suna tambaya yace katsina zai mayar damu amma aishi yana nan zai maidamune can saboda mu saba da yan uwa a can kuma muyi karatun boko don nan karatun sai a hankali idan ya barmu a daji.

Hakana dai basu so ba suna kallo muka shiga wanan akori kuran da zata kaimu har katsinan da muke jin cewa aimu yan katsinane ba yan durumi ba.

Tashin motan mu suka dauki shewa a inda suke lalabe ta danni zana suna leken mu lokacin ne baba Ado yace kaiya mugu kariyan nagari zaman Audullahi gidan nan shine alherin mu don shine hasken gidan nan yanzune zaku gane hakan da baya nan.

Mukan duhun gida suke a wajen mu yaya tunda bada cinsu ko shansu muke rayuwa ba akarata can inji yan iya magana har tsintsiya ta dauko tana share hanyar motan da mukabi wai ta rabu da alkakai a gida tsohun ya girgiza kai yashige ciki yana fadin.

Yanzune ma kika yadawa Audullahi da iyalinsa fitila da ada basu ganin haske komawanshi cikin yan uwansa shine silan darakin nan da baki son kiga sunyi don yanzu zaki san barnan da kikayi a baya nayin hakan.

Ina baya zaune rike da igiyan ukuyata ni da baba don inna tana da tsohon ciki a lokacin hakan ne ma ya dagawa baba hankali yaje ya shawarci babba tsohuwar gidan su data rage akan yana son ya dawo da iyalinsa nan.

Tace Abdullahi ai kakine mutum yana gudun gidan ubansa ya koma daji ya zauna wajen bare gidan uwa ai ba wurin zama bane ga magidancin da yasan kansa a zamanin nan dane ba,a damu da irin hakan ba amma yanzu kan kan kowa ai a bude yake .

Tun ina kallon har nagaji na takure a waje daya ga iskan sanyi da yake huro muna don yanayin da muke dosa din na daban da namu yanayin da muka baro a baya mai dan surkin zafi zafi zafi da kura.

Fada gari fada kauye har Allah ya kawomu lafiya gidane mai kyau irin ginan da din nan mai nuna halin gameshi don yaji simiti da yar dakalin zama a wajen gidan .

Ga wasu ginan na zamani wasu kuma shige daya da namu nan baba yace dani Humaira yau gaki a gidan ku na gado nan da kike gani kaf unguwar nan kusan duk abu daya muke sai yan tsirarune surke a cikin mu nan.

Ido na ware ina kallon ikon Allah wai yau mu dake cikin bunu mune a wanan gidan haka mai kyau duk dasu yan wajen sunawa gidan kallon ginan kauyaci don samfarin dane ginan bana zamani ba .

Da kyar na sauko saman akori kuran na diro kasa ina faman raba ido cikin unguwar ina bin ko ina da kallon kwam saida naji muryan baba yana fadin bissimillan ku mushiga gidan mana yasa naja kafana da sukai min nauyi na hango wata mota a guje ta shawo kwanan da gudu na manne da gina don kada tazo ta kadeni a wajen nawa ya sameni kafin nabi motan da kallo don gaskiya mukan mota a can akori kurane muka sani sai yan futu futun da can ba,a rasa ba da sukan shigo lokaci lokaci garin muyi ta ihum ehh mota mota mota.

Baba yaja hannuna zuwa cikin gidan ina jin yayi sallama nima nayi azatona zamu samu wasu mutanene a cikin gidan amma sai naga sabanin hakan babu kowa saidai akwai alamun wasu sun zauna ciki sun tashi don gidan ba sabo bane gaskiya.

Tambarman dake hannun baba dashine ya fara shigowa dashi a hannu ya ahimfida don inna yana fadin suzo su zauna ke kuma humaira muje waje mu duba abinda zaki iya daukowa ki shigo dashi koda muka fita yaran unguwama suka taya baba shigo da kayan sunawa inna sannu da zuwa a cikin ladabi sai hakan ya bani sha,awa .

Can kuma saiga matansu sun shigo su suka share gidan suka wanko dakunan kafin aka saka kayan mu ranan mun kwana cikin wutan NEPA ga fankan sama yana kadawa sai da muka dunkule saboda rashin sabo da hakan.

Washegari tunda safe muryan Dada tsohuwar gidan ya tayar damu din daga barci ta shigo yi muna sannu da zuwa suna magana da baba da inna da can jefi kake jin muryanta haka na fito na dauki buta na zaga bandakin dake can kuryan gidan na fito na duka ina alwala suna zance hankalinta yana kaina yadda nake alwalan naji tace.

Zaman kauye bai hana kaba yayan ka tarbiyan data dace ba Abdullahi hakan nada kyau yaro ya bude ido da ibada ko ina yaro ya shiga za,a sameshi da natsuwa.

Ban dai tsaya ba daki na shiga na tayar da sallah na fito bayan na fito nazo don in gaidasu da kwana a nan na samesu ita na fara gayarwa kana na dawo kan iyayyena.

Naji ta kara fadin ehh lalai wanan takwaran namu gaskiya anayi da ita idan haka ya daure mata kada ki biyewa yaran nan da basu san darajan babba ba sai shagantaka a gaban mutane da shakiyanci.

Bata bar gidan mu ba saida tajawa inna kunne kan zama da mutanen shiya har mu bata barmu ba ta danyi muna nasiha kafin su fice gidan tare da baba daya dafa mata baya.

Lokacin inna ta kalleni nima take fadin yar manya kin daiji kin daiji irin nasihan da nake maki kullun ko a can kusan shine tsohuwar nan ta maimaita maki a yanzu.

Don Allah kece babba a cikin ku ki kama kanki ki rike yan uwan ki a wanan bakon wajen duk da gidankune amma mu bakine a cikinsu don bamu san akidunsu ba nan.

Ki girmama kowa ki kama darajanki duk da kina yarinya akwai bata garin da basu san yaro ba basu yaro ba basu san babba kedai ki tsaya matsayinki a inda muka ajeki banda wuce gona da iri kije hangen nesa .

To inna nace duk da ban gama fahintar inda zancensu ya dosa ba sai ga baba ya shigo da ledoji a hannunshi yana fadin humaira dauko kwano ki juye kosan nan ga kayan shayi kuma ki hada koki kawo gaban innan ku ta hada a raraba a karya kafin anjima in fita in hado muna abin girki a gidan.

Yadda baba yace din hakan nayi na hada ruwan zafi a tsohon murhun inna da mukazo dashi wuta ya kama don inna ta koya min aiki tun ina da shekara bakwai na fara aikin gida tare da inna din.

Har zuwa yanzu din da nikanyi ni daya saboda nauyin da inna tayi na cikin jikinta da yake yawan bata matsala ko wani lokaci cikin rashin lafiya inna take.

Mun karya a cikin sallama da daukin yau bamu ci sauran tuwo da muka saba kari dashi saiga shayi mun fara karyawa dashi har muna fadan burodi baba ya karawa sadiya nasa don ya kashe maganan tunda tace karami muka bata.

Ruwa yai zafi na tashi na dora sukayi wanka na shafa masu mai nakaiwa baba ruwa yayi wanka naga ya dauko tufafi masu kyau ya saka sabanin can da yakanyi shigan yan kauye riga daban wando daban haka kuma zaiyi kwanaki dasu a jikinsa sai gashi nan naga ya saka kaya wankaku iri daya kuma yayi wankan safe.

Kinsan yaran kauye akwaimu da wayau da saurin fahinta indai nazarine ga iya maida fadi a bakin yan kauye saidai kaf din mu halin innan mu ne damu don bamu

da yawan surutu gaskiya don haka inna take shiru shiru da ita muma ita din muka dauko da rashin magana sosai.

Ganin inna bata zauna ba yasa nima na mike tare mukayi gyaran gida da inna mun kafa ransdunan mu na kasa mun gyara kitchen din kwanon na kwashe tokan da wa yanda suka tashi a gidan suka barshi da sauran kayayakinsu da basu so muma mun dan tsunta a ciki sauran nakai wajen shara na tara don bansan yadda zanyi dashi ba sai baba ya dawo ya fada .

Saiga gidan ya koma tas har yafi wanda makwabta sukai muna kyau na kafa labule ako wani dakin na gyara dan gada gadan inna na dora masu dan tsohon katifansu sama na shifida zanin gado mai dawisu da inna bata faye amfani dashi ba sai lokaci lokaci shina shifida mata saiga baba ya dawo da cefanai su mai magi gishi nama dan tumatur da tattasai inna tana gyara na fito na amsa na tayar da uwata nayi jajagen kayan miyan yadda muka sabayi a kauye .

Ban tsaya bakunta ba don a cikin gidan mune nan mu kadai saidai abin kurciya dole daga inda inna take zaune tanayi ta gyara min har na dafa muna shinkafa da miya muka zauna mukaci muna jin dadi har kasan rayuwan mu don bamu ganin tumatur sai ranan da baba ya shigo birni don hakane a kauye ko yaushe cikin cin tuwo muke ko shinkafa da mai idan anyi abin dadi a gidan mucishi man shanu dai ne baka raba baba dashi a gidan mu don hurda da fulani da baba ke yawanyi a daji wajen aikinsa idan yaje yake dawowa da nama da man shanu mai yawa ayi amfani dashi.

Amma baikai ko ina duk matan babban gida zasu kwasheshi wajen roko har sai sunga karshen kwano sanan zasu huta zuwa tambaya yanzu ko da bamu nan nasan saidai idan mutum ya saya din zaiciwa bakinsa

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[1/7, 21:41] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON BIRI

ZAINAB IDRIS MAKAWA

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DARI BIYAR KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DON MIN AMANACE HAKKI, , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

2

Zauren gidan namu sabo shine daga farko sai idan kashigo daga ciki kuma zaka fara cin karo da rijiya sai dakin farko wanda babane a cikinsa.

Sai tsakiya dake zaman inna na karshe kuma mune da kannena a cikinsa da shimfidan mu na tsohuwar katifan inna da take yar muna dashi kasa muke kwamciya tun a kauye.

Tsakar gidan da simiti tako ina sai kitchen daga gefen dakin namu sai kuma wani dan daki baikai sauran dakunan girma ba shi kuma sauran tarkacen mune a cikinsa da yan akuyoyina da aka saka a cikinsa.

Ban gajiya da kallon Gidan don abin yana burgeni ko yaushe ina waje ina bin ko ina da kallo sai ina ganin kamar munzo bakuntane zamu koma.

Inama ace su mama tambai zasuzo suga gidan nan namu da bakin ciki saiya kashesu don nasan zasu koma kauye da labarin bakina fadi tsuliya na fada na abinda suka gani a katsina din.

Saida muka kwana biyu ranan muka shirya da safe muka shiga gaida Dada daga nan ta turamu da wata jikanta taikai iyalan Audullahi gidan yan uwa su san mu mu sansu.

Matashiyar itace take fada muna alakan mu da inda muke shiga din wanda maganan babane duk yan uwane saboda yanayin inna muka dawo gida badon mun gama zaga dangin Ruma ba a lokacin.

Gashi yadda baban mu keda kalangu a gefen fuskanshi duka biyu haka suma nake ganin hakan a fuskansu har dayara a wani gidan muka dawo gida ina wanan tunanen ni kadai a raina.

Wanan abin kamar a mafalki saiga baba yana muna zancen makaranta nayi murna nayi murna sosai islamiya aka fara kai mu a nan kasan unguwa har uniform aka dinka muna.

Muka saje da sauran yan uwa wanda duk yawanci diyan dangine a wajen a gaskiya duk wanda iyayyensa ke da ilimi ko uwa ko uba ya godewa Allah don za a bashi tarbiyan da ba zai wahala ba a duniya sai idan shiya jefa kansa cikin wahalan.

Don hakane garemu don ko na sheda hakanne saboda ban wahala basakamakon tarbiyan da baba ya doramu a kai tun a kauye, sai sajewa dasu nan bai zamo min wahala ba ina dai kokarin kafa kafa da yan kannena a lokacin duk inda nake idona nakai gashi suna kiran mu da sunan yan bararo.

Saboda hasken mu da zubin mu daya huda jinin mu na uwa da muke kama da bararo din wajen kama ga tsabta koda yaushe kafan mu da kumshi na lalle har hannuwa inna ke kumshe muna don ta saba da hakan tunna kauye itama hakanne ko yaushe a cikin kumshi take gata fara sai abin yake muna kyau daga mu har ita din indan anyi.

Baba yai shawara da yan uwanshi kan bokon mu suka bashi shawara ya jefani secondary kawai zaifi don ya mace make girman diya mace baida wahala a yanzu.

Aka kaini makarantar yan mata na jeka ka dawo inda yawancin yan gidan namu suke karatu an min uniform da safa da jakkan tare da littafai guda goma sha biyu nayi murna ranan barcima banyisa sosai ba don daukim in gani school din.

Washegari aka kaini aji daya aka ajeni a kauye kuma ina aji hudu ne na daina don ba daukan karatun da wani ma,ana mukayi ba a can talla ko aikin gida yafi karatu muhinmanci a wajen iyayyen mu mata damu.

Allah ya gani ina da ra,ayin yin boko a rayuwana saidai daukan da akewa wanda ke boko a kauyen mu yasa nima na bar zuwa bokon don da waka nake zuwa dashi nake dawow ga yara kamar mahaukaciya wanan yasa na tattara na daina bokon ina zaman gida tare da inna.

Ashe ina da rabo sai gashi nice ranan zaune a aji cikin yan bokon da nake mafalkin ganina a cikinsu yau gani garesu muna cudanya atare dasu a cikin aji.

Nayi kamar sati da farawa suma Aiaha aka kaisu boko suka fara zuwa tare muke tafiya dasu dawowane baba yake zuwa ya daukosu donsuyi kankanta da bin hanya.

Yawan shiga gidan Dada ina kai mata abinci yasa shakuwa ya shiga tsakanina da ita don muddin na shiga zan tsaya indan mata aiki diban ruwa shara da dan wanke

wanken kayan ta daba wani yaw bane dasu kayanta kuma in dauko in kawowa inna ta wanke mata in an gam na wanke in kai matasu a nade kamar an goge.

Wanan yasa muka yi wani sabo da tsohuwan na sosai har yakai ta roki baba in dawo da zama a wajenta amma baba yasawa idonshi tankwa ya hana hakan .

Ya fake da cewa itace idon gidan Dada uwar tayi nauyi a yanzu ita ke taimaka mata da wasu aiyukan Dada tace gaskiyane kuma fa da can da nan ai kamar dayane tunda tana shigowa kullum .

A haka maganan ya shashance amma inna cewa tayi aida baba ya badani din ba komai ta dingayi da kanta gasu Aisha sai suna kama mata ai.

Baba yace ke dai bari fake min baya jiran biri abu ga hannun maishi shine abinsa zamani yanzu ya lalace gidan Dada gidan kowane ni ko shigan nan ba kasafai nake sonshi ba kinsan zainab ba wai ta gama wayewa bane haka.

Yarinyace har yanzu tunda ko goma bata idda rufewa ba barta a nan inda muke ganin abin mu yafi muna alheri a wanan zamanin inna tace hakane kumafa.

A haka har ubangiji ya sauke inna lafiya ta haifi danta kyakyawa mai zubin mahaifinmu sak nan yan barka suke ta shigowa gidan mu don Dada ta aikawa kowa a unguwa sun samu labarin haihuwan.

Dada mutumiyar arzikine sosai zakice itace ta haifi baban mu da cikinta yadda take manu nan ko kishiyar uwace matar mahaifinsane shima baba ya rileta tankar uwa a gareshi.

Nan a gidan mu tayi waya da wani danta da take kira da Alh ta sheda mashi zancen haihuwan ya saka albarka bayan haka da kwana biyu saiga baba ya shigo yana fadawa inna yayansa dake kaduna zaune ya tura masa da dubu hamsin yayi hidimar suna har ragon sunna.

Ranan muyi murna sosai haihuwan nan na mama ya jawo muna arziki a gidan mu zance don ta dalilin haihuwan baba ya gyarawa mama dakinta aka sayo mata saitin gado da mirror har da wardrobe a gidan dillaliya aka kafa haka yasa koda yan kauyen mu sukazo sun sha mamaki sosai a gidan.

Ganin waje lafiyeyayye mai kyau da daukan ido mama tambai sai kallon ikon Allah takeyi zancen baba Ado yana dawowa a zuciyar ta da yace kaiya ai kin masu silan takewa ke nan a rayuwansu don wani hassada takine ga mai rabo gashi ko ta gani.

Don yau innace zaune a gidan simiti da bugon kwano sun zama yan birni janta ya kara fitowa hakama yaranta sai wanan abin ya kashe mata jiki dama gulma ya kawosu katsina suka fake da sunan zuwa suna don suga kwam.

Ko haihuwan farko macen kauye tayi bata taba samun wanan abin arzikin da gatan da inna ta samu haka a kauye da wanan bakin cikin suka koma gida kowa na fadin albarkacin bakinsa a wajen.

Aikuwa wayen garin dawowansu labari har yabi gari sun kwaso karya da gaskiya suna bada labari a gari kowa da abinda yake fadi a bakinsa don sun kwaso saida suka cika akori kuran fam zuwa suna sunzo da sunan kwana baba ya hada baki da driver yace ba zai kwana ba jin hakan dole suka mike ba shiri suka bishi suka isa a cikin dare sosai garin.

Anyi suna lafiya an watse lafiya aka barmu mu kadai a gidan namu sai yayun inna su biyu don ba tafiyansu daya da tawagan kauyen mu ba zasu tsaya su dan kwana biyuwa inna a nan su kara ganin inda muke.

Don haka koda aka watse bansha wahala ba don aikin komai su sukayisa karshema gidan Dada naje sai yamma lis na dawo gidan na dan kama masu shara dana sama dayansu tanayi.

Akwai school don haka washe gari na shirya nida yan kannena muka nufi school bamu dawo ba sai biyu da yab mintuna na shigo gida tun daga nisa na hango mota a kofan gidan mu haka na shiga gida ina kallon motan dake sheki a cikin rana.

Tun daga soro nake jin wani kamshin turare har nayi sallama na shiga gidan a dan innuwan gidan na samu su baba da bakonshi saman sabon tabarman inna an shimfida masu suna zaune a kai.

Har kasa na gurfana na gaidasu sai naji mutumin na fadin kai yar tawa ke nan ashe ta girmane haka gaskiya Abdullahi kasa ka cutawa rayuwan yaran nan a kauye.

Wa yan nan kyawawan yaran masu kyau zaka aje a kauye ka cuci rayuwansu gaskiya da haka ya faru ba zamu yafewa kan mu ba ga hakan Allah ya taimakemu dai mun samu kun dawo garin nan gaba daya.

Ni dai na mike na nufi ciki na gaidasu inna nan na nufi dakina na kwabe uniform ganin bako a gidan yasa ban fito yadda na sababa don na wanke muna uniform din mu.

Muryan wanan bakon dan uwan baba naji tare da babana yana kwala min kira da zainab baba kuma yana fadin zainabu ke zainabu daga dakin na amsa da na,am baba da sauri na mike na nufo waje naji baba na fadin kizo baban ku zai tafi yana neman ki.

Kamar farko yadda na gaishesu ko wanan karon haka na zube a kasa gabansu ina fadin gani baba bakon yace yata zan tafi nace kizo muyi sallama ina sauran yan uwan nakine ?

Ya tambaya nace suna cin abinci nan ya fara magana yana fadin na fadawa babanki ki maida hankali ga karatu tunda ance kina da kokari don wata rana mukai ga babban likita mace ko wata babban office a cikin zurian anmu amma fa kinsan hakan bai samuwa saikin dage da karatu kada a yi wasa maison wanan matakin baya wasa da cikar burinsa sai ya dage.

Kaina fara dagawa kafin na bude baki da kyar nace to baba yana sa hannu a aljihunsa yace ina son muyi alfahari daku cikon yayan da zasu daga muna sunan wanan gidannamu ko bayan ranmune kamar yadda muma a yanzu muke alfahari da bazar namu mahaifin daya rasu.

Insha Allahu baba yace daga gefen shi yace ungo karbi wanan ki sayi duk wani abinda baki dashi a gidan nan na karatun ki ga babanku nan na fada masa duk wani abinda za ace za a bukata gun karatun ki ya sanar dani tunda nan kaduna nake zaune.

Kudi ya ban masu yawa saina kada kai alaman ya barshi akul naji yace dani ni babankine idan baki sani ba uban mu daya dashi tare kuma mukai karatu dashi zaria shiyasa kikaga munfi shakuwa dashi a cikin dangi kaf ni ashi haka muke kamar aminai ba zakice mu din wa da kani bane idan muna tare.

Jin hakan ga kuma baba a gefe yana wani irin murmushi yasa na mika hannu na karbi kudin daga hannun dan uwan baba din tare da fadin nagode baba cikin yar murya yace babu komai aike din diyatace halak malak ba godiya a tsakanin mu.

Jeki baba yace har lokacin fuskanshi yana dauke da murmushi na mike da sauri nabar wajen na shige gun inna dake daki da bakinta ganin sunanan dakin yasa na dunkule hannuna ban nuna mata kudin ba a lokacin.

Bayan kujeran inna na labe banda sakin jiki idan muna da bakon fuska a gidan mu har nakan kagara bako ya wuce ya barmu mu kadai wani lokacin don nakan ji na takura dayawa.

Inna taje sunyi sallama ta dawo dauke da dan jajiririnta a hannu wanda kayan jikinsa bani gajiya da kallonsu saboda kyau yadda aka saka kayan sabanin sakan mu na kauye dana saba gani ana sakawa yara acan.

Kwanan bakin biyu suka juya suka koma ba wasu dangin can bane ga inna kawai dai don sun fito nahiya dayane suke zumuntawa junansu a nan abin gwanin ban sha,awa idan ka gansu tare.

Gidan Dada na koma da zama da suke nan sai yamma nakan dawo nan gida in zauna don ban yarda kafe shidda yayi ina waje hakan yasa muka dayi sabo da yan matan dake yawan shigowa gidan Dada din hira da samun abin tabawa don baka raba gidanta da dan abinda diyanta suke aiko mata.

Wanan yasa yanzu da bakowa a gidan mu kona dawo daga school ina gida zaune ina dan aiyukan gida sai suka fara dan shigowa gidan namu wurina muna hira a nan ina aiyukana kuma.

Zasu girme min sa,adatuce sai Nabila amma haka muke kawancen namu dasu har yakai ko islamiya ko boko tare dasu muke jerawa mu tafi a wajen su nake jin komai daya shafi family wanda ni ban ma gama sanin yan uwa ba sai yanzune nake sanin wasu.

Nan nake jin ashe yawa garemu akwai wa yanda basu zaune a garin amma sukanzo gida jefi jefi tare da iyalansu lokacin sallah ko wani buki haka idan ya taso a family.

Zaman mu a nan cikinsu yanzu bazance zaman dadi bane yadda nake fadin su a,a zama daine yanzu wanda yafi muna na baya cikin yanci da sallama babu tsana babu tsangwaman kowa akan mu.

Zama na kasanni na sanka zama na cin gashin kan kai abinda kowa ya samu bakinsa saidai babu saka ido irin na kauye na lungun su wance kaza akeci ko kaza aka dafa yau.

Ko saka ido akan mu,amulan miji da mata don zaman babban gida irin wanda muka baro a baya zamane na kai mutum wuta idan bawa baiyi taka tsatsan da duniya ba a wanan zaman .

Gashi zamane na shagala kamar ba gobe sam ba mai kawo mutuwa a rayuwansa yace wai a,a bari nabar kaza a kwai mutuwa ko wani lokaci zata iya riskana saidai shagala da duniya ana dukar daji da kafafu.

Ban daki wurin wanka da bahaya daya ko biyu ansan tashin wace ansan sunyi sunna da mijinta mai kishiya akwai yan tayata gani suna saka mata ido a kishiyanta su zasu fada mata sunga tayi wankan tsarki ko sunga mijin yayi wankan asuba.

Duk damu da baba ya dan kebewa inna wuri bata tsira da hakan ba don sai kiga mace ta fado mata wai a san mata waje ta kewaya don gulma har yara suke turawa yin wanan laccan ga junansu.

Saidai ni dana dan tasa a cikinsu Allah ya kareni ga hakan don iyayyena basu yarda insha cikinsu ballema a koya min wanan akidan na babban gida babban bala,i.

Don da zaran aka fahinci mijinki yayi wankan tsarki baiyi a dakin kishiyarki ba aiki ya samu a gidan yanzu zancen boka da malam zai tashi aje kuma a zageki tsakar gida sai kin tsargi kanki da kanki kan hakan.

Idan kuma ke kadaine gun mijinki tofa nan ma ba,a barki ba za a sakaki gaba dasherin cewa kullun kina mane a kafadan namiji kin hanasa ya karo maki kishiya kin mallakesa kin hana wata tashigo itama taci arziki.

Wanan jahar su inna ke nan su akewa irin shaguben nan don duk ranan da aka ganta da sabon kaya zakiji an fara dama hakan take so taci ita kadai daga ita sai yayanta bata son wata tazo aci tare.

Saida baba ya tsaya tsakar gida ranan yai fada kan kewayawan da suke zuwa yi sashen mu sanan muka samu sauki saidai baiwai sun bar zuwan bane sukan faki idonshi s shigo su kewaya din don gulma.

Kai gaskiya zaman babban gida a kauye ba karamin fitina bana yasa ko baki da baki idan kin shigo dole bakin zai bude sai kiga yar karamar yarinya tana ciwa tsohuwa mutunci a tsakar gida gaban yayanta da kowa.

Nikan nayi barka naji dadi da Allah ya kadarta iyayyena suka taso dani don da karshensa a gidan aure zai kamani ace anyi auren hadi tsakanina da wani can a dangi.

ZAINB IDRIS MAKAWA

[1/16, 12:13] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON BIRI

ZAINAB IDRIS MAKAWA

3

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DON MIN AMANACE HAKKI, , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Yau weekend ne muna gida bamu fita school misalin shadayan rana ina kwance daki naji shigowan baki gidan hakan baisa na fito ba don naji muryan mazane ba mata ba.

Can naji muryan baba yana kwala min kira cikin daga murya na fito da sauri ina fadin baba gani yana zaune sun zagayeshi saman tabarman da suke zaune akai.

Yace kinci gidan ku bakiga yayyunki bane baki bakizo kin gashesu ba na dago kai na kallesu sau daya saboda kwarjinsu ina fadin sannun ku da zuwa ina wunin ku suka dago suna fadin lafiya lokaci guda.

Jeki ki kawo masu ruwa ya fada cikin bani umurni na mike ina tafiya cikin yanayina na yanga da tun ina fociciyata hakan nake tafiya wanda yanayin jikina yasa hakan sai wanda bai sani ba ya dauka yanga nakeyi.

A fakaice wasun su suka bini da kallo ruwan leda na dauko na dire a gaban su kafin na mike da zumar barin wajen muryan babane ke fadin dakata kinji kinga wanan.

Ina jin hakan na juyo na mayar da hankalina gun baba din dake magana dani naga ya nuna min na farko dake gefenshi yana fadin wanan dan babankine dake Kano zaune yanzune na wancan gidan na kusa da Dada din nan.

Wanan kuma dan kanwar muce Jummai matar babanku Ahmed dake Abuja wanan kanninsa ne data haifa a gidan babanki Ahmed din.

Baba na fadin hakan sai naga na farkon ya danyi kasa da kai ya lumshe ido a hankali kamar zancen bai masa dadi ba yadda baba ya fadi zancensa a gabana amma shima din mahaifinsa dan uwan mune saidai Allah ya karbi ransane tunda cikinshi.

Saida yayi min bayanin su kaf dinsu kafin ya barni in tafi suna ta hiransu dashi wanda yawan hiran tambayane yafi yawa da baba ke masu.

A lokacin na sulale daga gidan na faki idon su nafice zuwa gidan Dada don ganinsu a gidan mu yasa banda sukuni a lokacin duk na tsawala da ganin mutane a gidan namu kuma bakin fuska maza haka.

Na samu Dada ita kadaice agidan hakan yasa na dan saki jiki na debe hijjab fura ta miko min a wani kwanon shan silver mai marfi na girgiza kai ina fadin a koshe nake Dada nagode.

Tace ja,ira dama nasan ba zakici ba ai wanan mara yarda a bakuwa kike shigowa mutane ke a kullun kinki sakin jiki har yanzu da kowa kaf a dangi na dan turo baki ina fadin haba dai Dada akwai wanda nake sakin jiki dashi bayan ke kafin ta ban amsa na mike shara nayi mata na gyara dankin har tsakar gida kafin na dawo na zauna a kusa da ita muna hiran harira jikanta dake zama da ita datayi tafiya zuwa kaduna.

Anan mukaji sallaman su sunshigo gidan Dada din gaba dayansu yadda na barsu zaune a gidan mu din haka suka jero su hudu suka shigo gidan.

Farinciki naga a fuskan Dada din kafin ta fara tafawa tana fadin lale marhabin da bakin turai kune a tafe haka da rana tsaka ashe da rabon zamu gana daku kuma.

Koda yamma muka iso badai kin ganmu ba ina ruwanki da time din shigowan mu sai naga ta kwashe da dariya bakinta da goro ya bata mata hakora ya baiyana a fili.

Cikin dariyan take fadin ja,iri har yanzu dai kana nan a yadda kake ashe kai kam turai din baisa ka canza halin naka ba dama ance kada ka kara a yadda kasan halin mutum a baya.

Zama yayi a gabanta ya dora hannayesa bisa cinyarta yana dan murza gwiwanta din daya dora hannunsa a akai ta tureshi tana fadin ja,iri kaga kada ka karasa tsohuwar mutane don Allah.

Ka zama wani jibgege da kai kamar wani zaki nikan ma wanan karatun yayo a can ko zamancin abinci tana fada tana kallon yan uwansa da alaman tambaya a garesu.

Dariya ya kwashe dashi yana fadin nifa Dada nazaci kin mutu tuni don ko dan tsaraban goro ban riko da sunanki bani don na dauka ko kin bi mijin naki ashe kina nan gyagyau din ki baki tsufa ba.

Wani harara ta galla masa tana fadin da yake ni ba uwarka bace ai dole ka fadi hakan dadin abin dai akwai wanda suke son su ganni a cikinku koba haka ba ta kalli na gefenshi din sai ya murmusa yana dukar da kai.

Dariya ya fashe dashi yana fadin tsiyata da tsohuwar nan bata son mutuwa ko kusa yanzu da jin zancen mutuwa duk kinbi kin rude kina batun sakawa mutane kuka.

Allah sarki kaine dai baka sonta nikan ai yanzu a kullum zaman jiran nakeyi da fatan cikawa da imani a zuciyata .

A,afa Dada kada ki ganta a yanzu ki dinga kwala muna ihu kina fadin azo a taimakeki nan sauran suka kwashe da dariya Dada dai ta mike tana fadin ja,iri halin dai yana nan ashe bari na kawo maku farau farau ku jika makoshi kafin mu gaisa .

A,a Dada kibar wanan farau faraun naki kada kisa cikin mu tsatsa ni dai kan bazan sha wanan abin naki ba don haka dawo ki zauna muyi fira kawai na yaushe rabo.

Tsayawa iyan tayi tana kama baki kafin tace Ja,iri bakai kadai bane ai idan bakasha ba wani zaisha ai a cikinku ya kallo yan uwan nasa yana fadin to ku kunji da mai son shan tsatsan kwanonta a yanzu cikin ku?

Wanan kan kam anyi ja,irin yaro a nan ga yayyunka basuyi magana ba sai kaine da bakin iyawarka kake zuba haka ya dan dago ya kamo hannunta yana fadin Dada nifa naga kin koma min wata yar caras hakan nan ko kin fara zance da zawarawa suka kawo maki namane kika koma hakan wai.

Haba ta kama tana sallati kafin tace kaji min dan kawai ko to ubanka Amadi daya dawo garin nan ina kun sani dan albarka shine kullun ake dafo min nama a gidansa ana kawo min na tausa don gidan ku kaje kaima kaci a can din.

Ni kan ka isheni ka hana mu gaisa da yan uwanka muyi yaushe rabo dasu ta koma ta zauna dayan ya kalleta yace Dada ina farau farau din kinsa mun saka rai kin kuma zauna.

To na iya ja,irin nan ya fara fadan kwano da tsatsa zan halakaku da shi haka ta kallo inda nake tana fadin kinga Abule tashi hado masu ruwa a tulun nan mai sanyi da wanan sauran furan sai na dan kallosu a sace na kuma mike zuwa yin abinda ta sakani yi din..

Nakawo nake jin tana fadin yanzu kan tunda kun karasa karatu ai sai zancen aure ga yan mata a cikin dangi ko wanen ku a bashi anma gama magana akai yanzu gabatarwa ya rage a gareku.

A take fuskokinsu ya sauya kafin shi fitsararen nasu ya kalli tsohuwar yace ku baku da wani zance sai na aure karatun dama ko kammalashi ba ayi ba zaki daukowa mutane zancen aure daga mun shigo duban ki ki kawowa mutane zancen wani aure a yanzu kuma.

Yana fadin haka ya mike tsaye ya kallo yan uwa yana fadin ku sameni waje don Allah tama bata min da wanan zancen Dada ta waro ido waje ta dafe kirjinta tana fadin shu,umi ba dai ka manta alkawarin malam akan ku bane tun yanzu.

Dona ambaci auren zaka dauki zafi dani da ba,a aure za,a haifekane dan kawai koba aure ya haifeka ba kai .

Ya kallo tsuhuwar yace ko zaki maidani ciki tunda kinyi bakin ciki a yanzu nazo duniya ta hanyar aure to ba zanyi ba ku rike duk yar da zaku ban na yafe akaiwa wani.

Nifa bari kiji Dada ba wanda zaimun wanan auren hadin naku na gado tunda ba Allah da Annabi sukace kuyiwa yayan ku hakan ba balle kizo min da wanan zancen daga saukana gari ko ruwa bansha ba na huta.

Yana fadin haka ya fice ta fara salati tana tafa hannaye kafin ta fara kuka irin na tsofi tana fadin kaji min dan kawai har yanzu ashe iskancin nasa yana nan yadda ya barmu girma baisa ya bar wanan halin nasa ba.

Sauran hudun suka kwashe da dariya suna fadin barshi Dada yayi maki hakan ne don kiji tsoro amma ai ba hakan halinsa yake ba inma haka yake ai zai hadu da uban nan kune ida yace shi dan banane.

Ina makure ina kallonsu kafin su mike da kamshinsu nabisu da kallo har suka fice daga gidan bayan sun ajewa Dada din alheri sukai gaba sai gashi tsohuwar ta koma fadin yan albarka sun gado mahaifansu wajen alheri.

Yaki zoki kirga min kudin nan na boye kafin yaran banzan nan su dawo su wawashe min tare muka kirga kudin dubu goma sha biyar tana faman saka masu albarka.

Ta cire dubu daya ta miko min tana fadin ki karbi wanan kyasai foda sha wanan kuma daure min shi dakyau na tura a lalita kafin su dawo su gane ina da kudi a dakin nan.

Kaina girgiza kafin nace a,a Dada ki barshi nayafe rankwashi ta kai min a kai tana fadin ko uwarkice ta hanaki karban da sauri nace a,a Dada kawai ki barshi ta dangwara min kudin a jiki ta mike tana cire zip din lalitan bujenta irin na tsofi na mika mata kudin dana daure din ta tura a cikin aljihun nata.

Mikewa nayi ina fadin Dada barin koma gida kada baba ya nemini ban fada mashi zan shigo nan ba na fito na barta tana fada dani akan me zance za a nemeni bayan ansan banda wajen zuwa kaf unguwa sai wajenta.

A kofan gida na samu baba zaune da kanwata sadiya da dan ledan awara daya saya mata nake gaidashi yace dani daga wajen Dada ko nace eh baba naga gidan da bakine naje can.

Murmushi baba ya sauke a fuskanshi yana fadin banda abinki zainab ai duk yayyunkine wa yan nan kusan abu daya kuke dasu rashin sanine kawai don baki saba dasu ba tun farko.

Murmushi na sauke a fuskana ba tare da magana ba na shige gida inna tana zaune saman kujera yar tsuguno ta mata na shigo da sallamana ina gaida ita.

Gunsu na nufa ina lakatan fuskan yaro nace maizuka inna wai wanan yaron naki baya gajiya da shan nono ko yaushe nono a bakinsa .

Ta dago cikin haraea tana fadin ke bakya gajiya da cin abinci wayayi maki wani zance balleshi wanan meya samu har ya zuka bayan kun kwashe komai tundai ke na saka yar dariya ina cire hijjab din dake wuyana direct gun wanke wanke na nufa.

Ina wanke wanken muna hira da inna jefi jefi akan islamiyan mu nake bata labari har yakai nagama na kife na dauki tsintsiya na share gidan tas kafin na dauki bucket na dibi ruwa a randa na nufi bandaki don in watsa ruwa ko ya ruwa yake da sanyi kuwa don mun saba tun a kauye.

Bayan mun shirya har kannena muka fito don zuwa islamiya a daidai wanan kofan dake rufe ko yaushe na hango dandazon su ban daga ba ban kuma kallo inda suke ba haka muka shigesu zuwa islamiya.

Wa yancan yaran badon a kauye suka taso ba da yanzun sun fi kowa a family din nan shanawa don yaran gasu gwanin ban sha,awa dasu wallahi.

Kai uwarsu ce suka kwaso wa yan nan yaran akwai tsabta daga gefensu wasu ke fadin wai yarancan suna da girman kai basa gaida kowa fa yara kanana dasu amma sai girman kai.

Haba dai wa yan nan yaran me suka sani wani girman kai dayan da duk tsayinsu wajen kowa na fadan albarkacin bakinsa sai wanan ya furta daga hakan kuma bai kara tsunkawa ba ya juya shigewa yayi ya barsu a wajen.

Tunda na samu nabar wajen naci gaba da sauri ban tsaya ba na shige islamiya a kusan kullun mune farkon shiga islamiya har ma yanzun da abokan tafiyana sukai tafiya.

Har muka tashi islamiya gabana sai faduwa yake ba komai yaja min hakan ba sai ganin wa yan nan matasan da baba ya kira da yan uwana duk da naji su din yan uwanane amma hakan bai hanani tsoron suba.

Kodon shigar tufafinsu da yanayinsu da ban saba ganin shigar haka ba ga mutane don ko a nan katsina akasari irin shigan mutanen hausaw suke shiga wando da rigan jamfa amma wa yan nan gasu fara wasu chaculate color amma haka suke a tsuki dasu ba maiyiwa wani fada a cikinsu gashi ba zakace ga babba ga karaminsu ba komai a tare sukeyinsa.

A gaban mu motarsu tazo ta wuce mu sai muka samu mutum biyun su kofan gidan Dada sun faka motar dayan yakai bakin masalaci daga nisa kaina yana duke kasa yake fadin don Allah yan matan dada karbo min ruwa wajenta nayi alwala.

Sam ban dauka dani yake zance ba sai kokarin shigesu nakeyi kaina na dukr a kasa sai dayan dake gefen mota a tsayene yace ke yarinya dake ake magana koke kurmace bakya jine ,?

Jin hakan yasa na dago kaina ina fadin ayya banzata dani yake ba ai don Allah kuyi hakkuri baiko tsaya bin ta kaina ba hakan yasa na nufi wajen mai miko min butan na karba daga hannunsa tare da dan rusunawa na girmama a gareshi kansacewarshi na gaba dani.

Ya karba yana min turancin daba fahinta kwakwalwata zaiyi ba Dada tana zaune tana jiran ayi kiran sallah na shigo da sallamata ta amsa min tace kishiyata badai yanzun kuka dawo daga karatun Allah ba ?

Yanzune Dada sauri nake in karasama gida wanan bakin birni din sukace na debo masu ruwan sallah a nan tace shu,umai ni yanzu na kare zancensu a raina har ina zaton ko sun wucene ma don ban kara jin duriyansu ba tun dazun da suka fice.

Ni dai na debi ruwan nakai masu ruwan ya karba tare da furta kalman thanks ya juya nima na kama hanyan gida ina sauri kada a kira magariba ina waje kamar yadda iyayyena suka horemu dayi kullum.

Ina shiga gida daidai ladanin masalaci yana dauka loudspeaker zai kira sallah wanda wanan karan ke fara fadakar da nusulman unguwa lokacin sallah yayi.

Innace zaune da danta dake goye a bayanta tana jiran kiran sallah sallama na kara yi ina gaida inna din saidai bata amsa min ba bayan fadan data tareni dashi da fadin.

Meyasa bakya jini ina kika tsaya har aka kira magariba baki shigo gida ba sai kannenki da kika turo min suka shigo su kadai kallonta nayi a dan maraice nace ban tsaya ba inna tare muke dasu wa yan nan bakin da baba yace yayyun mune sukace in debo masu ruwan alwala a gidan Dada.

Ki dai kula ta fada taja buta ta fara alwala ganin hakan tunda na saba jin wanan kalman ba saudaya ba ba sau biyu ba a bakin inna din wanda bazance ga ma,anarsa ba a kaina yasa naje dakin mu na debe hijabin kaina na fito na dauki buta na zaga ban daki.

Bayan na idar da sallah na shafa addua ban zauna ba don nasan abinda zanyi basai an tuna min ba madafi nashiga na dauko kwanon silver da muke cin abinci na zubawa su sadiya.

Kafin na koma dakin inna na dauko shimfidan baba na shimfida har filo da yar redion shi da yake sauraren jakkar magori dashi da sauran shirin radio kaduna idan ya dawo daga sallah don bai kara fita idan ba wani kwakwaran dalili zai fitar dashi ba sai kuma Allah ya kai muna rai washegari yake fita kuma.

Bayan naga ana tayar da sallah na shiga nayi a nan na dan jima ban fito daga dakin ba har saida baba ya shigo naji yana tambayana na amsa ina fadin gani baba na fito ina gaidashi.

Yake tambaya kinci abinci kuwa nace yanzu zanci baba ina biya karatun mu na yaune kada ya shige min mallam yayi min duka gobe mai sunan iya banda abinki ai sai ki fara cin abincin kafin ki zauna karatu.

Na juya zan dauko abincin naji inna na fadin ai kasam halin ta da naku naku cin abinci sai ta saka mutane yin magana kafin ta zauna taci don sabo da wanan mugun halin a rayuwanta.

Zance nafi jin dadin baba bisaga innan mu don baba yafi inna lalaba mu ita inna koda yaushe a cikin tsawa take muna kamar yadda wasu uwaye mata kanyiwa yayansu wani lokaci.

Ballema ni da kusan don ina yar fari a wajenta take nuna kara a kaina ko banza koba kowa haka muke yar tsarguwa da inna din.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[1/17, 21:35] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FAKON,,,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

4

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZENETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DON MIN AMANACE AGAREK SHI HAKKI, BA ABIN WASA BANE , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

A zatona sun bar garin don washe garin lahadi ko kofa ban taka ba har islamiya banje ba don mun tsaya wanki da kitso da sai ranan lahadi mukeyi don inna ta camfa kamar yadda yake ga addini.

Bata wanki ko kitso ko tsifan kai ko yankar kumba ko sharama dole dai akeyinsa don jin da tayi malamai na fadin cewa ba a son mutum yayi komai daya shafi rayuwa a wanan ranan idan baya zama dole ba.

Wanda rashin sani da kuma akidan nasara yasa a yanzu mun take hakan muna aiwatar da abubuwan mu kai tsaye tunma daurin aure a yanzu harda wanda ba aikin gwaunati yakeyin ba sun mayar dashi wanan ranan ta asabar sabanin jumma da kakannin mu suka fiyi a da ayanzu a sabar din akeyinsa.

Sai yan tsirarune da suke da fatawan hakan akai suke zaban kyawawan rana da Annabin ya koyar damu suke abunuwa a yadda addini ya koyar damu yinsa din Allah yasa mu dace Amin.

Safiyan Monday mun fito zamu school daidai gaban gidan nasu na hangoshi a tsaye gaban wata jar mota kirar jeep da a lokacin bansan sunnanta ba ya jingina jiki da bayan motar yana tsaye.

Jikinshi yana saye da koriyar riga ta maza da akaiwa rubutu da manyan haruffa an rubuta VERSECE sai yar wandon maza fari mai aljihauya da yawa manya da ake kira cryzy ya dan wuce gwiwa har hakan ya baina santala santalan fararen kafafunshi waje da gashi ya dan rufe ga hannayensa saye da wasu zubba da biyu da suka karawa hannun nasa amarshi.

Ganin hakan da yake wanda kallo daya nayiwa yanayinsa na dukar da kaina kasa da sauri don kada na kwashi zunubi garin kallon kwam dinsa don nasan hakan ne zamana da yan matan gidan namu da nakanji kallo daya sun haddace abinda ke jikin mutum sin fada gashi nima a yanzu na iya hakan.

Magana suke da wani baban mu karami dashima muke kiransa da baba karami amma yanayinsa kamar yana sakar muna murmushine don mu din ya kurawa idanunsa muna tafe.

Sai naga ya juye min kamar mutanen kasan su inna da yan cikin tv da nake gani yanzu masu rawa da waka a wasanninsu din nan.

Ina kwananku nayi masu cikin dan rusinnawa da muka saba dashi tun a kauye idan zamu gaida mutum iya abinda na iya furtawa ke nan garesu sai naji muryan baba karami yana fadin yan buko har zaku tafi ke nan da safen nan ?

Ai gara suyi sammako zaifi masu abinda naji ya fada ke nan da hausa badon haka ba sai ince ko baijin hausane din zama a kasan turawan da ake fadin sunayi yanzu.

Kuzo ku karba kalman daya fito bakinsa ke nan sai naji kunya ya lulubeni gashi muna da tarbiyan cewa a,a ga mutum farat daya idan ya nufemu da alherin abinda yake ci idan mun riskeshi.

Toga wanan babu komai a hannusa ya kumace muzo mu karba yaya ke nan zanyi jin hakan yasa naja na tsaya ina kada kai alaman a,a sai baba karamine yace dani kuzo mana ana magana daku.

Tuni naji kunya ya lulubeni lokaci guda a wajen yayin dana dan sada kaina kasa cikin kunya na tako zuwa garesu din ina rike da hannun kanne na dake rike dani har zuwa wajensu din.

A daidai lokacin ya tura hannu cikin aljihun wandonshi ya fito da kudivyan dari biyar biyar guda uku ya miko min da sauri na sake girgiza kai ina fadin mungode suyi yawa baba ya bamu hamsin hamsin musai abinci muci.

Kai amma yar nan da wani zance kike ana batun dari biyar meya kawo zancen wani hamsin can kuma karbi don Allah kin tsaya kinawa mutane shirmen banza.

Shiko murmushi yayi yana fadin kinga kanwata karba ku kara ai harda na gobe na baku kinga baba ya huta baku gobe ke nan idan ran mu yakai koba haka ba ?

Jin hakan yasa na dan rusunna na mika hannu a cikin ladabi na karbi kudin a hannunsa tare da furta mungode na juya muka tafi har kafana yana hardewa waje daya.

Kwata kwata raina baiso karban wanan kudin ba gaskiya don inba Allah ya gyara ba nasan sai munsha fada a gida tundai ni har mukaje muka dawo suna cikin littafin dana sakasu a ciki.

Sam na manta da zancen su saida yamma da baba ya dawo gida sune zaune da inna suna hira naji yana zancen kudi abin ya fado min a rai daga inda nake tsaye nace lah .

Jin hakan yasa suka kallo inda nake duke ina wankin uniform din mu na school nace na manta in fada maki inna dazun da safe da zamu tafi school wanan yayan din da sukazo ya bamu kudi wai mu kashe a school shine na aje sai yanzu na tuna dasu na tsame hannu na wanke na nufi daki na dauko littafin dana adana kudin a cikinsa banko tsaya kidayawa ba don a zatona kwara ukune ya bamu kowa guda guda ashe ba haka bane.

Don ina bude littafin kudin suka watso kasa shar sabbi dasu mikaku sukai fale fale a kasa hakan yasa na fara sanin sunfi kwara uku ashe yadda nake zato.

Muryan innace ke fadin waya baku kudi haka masu yawa kika karbo ina jin hakan na dago da sauri na kallo inda inna din take zaune kafin naji baba yace dakata muji ai wanda ya bata.

Tunda har bata kashe ko kwabo a ciki ba aiba zamu fara mata fada ba sai munji ba,asi akai na hada kudin daya watse na dago ina fadin dazun ne da safe da zamu school mukaga wanan da kace su yayan mune faein nan dogo tsaye da baba karami suna magana.

Shine da muka gaidasu yace muzo mu karba muyi breakfast dashi nace ya barshi ka bamu hamsin hamsin sai baba karami ya kama min fada wai ai shima yayan mune don haka mu karba shine na aje na manta da muka dawo in nuna makine inna .

Amma aina hanaki karban abin mutane ko haba Rukkaiyatu kibi zancen nan a sannu itama ta sani ai na hanata hakan amma ai kinji tace babansu karami yasa ta karba don haka ai mata uzuri .

Da alaman inna bata gamsu da hakan da baba yace ba son yadda naga ranta ya baci har fuskanta ya nuna hakan a fili sai naji baba yace dani aje kudin kije abinki nagane ko waye mai sunan malam ne Aliyu ko tunda kince fari dogo shine ma dai fari sosai a cikinsu ai.

Bayan nabada baya baba ya rage sautin muryanshi yana cewa ina din ki dinga bin yarinyar nan a sannu tasan abinda takeyi ai tunda kikaga duk da abin kwalam a school din baisa ta kashe ko kwandala a cikin kudin nan ba gashi kuma a karshe ta kawo muna duk dai bamu sani ba ai tana amfani da zancen mu ke nan a kanta.

Malam tsoron zamanin nan nake ji a kauyema an yaudari yaro da kudi balle nan da yake birni abin ne sai ana tsawatawa haka ai nasani amma ki sani Rukkaiya insha Allahu Allah zai kare min zuriata dana musulmai daga masheranta.

Ban taba aikata zina a rayuwanta ba ko makamancin haka in Allah ya yarda Allah zai kare min zuriata da yardan sa insha Allahu amma fadan yana da kyau garesu sai dai a hada da nasiha.

Ai kinji hankali bai tashi ba don nasan yaron natsetsene baiyi hakan garesu da wani manufa ba sai da niyar alheri irin na yan uwantaka a tsakanin su dan uwatane donshi na kyale aida nine zan fara fadan karban da tayi din.

A haka rayuwa ke tafiya damu a sannu a hankali ayanzu nasan duk wani dan uwa na kusa dana nesa har matan babanin mu maza dake zaune wani gari izuwa yanzu dai nasansu gwargwado sai wanda baizo ba na gansane ban sani ba.

Gashi shakuwan mu da Dada yasa suma din sun sani sosai don yanzu mun shaku da ita fiye da dacan da mukazo rashin sabo yana sa ina mata make make narashin sabo a tsakanin mu.

Saidai cikin hikima da nuna so da kauna irin na tsofi har Dada ta saye min zuciyana dagani har iyayyena a yanzu banda wani zance sai nata a bakina itama kusan hakan.

Don duk cikin jikoki tafi yarda dani da kuma kamar sakani a rai bisa ga kowa wanda nasan shakuwan dake tsakanin mune ya kawo hakan.

Hakan yasa da tafiya kano ya kama Dada ta bukaci baba ya barni mu taka mata baya nida halimatu jikinta dake wajenta baba baiki ba don dama yana da burin hakan nakai ziyara ga dan uwansa dake masa korafin yana masu rowan mu bai bari muna shiga dangi a san mu.

Shiri sosai Dada takeyi na tafiyan mu din don a bakinta nake jin cewa buki za,ayi nan da sati biyu a gidan baban nanu dake can zaune kano din kusan duk dangi zasuzo wanan bukin don shine karo na farko da zai aurar da yarsa mace don maza basuyi aure ba saboda karatu.

Itama yar nasa da ake kira da anty baby naji Dada tace ta tsaya karatune yasa ba ai mata aure da wuri ba sai yanzu data kammala zatayi aure.

Mukan a bangaren mu ba wani shiri illa zaban yan tufafin mu mu goge sai kuma kitso da kumshi wanda inna da kanta ta zauna ta dandasa muna kitso har siifa a kafafun mu nida halimatu din.

Mota sukutum baba na kano ya aiko da za a dauki Dada din dashi don haka ba wani matso matso ko guna mu hudu ras aka dauka tare da baba karami da yabi gayyan Dada din zuwa kanon .

Gidane babba wanda mallakin baba na kano dinnne don dan kasuwane sosai shi a kware market din kusan kowa yasan sunnansa don yayi fice a kasuwanci kuma ya karbeshi sai hamdala.

Nasha wuya sosai a hanya don amai dana dingayi wanda warin mai da nashaka da sanyin AC motan suka hade lokaci guda suka haifar min da aman don da farko kaina ya fara juya min sai kuma sanyi saiga amai duk na bata jikina dashi.

Allah ya kare na riko dan leda a ciki na dunkule nayi tayi sannuko nashashi a wajen Dada yafi cikin kwado a lokacin don ta nuna damuwanta sosai ga hakan daya sameni.

Har take fadin data sani da bata zo dani ba ta daukoni lafiya hannun iyayyena gashi tun ba akai inda za ajeba yar mutane ta fada a wani hali a hannunta.

Hakan yasa muna isa bata tsaya takan taron da ake mata ba ta mayar da hankalinta akaina tana fadin ku kama yar mutane don Allah ta jigatar da yawa nan matar da suke kira da umma tazo tana fadin ya akayine meya sameta Dada ta fara fada masu wahalan danasha a motar.

Bata tsaya sanya ba ta wuce dani sashenta ruwan masu dumi ta hada min ta kaini bandaki don inyi wanka ta nuna min yadda zanyi ta fito nakoji dadin wankan don naji jikina ya dan sake gaskiya.

Ina fitowa na sameta zaune saman gadonta ga kayan tea a gefenta yana tururi a cikin kofi muryan ta a cikin sanyi take fadin ki sauya kayan jikin ki kafin ki sha ruwan shayi ga kayan ki nan na karbo maki a wajen Dada.

Karban kayan datake miko min nayi nawane amma kuma sabbine ai hakana na karba na daure na sauya tana zaune saidai tsabgabta takeyi bani take kallo ba ban tsaya shan tea din ba taga na tayar da sallah inayi.

Saida na idar na fara gaisheta ta dago daga karatun littafin da takeyi tana karba min gaisuwana tare da fadin kisha ruwan zafin zai taimaka maki.

Banki ba na dauki kofin shayin na dan kurba nan ma sugar naji yayi yawa saboda iyayyen mu basu saba muna da sugar ba ko kadan asalima muda muka fito kauye inamu ina sugar inba karya ba.

Amma saboda dan danon shayin da yai min dadi ga kanshin kayan yaji na tashi a cikinsa haka na daure na shayeshi tas na aje kofin burodin daine banko kallesa ba.

Gabin na aje kofin yasa ta dago kai tana fadin ki kwanta ki dan huta ko jikin zai dan sake idan kin tashi na danyi wani rau rau sai naga tayi dan murmushi tana fadin baki sanni ba ko idan yaya Garba ne ai zaki sanshi ko ?

To ki sani in ma baki sani ba kaf gidan nan nafi kowa kusa dake wajen alaka don kakan mu daya da ya garba sune suka haifi iyayyen mu rashin sanina da bakiyi ba yasaki kasa sakin jiki dani ko ?

Jin hakan yasa na dukar da kaina kasa nasan ko wani halaka ke garemu ashe ba karami bane babbane tsakanin mu da ita amma a lokacin ba zance ko ita wacece ba a garemu.

Saidai jin kalamin bakinta yasa dole na kwata a makure adakin nata dayaji kayan alatun zamani a cikinsa irin na zamanin lokacin.

Barci nayi sosai duk da farko a tsorace nake ga hankalina yana wajen Dada datayi nisa dani a wanan katafaren gidan mai girma ta ina zanje Dada ko halimatu a wanan gidan mai dan karen girma.

Banina tashi ba sai wajajen yamma lis koshi itace ta tayar dani don magariba daya gabato a lokacin don haka ta tayar dani daga barcin dana dan samu nayi din.

Bandakin na koma ban fito ba saida na tsabtace mata shi gabin ba wani datti a part din kada bukuntana a dakin ya takura mata ko a gida kuma da bandakin mu yake na kauyawa muna yawan kula dashi balle nan din da yake na yan birnine garesu.

A gagauce nayi sallah la,asar wanda ba,a dadeba akai magariba sai bayan sallah isha,i naji umma tace dabi muje ta kaini wajensu Dada don taga hankalina na gunta.

A falo muka samesu zaune har baban kano din daya dawo daga kasuwa tare da iyalinsa dasu Dada din dasuke baki a cikinsu mun samesu a cikin raha da annashuwa koda Umma tayi sallama fuskan dayan hjyn sai ya matse lokaci guda.

Zaman kauye da zaman babban gida irin da muka baro a kauyen ya saka min wayau da saurin fahintar mutum lokaci daya.

Tun lokacin na fara fahintar akwai yar tsama a cikin wanan gidan ke nan itako wace ta kirani da yar uwar baba a lokacin sai cewa tayi da Dada hjy ga mutumiyar ta tashi tayi sallah naga ta damu da son ganin ku yasa na kawota ko hankalinta ya kwanta.

Allah sarki yar gidan Dada yanzun nake zancen ki a raina nasan kina wajen gwaggonki yasa ban daga hankalina ba ai ya jikin naki ya koma daidai yanzu ko Dada ta tambayeni cikin mika hannu gareni kamar karamar yarinya alaman inzo gareta.

Ban bata hannun ba don ganin ido yai min yawa a wajen sai zama da nayi a gefenta kafin na dago kai ince da jama,an dana sama ina wuni murya kasa kasa kamar ina tsoronsu.

Wai yatace mai sunan mama yar wajen garba dama tare kuke ashe da ita sai lokacin wanan dayan hjy dake zaune a kusa da Alh tayi magana cikin isa da takama da izza tace ina zaka ganta kuwa tunda komai sai an nuna makirci a kansa an nuna son kai nima tunda suka iso sai yanzu na ganta ai na daiji ance tare sukazo da ita dama.

Maimakon naji ta bata amsa sai naji tayi murmushi tana fadin kaiya ko in nuna ko kada in nuna kowa ai yasan cewa ita din jininace dai sai lokacin mijin nasu yai magana yana fadin.

Shout up please har agaban wa yan nan bakin yaran sai kun nuna halin ku na banza da alama ma yarinyar nan bata da lafiyane yadda na fahinta amma fitinan ku ya hana mutum ya fahinci komai.

Ina wuni Abba na kara maimaita gaisuwana gareshi kafin ya dan kallo a hasale yana fadin mamana anzo lafiya ashe bakiji dadi ba kuma a hanya Dada ta karbe da fadin aini abin ta ban tsoro nafito lafiya da yar mutane a hanya kuma ta nade min haka ?

Yanayine hajiya baba din ya fada kuma da kauyanci kinsan ba mota suka saba shigaba irin haka sai jakkai da rakuma dole taga abin wani daban tunda bata saba shiga mota ba ai .

Wanan hjy yar likuti mai masifa don sunan dana laka mata ke nan tun ban sauke kayana a kaiba lokacin duk da ina karama na fahinci magana ta dasa min don kawai yar uwar zaman ta taji haushi .

Sai naga itako bata damu ba ta daga tana fadin idan kinci abinci sai kizo kisha magani ki kwanta ta mike ta bar falon har takai kofa naji muryan Abba din yana fadin.

Maryam ke nan dai a wajen ki maman tawa zata sauka ke nan to ki kula min da uwata kinsan dai bani wasa da mai wanan sunnan a rayuwata tsuki naji anja daga gefen shi wanda yasa har na dago kai na kalli wanan bakar matar mai jiki dake gefenshi.

Sai naga yayi magana kasa kasa da sai shida ita zasu iya ji kaita girgiza tana fadi niba zancen ka nakewa tsuki ba nawane nan a zuciyata ta fada tana kawar da kai gefe daya.

Ganin hakan banyi marmarin tsayawa ba nima na mike don kada in bace wajen komawa part din nata muryan halimatuce ke fadin jirani muje zainabu jirani muje tare ta mike tana biyo bayana ban tsaya ba naci gaba da tafiya tabiyoni.

Wanan shine tushen bakin hassadan daya shiga tsakanina da wanan ahalin duk da ban masu komai ba amma saboda akidansu na bambanta tsakani yasa sukaga na zabi wace take jinin mahaifina sama dasu.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[1/19, 19:17] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON BIRI

ZAINAB IDRIS MAKAWA

5

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Wai har naji dadi muryan halimatu ke fadin hakan lokacin da muka shigo dakin mai dakin tana cikin bayi batama san da shigowan mu dakin ba a lokacin.

A takure ta fito ta samemu zaune a waje daya har saida taja da dan baya tana fadin wai kune kunkoci abinci kafin ku zo muka girgiza kai alaman a,a.

Ai ba zaku kwanta da yunwa ba ta fada ta aje tawul din dake hannunta saman gado tana fadin bari naje na debo maku abinci ta fice daga dakin.

Kallon juna mukayi nida halima din kamar munafukai munyi tsuru tsuru damu zakice bamune muka gama daukin zuwa kano a jiya ba sai gamu kano ido ya raina fata don har na fara dana sanin zuwa a zuciyana ko.

Sallama tayi ta shigo dauke da plate shake da abinci ta aje muna a gaban mu ta juya ta fita halima ta kalloni tana fadin cikin kashe murya wanan tafi hjy can kirki kinji metace dani wai da Dada batazo damu ba ai tunda ba,a fara buki ba.

Da alama bata son baki ko bataso azo damu ba shigowan mai dakin yasa tayi shiru ruwa ta girke muna a gaban abinci tana fadin kuyi hakkuri ba kowa ke son shimkafa da dare ba amma shi aka basu umurnin yi yau.

Abincin dake girke din nakai ido na kalla jelouprice ne yaji hadin gajyen kabeji da caras da sauran tarkace sai nama manyan yanka guda hudu.

Duk haduwan abincin bai wani ban shawa,awa ba don lokaci guda gidan naji ya fita min a raina badon komai ba sai fahintar da nayi cewa mazauna gidan ba zaman lafiya a tsakaninsu don har mu baki daga zuwan mu abin ya fara shafan mu.

Saboda yanayin jikina na rashin sabo da mota ban ci wani abincin kirki ba sai halimatuce ta zauna ta kwashi abinta bandai da yunwar nama don zance gidan mu Alhamdullahi akan nama don har gobe baba na shiga kauye yayi kwanakinsa a can yana aikinsa mudai iyalinsane ya dawo damu cikin katsina inda gidansu yake muna zama don inganta rayuwan mu nan gaba da yan uwa suka inmasa yayi.

Amma part din mu na can kauye yana nan indan yaje nan yake zama sunso su mamaye wajen amma dole suka barshi da abinsa tunda sunsan yana zuwa lokaci lokaci kusan shi yafi rayuwa ma a can din.

Hakan yasa idan zai dawo zai dawo da nama man shanu nono da sauran tarkacen rugan dana kauye har sai inna tabawa mutanen arzikinta suma sun lakaci arziki a wajenta.

Wanan yasa banda kwadayin irin abubuwan nan nan shigowan mai dakin yasa na dan muskuta ina gyara zama saita kallo mu kafin ta mayar da dubata kan abincin dake gaban mu din aje tana fadin..

Ya kuma bakici abincin ba ko har yanzu jikin ne dai cikin sanyin muryan ayadda take magana cikin yanayin sanyi da kamala tare da mutumta mutum.

Naci gwaggo kalman ya fito min a baki don sanin cewa ita din alakar uba muka hada da ita don haka ta zamo gwaggona ke nan da ace ta uwace sai in kirata da mama ko wani lakanin daya danganta da uwa.

Murmushi ta sauke a fuskanta kafin tace dani toko jikin nakine bai sake ba har yanzu zaki kara shan ruwan shayi a hada maki kada ki kwanta da yunwa a cikin ki ta tambayeni cikin tsureni da idanuwanta daga inda take tsaye din gefen gadonta.

A,a nakoshi gwaggo na kara fada sai naji ta sauke ajiyan zuciya ta juya can kuma ta juyo tana kallon mu tace idan kun gama ga daki can a gyare kuje can ku kwant zakufi sakewa bisa ga nan din kema a nan zaki kwana ke nan ta tambayi halimatu din dake tattara dan kwaran shimkafan da suka zube a kasa.

Ta dago tana fadin ehh a nan zamu kwana tare don can inda dada take naji sunce kada a bata masu daki da kazanta sai ta sake murmushi tace kayya ku kananan yarane da zaku bata waje kuje ku kwanta ku huta ta fada tana fita ganin hakan yasa na mike nabi bayanta.

Dakine hadade mai kyau da katon gado da shimfida har da mirro a cikinsa tace kuyi zamanku nan abin ku har ranan da zaku koma kalman mun gode ya fito a bakina tace da akai maku me kuma gidan kune fa nan din .

Har takai kofa ta juyo tana fadim idan fankan yayi yawa kunsan dai yadda zaku rageshi ai muka amsa da mun sani ta fice ta barmu a dakin lokacin halimatu ta kalloni tana fadin wai matar arziki inda wacan muka samu kawai a gidan nan da iyalinta yaya zamuyi ke nan ?

Ya kuwa haka dai din zamu zauna a takure muma na fada ina bin dakin da kallo wai dakin baki ke nan kamar na wata mace don Allah halimatu ta fada nace wanan dakin ne na baki tace ehh,mana.

Bakiga ko acan cikin irinsa aka sauke mu ba amma naji yarinyar na fadawa uwar da turanci ko ta dauka ban bokone wai in babansu ya dawo amai damu boys quarter.

Allah ya kyauta yanzu damuwata shine inda zamu samu kayan canzawa tunda kayan mu suna wajen Dada mun barsu na fada ina dan dube dube gashi wanda na bata da amai bansan inda aka kai munshi ba.

Haka muka kwanta duk yadda halimatu taso muyi hira na kasa sakin jiki inyi haka din saidata fahinci cewa nayi barci ta kyaleni sai dana falko da darene na samu an kashe muna fitilan dakin halimatu na tayar ta rakani zuwa bandaki na kewa bamu kara falkawa ba saida safe da mai shiyan ta tayar damu daga barci don muyi sallah bayan hakan namu kara jin duriyanta ba kuma again.

Ban iya komawa barcin safe ba don haka dana gaji da kwanciya na mike na fito gidan tsit yake babu kowa ba wani motsin wani mahaluki kuma Allah ya taimaka naga tsintsiya a kofan dakunan na dauka na sharo ko ina na part din don zaka gane iyakar part din don a rabe suke falon gidan yana tsakiya daga sama kuma benene na maigidan a tsakiyansu sama.

Tsab na gyaro ko ina kafin nafito har ta waje main falo dinsu shima na gyarashi tsab na dawo dakin har lokacin halimatu tanata kwasan barcinta wanka nashiga rashin sanin heater a ban dakin yasa na watsa ruwan sanyi a jikina.

Na fito ba mai da zan shafa duk suna cikin jakata inna tayi min guzirinsu har kayan shafa na yan mata don na shafa ba sai na nema a wajen su ba inna ta saka min akayana.

Don inna irin mutanen nan ne masu kula da kansu suna rike kima da darajansu talaucin mu baisa ta zubar da kimanta ga kowa baka taba jin taje wajen wani yin karamin murya kan neman wani abin rayuwa daya shafi gidanta.

Haka kuma bata da lokacin zama yin kananan magana da mata kan saka kansu kan abinda bai shafesu ba har su daukarwa kansu zunubi donshine ba zakace ga abokiyar fadan ta a shiya ba indai innace.

Yaushema taje wani gidan balle ta saka ido ga abinda mutum keyi koda yaushe kake nemanta tana kofanta a zaune inda Allah ya ajeta dan dama kwana bibiyu zata shigata gaida Dada ta dan kumsa alheri takai mata shine kawai yawan fitanta a cikin shiya ita.

Daga dakin da nake zaune nayi zaman tagumi ina tunanen duniya najiyo muryan mai shiya tana fadin yau wani dan albarka na samu yayi min wanan aikin haka ?

Can na danji kara bude part din sai kuma ta dawo ta nufo dakin da muke din zaune ta turo da sallamanta nayi firgigit na juyo ina dagowa kamar mara gaskiya har kasa nakai ina mata ina kwana.

Ta amsa tana saye da hijjab sky color har kasa a jikinta sai dogon rigan daga ciki dake baiyana kansa lokaci lokaci ga kamshi na dan busowa a jikinta har inda nake take fadin kardai ince duk ke kikayi wanan aikin haka tunda safen nan.

Na dukar da kaina tace Allah yaiwa rayuwanki albarka da alaman tarbiyan da matar yaya ta baki ke nan kike nunawa ga halaiyanki ki kara tsare kanki kinji duk dan mutunci kallo daya zai maki yasan kin samu tarbiya yadda akeso.

Ta juya zata fita lokacin nace gwaggo cikin sanyin murya sai ta dagata ta hanyar juyowa tana fuskantana nace dama mai nake son in shafa nayi wanka maina danazo dashi yana cikin kayana a wajen Dada.

Au har wanka kinyi da safen nan injin dai kin kunna ruwan zafi na manta sam na kunna maku heater ai da nashigo jiyan ta fada tana kallon hanyar bandakin.

A,a ruwan sanyin dai na watsa na fada lokacin halimatu dake kwasan barci duk abin nan da mukeyi ta motsa ta mike firgigit tana gaida ita da kwana ta amsa kan ta juya ta fice a dakin.

Kizo ki karbi man ta fada bayan takai kofa halimatu kuma ta shiga bandaki na mike zuwa dakin nata na samu tana bincike abu a wardrobe din ta sai ga man shafi babban gora ta dauko tare da wani marron din dogon riga yar kanti material cikin irin kayan data kan tara idan sunyi tafiya rigan ya burgeta duk da bata da diya mace ita a rayuwanta.

Diyanta mazane shidda cip a duniya biyar a wanan gidan ta haifesu dayan wanda shine babban mahaifinsa ya rasu tun tana da cikinsa shima din irin auren hadin da zurian mu sukeyi akai masu.

Bayan ta gama wanka tana zaman zawarci saiga baba na kano kuma ya nuna yana sonta sai kuma aka kara dada auren gida a kansu din ashe rabon zuriane haka tsakaninsu sai gashi ta haifa mashi diya biyar duka maza.

Wanda ya kara haddasa kiyayya a tsakaninsu da abokiyar zamanta hjy malka wace ita ma dai din a cikin dangi take duk auren zamane a tsakaninsu amma kuma tunda zaman kishi ya hada a yanzu sai aka kawar da zumuncin aka kama hanyar shedan ana fafata zaman kisantaka zallah a gidan wanda har hakan ya shafi yaransu.

Bai tsaya a nan ba don har wasu dangi abin ya shafa ashe muma dai don muna yarane bamu san dawan gariba har muka yarda ta jamu zuwa sashenta wanda niko a lokacin kwadayin kiran yar uwar mahaifina take na kusa data furta min yasa na karkare yarda da komai nata.

Wanda hakan ashe baiwa hjy marka da yayanta dadi ba a take suka dauke mu munafukan bakinsu kamar yadda suke daukan duk wani wanda yazo ya danganta da hjy kubra din.

Wanan kuma shine dalilin zuwan Dada da wuri kafin buki don yana son aiwa abin tufka tun kan jama,an arzikinsa su taru su hautsana masa gida da kaidinsu na mata

don yasan yan uwa da abokan arziki zasuzo sha,anin har wanda bai taba zuwa ba labari yakeji a yanzu zaizo yaga abinda ke wakana a gidan shima.

Ashe a daren jiyan bayan fitan mu sun fara fafatawa don ya gabatar da zancen a gabansu gaban Dada din don ko muna fita tace ashe har da yara sun iya munafunci to an riga da an kulla masu tun a gida kan suzo ga inda zasu sauka mana.

Lokacin ya juyo yana fadin wanan wani irin maganace kuma yaran nan me suka sani da zaki fara fadin haka akansu yarane fa wa yan nan kanana duka duka har yaushe suke wai ?

Dada da sai lokacin tagane me ake nufi tace Allah sarki wai su Abu take zance dama in hakane ai laifinane da muka iso baku gidan yarinyar ta jirkita da yawa naji tsoro nace a kira min dayan ku.

Akace ku bakwa nan sai Kuburah a gidan shine na aika tazo ta taimaka min da ita shinefa ta dauketa zuwa sashenta kinsan shi yaro karene inda yaga fuska can yake dama wanan ne dalilin kika gansu tare ai amma kayan su yana nan guna ai ko yanzu kinji nace ta bata magani kafinta kwanta ai.

Dada banda hakan shin akwai wani barene a cikin yaran nan don Allah ko banza yarinyar nan kakarsu daya da mahaifinta da ita kuburah zaki iya raba halakan dake tsakaninsune kome ,?

Ai gata gasu dama ni nauyi ta rage min ai yace baki san hakan ba tunda kin fassara hakan da wani manufa daga inda Dada ke zaune tace wai tsaya intambayeki marka.

Mu din ne nauyi yau a gareki da kike wanan zancen ko suwa kike nufi da nauyi a wajen ki ina dai nine sai diyan nan naku biyu da shakuwa yasa nazo dasu tun yanzu garin nan don su debe min kewa.

Kin fadi hakan tun yanzu inaga kin tara taron yan uwa an cika maki gida da jama,an arziki kuma kaga musa wanan yasa na daina zugan zuwa gidan ka dama don iyalinka har yanzu ba hankali ne dasu ba.

Hjy kin dai ji kin kuma gani da idon ki ni bansan yaushe malka zatayi hankali ba ta daina wanan bakin kishin data dorawa kanta kan kuburah.

Wanan yasa na matsa ki taso akwai matsala kin fara ko ganin inda matsalan take yanzu mikewa Nafisa tayi wace za aiwa auren don barin falon don ba zata iya juriyan jin abinda ke faruwa tsakanin iyayyen nasu ba lokacin.

Mahaifin nasu yace ki dawo ki zauna kiji abinda za a fada koke abin ya shafeki don gidan wani zaki bako dukkan maza zasu dauki wanan akidar ba ki sanni.

Simi simi ta dawo ta zauna tana turo baki kafin muryan Dada ya karde falon tana fadin wallahi marka kin bani kunya sai inje gidan dan uwanku indawo muna

marmarin juna dasu kuko nan duk nazo da bacin rai nake barin garin nan kuma duk kece ummul,aba,isin hakan a gidan nan kuburah dai zuwa kikayi kika sameta sun zauna da zuciya daya da wace ta fara samu a gidan nan amma ke kin kasa hakan.

Bani ba kowa a cikin dangi ba maza ba ba mata ba tsoron zuwa gidan nan sukeyi don masifan ki da fitina bako bai zuwa baki samu sherin da kika lakaka mas ba kice yayi maki keda diyan ki.

Haka yaron nan Aliyu kin hana yaro shakat a gidan nan yau in Musa bai rike Aliyu ba duniya koda bai auri kuburah ba wakike son ya rikeshi a cikin dangi.

Yanzu kuma nime nace akan Aliyu hjy ta fada cikin hasala da dago kai tana aon jin ba,asin jefo Aliyu a zancen da sukeyi yanzu din.

Ai magance data shafi hakan malka uwar tawa zaki tsare da tambayan nan asheko ranki zai baci dani kiyi fatan ayi bukin yarki kina gidan nan na fada maki hakan ba yau ba.

Zan dauka na shaye duk wani hali naki amma banda wanda zakiwa uwata ko wani dan uwana a cikin sha,anin nan kai dagata don Allah Dada ta fada a cikin tsawa yasa ya tsaya.

Mikewa Dada din tayi da kyat tana fadin baidai zuwan mu dana yan uwanka da zasuzo daga baya ya kawo wanan kace nace ba a yanzu ?

To ku bari goben na dasafe zan saka yaran nan gaba mu koma katsina su kuma dangi zan gargadi kowa kada wanda ya kuskura ya tako sha,anin ku indai ina fada maishi yaji a cikin dangi.

Kuka sosai hjy malka din ta saka tana fadin nikan bakin jinina yakai haka yanzun nan kuma za a lauyeni har me nayi da za ace hakan a kaina.

Bakiyi ba marka yanzu na kara gane manufanki akan mu sosai burinki shine ki mallakemu kamar yayan ki sai yadda kika juya mu a gidan nan toba zai yuyu ba na fada maki.

Kama kanki a watse lafiya shiyafi don a yanzu ba mai daukar maki wanan bakin mulkin naki na kafirci kishi haukane koke kadaice farau tarda kishi a zauna lafiya.

Hannun Dada Nafisa ta kama suga shiga daki har lokacin Dada tana masifa Nafisa din tana bata hakkuri saboda tasan idan batayi hakan ba zata kwabewa mahaifiyar nasu kan bukinta din.

Mukan bamu san anyi hakan ba amma ita mai shiyan ta sani tun tana sintirin kawo muna abinci tana jin hayaniyarsu a lokacin.

Hakkuri irin nata yasa bata kula ba har wayewan garin nan kuma da muka tashi tasan akwai zance a kasa tsakanin abokan zaman nata yasa tayi shiru amma abin nacin zuciyar ta.

Ki karbi wanan ki saka don nasan yanzu basu bude part dinsu ba ina ai zai maki irin rigunan da nakan ajenevson haka rabonkine ya dan jima a dakin nan ban kyautar dashi ba.

Ki zauna nan ki shirya inkin gama ku dauki man kuyi amfani dashi ga kayan kwaliya a mirro duk dani ba wani kwaliya nakeyi ba amma ba zaki rasa abinda zaki amfani dashi ba a nan.

Tana fadin hakan ta fice daga dakin kitchen ta nufa don hada abinda zamu karya dashi din lokacin na bude roban man shafin na lakoto naji yana kamshin wani icce kamar saye ga laushi mai dadi a jikinshi kamar man bama da akecin ganye dashi.

Daga roban nayi ina kokarin karanta sunan man naga an rubuta naturalsense nayi nayi na fassara kalaman da hausa na kasa har nagama mulke jikina badon naso ba na rufe roban kada ta dawo ta samu ban gama ba na nufi mirro din a nan ma na rasa me zan shafa kayane birjit a wajen da bansan amfanin su ba lokacin.

Bayan na dan shafa na mayar da komai a inda na sameshi na saka rigan a take naga na koma kamar bani bace a gaban mirro din haka na daure na fito daga dakin zuwa inda muka kwana.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[1/20, 17:40] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON ,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

6

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Ranan bani gajiya da satar kallon kaina a jikin mirrow halimatu ba zatace ga tufafina ba don haka bata gane wanan din daga mai shiyan ua fito ba sai faman yabawa da itama takeyi akai da yayi mi kyau .

Har lokacin da hjy ta kawo muna abincin mu har daki kokone da fanke sai ruwan shayi kuma shi mukaci muka koshi lokacin halimatu take zancen wanka.

Kafinta shiga tace bari ta karbo kayanta wancan dakin ta dan jima kafin ta dawo dauke da jakkunan kayan namu data dauko muna saida ta aje take fadin.

Anya ba gida zamu koma ba kuwa zainab don naji Dada na fadin kada mu yamutsa kayan mu tafiya zamuyi yau din nan ina ganin wani abu ya faru jiya bayan mu yadda naga ran Dada abace dana shiga.

Inma gida zamu koma zanfi son hakan ai halimatu don ni sam yanzu kanon ya fice mun a raina danazo kuma sai naga ta kalleni tana dariya kafin tace dani kuma dai ?

Yanzu har kano din ya fice maki a raine kuma daga zuwan mu na dan bata rai kafin nace gidanne sai a hankali halima tunda naji me wa yan can sukace daku jiya ai.

Kedai bari ga wanan ita babu ruwanta sai haba haba da takeyi damu a nan wanka ta shiga kafin ta fito na mike na gyara gadon har daki ta fito tana santin bandakin kafin kuma ta fara zancen man shafi na nuna mata wanda na shafa ta dauka tana wani dubawa kafin tace.

Nifa irin mayukan nan ban faye son shafasu ba nafi ganewa ainihin vessiline dina in shafa yafi kama jiki nayi murmushi na mike na bude jakata na dauko mata wanda take son shafawa din na mika mata.

Kuje ku gaida mutanen gidan muryan mai shiyan ke fada muna hak daga koda muka amsa da to lokacin halima tagama shiri muka nufi part din don ita tasan hanya niko shiga banyi ba tun zuwan mu din.

Ina kallon part din baida bambamcin tsari dana wanda muka kwana iya bambancin kayan alatune kawai da wanan yafi wacan dashi kuma ba gyara gasu duk sunyi kura a jiye wajen da suke.

A haka har muka kai daki da Dada ke ciki mukayi sallama muka shiga Dada din na zaune ita kadai a dakin muka gaida ita take tambayan jikina nace da sauki.

Dan shiru ya biyo baya wanda hakan zai nuna maka cewa bata cikin yanayin dadi a lokacin can ta dago tana fadin kuyi hakkuri baku karya ba har yanzu ko ?

Halimatuce tace tun wani shekara Dada mukan munsha koko da shayi har da fanke tun dazun mun kumayi wanka kafin mu fito.

Ai kaji kaji abin su wa yan nan suna nan sunata faman barci kamar masu barcin mutuwa wai sai yanzune suka tashi ake neman abin karyawa din.

Duba min don Allah wai har tana fada don me zakuje wajen kubura ku kwana baku tsaya a nan ba ko in kun tsaya uban wa zasu baku yanzu da kun kwana nan din ?

Ai har fada tayi dama kan hakan Dada halimatu ta tambaya sai Dada din tayi mata wani irin kallo mai kama da ina ruwanki taja bakinta tayi shiru ni dai ina gefe zaune ina raba ido kafin in mike ina fadin bari na gyara maki dakin Dada.

Ban jira tace ba na mike na hau gyaran daki sai gani har dogon corridor dinsu har falonsu har suka sameni muna gaisawa ba laifi don banga komai ga yaran matan ba saidai uwar.

Da dakyar ta amsa gaisuwan nawa ta wuce saida nayiwa komai kal saboda sabon zama da tsabta har ita babban Nafisa take fadin.

Kece kika gyara wurin nan haka na dago cikin gajiya ina gyada mata kai da sauri naji tace a zozozo don Allah idan kin gama sister kin huta kizo mu shirya dake kinji gaskiya kin burgeni.

Ban zauna ba tsakani da Allah da zuciya daya kamar yadda uwata tayi min tarbiya haka na gyara masu muhalinsu ya koma yana sheki tas don dole hjyr nan tazo har dakin Dada muna zaune halima nawa Dada dariya abin karin data kasaci .

Don doyace aka soya busai busai sai taliya aka kawo mata tace ba zataci ba ita kan cikinta ya baci don haka mu muci nace nikan na koshi halimatuma tace itama a koshe take sai ga hjy din tashigo tana fadin.

Sannu yar nan kece ke kadai kikai wanan aikin haka har ina batun nayo hayan ma,aikata wallahi su gyara min wajen sai gashi karamar yarinya haka tazo ta gyara min shi tasa Allah yayiwa rayuwa albarka.

Dadace ta amsa da amin aishi da na kowane don baka san inda zakaci alherinsa ba abinda uwarta ta koyar dasu ke nan ita kan bata kyataci diyanta ba wallahi don

ko yaushe zaki shiga gidansu sune a tsaye har kananun kannenta zaki samu suna dan aikace aikacesu a cikin gida.

Yasa ko ko yaushe gidan nasu ko abinka ya fadi kasa zaki iya dauka kici do tsabta karyane kije gidan maryama kice kinga kazanta a gidansu.

Wayancewa hjyn tayi kamar bata san gugan zanan da Dada ke mata ba tace ai kinga ta huta gashi yarta ta nuna hakan ai yanzu .

Fitan hjy nima na mike nace ina zuwa halima nabar Dada na fadin sakarai kin zauna don son kai kin lalata kanki da yayan ki kuma ki hana ayi magana kina takama da bin bokaye sakarai kawai.

Part din nan na koma jug din da ak zuba muna kunnu na daukowa dada da sauran fanke na zubo a leda tayi damke muka hade da hjy sai na dan rude guilty,conscious ya kamani nake fadin .

Dama Dada ce bata iya cin doyan da aka kai mata ba da taliya shine na dauko mata kunnun nan tace a,a shine baki fada min ba aje wanan din bari na baki me zafi ki kai mata yar gidan Dada.

Wani dan flask ta kawo tare da dan kulanshi ta mika min na fita dashi na kai mata na dire a gabanta saiga tsohuwa ta shiga saka min albarka a take tana fada tana zukan kunu hadi da fanke ta shanye kofin kokon ga baki daya.

Banje gaiyatan da anty Nafisa din tayi min ba a ranan don ko ana azahar na mike na koma wajen hjy inda muka kwana wace nake kira da gwaggo a lokacin gyare gyare nayi mata sai gani har kitchen dinta ashe kowa nada kitchen dinsa a part dinshi.

Nan ma na gyara mata shi tas sai magariba lis na samu kaina a gajiye na koma wajen su Dada ta kalleni tana tambayana ina kika shigane kin gane uwarki kina can ko ?

Nace gyara nayi mata shiyasa na dade kin huta nace ke kan kin huta da Allah bai sako maki son jikin banzan nan na yayan zamanin nan ba uwarku ta hutar daku wallahi.

Meye cikin son jiki da lakacin matan zamanin nan banda zancen banza aiko gashi aure baikai ko ina ba zakiji ya mutu don lalaci da son jiki mace ko yaushe tana makake da waya tana dariya a daki kamar me hira da aljannu ita kadai.

Koke yanzu sai kiji dadin jikin ki ba zancen dibgewa a gareki sai kaji ka tashi wasai washegari don ka motsa jikinka ka hana wani cuta samun wajen da zai makele maka a jiki har yai maka illa.

Aiga wanan sakaran da bata da wayau kwance ta wuni tana lalaci anan ko dan kara bata iya nunawa ba dai ta tashi ta biki kuyisa a tare dai itama ta samu wanan albarkan da ake saka maki a,a ta saba da kwanciyan lalaci tana bin gado .

A hakane har wai kike da saurayi hakan zai aureki ko shara baki iya ba balle ki masa abincin kullun ina maku kwantace da halin yarinyar nan amma kunki wai ku gata tana zagin halimatu dake kwance saman gadon.

To aini bata fada min inzo muyi bane hakimatun ta bata amsa daga inda take Dada ta tare da fadin ke arr ita waya fada mata ta tashi tayi niko ubanki dake gida zaune.

Haba Dada har da zagan muna uba dai kan wanan maganan na fada ina zama gefen halimatu din itako cewa tayi ai kinsan dada idan bata zagi uban mutum ba bata huce haushinta akan mutum.

Nikan bam aikin banza ga mutanen da basu san darajanka ba su daukeka dan kauye ko nakasashe na kasa dasu tunda ina da uwata da ubana wallahi banyi haka kawai in karar da karfina ga banza saboda su.

Dada na fadin kinji ko kinji girman kai irin na dan arewa kaiba kowan kowa ba tusan galadima amma ka dauki girman kai ka dorawa kanka don fadin anta.

Yayin da ni kuma nake fadin ayya halimatu gidan uban mune fa idan mun masu abu shine ragewa ko kasawa innan mu kance mu kyautatawa duk wanda ya tsofe muna idan yana bukatan taimakon da mukafi karfinsa ta hanyar bada karfin mu tunda bamu da abin basa sai hakan ya zamo muna alheri a karshe.

Innan ku kukace Abu inan ku ai ta dabance don ta tarbiyantu ta kuma baku tarbiyan kuma don ta fadi hakan ai ba abin mamaki bane idan kunyi hakan.

Kawai sai jin sheshekan kukan halimatu din mukaji hakan yasa na juya da sauri cikin mamaki din ban taba zaton zataiwa kalamin Dada kuka ba don a kullun haka suke cikin rigima da juna wai a cikin itace mai daman yar uwartama da muka bari a gida sunfi kwasan rigima da Dada din donshi tace bata zuwa sai yan gida zasuzo ta biyosu don halin Dada din.

Haba keko don Allah meye haka kuma azo a samu daga zuwan mu kinawa Dada kuka haka na fada cikin jiyowa ina taba mata kafa jin hakan yasa ta dan rage sautin kukanta tana fadin.

Ke bakiji zagin ta take min bane tana nufin uwatce bata da tarbiya bata bamu ba daga can kuwa Dada tace na fada tana dashi din ne ta baki ko me ?

Fadan nasu dariya ya bani don inda sabo a yanzu na saba ganin fadansu fiye da hakan ma tun agida kuma nan da nan su shirya nace kai amma halimatu akwaiki da wani zance kema.

Yanzu aiba a hannun umma kike ba a hannunta kike inma batacine ita ta bataki ai da zaki tsaya zuciya haka tace ai bata ganin laifinta saina umma ko yaushe.

Dada tace nace uwarki nakara fadan uwarki din ke kuma kodana daukota ta dawo wajena aida hakoranta tab a baki na daukota nace kwantas tsohuwa kada fadan ya koma nawa kuma kingani Dada bata da gwani a wajenta nima gashi tana shirin sauke min nawa yanzu.

Shigowan wanan amaryan dakin yasa mukai shiru banda Dada dake masifa ta kalli Dada din tace ke kuma waya tabaki kike masifa budan bakinta sai cewa tayi ai dole in masifa yarinyar banza zata raina min wayau.

Ku halan baku san halin Dada bace kuke biye mata kunsan fa kishiyoyinta basu nan yanzu ku zata mayarwa da kishin kuyi ta fada da ita ko bakuji labarinta ba lokacin mijinsu malam yana raye.

Labarin arziki ba nikan lafiya muka rabu da yan uwana ki tambaya ki kara bamuyi irin wanan bakin kishin zamanin nan na iyayyen ku ba.

To nikan bari in fita kafin a sake min layi nawa ya sameni ta fada tana juyowa wajen Dada din ta kallo inda nake tace sister banganki ba kuma nace ehh anty na bari nagamawa su mamane sai gobe da safe idan Allah ya kaimu sai nazo na gyara maki hankali kwance.

Tace hakan ma yafi ko kinzo kin samu ina kwance ki kwankwasa min zan tashi na bude maki tunda nasan da zance daga can mukaji muryan Dada na fadin sannu kwamishiniya watau ma kinsan da zancen ko daba zaki bude kofan ba ke nan.

Wanan kam anyi yarinyar kawai a wajen nan sister don Allah kada ki manta kinji nace to anty tafice tana dariya muka bita da kallo dada na fadin haka za a gidan mijin solai solai ba asan komai ba sai daukin ayi aure ake fadi a baki.

Wai dama itace zatayi auren na fada cikin tambaya lokacin Dada din ta mayar da kallonta gareni tana fadin itace mana ba ita bace babban yar ita marka duk haihuwan marka din ai matane sai dan namijin na biyu sauran duk mata gashi a karshen nan ta sake namiji shi kuma gashi ta sake masa ya taso wani sakarai dashi haka.

To Allah ya shiryamu baki daya na fada tace amin ai zaki sanshi ba kwanaki sunje can inda nake ba da sukazo mukai ta kwasan rigima dashi dan kawai.

Tsofi kan akwaisu da zagi gaskiya komai kayi zagine wajensu nake fada a zuciyana muryantane take fadin ai kinsan ita kubura mijinta na farko rasuwa yayi yayi hatsarin mota hanyar iko ya mutu.

Shine data gama wanka wanan baban naku dama gasu yan uwa gasu abokai saiya mayar da ita dakinshi don dan lokacin yana da mata daya suka zama su biyu.

To shigowan wanan marka din gidan yasa har ya rabu da ita ta farkon yar makwabtan muce can katsina ita dai kuburah dince data zamo ta gida ba yadda zatayi dole ta barta har aka kai yanzu ciki ba dadi ga zaman nasu.

Shiyasa jiyan nan naci mata mutunci iya son raina dama ina da cikinta tun kan abinda tayiwa mai sunan malam yaro marayan Allah kice ba a taimaka masa don son rai irin na marka.

Mukan ba zancen mu bane don haka ban tsuka ba saima halimatu da naji tace dani aida gani sai tayi izzan tsiya dama bakiga yadda take kallon mutane a hankade ba.

Ni hakan yasa ko zuwa sukayi katsina bani shiga gidansu idan basun shigo gidan Dada sun rutsa dani ba in gaida su kowa na complain akanta gashi ance tana da saurin dafawa mutum sata idan yaje wajensu.

Nace me ?

Halimatu shine baki fada min in kama kaina ba naje ina gyara masu waje tace karanbanin ki na tsiya zainabu nifa nan kingani duk wani zancen Dada baisa inyiwa kowa aiki.

To shine me ko zaki hanata ita da takeyi samun albarkane komai tsiyan marka da iskanci ba zatacw yan nan tayi mata sata badai ko har meta aje da zai tsonewa Abulle rai takai ga tabawa ban ga wanan abin ba gidan nan.

Ni ban hanata ba ai ta fada tana murguda baki ta kawar da kanta gefe daya nace a raina in ma bata hanani ba ni zan hana kaina ai bandai tsunka ba balle nawa ya sameni a wajen Dada.

Saiga hjyn da muke dakinta tayi sallama ta shigowa Dada da abinci har kasa takai ta gurfana tana fadin ga abinci hjy tace sannu yar albarka har kin hada girki.

Ta danyi murmushi tana fadin tare da yata mukayi hjy ashe yar nan ta iya aikine haka itafa ta tuka min tuwon nan kwasan ledane kawai na karba nayi don da alama bata iyasa ba.

Dada ta karbe da fadin saina kwano kwaso zube da muka iya mukan shita saba dashi a can ba ruwan mu da cin tuwo a leda kamar yarbawa donsu muka sani da da kwasan tuwon leda idan suna buki.

Sai gashi yanzu kuma yaran mu kun iya wanan tabi,an nasu har makun darasu hjy idan ka kwashe a ledan ne yafi kyau da kuma karko amma a kwano sai yayi saurin lakacewa yayi sanyi nan take kuma.

Ayyo haka zancen yaje ashe Dada ta fada tace ku kuka gane hakan mukan bamu sani ba shiko mukai taba mahaifanku kuma basu korafi.

Cigaban zamanine hakan hjy yanzu kan idan mace na wancan kwasan naku saima a dauketa kazama a nan jin hakan yasa na dan dago kai na kalleta kadan na sada kan nawa kasa.

Ta kallomu tace yan matan Dada ko a kawo maku naku nan da sauri nace gwaggo bari nazo na daukar muna na fada ina mikewa tsaye da sauri nabita na karbo muna abincin.

Wanda zamuci har mu rage sabanin wanda hjyn su Nafisa ta kawo muna shimkafa da wake da salat sama wanda dada bataci ba wanan din yanzu taci sosai har wanda muka raga tana fadin a je zatayi saura dashi da safe ta karya.

A nan part din kuwa taliya suka sulala shine abincin darensu wai tunda baba ba a bangaresu yake ba ranan shi zasuci su kwanta hakana.

Ranan sunsha tsina wajen Dada yafi cikon kwando don sai fadin take saboda lalaci ga abinci amma saboda kyiuya mace bata iya tsayawa ta girka don lalaci.

Karfe tara mukaiwa Dada sallama zamu kwanta take fadin har zaku barni jifa Dadan nan kamar bake bace kika ishemu da fada tun dazun yanzu kuma munce zamu kwanta kin koma fadin har zamu tafi.

Koda muka shigo part din yana rufe amma muna murdawa ya bude muka shiga ashe mai part din tana falo wajen maigidan a lokacin.

Sai muna batun mu kwantane mukaji muryanta tana fadin har kunshigo sannunku da dawowa nayi mamakin jin hakan a bakin babban mace kamarta saidai dana tuna hali kowa da nasane na kyale.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[1/21, 22:25] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON ,,,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

7

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN

LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Washegari ban ma san hjy din tana turaka ba nidai na tashi kamar jiya nakama gyaran waje har zuwa kitchen dinsu da yanzu nasan lungun da yake shine can karshen part din.

Sai kofa da zaka iya budewa kayi wasu aiyuka a baya wanda ba cikin part din yake ba shi bayane fili sai bakin famfo dake wajen da wasu abubuwa dai haka.

Ba inda bangyara ba a wajen komai tsab don na tari sa,an asuba babu jin zafin aiki saboda a kwai ni,ima a lokacin aiki yana da dadi.

Takwas da rabi har nagama wanka na saka yar dogon rigan atamfam rubata a jikina irin dinkin mu na yaku bayi da zai nuna nidin ba wata bace.

Ko dakin Dada ban shiga ba na nufi dakin Nafisa din kwankwasawa uku na samu ta bude har ina niyar komawa baya a lokacin ciki magagin barci ta taso tana fadin wai wayene haka dan Allah ?

A raina nace tirkashi tana bude kofan take fadin wai kece dama ai kofan ma ban rufe ba sabodake don shigowarki na barta bude.

Bayanta nabi take fadi kinga wanan kayan ta nuna min tarin kayan da aka jibge saman kujera tace wanan kada ki fara tabashi amma na cikin closet din nan don Allah gaba daya ki gyara min su ki hada ko wani da dan uwansa har gyalen ma.

Duban tarin kayan nayi a raina nace tirkashi wanan duk kayan mutum gudane haka yaushe har mutum zai tsaya sakasu don Allah wanan irin abu haka ?

Wasu manyan ghana most go ta jefo min guda ukku tana fadin ki jera minsu a cikin nan amma don Allah na less daban buje da riga daban sai na zannuwan suma daban.

Na,amsa da to saidana dan nisa na fara yin yadda tace takoma ta nade a cikin bargo nan dai naci gaba da aikina abu wasa wasa har yakai ta tashi tana kallona daidai nagama jera zannuwa din zan fara na less ina dagowa naji taja tsuki daga bayana.

Hakan yasa na dan juyo tace kin ganene dinga nuna min akwai wa yanda zan cire dama kin hada wanan dinne nace ehh to ki fara wanan haka dole ta mike tare muka hada kayan da ita don nikan yafi karfi na.

Saukin abin takance dani ai wanan zai maki ko idan nace ehh sai ta nuna min gefe daya na aje da haka har muka karasa da kyat komai nata da takeso saida muka hada a dakin nan tsab mukayi packed dinsu a waje daya tasa na daure wanda ta bani cikin wani zanin gado gefe daya.

Ashe gwaggona ta taso taga har tayi aiki bataji durina ba ga alaman nayi aiki kuma don ta samu komai tsab a kitchen din ma na gyaroshi tsab har yakai taje daki bata ganni ba yasa taje dakin Dada nan ma banciki.

Saida ta kawowa Dada abin kari take tambayana don halimatu tana bandaki bata samu tambayanta ba Dada ta tsoratata da cewa bakiga Abulle ba tun safe ?

Ina ta shiga ni safiya a garin nan kuma sai gashi wai ana nemana halimatu tace ba tana wajen antyn nan ba ke Dada kin mantane da tace yau da safe zasuyi aiki dakinta hakan yasa Dada ta samemu dakin tana masifa.

Lokacin ma mun gama ina gyara kulle abinda ta ban tace don Allah Dada ki rage wanan fadan yarinyar nan ta gaji da yawa wallahi tun safe muke abu daya da ita ni nama gode maki wallahi dakikazo da ita ai da bansan yadda zanyi ba.

Ehh kyace hakaman tunda ga jaka na kawo maku ko to bari kiji bata karawa kowa wanan aikin wahalan kinji ke kuma na fada masu.

Haka na kinkimo kayan data bani din muka fito da Dada lokacin Dada tace wanan fa badai wanki bane kuma tace aiki tambayeta na juyo cikin muryan nan nawa nace Dada bani tayi fa.

Owoo yanzu naji batu ashe kinsan ya kamata na dauka halin banzan dai zaki gwadawa yar mutane kuma tunda ba sanin ya kamata kukayi ba ku.

Ke dai akeji yanzu ta fada tashige bandaki ta turo kofan da karfi zamu shige wurin Dada dayan ta fito tana yauki tacewa dada din duk kin hanamu barcin safe yau wajen masifan ki .

Saida ta juyo ta kalleta tace saiki kira ubanki ya koreni gidansa tunda na hannaku barcin hasara barcin safe tana fadin hakan muka shige daki.

Zance zuwan Dada gidan gaskiyane kamar ya takurawa yan gidan gaskiya don yadda take basu amsa gatsal zaka gane babu shirin arziki a tsakaninsu da ita.

Zakace ba irace kakarsu data haifi mahaifinsu bama don bata raga masu ko kadan da sunyi mata take basu amsa take a wajen kusan haka halinta yake ko banza saidai nasu din yayi yawane nagani.

Nikan dana rugumo kayan zan nufi masaukin mu dashi muka hade da gwaggon mu cewa tayi dani bayan nagaisheta wanan kayan na meye kuma ?

Cikin dukar dakai nace wanan antyn da zatayi aurene taban su ta mede baki tana fadin nasan tarkacen tsunmakarane ko ke me zakiyi dasu kuma bandai tanka ba na shige dakin dasu na zauna ina dan dubawa daya bayan daya .

Ni dai ani kan kayan sunyi min gaskiya ba laifi ina na taba saka less me kyau irin haka aina samu na shiga buki na fada a raina.

Wanda naga bani so suna ajewa halimatu don nasan zatayi korafi ban bata komai daga ciki ba kala ukku nacirewa halimatu din na kwashi wanda na zaba har na halimatu buuu nakaiwa gwaggon namu ta gani.

Sai cewa tayi suna da dan dama dama ai kin gode nidai naja bakina nayi shiru inda naga suna saka kaya a drower dakin nabude nasakasu har yar jakkar kayana na warewa halimatun nata.

Data shigo na bata takoyi murnan hakan lokacin dana bata din don ta nuna farin cikinta sosai nan muka wuni muna taya mai shiyan girki har yamma muka shiga wajen Dada.

Tana zaune saman carpet data idar da shaf,i da wutir din ranan muka shigo ta dago kai ta kallemu gaida ita na farayi da Dada mun wuni lafiya ?

Ta amsa cikin dadin rai tana fadin ai nake tambayan ku dazun uwarku take fadin kuna can kuna tayata aikine kun karasa ko na amsa da ehh Dada halimatu wuri ta samu tahaye gado ta kwanta.

Ke kam anyi mashiririciyar yarinya duk wahalan ki kin kai na yar uwarkine da suka mayar kamar boyarsu ni inkin debe Kubura sai ince duk ta bar masu ko kawarda kara a gidan nan.

A,a Dada aiko aikin ta yaja muna alheri gashi har nima da ban masu komai ba nakai ga kala ukku masu kyau da tsada kaya masu kyau ta samo muna fa da batayi ba ina zama zai samo muna wanan alherin kuma ?

Ke arr ja,iri dayi banzane ke kiyi mana ko duniya da kayan cikinta zasu bata ba kumce ba na hana wanan bakin aikin da batazo wazaiyi masu shi ?

Dada ki bar halimatu kara zugaki fa takeyi tace aina fahinta basu dai son suga bakin mutum yayi shiru ke dai yar albarka mikon min tuwo naci tun dazun nake son in bude naga me suka kawo min koda yake kuburace a kitchen din banda matsala yau da bakin cimarsu.

Mata ki zauna kiyi girkin kwarai ba zata tsaya ba yau ko wuni gidan nan marka batayi ba inama har yanzun bata dawo ba wai suna wajen hada kaya can gidan da za akai yarta.

Banda lalacewan zamani ina uwa ina zuwa kallon jerem yarta kuma kisan zamani yaci baya a yanzu kunya ya fita idon mutane ni wanan abin kunya ina zan iyashi don Allah ?

Da dane ai tana gida ta saka yarta gaba tana kara mata huduba kan zaman aure amma kaiya haka zata dunkulata ta kaita solai solai kamar rukumi da kaya sai karyan arziki kawai ina aure zaiyi karko a yanzu don Allah.

Toke Dada mu ina ruwan mu da wanan zancen ki samesu mana ki fada masu kinzo nan kin tasamu gaba kina zuga fada kamar mu zamu hanata hakan.

Ban iya fadan ne kome ta fada a hasale wanda hakan yasa na tsoma masu baki nace a,a Dada don Allah dai kyale halimatu ba komai ne zakiga sunayi kice sai kin maganta ba don Allah ki kyalesu kila haka al,adan garin yake.

Tace kuma fa yar nan shiyasa nake sonki dan halin manya iyakata ko idon don kinji dazun mara kunyar yar nan ta fara zancen nazo ina takurawa rayuwansu ai.

Ki kyalesu Dada a rabu lafiya tunda haka suke abinsu kinga sai a zauna lafiya inma tayi maganan bari zasuyi halan wahal da kanta kawai zatayi.

Waini kike fadawa hakan to kaf dunsu gidan suyi kadan duk iya shegensu kyalesu nakeyi bani hauhuwan da wata tazo daga baya ta nuna min iko a kansa.

Mikewa nayi na dauko kayan abincin na dire a gabanta ina budewa kamshin man shanu ya bure dakin lokaci guda jin hakan yasa ta kallo miyan tana kura mai idanu.

Tuwon shimkafene miyar kuka da tantakwashi yaji kayan yaji gwanin ban sha,awa sai kamshi ke tashi na kara jawo plate gabanta ina fadin Dada biyo za a bude maki ?

Fara bude min gudan ta fada tana shafa wai addua a jikinta bayan ta gama yanka masifa yanzu na ba gaira ba dalili kan abinda bai shafota ba a daidai lokacin kuma wanan hjy ta shigo dakin.

Tan fadin hjy kin ganmu sai yanzu yau tun safe dana fita ban samu kaina ba mutanene yanzu basu sa gaskiya ko kadan mun bashi kudin kayan nan da dadewa sai jiya da mukaje kwasa yake son ya kawo muna wani zance kuma.

Sannu da zuwa mama na fada tare da gaida ita ta da mika hannu tana fadin yauwa yan matan hjy kuna nan kuna fama da rigiman tsohuwa ko ?

Ta kalli abuncin tana fadin yauwa ankawo maki abinci ko dama na damu wallahi na barku tun safe to ai dadin mutum biyu din ke nan a gida in guda bata nan daya na nan sai kiga gida ya rayu yadda akeso.

Jin hakan batace komai ba sai cewa da tayi ke Nafisa yau tana ta yabon ki kin mata aiki sosai kun shirya kayata nikan ina naga lokacin wanan yanzu.

Muryan babane shima ya shigo dakin nan muka zube muna gaidashi din har halima dake saman gadon ta sauko yake fadin ashe kina nan kina cin abinci yanzu nake maganan ki shigowa na kenan daga kasuwa.

An dawo lafiya ko Allah yayi albarka abinda ake nema Allah ya baku ya amsa da amin lokacin hjy ta juya tabar dakin ya kai zaune gefen gado ganin hakan yasa da sauri namike zan fice daga dakin.

Muryanshi naji yana dakatar dani ta hanyar fadin dawo ki zauna abinki ina kuma zaki mamana ba a binci zakuci bane ?

Dada tace wanan nawane nasu nacan gun uwarsu ai aini kubura ta kyauta min datayi min tuwon nan amma wanan hanjin da matarka ta dinga tura min kwana biyu ai saiya kaini asibiti ba shiri.

Kallon juna mukayi da halima muna kumshe dariyan mu ya dade a dakin yanawa mahaifiyarshi bayani kan bukin anan muke jin cewa ai mai mata zata aura ashe .

Da sauri Dada din tace aikaji ita kuma gun mai mata ta kare sunki auren hadi da zuria suka gada tun iyayye da kakani a nan kuma yanzu ta fada.

Aina fada mata tun farko daga ita harshi babangida din tunda sunki hadin da mukai masu yanzu banda korafi daga baya sai Dada din tace Allah dai ya gyara kundai bi ra,ayin diyanku kada ransu ya baci a nan .

Amma banzaci hakan ba gareku don ban taba tunanen wanan zamanin zaizo ya sameni da raina ba Allah ya gyara yace ya dan dukar dakai.

Muma dakin shiru mukayi kamar ruwa yaci kafin Dada tace dashi jeka huta da iyalin ka Allah ya bamu alheri ya mike da kyar da alaman wanan maganan ya dan tabashi lokacin.

Yana fita nace ci abincin Dada kar yayi sanyi tace to yar nan ke dai ta jawo abincin ta faraci halimace son jan magana ta sauko daga saman gadon zuwa kwabon abincin Dada ta tsami nama daya ta mike da sauri tana dariya.

Dada din tace ja,ira baki jin bakina tunda mai kaunata ta hanani yawan magana nace haka shine daidai ai Dada dinga sawa kowa ido wata rana zasu tunaki.

Ashe gaskiyane wasu yaran zuciyan manya ake dora masu ashekarun nan naki kike wanan maganan tankar yar shekara hamsin gareni Abbulle gaskiya ba karamin tarbiya da hangen nesa iyayyanki suka baku ba .

Da duk uwan zamaninan zasu diga lurar da diyansu alkibilan alheri da har yanzu duniya tana kwance tana barci yadda aka santa a baya amma kayya a yanzu mun aro wani akida mun yafawa kan mu na bata da sunan boko.

Naman ta dauko ta miko min na girgiza kai ina fadin a,a muma ansaka muna munci Dada wanan rabonkine ai wanda naci ma gashi ya lake min a hakori yana damuna yanzu.

Yarinya mai dabara karna matsa maki ki karba kikace hakan sai na dukar da kai ina dariya adaidai lokacin wanan karamar tasu data dan girme muna tashigo dakin babu ko sallama da waya makale a kunnenta tana fadin gani dakin ai nashigo.

Duk muka bita da kallo cikin mamaki wanan shigowan nata haka babu ko sallama itako sai cewa da tayi ehh gata zaune ai OK sai kawai ta miko min wayan dake hannuta din.

Ban karba ba sai dago kai da nayi na kalleta a cikin mamaki kafin na mika hannu na karbi wayan daga hannunta bayan tace a cikin tsawa ki karba mana sisterce ke son magana dake.

Na karba na kara a kunne na naji tana fadin sister ki shiga dakina cikin wanan jakkar da muka saka less din nan wanda nace zankai dinki ki dauko min gani kofan gida ki kawo min amma ki sak a leda fa.

Nace to anty ina mikewa namikawa mai waya abinta naji Dada na fadin wane kuma nace amaryance ke magana tace na dauko mata wasu kaya a dakintane.

Shine wanan ta shigo muna daki haka kimkau kamar me shaga coci bako sallama kina faman wani guntaci kamar gaban baya.

Wai dani kike Dada ta juyo tana fadan hakan baisa ta tsaya ba ta fice daga dakin kai tsaye nabi bayanta nima zuwa dakin Nafisa din inda ta aikeni .

Zakice ba dakin da muka gyara dazun bane yana kamshi kan dakin amma ga kayan da tayi amfani dasu a wanan yinin ta cire watse a dakin ko ina nayi mamakin hakan taya mutum zai debe tufafin amfanin shi ya watsar kuma ?

Nidai na dauko abinda tace din nafito bayan na dauki wani leda danagani saman kujera na saka aciki har na dan gwauta dakin sai kuma wani zuciya ya ban shawaran nasawa dakin key don kare mutuncina a gidan.

Hakan nayi nasameta a wajen saidai ban ganta wajen ba nan na tsaya dan dube dube ina neman inda take din naga an sako min wutan mota anyi horn saina doshi wajen don ina ganin yadda yan mata ke hira a mota unguwar mu don haka yanzu nasan wanan don tun ina mamakin hakan har na dmotar.

Dan nisa dasu na tsaya kadan sai naga an sauke glass din motan muryanta naji tana fadin ya kika tsaya can kuma miko min mana ta fada daga cikin motar.

Hakan yasa nataka zuwa bakin motar ina mika mata cikin ladabi kallo daya nayi masu na kawar da idona don yadda suke zaune din a motar ban taba ganin wasu mahaluki a hakan ba.

Yauwa yar kanwata shi kika dauko ko nace ehh anty ki duba ki gani ko shi din ne tana kokarin bude ledan yayin da kamshin su duk ya cika min hancina a wajen.

Muryan mutumin naji yana fadin wanance bakuwar bakatsiniyar tamu ashema yarinyace karama haka take da kwazon manya amaryata ta fada min kin mata aiki sosai yau dole in maki wani abu nima.

Yana kokarin tura hannunshi daya cire cikin jikinta cikin aljihunshi ya ciro kudi dabai tsaya kirgawa ba yan dari biyar biyar ya miko minsu yana fadin ai tunda kikeson matana nima ina sonki dole na yabawa kwazom ki.

Kallon kudin da yake miko min nayi na girgiza kai alaman a,a yace dakyau bakatsiniya kunya gareku badai tsoro ba ki karba aike kanwar muce ko nayi maki kama da dan yankan kaine da ba zaki karbi kudina ba ?

A,a wallahi aikai yayanane yanzu don nayi maku abinda kukaji dadi basai kun bani kudi ba to ki karba wanan kyautane tsakanina dake ai na dan kalli anty Nafisa din tace don Allah karba ki tafi kawai saina shigo.

Na mika hannu na karba ina fadin nagode najuya da sauri zuwa cikin gida do na fahinci bata jin dadin tsayina wajen yasa nasa kai nashige da sauri ciki.

Ganin halima ban fadawa kowa komai ba sai na cusa kudin cikin jikina saboda nasan halin halimatu din saida ta dan kauce nake fadawa Dada nace amma tace saita shigo zan aje harta shigo din in bata.

Don su ba,a shige masu gaba amma don mai nemanka yaba kaninka kudi shine kuma zaka karba inba komawa baya ba su basu gudun abin kunya dama ai waisu idonsu ya bude yanzu.

Yar uwa kiyi hakkuri da rubutuna yadda kikeso din ba haka tsarina yake ba idan zaki karanta ki karanta sabodake ba zanje lahira inkasa amsa tambayan da za ai mun kan rubutun nan ba.

Akwai masu rubuta rommatic novel saiki nema ki karanta hakan ba laifi bane novel dina yana tafiya bisa ga yadda rayuwan mu kan kasancene a tallakance don babu karyan arziki ko karyan al,ada aciki saidai idan na rubuta bisa kuskure don haka kiyi hakkuri ki barni hakan.

Saukin abin masoyana suna fahintar hausana da kuma sakona wanda nasan dole cikin kashi dari kashi biyar suna amfana da rubutu na don haka donke kadai kince wani abu bazai dameni ba haka tsarin rubutuna yake masu hankali ke gane sakona garesu koda yaushe.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[1/22, 09:09] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

8

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Buki kan ya soma don zance tun zuwan mu dai masu gidan basu zauna ba sukan inka debe hjy mum dake dan harkokin ta itama don shirin bukin don muna nan aka canza masu set din part dinsu dag daki har falo komai iri daya kalane kawai bambancin kayan.

Koshi saida hakan ya dan kawo rikici a tsakaninsu donko hjy malka tace kalan data zaba ke nan tun shego don me hjy mum zata daukeshi.

Ita kuma hjy mum tace ai bata san itace ta sayo masu kayan ba dama sai yanzu data fada in haka ba za a bari matsayin ta na babba ta dauka ba saidai baba ya bar kayansa.

Nan rikici sosai ya tashi saida Dada ta fito ta tsawata masu a cikin fushi tace ke marka ban gane me kike nufi ba a nan shin ba shigowa kikayi gidan nan kika samu Kubura ba.

Ko har kin mantane wai in tuna maki don ni komai yana cikin kaina kamar yanzu akayishi kada ki mayar da mutane wasu bican don kawai shi ya zama shasha kuna juyashi keda diyan ki yadda kuke so.

Tirkashi ranan kan naga fadan manya ba dadi don idan kana kusa kunnene kan girmi kaka duk da muna daki hakan bai hana miji komai dake wakana ba wajen.

Shi ya dawo daga kasuwa ya kashe wanan wutan daya hada inda yace don ya bata kudi ai basuyi za,a sayo wa yanda kalansu ya bambanta ba tun shago kudin komai iri daya ya basu don haka ta bari hjy kubura da itace babba ta fara zaba.

Dole ta dauki kalan milk din ita kuma hjy mum ta dauki ash color din aka zauna lafiya yan company suka jera masu kayan aka fitar da wanda muka sama akai sauyin su zuwa wasu dakunan.

Don haka wuni cur mukayi muna wanan aikin na gyaran part din duk da son jikin halkmatu ranan saida ta amfana ga aikin itama aka rutsa da ita.

Don bayan mungama na hjy mum kamar yadda mukaji yan gidan nakiranta muma muka kama nabar gwaggon da nake fadi da farko don ko nace gwaggo sai su kama min dariya kawai.

Wanan yasa nabar kiranta da gwaggo din nakama hhy mum yadda kowa ke fadi a gidan a yadda ta rikemu dole na mayar da hankali kanta yanzun ma na rage shigowa wajen Dada idan ba aiki muka rarage a part dinta din.

Bata da yawan magana haka mukan zauna zugun sai in akwai wuta ta kuna muna kallo wanda kallon ma dai wa,azine su tafi kamowa sai idan zata shige zata kai muna tashan da ake film mu kalla.

Zaune muke mun zubawa tv ido ana wa,azi akan sallah nan kan bamu da laifi gaskiya duk mu muna tsare sallah saudai kara fahintar hakki akan sallah din da yanzu muke sauraro a tashan da malamin keyi.

Talla sukaje irin na gidajen talabijin lokacin ta dan nisa tace damu yakamata gobe na kaiku wajen gyaran kai a wanke maku kai kuyi kitso har kumshi don idan sun fara shagalin bukin nan baku da lokacin hakan .

Daga inda nake kwance na amsa da to tace kawunan ku yana son kitso koba duk sati kuke kitso bane budan ba halimatu sai cewa tayi sai zainab ba ita da mamanta ta iya kitso duk sati take masu.

Kefa hjy ta tambaya cikin kallonta tace nikan gaskiya yana kai sati uku huduma banyi kitso ba ta fada tana dariya tace jam kina diya mace kike barin kanki babu gyara haka ko baku san kun girma bane wai ?

Muka kalli juna nida halima din tace kunyi sa,a kunzo lokacin kakanin mu sun mutu aida suna nan da yanzu ko wacen ku tana gidan mijinta tana aure.

Indai yadda nasan akidar gidan mune na da komu dai primary aka barmu mukayi zamana ikko ne nasamu har nayi secondary a can din ina batun shiga jami,ane Allah ya karbi ran mijina lokacin.

Zakice sa,arta muke wani lokaci idan mun zauna muna hira da ita amma saboda cika idonta a fuskan mu bamu iya sakewa da ita muna zance haka dan dama ma halimatu don ko lokacin itace tayi magana.

Tace haka Dada ta fada muna Allah ya jikansa ta amsa da amin nima na kara fada tare da dorawa da Allah yasa ya huta aljanna makoma a garesa tace amin .

Ban taba tunanem zan kara aure ba a lokacin amma abu ga mai magabata ban jimaba suka kara hadamu aure kuma da babanku nan ashe rabon yayan nan ne dama sai bata karasa ba yadda bahaushe kan fada din suce ya kashe shi.

Hjy mum ina suke ne wai bangansu ba mana Dada tace muna kuma kina da yara ai tace suna waje suna karatune dukkansu naso ko karamin abar min nan Alh yaki ya turaahi madina karatu .

Tunda ya tafishi har yau ko hutu baizo bama shiyasa yanzu aida nasameku nake jin kamar kada ku tafi wallahi don kuna debe min kewan kadaici sosai wanan zuwan naku.

Sai lokacin nayi magana nace wai mukan ai mun kusa komawa school ma hutun mu ya kusa karewa kai mai sunan hjy har ina cewa zanwa babanki magana ya bar min ke nan mu zauna tare.

Da sauri nace wai innata bata yarda ai shima baba nasan bai taba yarda da hakan wallahi bai yarda halimatu ta fada a karshe tace ranan fa da Dada tace ya bari ki dawo nan da kwana wajenta cewa yayi ai Dada tayi hakkuri.

Duban baya fakon biri sai meshi don Allah Dada tayi hakkuri ta barki a gaban innanku zaifi tunda kina shigowa ai ko wani lokaci.

Ninayi mamakima daya yarda kikazo din nan wallahi koda Dada ke fadin ai dake za,azo wallahi ban yarda ba saida kika fada min da bakinki cewa tare dake zamuzo.

Dariyan hjy mum din yasa muka kallota don bamu fahinci me takewa dariya a cikin zancen ba tagane me muke nufi tace shi yaya garba din yace DUba min baya fakon biri ?

Hakafa yacewa Dada lokacin nakasa fassara wanan maganan nidai na rike kalman kawai a bakina lokacin amma bansan ma,anarsa ba.

Aiba wani abu hakan ke nufi ba duba ga zamanin nan da yara basuji suma mutane baka yarda dasu abu a hannunka shine yake abinka ba,a hannun wani ba.

Irin hakan da mukan dan zauna tana sake muna fuska yasa muke jin dadi yanzu a gidan bamu ko zancen Dada da sai wani lokaci ma ta kekomu ta samemu zaune ko muna aiki.

Washegari din kuwa kamar yadda tace acan muka wuni wurin gyaran kai da kumshi dama ba dabi,ata bace karin gashi don Allah ya hore min suma har gadon bayata da acema ina saka mashi mai da ya sauko min sosai a baya amma kaina yana da santsi don haka shagon mai ya huta dani.

Da gashin kaina aka tsantsara min kitson bare bari mai kyau ga wani kamshi dadi na gargajiya mai dadi na tashi a kawunan namu da halimatu dai suka kwasa don tace ita sai ankara mata oulu a kai.

Su kuma masu wajen sukace hjy batace ai muna kari ba hakan yasa tayi fushi amma da aka gama kuma sai ta koma murna don sun iya kitso da kumshi kamar tsiya a wajen nasu na bare bari.

Hjy mum din tazo ta kwashw mu cikin motarta ni sai kallonta nakeyi ina mamaki don ban taba zaton ko tsamanin ta iya mota ba har tanada shima ashe saida naga ta fito da key munje mun sallami Dada mun fito ta danna key motar tayi kara tun kan mukai waje motar.

Yanzu ma din da yamma kuma itace tazo ta kwashemu komawa gida muna faman raba ido ba gida muka nufa gun tella mukaje ya dubamu bai auna muba ya dai ganmu kawai ya tambayi sunan mu ya danyi rubutu a wani littafi muka fito zuwa gida.

Mun kamo hanya gidane sai lokacin tayi magana don tunda ta dauko mu kamar ranta yana a bace don yanayinta daya nuna hakan har kana iya ganewa tace.

Zaku koma ku samu munyi baki fa don su Addal sun dawo dazun da safe bayan fitar ku duk da nima bansan da zuwansu ba sai ganinsu kawai nayi daga sama kamar anjefosu.

Sai ranan na yarda da damuwa nasa babba ya maida yaron dake yawan zama kusa dashi kamar sa,ansa ko amininsa don yadda hjy mum din ke fada muna magana lokacin.

Da farko halimatuce tace hjy mum wai Addle kuma tace ba Addale yake ba Addal don yana da sunan baba malam ne mahaifinsu babanku muke kiransa da Addal.

Sunan nake maimaitawa a zuciyana na rike sosai can tace akwai dai Allah yanzu don Allah ace an min adalci ke nan duk yaran mamanku malka ankosusu don bukin nan amma ni don son kai dan karamin akawo min shi na ganshi babanku yaki hakan don kuntatawa kawai.

A,a,a gaskiya ba,a kyauta ba kan na kallo halima din kafin ta zake nace hjy mum don Allah kiyi hakkuri Allah yasa rashin zuwansu shine alheri su kuma da sukazo Allah ya tsare ya kare ya mayar dasu lafiya tace Amin zainab naji dadin wanan maganan taki sosai wallahi kuma naji zuciyana tayi min sanyi sosai da wanan kalamin naki yanzu.

Nace wani lokaci ai mummy zamuga abu muna sonshi amma kuma hakan ba alheri bane tace kwarai tana nisawa zakice wata sa,armuce a lokacin tayi shiru bata kara magana ba har muka shiga gidan nasu tayi packing a inda ta dauki motar da safe.

Muka fito zuwa ciki dauke da wasu kaya data miko muna da zamu fito motan nan muka shige ciki wani kamshin dadi part din nata yakeyi kuma yana bude don haka nidake gaba na shigo da sallamata falon.

Ciki ciki ya amsa muna yana kwance saman doguwan kujeran falon jikinshi saye da farar jallabiya ta maza mai dogon hannu kafansa farare sun dan baiya ga gashin jikin nan nasa sun kwanta masa lub a kafafun nasa.

Ya dan dago yana amsa sallaman tare da fadin mai shiyan bata nan fa saiga hjy mum din ta shigo daga bayan mu tana fadin ki kai min wanan daki halimatu wanan kuma zainab ki aje nan in huta in bude mugani.

Mamakine ya kasheni lokaci guda ina kokarin tuno fuskansa in ba karya zanyi ba sune bakin da sukazo katsina wani lokaci har baba yai min bayanin su din nan.

Tabbas ma sune shi din ne dai dama dan hjy mum ke nan ake nufi kome ko kuma nan din ma yazone dai kamar yadda yazo muna latsina wani lokaci can lokacin bamu kai hakan ba girma.

Halimatu nikan wani suna kika kira dazunne ma ga yayan naku ina sulaiman din ta fada tana kallonshi yace cikin dan dagowa ya fita bansan inda yaje ba sai lokacin nace sannu da zuwa ya dan kalloni.

Da sauri nakai kasa ina fadin ina wuni anzo lafiya ya amsa cikin dan kura min ido kafin yace yar gidan baba garba ko ?

Itace ashe ka santa ya koma ya kwanta yana fadin wancan zuwan da mukayi katsina na santa kinsan lokacin sun dawo suna katsina tace ehh ai yanzu kam ya dawo gida ke nan .

Halima ta fito ta gaidashi itama kafin ta fice da sauri zuwa wajen Dada din dakin mu na shiga nayi sallah ban idar ba nake jin hjy mum din tana kwala min kira ni kuma ina sallah.

Saida na idar nazo na sameta ina fadin hjy sallah nakeyi kada lokaci ya shige azahar kawai nasamu nayi a can din dama zance ne ki debowa yayanku abinci ai na debo masa.

Na dan rakube ina fadin ayya sallah nakeyi bari naje gun Dada mu gaisa don zuwa yanzu hankalina ya fara komawa gida kan don ban taba tafiya nayi nisa da iyayyena da yan uwana ba sai wanan karon.

Da nazo gashi satin mu biyu muka rufe har mun zama yan gida a kano yanzu ko baba na kano ya dawo daga kasuwa baiji duriyan mu ba sai ya tambaya inasu mamana banjisu ba.

Wani lokacin idan hjy mun ne kusa dashi zata fada mai abinda muke inko hjy mah ce zata dan basar da tambayan nasa sai yasa murya ya kira wani daga cikin yayansa akiramu.

Gashi da halin arziki sai ince sukan haka zariyansu yake da alheri da kuma kula da iyalansu don duk dare baba na kano zai dawo da dan tsarababsa da za,a raba ako wani sashe nagidan.

Irinsu yought kilishi limu kaza da gadaden nama mai zafi tare da abin sha kuma sai kowa ya samu a gidan yaci bawai sai wanda yai ra,ayin bawaba kawai zai samu.

Tun shigana part din mukaci karo da wanan uwar feleken yar wurin hjy mai nuna kamar tana jin warin mutane idan aka hadu da ita din nan.

Nunani tayi da hannu tana fadin wai kece dama ban ganeki ba haka na dauka irin yan classic din nan ne ma a ina kukayi wanan gyaran hakane naga dayan ma yau ta canza sosai.

Ban iya bata amsa ba ina kokarin shigewa ga rainin wayau a na magana kina kokarin shige mutum ko ance kada ku fada munane kuma ?

Dan murmushin yake nayi mata ina fadin nikan ban dauka dani kike ba ai ku bansan wajen ba wallahi tunda ba garin na sani ba ni andai kaimu an muna hakan na shige dakin da Dada din take.

Halima na zaune tana cin abinci nace ke kuma ina can ina jiran kizo muci abinci har na idar da sallah banji ki ashe kina nan kinaci ke ban sani ba Dada tace kyale ja,ira ai na fada mata abincin ku yana can wurin uwarku dama.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[1/25, 15:44] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON ,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

9

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Alhamdullahi yan buki sun fara taruwa a gidan don iyalan baba na bauchi sun iso da na baba na zaria dake aiki a ABU zaria suma sun shigo don haka mun kara yawa a gidan.

Yinin yau aiki mukaci sosai a part din hjy mum don hakane ban samu fita inga bakin da suka iso din ba don suyan nama muka wuniyi ko ince na wuniyiwa mum din a kitchen dinta.

Wanda lokaci lokaci halimatu kan dan zagayo ta dan tayani kuma ta gudu don bata iya tsayawa ta soyashi kamar yadda nina tsaya nayi mata.

Itama mai aikin takan zagayo mu danyi tare kafin kuma ta kama wani tsabga sai wani lokaci ta lekoni don haka a wajen halimatu dake dan zagayowa nake jin komai.

Dakyat na samu nagama mun cika wani roba babba mai marfi nayi mata suyan yadda ba zai lalace mata ba wanan yasa na dade ina wahala wajen suyan yaji gishiri da maggi danake dan mirginashi kafin na soya don masuci hakana din.

Dakinta nakai roban can kurya na boye wanka nayi na dauro alwala don duk jikina ciwo yake min alaman yayi tsami a lokacin yasa na dan watsa ruwa na dauro alwala don in gabatar da sallolin dake kaina lokacin.

Bayan na idar ina wajen zaune lokàcin nake jin wata irin iska mai sanyi yana shiga jikina hakan yasa na mike na dauko mai nashafa don kada zazzabi ya kamani a lokacin.

Wani dogon rigan da anty Nafisa ta ban na saka a jikina rigan tayi min dagwas a jikina har ina mamakin yadda za,ace wanan kayan suyi mata ita tunda ta darani kiba da cika na yan mata sai kumani ga rigan yayi min daidai a jikina dana saka.

Duk da ina son hutu a lokacin amma hakana daure na nufi dayan part din wurin Dada da niyar inje can in kwanta sai kuma na samu dakin nasu da mutane.

Sallama nayi na shiga suka zubo min ido gaidasu nayi kafin suna amsawa na raba zuwa wajen Dada na zaune na manne a jikinta ta kalloni tace.

Ban sanki da raki ba badai wanan aikin da kikayi bane ya saukar maki da gajiya ko nace a,a Dada amma kamar zazzabi zazzabine ke son kamani yayin dana manna hannuna a gefen wuyana ina tabawa a hankali don naji zafib jikin nawa.

Wanan kallon banzan nasa ya watso min daga inda yake kwance saman carpet ya dan kishingide bashi ba dukkansu kallona sukayi lokaci guda.

Aiga likita kusa ki fadi abindake damun ki ya baki magani koya rubuta maki a in ma allurane duk yanzu sai a sayo ayi maki karamin ya fada yana kallon mu.

A takace nace lafiyata ai kalau kila gajiyace daice a kaina yasa nake jin hakan sai naga duk sunyi murmushi shi din dai ke fadin ashe kina da wayau yau da yarinya kinsha ihu din hannunsa akwai zafi sosai ya dan murmusa yace yaushe rabon da in maka allura kai ?

Wai wanan mugun kake zance dama ina zan bari ya makure yar mutane ya halaka masu ya yaje can dai ya samu wa yanda basu san ciwon kansu ba yayi ta zurnuka masu idan sun yarda.

Baiyi magana ba sai mikewa da yayi tsaye yana fadin kai Auwal kama min tsohuwar nan in mata allura ko bakin nan nata zai mutu jekaiwa ubanka musa dake kasuwa ko kaje kaiwa Audu ko garba kafin kazo kai mun.

Au har da zagi yau zaki fada kuwa don nayi niya babu mai hana in maki allura a gidan in ka isa ai gani gaka.

Gadan gadan yako harota saiga allura ya fito dashi daga jikinshi yace yau zamuga karshen cika baki don gaba daya saina dura maki wanan alluran a jikinki.

Ganin yadda ya nufota din yasa Dada ta dauka dagaske yakeyi tace yau zanga inda za a binne tsohuwa da ranta kuwa ya cakunata ya rike ta fara sallati tana kai mai duka tako ina tana zagi.

Tunda suka fara abin bai dago kai ya kallo inda suke ba sai kallon wayanshi da yakeyi jin hayaniyan yayi yawa ya dago yana fadin kai rabu da ita mana.

Wanan ai haukane idan kajin mata ciwofa ya zakayi hakan baisa ya sake ta ba bansan lokacin danace haba don Allah kada ka halaka muna ita mana.

Cak ya tsaya yana juyowa ya kalloni zanin Dada dake kokarin kwancewa a gabansu nayi saurin rikewa don nasan a rude take itako Dada sai dura mai ashar da takeyi ta uwa ta uba tana kira masa rashin tarbiya.

Ke ina wasa dakene ko rashin kunyan ku na yan kauye zaki kawo min a nan yanzu zan tatakaki wajen nan idan kika kara budan bakin nan naki mai wari a nan.

Badai bakina ba na fada ina kawar da kai gefe don na zuciya dashi iya makura don abinda yaiwa tsohuwar bana kai sake bane kokarin kai min mari yayi yaji an rike hannun nasa ta baya ya juyo a fusace yana fadin.

Ka sakar min hannu nayi maganin wanan karamar yar iskan haba dai meyasa kake hakane wai da wanan karamar yarinyar zaka tsaya kuma fada haka.

Sai yayiwa dan uwan wani irin kallo kafin ya kuta ya fice yabar dakin Dada tace mahaukaci sai turu kuce min ashe kara haukacewa yayi acan turai din yanzu.

Suka kwashe da dariya suna zolayan Dada din tunda ya bar dakin ban kara cewa uffan ba suma basu dadeba suka bar dakin kamar jira nake su fita na saka kuka sosai lokaci guda.

Hankalin Dada ya tashi tana fadin dama nasan za a aika hakan wanan yaron kan baisan arziki ba a rayuwansa daga maganan fatan baki gashi yanzu ya saka yar mutane kuka.

Duk lalashin da Dada tayi min hakan baisa nayi shiru ba saida ta fita can sai gasu tare da hjy mum sunshigo tana fadin kingata nan badon Allah ya gyara ba da dukanta zaiyine kome oho.

Ki taso muje part dina ta fada cikin bani umurni banki ba nabi bayanya zuwa part din ta dakin da muka sauka nayi niyar shiga amma naji tace nazo dakinta sai nabi bayanta muka shiga tare da ita.

Zama mukayi bakin gadon dagani har ta dan kura min ido na wani lokaci kafin ta soma magana ki bar kukan nan hakana mai sunan hjy nasan ba karamin abu bane yasakaki wanan kukan haka amma kinyi hakkuri don Allah.

Nasan an zaluncekine yasa kike wanan kukan amma shima ya kuru da bai kai ga taba jikin ba yau da ranshi yafi naki baci a gidan nan kuwa ta fada a cikin sanyin murya.

Ni gida nake son komawa mummy na fada ina sake barkewa da sabon kuka lokaci guda ta girgiza kai tace akan Hafiz zakice zaki koma gida yau.

Saida buki yazo gab zakice ke gida zaki tome akayi ke nan idan kin koma gida yanzu sai kace wace ba gidan ubanta tazo ba.

Nasan Hafiz baya da kunya ko sagarcine ke damunsa ohh komu mata yaushe kika tsaya shiga tsabgan mu balleshi namiji don Allah kiyi hakkuri ki daina wanan kukan haka.

Koda yake nasan bayin kansa bane iyayyensane dai basu yarda da hakan don sonsa ya rufe masu idanu basu ganin laifinsa su.

Da kyat ta samu na tsagaita kukana bankoma part din da Dada din take ba don nasan idan naje can zamu iya haduwa dashi wurin ni kuma ba zanso wata halaka kota gaisuwa ya kara hadani dashi ba kuma.

Nan nake zama wurin gwaggona inkin debe zuwa gaisuwan safe da nakeyiwa Dada din bayanshi yanzun na daina zuwa mata hira ga baki daya.

Wanda yasa Dadan ta fara korafin hakan har yakai tana biyoni part din hjy mum mu dan zauna idan tazo zakiji tace na biyo wanan matsorociyance data zama ta gudu yanzu gidan nan tana tsoron miskilin yayanta har ranan da har aka wuni ban samu lekasu ba yakai ta biyoni da yamma har part din hjy mum din.

Nan baba na kano ya dawo kasuwa akace tana wajen hjy kubura ya biyota nan din yana fadin Dada naje daki akace min ai kina nan Dada tace gani nan na biyo matsoraciyan nan Abulle ne kasan miskilin nan ya tsorata ta da shiga wajen mu tunda ya daga hannu zai mareta ranan ta daina zuwa inda nake.

Baba yana kaiwa zaune yakr fadin mari kuma Dada wa ke nan wai Hafiz wazai mara din wai tace gata nan don kawai tace mashi ya daina tsoratani shine nan ya dago hannu da niyar zai mareta saida mai sunan malam ya tareshi ya fita yana zuciyan banza don an hana ya mareta.

Aiko daya gane kurensa daya dora hannu akan jikin yarinyar nan don zan gwada mai daya suke da ita a gidan nan ita din ba bare bace a cikin gidan nan don itama mai galihuce kamar kowa a cikinsu.

Daga inda hjy mum ke zaune suna hira da Dada ta jefo baki tana fadin gara dai a tsawata mashi din don kasan halin Hafiz idan ya tashi zuciyarshi na banza bajin zancen kowa yake a gidan ba shi.

Idan ya isa ya taba ta ai gani hjy mum bata dadara ba sai cewa da tayi dashi gara dai din a tsawata mashi kansu don kada yazo ya takurawa yar mutane ko yanzu din ma a takure take wajen nan ai tunda ta daina fita ko ina sai nan part din kagako ba,ayi ba ai.

Bari zan gashi in masa kashedi akansu tace dadai yafi gaskiya ya jiyo wajena yana fadin haba uwata akanshi saiki daina fita ko ina ai nan gidan kune kema kamar ko wani da kike a gidan nan ai.

Hawaye na dinga saukewa ya tsaya ya dan lalasheni wajen kafin ya fita bansan ya sukayi ba da baba din halima daice ke fada min wai ya samu Dada yana fada ankai karashi wajen baba.

To yanzu kuwa zai saka kafan wando dani a gidan nan ke nan idan ya ganeni sai ya makeni ko a inane naja tsuki ina fadin ya kasheni idan yaso an fada mashi kowa mahaukacine irinsa ?

Washegarine kamun anty Nafisa don haka tun safe kowa yake busy a gidan duba ga yadda gidan ya kara cika sosai da mutane tako ina mutane sai zowa sukeyi na dauka part din hjy mum ba zai cika kamar na mai bukin ba sai gashi an kai ga bude sauran dakunan dake rufe a part din bakin katsina sun sauka ciki.

Don ita bangaren mai bukin yan gayu ire iren matan abokan baban kano da matan yan uwasa dake birni aka sauke a cikin part din su kuma yan gida anan wajen .

Don haka nike faman dawainiya dasu kome sukeso nice zasu kira su tambaya donko sun tambayi hjy mum zatace su nemoni don haka ko yaushe ina basy.

Dole ina kallon kowa nashiri don fita zuwa wurin kamun amma ni hakan bai samu gareni ba don ko wanka banyi ba ina faman dauko min da miko min ga mutane ga mutane da ganin iyaka.

Haka nayi ta daurewa ina komai sannu a hankali har yakai saura iyamu da hjy mum data tsaya shiryawa a lokacin sai wata da nake yawan yiwa dawainiya a dakin nata mu muka saura a part din don haka zamu rufe kafin mu dawo daga can din.

Na dauka zan samu su halima a waje amma kodana rufe kofan nafito kamar yadda hjy mum ta umurceni dayi saina samu babu kowa a wajen sai inta da wanan kawar nata a wajen.

Hayaniya gami da dariya danaji a bayana yasa na dan juya hjy mommyce tare da wasu abokanta suka fito suma a cikin shirinsu lokacin har hjy mum ta bude wani mota tashiga nan naga sunja sun tsaya cikin mamaki.

Kizo mu tafi hjy mum ta fada hakan yasa da sauri na dago kafa na samesu na bude motan nashiga ta tayar muka bar wajen wai ashe ban sani ba nan rigima sukeyi akan motocin maigidan saisu da shakikanaune suka san hakan.

Don abinda ya faru shine hjy mummy ta karbi mota daga hannun mijin datake ganin zatayi sha,anin bukin ta burge kowa a wajen har kishiyan nata tasha mamaki wajan .

Sai gashi ta fito taga hjy mum ta shiga dayan motan nasa dayafi tsada a gidan ta wuce ta barta nan gashi kuma itace ta zabi wanan dake wajenta don haka yanzu me zatace dashi kuma ?

Don bata taba zato ko tsamanin wayewan hjy mum yakai haka ba a ganinta don ita hjy mum komai nata a addinance takeyinsa bata faye irin rigingimun duniya din nan ba.

Gashi kuma tana zaunene bata kaiga ganin irin shigarta ba inda itama hjy mum din sam bataso hjy mummy din taganta a yanzu ba sai idan anje wajen ni kaina da yanzu na zamo yar koren hjy mum din ta kyashewa shigata na buje da rigan less daya fito min da suran matashiyar budurwa mai tasowa a jikina.

Wanda kalan light pink din less din yai matukar min kyau ga dinkin da ganinsa an kashe mai kudi sun min dauri dayake dan baiya kitson kaina hakan yasa hjy mommy jan guntun tsuki tana fadin.

Haukar banza wai hankaka maida dan wani naka ke nan ita ala dole ala tsiya yar nan take kokarin mayarwa nata abinda ba zai yuyuba ke nan kuwa a gidan nan ta dauko muna wata yar ta jefa muna gida don kawai kyashi da hassada mafarin duk abinda akaiwa yayana tace sai anyiwa wanan yar ke nan ko ?

Koda yake ma aikin banza idan mutum ya isa ya haifo ya macen mana mugani da ake min wai kallo adole itace mai yaya maza a gida yanzu ko ga yaya matan sun taso sun tsone idanu.

Kai hjy malka banga abin damuwa bafa wajen wanan bagidajiyan mata daba kowa yasanta bama sai yan tsiraru in fitsari banzane kaza tayi mana duk inda kika shiga dai dole akalleki a barta wani hadewa zatayi gaki a wajen.

Wanan ya karfafawa hjy mummy din gwiwa don dadata da na kut da kut dinta sukai mata saiga waya ana cewa suyi sauri an fara program din event din.

Ba can mukaje ba saida muka biya wani gida muka dauki wasu mata biyu muka koma mu uku a bayan motan kafin muka doshi wajen.

Karyan yan kano da son bidi,a wajen ya hadu da manyan da kananu kowa tana nuna halinta don bame bari a barshi baya wasu sunzo daga bangaren amarya wasu kuma daga bangaren ango haka wasu sunzone ta uwar amarya haka dai kowa da dalilin zuwanta wajen taron.

Tun shigowan mune kallo ya koma gun hjy mum din da yaranta suka sayo mata tsaraban lafaya tun daga Dubai don kawai su fidda uwarsu kunya basuji tsadansa ko kudin da zasu kashe ba a wajen sayan .

Haka nima a cikine bataji zafi ko kuashin dinka min ba don kawai yadda ta amince kuma ni din na zage ina fitar da ita nauyi da kunyan da bata zata ba a lokacin saboda kawai banso kaina ba nima.

Ance kaso kanka duniya taki ka haka kaki kanka sai duniya ta soka nako sheda wanan karin maganan don ko nagani ga halima da hjy mum din don sai tayi min abu kiri kiri tabar halimatu din.

Tun zuwan mu na sance jiki nakoma wajen su halimatun dake min wani kallon mamaki don bata sanni da wanan kayan ba gashi kuma ta ganesu a jikina.

Nan ta fara fadin kaji yan kyashan na mane da sarki banda wanan basu iya daukaka rayuwan mutum sai idan yana masu bauta ni ina zan iya wanan don ragar banza.

Duk da irin maganan ya bata min rai amma ban tsaya kulata ba saboda nasan halinta akwai kyashi da nuna hassada bata iya boye hassadanta ko ta hade kowa yasanta da wanan mugun halin.

Amsa daya nasan na bata shine ko hakan iyawane don wasu sun gwada sun kasa ko kuma hakan laifine kayiwa dan uwaka tsakani da Allah kuma yanzu ya zama laifi.

Hakana a dunkule mukai maganan hjy mum bata tashi burgeni ba sai da aka kirata tayi bayani a matsayinta na uwa irin addua da nasiha mai kashe jiki datayi ta watsowa mutane hakan sai ta burgeni har kasan zuciyata.

A haka dai taro ya watse bayan ansha bidia da sauran abubuwa a wajen tun kan a tashi ta nemoni muka dawo gida do makulin part din yana wajena.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[1/27, 20:17] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON ,,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Mun dawo da wuri gida inda halimatu ta lake muka dawo da ita nan din ma ba zama mukayi ba don hjy mum din ta turamu makwabta mukai mata sakon hadin sinasir da zataiwa baki na karyawa da safe don hjy mum bata yarda tayi sanyi da bakin part din nata ba lokacin itama don tana iya nata kokarin gaskiya.

A hanyan dawowane kawai mukaga gari ya hade da hadari lokaci guda nakali halima nace kinga ikon Allah ko halimatu wai hadari aka shirya yanzu kuma .

Tace nima haka nagani Allah ya taimaka mun bar wajen taron nan da yaya zamuyi mu dawo gida yanzu garama ke hjy mum taje dake niko badon nayi dubaraba duba ga yadda mukaje na biyoki da bansan ya zamu kare a wancan wajen ba.

Sai ta kara daga kai ta kalli saman tana fadin da alaman amaryan nan zata shiga a sa,a irin wanan hadarin hakan inama yau za a kaita gidan miji aida ta more.

Ta more dame ruwan kome na tambayeta tace ke banson shakiyancin tambaya baki taba jin inza akai amarya akai ruwa ace tayi sa,an tafiya ba komai ?

Nikan ban taba ji ba sai yau a bakinki kuma wanan ruwan wata kila iskane kawai ke nuna alaman damana zai sako haka har kina wani dogon fassara haka.

Bamu ankara ba mukaji wani irin iska kamar guguwa ya taso lokaci guda tuni wuri ya turnike da kura cikin sauri muka daga kafa don akwai dan taraza da gidansu hjy mum din da gidan da muka fito.

Wata motace tazo ta wuce mu lokacin muna kokarin mannewa junan mu don iskan yayi yawa a lokacin sosai har yana shiga ido hakan yasa sosai na tsorata da yanayin.

Sannu a hankali motar ke dawowa da baya wajen mu ke wancan motar fa kamar wajen mu yayo ta fada nace kewa kika sani garin nan da zai tsaya maki cikin wanan yanayin yanzu.

Motar ta dan tsaya gaban mu kadan tace kingani ko na fada maki ai don mu ya tsaya donki dai nikan tun kan nabar gida baba sunja min kunne da garin nan .

Ahankali ya dan sauke glass din motan yana fadin kuzo na karasa daku mana ina kuka fito haka cikin iskan nan muryan dan gidan hjy mum din nan a gaban motan.

Ganeshin da mukayi da sauri muka kutsa cikin motan daya bud muka shiga wani sanyi da kamshi ya dakemu lokaci guda saina raina wancan iskan mai kuran da muka fito cikinsa.

Bai kara magana ba muma bamu tanka masa ba dan tafiya kadan sai gamu a gidan nasu saida yayi packing ya bude muna muka fito.

Zuwa lokacin iskan ya dan tsagaita sai wani iri iskace mai tattare da kamshin ruwa irin na farkon damina din nan da alama andan sake ruwa a wasu wuraren garin ke nan lokacin.

Cikin gidan muka nufa da saurin mu don iska da yanayin duk sharaban mu yana baiyana sarari saboda karfin iskan dake kadawa a lokacin.

Wani irin ajiyan zuciya na sauke don kin dumin part din hjy mum din daya dakemu a lokacin gashi kuma NEPA sun dauke wuta sai wajen ya dayi duhu sai masu hasken waya ke amfani dashi.

Hjy mum da hankalinta bai kwanta ba da rashin ganin mu tana jin muryan halima ta ambaci sunan ta tana fadin halimatu kun dawo ke nan ina nan na damu har nayi waya take fada min aikun fito ko nasan a hanya iskan zai tsura daku.

Ina zainab ta tambaya na amsa gani nan ai halimatu ke fadin badon wanan yayan na wajenki ba daya gan mu ya dauko mu aida bamu dawo ba har yanzu ga gari yayi duhu kuma.

Wanan ai yasa hankalina tashi gara wa yan can ba,a rasa motar da zai kwasosu ai tunda wajen har yanzu akwai yan gida amma wasu sun dawo daga cikin su sunce sauran na hanya tafe.

Kizo zainab ga ummanki sun iso ai bansan lokacin dana daka wani uban tsale gami da ihu ba na nufi inda take nuna min din.

Ke tsaya daga can kada ki fado muna inna ta fada tana bawa karamin danta abinci don dashi tazo kawai kallon inna nayi ina fadin ina su habiba tace suna gida banzo dasu ba.

Hjy munce ke fadin ashe motace ta lalace masu a hanya har suka bata lokaci haka basu karaso da wuri ba hannu nakai ina kokarin taba kanina din sai naga yaki ya make yana harin jikin inna din.

Kai bashar badai wai har ka manta dani ba zakace sai kawai nakai hannu na daukeshi don dole ai dole ya manta dake kin zama yar kano yanzu mana hjy ta fada.

Nan zuwan inna din ya dan dauke min hankali duk da inna na kogeni irin na yar fari a gaban mutane hakan baisa na barsu ba jin sauran mutane sun dawone yasa na mike naje na gyarawa inna din waje inda zasu faku don anyi yawa a part din .

Ko wani dan katsina yazo a nan part din ake turoshi nan zai zauna wai yasa wajen ya cunkushe muna gashi anzo da yawa don yana bukin su na farko a lokacin kowa ke kwadayin zuwa don baba na kano mai kula da dangine shi don shi da yawa sukazo masa kara.

Sau biyu ina jin hjy tana kwala min kira ban taba jin haushin hakan ba sai wanan lokacin data kasa barina da uwata in gansu lokacin kan naji haushin hakan gaskiya.

Innace ke fadin wai bake hjy ke kira bane na amsa daga ciki ina fadin gani zuwa mum na mike na fita daga kofa take fadin kinga jeki muje kitchen a kawowa mutane abinci don Allah.

Na amsa da to muka nufi kitchen din ban huta ba saida naba kowa abinci yaro da babba a daidai lokacin kuma aka gwauce da wani irin ruwan sama mai karfi a garin kamar ba ruwan farkon damana bane yadda ruwan yazo ranan.

Ranan nagaji iya gajiya muna wajen inna hjy mum ta leko dakin tana fadin zainab kizo dakina ku kwana keda halima don nan din ba waje nagani.

Dan lokaci na kara nayi masu saida safe saboda gajiya na nufi dakin mum din don in kwanta da sallama na shiga azatona ita kadaice ciki amma sai naga sabanin hakan.

Tana zaune ita da yaran nan nata maza ukku da sukazo kamar suna magana da sauri na juya da nufin komawa baya naji takirani tana fadin shigo mana abinki zainab nida yan uwankine ai a dakin.

Sallama nayi na shigo a darare dakin ina dan gaidasu kafin hjy mum ta juyo tana fadin mama ya akayine ko har zaki kwanta ke nan na amsa da ehh cikin kada kaina gareta.

Dole don kugaji da yawa da badon zuwan ku ba aini da bansan yadda zanyi da wanan taro ba haka sai karamin ke fadin muma mun fadi haka ai mun dazun muka gama zancen nan da Bros nake fadin gaskiya yarinyar nan tana da kokari da mun shigo zata tambaya a baka abincine yaya kuma cikin ladabi.

Dayan yace zuwansu ai sunyi kokari wallahi don ko big brother yana iya cin abincinsu don tsabta kinsan ko tunda yaci ai akwai tsaba banda abincinki da inya dafa bai tsayawa yaci abincin kowa har yanzu amma jiya naga yaci wanda ta bashi saidai ba sosai ba ya fada yana dan dariyan shakiyanci.

Tsam ya mike tsaye don barin dakin nidai ina tsaye daga kofa ina binsu da kallon kasan ido kai kuma ana zance zaka tafi mana Bros ba wanan bane a gabana ya fada har yakai kofa.

Uwartace wanda ke gabanka din aina fadama yadda za,ayi shine ka samu Alh da kanka da zancen don bansan yadda zanje masa da wanan zance bani yaji dadin nike daure maka dama gashi har kaiga dauko bare bayan kansan yadda tsarin iyayyenka yake tun farko.

Baice komai ba yasa kai yafice daga dakin saidai kafin sauran su fitane saida suka dan tsaya sukai dan zance da mahaifiyar taso inda na kara fahintar akan aure suke magana.

Ko bayan fitansu din hjy mum din fada takeyi dashi wai zai ja mata matsala tana zaune kalau ya dauko mata magana wurin Alh ni dai ban amsata ba don zancen yafi karfina.

Irin wanan bani kan tanka mata dan dama dama abinda ya shafi aikin kitchen dana cikin part din ta amma wanda ya shafi rayuwanta gaskiya ya girmewa tunanena nikan duk dako wani lokaci ko damuwane ke saka tayin zancen dani ban sani ba.

Shigowan halimatu dakin ya dakatar da ita ga fadin komai ta kallo halimatu din dake fadin ashe kin min wayau kin shigo nan ko nima wallahi wurin kwanci nake nema inna ke fada min ai kina nan.

Gashiko dama ke nake jira ki shigo in aikeku nan bayan layi gaki kuma kina fadin kin gaji saita kallo hjy mum din dake shiri tana magana tace ehh aiken ku zanyi yanzun nan kuwa.

Nima na kalli mum din dake magana ba alaman wasa a gareta ganin nima na yarda da abinda take fadi yasa mum din cewa wasa nake mata mamana har wani aiki tayu datake fadin wai tagaji haka ina karfin aikin uwatace tayisa ai.

Wai da sai ince yanzu ga wayanda aka bari wurin buki dazun suna fadin yadda gari yayi duhu mukan da aka kunna inji ai kinga bamu san wanan ba nan muka dauko hiran bukin tana dai shirinta sai lokaci lokaci take bamu amsa.

Zata fitane take fadin idan kun tashi don Allah mamana ki fita ki rufe kofan nan na cikin gida kada ku kwana a sake na amsa da to tayi muna saida safe ta tafi wurin mijinta.

Mun dan jima muna hira kafin namike don jin part din yayi shiru nafito don in rufe wajen ganin mutane sun dan rage zirga zirga a lokacin don haka zan rufe gidan kamar yadda ta umurceni dayi din.

Kodana fito mutanene har corridor din hjy mum din don dama nasan za,a rina don ba karamin mutane sukazo yiwa baban kano din kara ba sabodashi mutum ne maiyi ga zumunci da kula yan uwa sosai irin mutanen nan da kudinsu bai rufe masu idanunsu ba.

Haka na tsatsalakasu don wurin a gyare yake ko yaushe ties ne malale masa har karshe kuma babu wani datti don hakane basuji kyaman kwanciya a wajen ba.

A yadda naji suna dan tsegumin cewa da mutum yaje part din hjy malka za,a koroshi ace ga wajen yan katsina can wanan abin yai masu zafi sosai don sunata magana akan hakan nasan ko dama za,a rina dasu din.

Don ance wata gwaggon mu saida sukaso fada da hjy malka din take fadin malka ki tuna ba rawa kikayi gaban Allah ya baki wanan matsayin ba ya barmu duk da kika ganmu nan saboda ku mukazo wajen nan balle kita koran mu kauyawa.

Itama hjy mum din tace ke kika sani dai haka nace ku koma shiyan hjy kubura don can akai maku masauki matar tace don tana yar kauye yar uwarmu ko to ai zamu koma kuwa inda aka san mutuncin mu din.

Jin karan rufe kofa yasa dayan tambayan waye na amsa da nice gwaggo ina rufe kofanne nasa sakata tana gyara kwanciya tace hakan ma yafi sannu kinji nayi masu saida safe nashige ciki.

Washegari ban bari an tayar dani ba na tashi kitchen naje na kunna wuta kafin na koma bin daki daki ina kunna heater don a rage wahalan ruwan zafin wanka.

Gamu katsina duk yadda kayi da bakatsinem mutum bai yarda yayi wanka da ruwan da baida zafi koda kuwa dan dumi sukayi basuyi zafi sosai ba basu iya wanka dashi.

Tun wanan ranan muka samu sauki a part din don hjy mum bayar da aikin tayi ana dafowa ana kawo muna anan saidai muce wahalan rabone muba mutane shine kadai wahalan mu gashi kuma wasu sun karban muna aikin don haka muka samu akai sha,anin bukin damu babu takura.

Kamar ko wani gida suma wanan gidan suna da nasu a boye wanda dama sai mutum daya ya kwanta irin hakan har mutane kan zata akwai zaman lafiya a tsakani.

Don a zahiri dai hjy mum ce a gidan nan ta kwanta ake takanta iya son rai wanda har mai hankali zai iya gane hakan shigar a farkonshi gidan.

Saidai hakan baiyiwa hjy malka ba son ita burinta kawai tabar ganin a gidan ga baki daya shine muradinta a kullum cikin irin hakanne ta samu mijin nasu da wani zance daya bata mashi rai.

Har tayi ta kare bai tanka mata ba saidai bata sanda wanan karon takaishi makura ba don ya gama fahintar idan ta dosa dai a yanzu har yan uwashi na kud da kud duk hjy malka bata kaunan kowa dashi to me hakan yake nufi ke nan ?

Da yake daurin auren ranane sai ranan dauri aure iyayyenmu maza sukazo daga katsina ciki ko har da babana saidai baizo da kannena ba ya barsu a can gida wajen wata kanwarsu baba musa da keda tsohon ciki ita bata samu zuwa bukin ba.

Yayi murna sosai yadda yaga na koma a dan zuwan nan namu kano din sai washe baki yake ya kasa boye farin cikinsa a lokacin gareni na tambayeshi kannena yace suna gida tare da gwaggon mu a can ya barsu da zaizo ninayi ta dawainiyar kawo masu abinci da abinsha da aka tanada donsu dama.

Sai bayan daurin aure da sukaso tafiyane baba na kano ya hanasu tafiya ranan sam basuso hakan ba don tafiyan nasu bana kwana sukai niyar yi ba a ranan suzo daurin aure idan angama su juyane sukazo sai gashi yace yana da magana dasu kada su tafi.

Dole suka dagata da tafiyan sai washegari da safe aka hade a wajen nan akaita dawainiyar kai masu abin karya kummalo bayan sunci sunshane Alh ya dauko masu zancen ya fara da sallama tare da godiya kafin ya danja lokaci irin ta manya yace.

Dalilin dayasa na tsayar daku a nan shine kan matsalana da iyalina shine ma musassabin tsayar daku din da nayi din ina son in kafa sheda daku don ku sani na kusa rabuwa da malka a matsayin matata na sunna don ba zan yarda ta konani ba saboda son zuciya irin nata.

Nan suka dauki fadin subbahanallahi meyayi zafi haka Alh yace hakane donshi na tsayar daku don kafa sheda don kada kuji zancen kuce ban kyautawa iyayye ba ko wani abu a gaskiya nagaji yanzu.

Don nasan bayan wanan bukin akwai gagarumin fitina da zamuyi da ita wanda zai biyo baya tsakanina da ita don haka ku sani wanan karon zan dauki mataki akanta.

Baikai can ba Alh ka bari abi komai a sannu zamu zauna da ita din akira muna ita yanzu basai mun tafi ba nan ya fayece masu irin zaman da sukeyi dashi yace kowan ku nan yasan yadda na auri malka.

Takuma shigo gidana ta samu kullu da kubura har tayi sanadin fitan kullu data biye mata a lokacin sukai ta tashin hankali har yakai saki ya shiga tsakanin mu.

To hakan takeson yanzu a maimaita kan Kubura kuma ya kasance an barta gidan ita kadai daga ita sai yayanta a gidan nan tana yadda take so wanda ko hakan ba zai taba yuyuwa a gareni ba.

Don ba zan yarda inje lahira in tashi da barin jiki shanyayye a na nunani ana fadin ga wanda mace ta halaka a duniya to ba zan yarda takaini can ba donta hakan ya faru dani.

Hakan ma ba zai faru ba insha Allahu Alh kowa yasan kai mutumin kirkine a cikin yan uwa bamu fatan hakan ya faru dakai insha Allahu wani dan uwan hjy malka din daga cikin iyayyemu ya fada.

Nan sai aka kirasu har Dada da hjy Mum sukazo a zatonsu sallama zasuyi da bakin gida din zasu koma sai bayan sunzone sukaji sabanin hakan ga bakin baba sani.

Indaya zaiyano abubuwan garesu cikin hikima amma kafin yakai hjy malka tareshi da fadin shi Alh din ya fada maku hakan ko wani dan game game ya tsayar daku ya fadi hakan a kaina don makirci.

Tunda wanan zancen nasan gun yar bakin cikin nan zai fito tunda ba kauna takeyi ba ta kallo inda hjy Mum din take zaune a falon gefen Dada.

Au wai dama dani kikeyi hjy malka niki sani baku cikin zancena don nina dogara da turban da iyayyena suka dorani tun farko nasha tmTabara nasha Yasin sai gani sai hange a wajen ki duk wani sherikin a yanzu ni baya girgizani tunda ba kallan sherin ki daban sani kuma ba hjy Malka.

Haka dai kikace fadi a baki Annabi a baki zuciya fir,auna waye bai san abinda kema kikeyi in kina takama kinsan na wani.

Saidai zargi irin haka din don ba zan biyewa sherinki mu lalace a tare ba saboda duniyan nan me karewa ga bawa.

Kina ganin akwai wani abinda zakiyi koki fada yanzu da zai firgitani kuma nasan irin ku shedanun mutane masu kai mutum ga halaka to bani cikinsu kin sani.

Ku dakata don Allah ba mun taraku a nan bane kuyi muna irin wanan haukan yanzu mun tarakune don mu sulhuntaku mu gyara tsakanin ku kun tsaya kuna muna hauka.

Mune ma mahaukata yau Garba don samun waje wai tsaya kina nufin Garba din ma baida daraja a idonki ke nan kome ta kallo baba na kano dayai maganan yace kun gani da ku barni da ita in nuna mata iyakarta.

Nan dai akai ta magana aka taru wajen aka bata rashin gaskiya tare da ja masu kunne kan zaman nasu kamar kananun yara dasu.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[1/28, 09:55] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

11

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Da ace nashiryane aida mun sauka gida a yau din nan muma Dada ta fada daga inda take tana mikewa tsaye don tagaji da jin irin jayayyan da akeyi da hjy marka ana tausanta a wajen.

A,a mama ku dai bari ku kara dan kwana biyumana kafin ku koma gida zaifi ai tunda dama ba tare da sauran yan uwa kukazo ba babana ya fada.

Dama baka tsaya fada ba don a nan zatayi muna azumi ko zata shigo katsina killa sai ubangiji ya kai muna rai bayan babban sallah in Allah ya yarda.

Wace Dada di badai wanan ba idan na zauna yaran fa dana kwaso zan barsu su koma su kadai ne gida lokacin baban kano ya kara fadin yara waisu mamana kike magana.

Aisu sunzo ke nan garin nan ba zasu koma katsina ba koda ke zaki tafi su anan za a barmin su don har na yanke shawaran makarantan da zan sakasu ana gama buki nan insha Allahu.

Wani kallo Dada tayi wa babana daya soke kansa lokaci daya don jin abinda abokin haihuwansa ya fada akaina gashi ba wurin gardama bane balle yaja a gaban kowa.

Lokaci daya zancen na shiga masa kunne yaji gaba daya gabobin jikinshi sun daina aiki sun bada wani sauti kamar sun tashi aiki lokaci guda.

Shiko Babana kano din yaci gaba da magana yana fadin zanso zamansu a nan don su kara fahintar abubuwa saidai ita wanan dayan da kamar banda iko da ita ya kallo Dada yana nufin halimatu ke nan.

Yace ita idan zata koma ko yaune zatabi yan uwa tana iya tafiya ita idan tace bata zama a nan damu tunda banda karfin ikon akanta kamar yadda nake dashi ga mama.

Amma ita mama nagama yanke shawarana akanta ni zan karasa rike uwata kafin na aurar da ita ga mijin dana zaba mata don na riga da nayi mata miji ko a nan din gaban babana ya kara faduwa har yakai dan muskutawa yana gyara zama alokacin.

Yawan kallon da Dada kewa mahaifina aduk lokacin da baba din ya fida harafinsa yana jin kamar ana daka masa guduma akai lokacin hakan yasa babana kano fahintar shi take kallo don haka a gaban kowa yace da mahaifina Garba ko kana daja da hukuncin dana zantar ne ?

Da kyat baba dake dana sanin zuwana kano din tun bayan tafiyan mu da Dada har zuwa yau yace nina isa Alh dakai da kafa ai duk mallakan wuyace don Abbu yarkace ai halal malak don haka kana iya zatar da hukuncin komai akanta ai kamar yadda nima nake da iko da iyalinka.

To shina gani naga kamar akwai maganane don irin kallon da Dada ke maka a yanzu din yana nuna kamar akwai matsala ga hukuncin dana zatar ga yarshi.

Haba dai shiya isa ya musanta hakan kan yarsa don ka yanke hukunci akanta tunda dakai dashi duk daya kuke a wajen ta duk da kowa yasan dole abin ya daki Garba dubaga irin rikon taka tsantsan da yakewa yaransa gaskiya.

Nasan da wanan shiyasama na zabi zamanta da hjy kubura wanda dama kamar Allah ya hada abinsane don tun zuwanta tana hannunta dama kaga ka kwantar da hankalinka idai gun kuburah insha Allahu kamar yarka tana hannunkane.

Kuma nayi hakanne don yan uwa su tuna da abinda mahaifan mu sukeyi a baya na kai baka isa ka rike diyanka a hannunka ba sai dai na wani dan uwa da zaran an yayye za,a kada a wani zariyan saboda karfin zumuncin su kowa nan yasani kuma.

Da biyu da uku na dawo da rikon mama yanzu a hannu na na farko har kasan raina har yau banyi wani abinda zan iya rama irin rikon da hjy mamana tayi min ba kowa nan yasani a cikinku.

Yau duk abinda na zama ban taba mantawa itace dalilin zamana hakan a duniya agaban kowa mamana ta sayar da jeren dakinta lokacin dasu malam sukace babu kudin da zanzo kano karatu har abin ya zamo rigima akarshe tsakaninsu da malam ke Dada kin sani ai.

Dada ta dan gyara tana fadin kwarai kuwa wanan ne kuma mussababin barinta katsina ta koma can kauyensu da zama har shi Garba a karshe ya bita suka zauna a can din.

To Alhamdullahi yau Allah ya ban ikon fitar da wanan maganan daya dade yana damuna don hakane nima nake son mama tasan tabar baya a duniya batayiwa banza ba.

Shago na nan a kasa dani ina ginawa da sunan Garba insha Allahu idan an kammala an saka kaya nasane halak malak akwai kuma gida nan bayan mu kadan wanda na tanada donshi da iyalinsa da zasu zauna a ciki shima nasane nasaye da sunansa ga takardun gidan ya tura hannu cikin aljihun riga ya zaro takardun yaci gaba da fadin.

Ko yau kaga daman dawowa kano ka zauna kana da ikon hakan na fada a gaban kowa don ku sheda wanan nayine sadakatul jariya zuga ga uwata mama data rikeni da zuciya daya har na zamo hakan a yanzu.

Amma ai yaya mama tayimane da zuciya daya basai ka wahal da kanka wurin cewa zaka rama abinda tayima ba ta hanyan kyautatamin da iyalina.

Shin Garba kana son ka hanani alherine nima in samu lada da ake samu ta hanyar zumunci babana kano din ya tari numfashin babana da fadin hakan.

Mahaifina ya girgiza kansa yana fadin ko daya wallahi yaya ni maison kayi fiye da yadda kakeyi din nan ne ma wallahi yace to ka barni haka na tsara haka kuma zai tafi.

Sai kuma yan uwa kai sani naga kafi karfi ga wanan sana,an naka na yashi don haka mota nan zata shigo gobe katsina insha Allahu da sunanka halak malak na saya makashi.

Kai Amadu dakafi karfi a fannin gina kuma shagona ma bakin layi nace a gyara ina fatan kagani ana gyaransa suka amsa da ehh kwarai kuwa yace to kai akewa gyaran za,a zuba maka kayan gina aciki kana juyawa.

Gaba dayansu kaf falon saida yayiwa kowa alheri kwatabkwacin aikin da mutum keyi ya habbakashi ta yadda ba zai koma cima zaune a cikin dangi ba kuma kowa nada abin yi ke nan a cikinsu.

Ranan anyi farin ciki sosai inka debe babana da abin bai masa dadi ba don yana ganin dawowa kano a wajenshi komawa bayane haka kuma rabashi da yarsa tankar dabawa cikinsa yuka yake jin abin har yakai an fahinci rashin walwalanshi a motan baba haruna dake kusa dashi shiba mai yawan surutu bane kamar saura ya dafa baba din yana fadin.

Da nan katsina da kano duk dayane a wajen Allah iyaka bawa yayi hamdallah ga duk abu yadda yazo mashi kasa a ranka hakan ya zamo maka alheri nan gaba.

Gyara dan zama baba yayi yace hakan nake fata tun dazu don bada wani zabi dayafi ba ubangijina haka kuma ba zanso na zama tushen rusu ginan zumunci da Alh ke kokarin yi a tsakanin mu ba dashi don wanan wani hikimace dashi ya barwa kansa sanin dalilin hakan kayi tunane maikyau anan garba Allah yasa hakan yafi zama muna alheri ga baki daya ya amsa da amin.

Lokacin da labarin hukuncin da baba ya yanke akai yazo min kuka na saka ina fadin wallahi ni banzama gida zan koma kuka sosai nayi amma haka baisa inna ta kulani ba duk da itama daurewa tayi ta cije kada aga kasawanta don ba yadda ta iya da hukuncin iyayyena.

Hakana inaji ina gani duk iyayyena suka tafi suka barni zamana a kano wajen su baba da mommy ya tabbata ke nan a kaina yanzu don dole ko naso in zauna a hannun hjy mum din.

Wanan yasa zazzabi mai karfi ya kamani zuwa marance dama kuma jikin nawa akwai gajiya sai abin ya taru ya hade min ya saukar min da wanan zazzabin daya kaini kwance lokaci guda.

Ban fadawa kowa halinda nake ciki ba a lokacin har yamma da hjy Mum tazo kirana take fadin daddy yana son ganina ta fita har takai kofa ta juyo tana fadin mama nine baki son zama dani ko kuma muga baki dayan mu yan gidan nan ne bakya son zama tare damu.

Shiru nayi ina hawaye taja kafanta ta fice daga dakin don ba zata iya jure kallon hawayen da nake sakewa ba saidana tsaya na gyara kaina na nufi fallon wajen daddy din inda tace min yake.

Kusan tare muka shigo da hjy Mum din falo inda ta zauna na zauna a kasa gefen kafanta ina gaida daddy din cikin raunin murya dake da alaman maishi yayi kuka sosai a lokacin yayin da Dada da hjy malka dake zuba mai zuma a kofin shayin dake hannunsa yana fidda tururin hayaki take tsaye a kusa dashi.

A,a mamana wai da gaske ko kukan kikeyi har yanzu na dauka ai kina da wayau da zaki san nan ma gidane nima ubankine kamar Garba.

Idona runtse da hadiyan wasu busasshen yuwu da suka tsaya min a baki suke damuna kamar zan hade kaya a lokacin sam bani cikin hayacina a lokacin amma su basu farga da hakan ba gareni dama da kyat na iya takowa zuwa falon amsa kiran daddy din.

Dago kai da daddy yayi yaji shirun da nayi ban bashi amsa ba ya fara ganin halinda nake ciki anan yake furta ya subbahanallah wanan kalman ce yazo min a kunnena karshe.

Bansan tsawon minti nawa na dauka a hakan ba saidai sama sama na dinga jiyo muryoyinsu yayin da nake kokarin bude idanuwana cikin karfin hali duk suna kewaye a kaina lokacin cikin wani yanayi daba zan iya fassarashi ba a halinda nake din.

Muryan Dada naji tana fadin dama nasan za a aika hakan yadda yarinyar nan take da iyayyenta kamar cingan da rana tsaka ace za,a raba zamansu zaiyi wuya gaskiya hakan.

Itako hjy Mummy na fadin abu daine irin na Alh ma da kuma an zugashi don me zai dauko yarinya haka da girmanta yace ta dawo nan da zama dole don wani ra,ayi.

Kokarin dagowa nayi sai lokacin naji ashe a jikin hjy Mum nake kwance murya take fadin kankine yake ciwo mama ?

Da kyat na iya daga kan nayi mata alaman ehh tace asibiti ya kamata mu kaita duba yadda jijiyoyin goshinta sukai wani radau suna harbawa.

Da sauri nace ban zawa asibiti Mum abani magani zazzabi nakeji dama a cikin raunin murya dauko panadol a daki ku bata tasha hjy Mum dake rike dani tayi kokarin ajeni ta mike don hjy Mummy ko gezau batayi ba lokacin balle taje dauko maganin.

Cikin tsawa daddu yace kije mana malka sai ta mike ta tafi ta dauko gami da goran ruwa a hannunta ta bare ta miko min duk da halin da nake ciki dana karba zan hadiya saidana furta nagode a gareta.

Da kyat na hadiye nakoma na lafe a jikin Mum din ina sauke numfashi wai dama bata da lafiyane Mum tace ina zato don kwance na sameta kuma ai dole hakan ya faru da ita tun safe take abu guda baya tafiyan yan gida.

Batune dai bai faduwa amma a maida yarinyar nan gun iyayyenta shiyafi don me za a mayar da ita ko tana can ciwo yazo bayi zatayi ba halan banson irin wanan

kalamin daga yanzu naji zancen a mayar da ita zan sabawa maishi a gidan nan kowaye.

Nikan ina jin kan nawa ya fara lafawa na yunkura na tashi zaune nabar jikin hjy mum din dake rike dani lokacin tana dan min tofi a jikina duka.

Ina zaki na juyo ina kallo daddy din a raunane nace daki zanje in kwanta yace kubura kaita dakin ta kwanta ta amsa da toh Alh muje mama ta fada ta rikeni na mike duk da ina dan iyawa a lokacin.

A cikin bargo na kudundume don sanyin da nake ji a jikina gami da runtse idanuna ina jin wani zazzabi mai karfi yana son kamani ina dan rawan dari aciki.

Muryan mum naji tana fadin haba mama dama baki da lafiya baki fada min ba aisai a dauka tun yanzu ban iya kula dakene yanzu bari na kawo maki ruwan shayi kisha ko zazzabin zai sauka tunda baki son asibiti kamar daddynku kike.

Duk sai naji tausayin hjy Mum din ya kamani lokaci guda don ita din dai me kaunatace gaskiya don tunzuwa gidan ta nuna min so da kauna irin ta jini duk da naji Dada tace min dukkansu zaman gwaggonina suke don jininsu daya da ubana dukansu.

Barci barawo ina wanan tunanen yayi awon gaba dani da har bansan dawowanta ba dakin ban falka ba sai tsakan dare kuma naji garau ina yankan zufa a jikina.

Kokarin yaye bargon nayi lokacin naji muryan hjy mum dake gefena zaune ta kafa glass din idanu tana karatu tace

Ya mama wani abu kike sone ya jikin naki ko yunwa kikejine ta jefo min wanan tambayoyin lokaci guda don haka na rasa wani zan amsa mata sai cewa nayi kewayawa zanyi inyi sallah.

Kaita girgiza tana kokarin mikewa tace zaki iya tashine nace naji sauki mum zan iya na samu na mike zaune ina jin jikina wani iri alaman jikin dai ya tabu a ranan.

Hanyan fita daga dakin na nufa don fahintar danayi a dakinta nake naji muryata tana fadin ina zaki yanzufa karfi biyu da rabi na dare ki kewaya a nan mana .

Alwala na dauro na gabatar da sallalolin dake kaina tun daga la,asar duk da hijjab din Mum din kana na mika kukana ga ubangiji Allah wanda yafi kowa sanin daidai ga bawansa zamana a gidan nan yasa alherine a gareni kamar yadda yan uwa suka tafi suna fada min har hakan yasani kuka a lokacin.

Wanda a yanzu ya haifar min da wanan zazzabin da nake ciki komawa nayi na kwanta har lokacin mum na zaune saman gadonta tana karatun Al,kur ani mai girma cikin dan murya.

Banyi barci ba nima har zuwa lokacin data gama ta kwanta duk ina jinta sai zuwa asuba barci ya dan saceni saida ta tayar dani nayi sallahn asubahin ranan.

A gaskiya zance a dan kwana biyun nan naga canji sosai ga kowa na gidan har hjy malka da yaranta don wuni suke suna shigowa part din hjy mum din suna min ya jiki.

Don haka a dan wanan karnin tayi iya kokarinta kamar yadda mijinta ya umurci kowa da baison yaji ko ya gani a garesu kaina don hakane ashe suke kokarin nuna min kulawansu akaina lokacin.

Yayin da hjy mum ce da Dada suka zamo sanyin idanuwana a gidan saboda natsuwan da nake samu a wajen mum din tare da kulawa irin wanda mahaifiya zata ba yarta.

Don mum ko fita zatayi tare danine saidai idan ni naki fita amma kafanta kafana duk inda zata shiga islamiyan da take zuwa nan nima ta sakamu nida halima bata yarda ta kaimu wanda yaran gidan kezuwa jefi jefi ba sai sunga dama.

Cikin hakan zance Alhamdullahi don yanzu gaba daya na manta da zancen gida don nasan ba komawa a gareni na kuma ba kaina shawara gara na hakkura da ida Allah ya ajeni din inyi biyayya kamar yadda suke so a zauna lafiya.

Sati biyu da yin hakan daddy ya kaimu wata makarantar kudi don ba karamin fiti akayi da hjy malka ba data nuna bata son akaimu inda yaranta suke tunda tagane gasa hjy mum keson yi da ita wai yasa ta matsa mu dawo garin da zama .

Wanan yasa mum taba daddy shawara ya kaimu wani school shima na kudi don nasu baifi namu din ba duk bamu san anyi ba sai murnan hakan mukeyi mukan tunda ba abinda ya damemu sai kewan gida wanda yanzu mun rageshi koshi tunda ga Dada a tare damu.

Da mun dawo daga boko zancen islamiya ne don haka ko aikin gida yanzu bako yaushe muke yinsa ba sai weekend da muke gida zamu dan kamawa hjy mum din aikin gida din muyi.

Ga kuma kulawa ta musan man daga daddy da muke samu don zai kiramu har yayansa biyu da dai sun dan girmemuna ga shekaru yaji korafin mu zai zabi na zaba dake da muhinmanci yayi muna nikan kullun aka tambayeni zance hjy mum ta saya min ban karban kudin daddy din amma daya gane hakan halinane saiya ban kudin yace saiki kaiwa mum din naki ta kara tayi maki yar gidan mum.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[1/31, 08:06] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

12

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Shi baiwa ko daukaka wani abune dake zuwa daga Allah halittan bawane da aka haifeshi dashi hakan saidai mu yan adam bamu gane hakan.

Na fadi hakan ne duba ga yadda na koma cikin dan lokaci kadan dubaga yadda na saki komai na rugumi kaddara sai gashi cikin dan lokaci kadan rayuwata ta canza ga baki daya.

Zakice ni din ma haihuwa binnine ban taba zama kauye da muka baro nida iyayyena ba da farko to ba komai araina sai zalla kwakwan karatu both bokon dana mahamadiya dana sa a raina.

Bazance ban tunanen iyayyena ba wanan yana min makale a zuciyata dare da rana ina cikin kewansu koda yaushe suna a zuciyana saidai ban nuna damuwa akan hakan.

Wanda hakan yasa aka fita zancen nakoma ina bawa kowa mamaki daga karshema aka daina damuwa akan hakan dani tunda anga na sake a gidan.

Saboda hjy Malka yasa bana shiga part dinta don bata iya boye bakin cikinta akaina don ma tafi matsa min saboda ban bada kafa irin na Halimatu ba da har zasu dan bugi cikina suji halin da hjy mum ke ciki kan wani abinta.

Nima daga baya nagane cewa halimatu din nawa hjy mum din mu zagon kasa tana fadin zancen ta yana fita daga bakinta don da farko hannuka mai sanda mum kanyi muna takance amma kuke wurina bani kaunan abinda zai taba rayuwan ku.

Na dauka irin rikon da nake maku kuma zaku rikeni har zuciyar ku ba tare da munafuntata ba idan tayi wanan maganan nakan tsargu da ita nakanyi mamaki don me take yawan fada muna hakane.

Da hankali ya danzo min ya karu saina fahinci ida matsalan yake watau dai halimatuce ashe shakuwansu dasu mairo diyan hjy malka da biyu sukeyinsa don wani lokaci zaka sanesu a part din zaune ana yan dararaku a tsakaninsu.

Bankan tsaya kulasu zan shige wajen Dada mu dan jima muna hira wanda bai wuce hiran takuran da take ciki ba a nan din dkgidan rashin fita yadda takeyi a gida yanzun kuma bata samu sai abin yake damun ta sosai yanzu.

Yau ya kasance asabar don haka nakan dan zauna na wanke kayana tunda safe na hada hardana hjy Mum din idan sun bushe saina goge nakai mata daki yanzun ma haka nayi.

Nashiga da salamana tana zaune a bakin gado tayi tagumi da hannayenta biyu yadda ta amsa tun nan nagane a cikin damuwa take lokacin.

Kafin matace na bude durowa na saka na nufi wajen kai tsaye na bude na jera kayan har nagama zan fita batace dani komai ba hakan yasa na dan koma satan kallonta don na kara tabbatar da zargin da zuciyana ke mata.

Sam bani take kallo ba asalima a yanzu hawayene ke sauka a idanunta hakan yasa naja na tsaya cikin dan rudewa da nuna damuwa agareta.

Nake fadin Mum lafiya kuwa naganki hakan lokacin ta dago kai tana fadin ba komai mama jeki abinki kawai ganin hawaye a fuskan nata lokacin da take maganan yasa na tsaya a hankali na taka zuwa gareta ina fadin.

Mum ko mun maki laifine bamu sani ba na duka gabanta ina fadin hakan sai naji ta dan sauke ajiyan zuciya tace inma an min laifin bani tunanen dake ciki mama.

Nafi kyautata zaton halimace don a yanzu nasan halinku kaf nasan abinda kowan ku zai iya da wanda mutum ba zai iya yi ba a kullun burinki a zaman mu shine kiga farin cikina mama a gidan nan ni shedan hakanne akanki amma halimatu tana yarda ana hada kaida ita wajen cuta min ma,ana dai tana munafuntana a yanzu.

Don kusan ince banda siri a sashen nan da zanyi Halima bataje ta fadawa su hjy malka ba don na tabbatar bake bace ke fadin wanan.

Innalillahi amma halimatu bata da kirki ashe sakariyace haka ban sani ba har wani dadi taji a wajensu da taje tana sakin maganan mu a can ?

Rashin wayaune don sun fita dubara ashe har kayana take dauka ban sani ba take kai masu sugani amma Mum ba za,a kyaleta ba gaskiya na fada ina kallonta.

Kaita girgiza min tana fadin bazanso nayi sanadin zaman ta gidan nan ba insha Allahu halinta dai zai baiyanata illa iyaka yanzu tunda mun ganeta saidai mu dauki mataki a kanta ki kara kula sosai ga duk wani motsi nata a gidan nan.

Na amsa da to bata fada min me halimatu din tayi mata ba a lokacin nima kuma ban tambayeta ba na fice a dakin ina mamaki hali irin na halimatu din na munafunci.

Tun wanan abin ban kara yarda da halimatu ba dama ba wani lakkane da ita ba ko kan ta tashi nayi duk wani aikin da zanyi na taimakawa Mum din kafin mu tafi school.

Hakan ko a jikin halimatu din sai Dada ce bama tayi magana ganin rashin jittuwan mu a tare yanzu ba kamar da can ba da komai a tare mukeyinsa .

Yanzu har yakai ta daina kwana part din Mum din ta koma can wajen su mairo tana kwana dasu haka kuma tana jidan yan kayanta tana mayarwa can.

Sai a karshe ta dainama shigowa wurin hjy mum din gaba daya abu dayane shine tare muke zuwa makaranta da ita wanan kan munayi har yanzu don ba yadda za,ayi mota daya muke shiga dukkan mu mu hudu a fara saukesu sai a kaimu namu school din wanan dokana daga wajen daddy.

Ranan da yamma daddy ya shigo part din Mum a falo ya sameta zaune tana kallon wani shiri na girke girke jin sallamansa ta dago tana fadin Alh an dawo ?

Yace na dawo yana kaiwa zaune yake fadin hakan ta gaisashi da yamma ya dan amsa a gajiye kafin ya fara raba ido yana fadin a,a ya banga yaranki ba ?

Yace wai su mamana yace su mana don ya saba tambaya idan ya shigo tace yanzun nan ta daga zuwa kitchen wai yau tuwon take muna sai gani na fado falon ina tambayanta kayan yaji.

Ganin daddy din yasa naja nayi turus tare da dan gaidashi cikin daburcewa daganinsa din ya amsa min cikin irin fara,an nan nasa yana tambayana karatu.

Kafin yace ina yar uwar takine saina kalli mum din tace wai halima yau ne ta koma part din hjy malka ai can take zama yanzu daga ni sai mama a nan.

Yaushe akai haka ya tambaya cikin son jin ba,asin dalilin komawarta can din mum tace can din taga yafi mata sauki ai da nan da can duk dayane.

Dole dai nasan akwai wani abinda ya faru har tabar nan din amma aini wajenki na barta donke nabawa amnansu tun farko .

Murmushi Mum tayi kafin tace can din yafi mata dadi tunda kaga ta koma can da zama kabarta kawai nima hakan yafi min sauki data zauna nan hankalinta ya kasu gida biyu.

To shike nan amma zanyi binkice in gano inda matsalan ya fara don banson mutum mai baki biyu Mum tace Allah ya bada sa,a ya mike ya fice bai sake wani magana ba kuma.

Lokacin Mum din ke fadin ai gara ka bincika din kaji koka gane gaskiya ba zan taba zama da ita ba kuma tunda ta zama munafuka mai baki biyu karamar yarinya da ita har tasan tayi munafunci irin haka inaga ta kara girma kuma.

Nikan aina gama zama da wanan yarinyar a rayuwata.

Tsam na juya zuwa kitchen da tausayin gwaggon namu a raina nina fara fadawa Dada abinda halimatu din tayi tace haba naso gane hakan amma koni nan sai ayi sati saidai inji muryan halimatu a sashen nan amma badai ta shigo inda nake ba .

Bakomai bane Dada harkan wayewan nan nasu ne da kwadayin dan kayan dasuke kashewa su mika mata ya rudeta Dada tace ku kyaleta har yaushe ne muna nan zaki jita dasu indai yaran nan ne masu halin uwarsu.

Kudai Dada in zance ya tashi uwayen mu daine masu halin banza ba,ataba cewa uban mu saidai uwa na fada ina dariya tace rabu da nono dakike gani nono shine babban alkalin da a duniyan nan.

Indai ka tsotsa to sai kayi wanan halin kai,ko don shi ake son uwa da hali nagari mai kyau don zurian da zata haifa gaba suma suyi koyi da halinta nagari a duniya.

Haka abubuwan gidan suke tafiya da dadi ba dadi son babu yadda za,ayi ace an zauna a cikin dadin rai ko yaushe abu dayane dai dake sa ban damu ba don sakewa da hjy mum din ya taimaka min sosai zaki samemu a tare ko wani lokaci ba zaki dauka cewa ba ita bace ta haifeni don sai ince yanzuma da nake ni kasai din nan a wajenta nafi farkon zuwan mu jin dadi.

Don ina samu kula na musanman daga wajen yayanta maza sun daukeni tankar kanwa a garesu wani lokaci suvtsawata min wani lokacin kuma idan kin samemu a tare muna hira dukan mu a falo har mum idan suna gari saiki zata dai uwarmu daya dasu dama.

Saboda natsuwa na fara hango matsala a tsakanin halima dasu Mairo bandai gaskanta ba don haka ban fadawa kowa ba nabar zancen a cikina.

Ganin yanayin da muka fito gida ranan har aka saukemu halimatun batayi magana ba yasa na dake nima ban tambayeta ba duk dako idonta ya nuna tayi

kuka a ranan sosai saboda yadda idanuwanta sukai hulu,hulu dasu alaman kuka tasha a lokacin.

Ban damu da zuwa da kudi school ba amma duk da hakan sai mum ta matsa na dan riko kudi don wani lalura amma abinci kan mai kyau har saina koma dashi gida don kadan zanci in rufe inkoma gida dashi .

Wata rana kuma inba wa yanda ke bukata don a waje ko yayane saika samu wanda kafi koka darashi sukan zo takanasa su tambayeni abincin na basu.

Duk da zuwa yanzu kusan yan ajinmu sun gama sanin cewa rikona ake gidan daddy ba shine mahaifina ba kamar yadda suke zato don halima ta gama fada masu cewa rikona akeyi a gidan ai.

Kwatsan saiga halima tazo during breakfast tana fadin don Allah zeey kokin raga abinci ki taimaka min inci tun jiya da rana rabona da banci komai banci ba.

Cikin tsoro nace subbahanallah garin ya keko halima zaki hora kanki da yunwa haka alhalin ba abinci kika rasa ba don Allah batace dani komai ta karba ta zauna a seat dina tana ci saida ta gama dashi.

Gashi ranan doya da kwaine da soyayyen nama mukayi breakfast dashi don mu biyune kadaica part din dagani sai Mum kowani sati kuma ana kawo masu kayan abinci a raba a gidan.

Don haka gaskiya zance Alhamdullahi gaskiya do banda kunci rayuwa ko kadan abu daine wanda ba,a rasa ba tsakani idan ance mutum bai haifeka ba dole sai kaga ta wani fannin bai kyautama ba a ganin ka shiko yana maka iya bajintarshine.

Kodana dawo sayo muna drinks kallon kulan data aje gefe nayi ina fadin bakiji dadin abincin bane halan don harda girki kiri kiri tace min part din hjy malka sunfimu abincin zamani mai dadi ita hjy mum kullun sai abinci iri daya takewa mutane .

Wanan yasa nakai ga tambayata hakan ta dan sake murmushi afuskanta na mika mata goran cock da ruwa dake hannuna ta karba da sauri ta bude ta kwankwada sai gyatsa har abin ya bani dariya.

Kusan kwanaki muna hakan kuma Allah bai ban ikon tambayata ba ina dai saka abinci mai yawa wanda zamuje muci tare da halima duk mum bata sanda hakan saini da kaina wajen sabarin bakina na tonawa kaina asiri.

Nace ai yanzu da halimatu muke cin abinci shiyasa nake cinyewa ban dawowa dashi gida kuma don kullun kamar da yunwa take kwana wani lokacin kafin ma a tashi break take soma satan cin abincin.

Wace halimatu dai badai ta gidan nan ba sai datayi min wanan tambayan nagane katobaran danayi din wajen fallasa kaina a sanyayye nace itafa Mum.

Ya akayi ta zauna cin abincin da baida dadi nace nima ban sani ba kullun dai tana zuwa kamar mai yunwa a haukace wani lokaci ma saina bar mata abincin taci ita kadai.

Amma ko yar nan bata da kunya tunda har ta iya zama taci abincin mu nace mum baki ganta bane halan kwana biyu duk ta fita hayacinta fa ta rame ta lalace yan kwanakin nan.

To Allah ya sauwaka saiki kara yawan abincin yadda zai dinga isarku kada ki takurawa kanki kumake nidai bani hora mutum da abinci dama ita tagujemu ai.

Abinda ban yarda shine tace zata dawo part din nan kuma da zama yanzu in yarda gaskiya wanan ban dauka amma don abinci ki dinga zubawa da ita kuci kullun.

Irin wanan halaiyan na hjy mum yasa nake kara ganin mutuncinta a idanuna don macece wance tasan kanta da darajan duk wani mahalukin dan adamba duniya.

Don hakane na canza muna kulan abinci ko ya akayi yaran suka gane suka fadawa uwarsu zamu tafi da safen Friday sai ganin hjy mummy nayi tsaye bakin mota har na karaso ina gaida ita bata karba min ba.

Sai cewa da tayi ke wanan meye kika dauko haka na dan daburce ina kallon bayana don ban taba zaton dani take ba a lokacin sai cewa tayi dake nake na dan kalli hannuna dake rike da ledan da na riko na kayan abincin nace wanan abincinane a cikinsa.

Dakata kiji don nasan ku da gadon munafunci kamar tsiya inke da uwar rikonkoki kuka daurewa halimatu a gidan nan wallahi sai ranku ya baci ai ita hjy kuburan tasan halina idan ke baki sani ba.

La,ila ina ruwana da halima da zaki kirani da munafuka na fada a dan hasale don nasaba data taba a lokacin tace mun gada gunwa ke nan iyayyen mu take nufi wai wazan baka so a jikinka kamu na zagin koko.

Amma yarinta da tashen balaga bai bari na tuna hakan ba lokacin sai wanan amsan dana bata nima bansan zai fito min ba sai naji tace ke nikike son mayawa da magana ki kama kanki kafin bakin nan naki yaja maki matsala a gidan nan wallahi.

Mota nayi kokarin shiga ina gunguni ciki ciki ina fadin ni ina ruwana da zabcen ku nidai nasan ba munafuka nake ba wallahi.

A,a mommy na fada maki kibar yarinyar nan don yanzu inkinyi haka wallahi zai koma tsakaninki da daddynmune kuma ku kyaleta don Allah gadai shegiya nan wanan munafukan halima Asiya yarta ta fada.

Yan iska duk sai kun bar gidan nan koda tsiya da bala,i babu shegiyar yarcin arzikin da zatazo ta mamaye muna gida ta hana mutane walawa saboda kwadayi .

Mairo data shigo motan bayani taji me nace don cewa nayi cin arziki aiba akan mu aka faraba don kowa yaci saidai idan ya manta yanzu.

Lokacin ta juyo gareni tana fadin kewa kike fadawa hakan mommy kowa jin hakan ban tankata ba nace gaba da yan suraitana ciki ciki ina jan tsuki.

Koda muka isa ban tsaya binta kan halimatu ba nashige aji ranan na hasala sosai na yanke cewa idan mun koma gida zan roki daddy ya mayar dani gidan mu.

Bayan an taso breakne halimatu tazo ajin mu take fadin kingani ko kinga wanan muguwar yau dai da idanunki kin gani ke nan halinda nake ciki.

Wallahi sun yaudareni zainab sunci amanat,,,, tareta nayi da fadin ni banga komai ba don Allah bar zancen wanan matar banso tunda ba a karkashinta nake zaune ba.

Ke zaki iya tuda kina da sauran kimarki a gidan ni kuma sun rabani da hjy mum yanzu kuma sun koma hattarata ga bakin aiki kamar boyar su haka na koma a part din nan.

Abinci na bude muka faraci tanata zuba surutu dayasa har naji abincin ya fice min a rai na kudurta zan samu daddy da zancen komawa hannun iyayyena da zama.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[2/3, 07:47] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

13

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Tabbas ba a nunawa shege hanyar neman uba saidai ki sani hjy malka duk wanan dukiyan dake gareni yanzu zan kara fada a gaban iyalina kuji sanadiyar kakan yarinyar nan na sameshi.

Ni Alh musa ba butulu bane ko kaza mai ci ta goge bakinta nafi gaban wanan yau har a samu daya daga cikin iyalina yace zai gorantawa iyalan Garba wani abu a cikin gidan nan wallahi karyane daddy ke fadin hakan a gaban iyalinsa.

Da akai komai a gaban idanunsa ashe yace hjy kece shedana a madadin yan uwana dana kafaku sheda a ranan kada wani yace zai matsawa yaran nan dana dauko a gidan nan da suna riko in samu lada.

Sai gashi yau hjy malka tayi kokarin take wanan dokan da sunan gida na diyansuns don haka babu dan shan miyan da zaizo gidan nan ya takurawa rayuwansu da sunan zaman riko.

Yau yar garbace ta zamo yar riko a cikin gidana ko kuma yar saudatu kanwata ce diyar dan uwana isa ta zamo yar riko a gidan nan ya juyo yana tambayan hjy malka din da tun farkon zancen take mamaki yadda yasan wanan zance.

Da ace yaran sun dawo gidane da sai tace a bakin mu yaji hakan don mu kadaine a wajen saiko yayanta da driver to ko driver ne ya fadawa Alh din ?

Ta tambayi kanta wanan zancen cikin mamaki kafin tace amma ai Alh kamata yayi ka tambya har in ma wanine ya tsegunta maka zancen kaji meya faru har na furta hakan garesu.

A,ahaa gareta dai don ita dayan ta kasance mai baki biyu wajen ki take donke ke rikonta yanzu gidan nan ita dayan kuma da kikabi da zagine har da gori ban fahintaba ni.

Shiru tayi kafin ta dago cikin karfin hali tana fadin aida munafunkin daya fada ma anyi sai ya fada maka ita metace dani har na fada mata hakan.

Kin dai fada ke nan marka aiko yaran nan basuci hakan gareku ba gidan nan nina dauka koba Alh kuke aure ba suna da daman zuwa wajen ko wacenku su zauna a karkshinta.

Balle kuma nan din daya zamo gidan wan mahaifansu kuma yan uwanku har wanan kalamin ya fito a fatan bakinki yanzu sai yarkice zata kwaba maki karshe.

Lalai tabbas munafukin nan yakai tunda komai ya kwashe ya fadawa Alh duk yadda akayi Sani driver keda wanan munafuncin ta fada a ranta.

Banyi magana bane don naga takai ga samun yadda takeso zubar mutuncinta don ko yarinyar ta bata ansa a bakinta ai yadda zata iya kwatan kanta gareta .

Kallon mijin nasu tayi yace agabana komai ya faru malka da wani zai fada min ba zan yarda ba zance yai maki kazadin da kike fada kullun an maki agidan nan ne amma sai gashi idon ki ya rufe har kuka tafi baku san ma ina tsaye a wajen ba nida bakona a lokacin.

Kai ta dukar kasa lalai in ba ta mata ba motarshi tana wajen a lokacin ashe yana ciki ke nan ake nufi lokacin lalai ta tafka babban kuskure nayin hakan a ranan data bari tabi shawaran yarta Asiya zaifi mata sauki amma ina zafin zuciya ya hanata yin hakan alokacin.

Muryan dadine ke fadin don haka kan taka min doka zan dauki kwakwaran matakin da nace zan dauka akan ko waye yace zai takurawa yaran nan tun farko.

Kafin daddy yakai karshe har hjy mommy tace dashi don Allah Alh kayi hakkuri kusukure aka samu ba za,a karan hakan ba insha Allahu bacin raine don Sadiya sata take mum sosai yasa naso in horata ga hakan.

Duk suka kallota tace kwarai kuma saida na tabbatar da hakan gareta nagane itace take daukar min kudi da wasu abubuwa yasa na dauki mataki.

Itama yar uwan shine tambayan da nake mata taso ta kawo min rashin kunyane harka jimu da ita idan ba haka ba aini ba ruwana da sha,aninsu.

Kuma ita din ta saka kanta cikin harkan kishin mu bata kallon kowa da kima a gidan nan lokacin hjy Kuburah tayi magana tace bako Mama ba don ba mecewa tayi mai rashin kunya don ba halinta bane.

Idan batayi yau tayi min ko karya nayi mata kuma ta fada a dan hasale don hjy mum tayi magana a lokacin abinda bata kauna ke nan taji don tana ganin batayi matsayin da zata saka baki a rigimanta ita da mijinsu ba ai.

Saida Dada ta saka baki ganin yadda hjy malka ta kwanta yasa daddy ya hakura bayan ya kara jadada masu akan kafin suka watse har lokacin hjy malka bata yarda cewa daddy ne yaga abinda ya faru da idanunsa ba.

Koda muka dawo ina cika saiga hjy mum tafito min da zancen nima nayi mamakin jin zancen a bakinta takuma fada min matakin da daddy ya dauka akai wanan yasa naji dan sasauci a zuciyana.

Sai gashi kuma a yammacin anty Nafisa ta dawo gida ba dadi ita da miji har abu yakai ga sakin daba gyara a tsakaninsu ga kuma karamin ciki a jikinta duk uban kudin da aka kashe da wanan bukin da baifi wata uku ko hudu ba a yanzu ya tashi ga banza tunda auren ba gyara kuma .

Mun dawo daga islamiya muka tsinci wanan bakin labarin a bakin Dada daketa yankan fada a dakinta don nashiga ingaida ita tunda tun safe ban shiga ba mun gaisa.

Nan take fada muna abinda ya faru cewa ashe shi din dan duniyane wai baison haihuwa matarsa ma ta gida haihuwa biyu yasa ta dakata da haihuwan.

Saboda baison mace mai haihuwa yasa ya nemi anty Nafisa din don yaga kanta a waye yake zatayi na,am da bukatashi sai gashi takiyin planning din daya bata tayi ciki ya baiya daga kaita gidanshi.

Wanan ya kawo masu fitina ba dadi yace ba zai zauna da ita ba tunda tun farko ya fada mata shirinsa taki daukan mataki don haka ko a zubar da cikin tayi planning ko kuma su rabu tace ba zata zubar da ciki ba tunda ta samu.

Sunsha rigima kuma uwarta ta sani amma bata fadawa kowa ba saidai tana tausan yar nata dako yaushe cikin bugo mata waya take tana kuka idan sunyi rikici dashi din ta bata hakkuri wai kada aji ai masu dariya saboda bakin kishi.

A karshe dai sai takarda ya mika mata ta bar mai gidansa hakan ko akayi da tace saita haihu zata bar gidan amma ya dauko mata yan sanda da mota yasa aka kwaso mata kayanta kaf a lokacinne gida aka sanda zancen.

Anan kuma bayan dan sandan ya korawa daddy komai yace baison har cikin ya yafe gidansu su rike idan ta haihu nan daddy yace a fada masa bai isa ba ko dan gidan uban waye shi a garin.

Da kyar dai dan sanda dayake na Allahne shi yabawa daddy shawara akan a kyaleshi idan an kwana biyu ko bayan ta haihu a makashi kotu ko kuma da daddy zasu iya hakkuri wata rana dole zai waiwayi abinda aka haifa masa shida kansa gidan.

Dada tace wanan ya dan kwatar da hasumin da daddy din keyi don bata san abinda ya tuno ba da kalamin dan sanda har ya hakkura lokaci guda.

Dada din kuma ta daukemu zuwa dakin Nafisa din wace muka samu kwance duk ta rame ta lalace ba zakice Nafisa bace da akai bukinta lokacin tana baka sha,awa.

Muna shiga dakin muna sallama Dada na fadin Allah sarki kibar kukan nan hakana yar nan tunda ya riga daya cuceki dan banza wanan yasa ake kyautata zurfin bincike akan mutum kafin ayi aure.

Haba Dada ki barta taji da abinda ya sameta koda anyi bincike din tunda Allah ya kaddara hakan saiya faru tsakaninsu ba makawa sai hakan ya faru din.

Tayi hakkuri tabarwa Allah komai ta dinga istigifar ga ubangiji shi zai duba mata lamarin insha Allahu na fada daga inda nake tsaye bayan Dada din mun kura mata idanu muna kallonta cikin tausayi.

Allah ya saka maki da mafificin alherinsa anty ya kuma saukeki lafiya ya baki mai albarka amin na fada ina shirin barin dakin yayinda halimatu itama ta amsa da amin daga bayana har mun juya naji tace Sister nasan dani takeyi don haka take kirana tun zuwan mu gidan har lokacin bukinta din dashi take kirana a gaban kowa.

Najuyo tace idan kinje ki dawo don Allah na amsa da to nafice nikan ina zuwa part din mu na manta da zancen ta don na samu mum tana fama da ciwon kai ko girki bata iyayi ba a ranan gashi kuma ya Addel yana gari yazo .

Hakan yasa na kwabe hijjab dina zuwa kitchen na dora ruwan zafi naji muryanshi a bayana yasa na juyo ina gaidashi yace ruwan zafi nake son in kaiwa Mum tasha magani tace kina nan.

Ruwan dana saka din na debo mashi a cup na hada dana surkawa na gora na mika mai ya karba har ya juya sai kuma ya tsaya yana fadin idan abinci zaki girka ki bari dare yayi zan fita inyo maku take away na amsa da to.

Bayan fitarshi na kashe wutan gas din na gyaro kitchen din na fito na koma wajen mum a falo na sameta zaune da alaman har tasha maganin a lokacin.

Kara gaida ita nayi kafin na kai zaune a gefenta zan fada mata abinda yace saita rigani ta dan dago tana fadin yayanku yace kibar girkin dare yayi ko ?

Nace ehh shine nazo in fada maki tace nima nayi tunanen hakan yaushe zaki gama dare bai maki ba yanzu shida da rabi har ya gwauta ai.

Nabi ta part din hjy mommy ne nagaida Dada sai kuma ta tsaya bamu labarin abinda ya faru da anty Nafisa kinsan Dada bata bari na fito ba ta kaimu wai gaida ita.

Gaskiyane basa so ai dama nasan hakan zai faru tunda basu tsaya sunyi dogon bincke ba a kansa suka dauki yarinya don kada ranta ya baci suka mika mai.

Damani ina ganinsa nasan dan duniya ne don daganinsa irin tashin turai din nan ne ba kwabo komai a sagarce yakeyinsa suko hakan naga bai damesu ba illa murna da sukeyi yarsu ta samu gidan hutu.

Dan gidan nan wani irin hutune bai samu ba inba yanzu da Alh ya kori yan aiki muke yan aiyukan mu da kanmu ba da yan aiki nawa ke gidan nan nasa dai akaji amma da za a zauna dashi shima ya fadi nasa nasan tana da laifi itama.

Bayan sallah isha,i har lokacin ina lake a wajen mum dana shafawa abonake a jikinta don tace ko ina jikin bata jin dadinsa a lokacin.

Ya Addel ya shigo falon da ledoji a hannusa da sauri na mike na karba na aje a gefen mum din fita nayi na wanko hannuna dake warin man na dawo mum ta dago tana fadin na dauka ai plates kije dauko muna.

Na amsa da hannu na wanko mum bari na dauko yana zaune shidai haka halinsa yake koda uwarsa bai yawan magana kamar sauran yan uwarsa zai zauna yayi shiru kamar maraya ashe shi.

Sai uwar ke magana ina shigowa da plate din tace amma kamar wanan abincin yayi muna yawa fa lokacin ya dago yana cire tagumin da yayi din yace ba abinci bane ai mum don nasan da wuya ki iya cin abinci a yanzu.

Ledan nake kiciniyar budewa jin yace ba abinci bane take away na fruit sald nagani guda uku sai dayan leda kaza guda biyu manya irin gyaran shagalinka kudinka din nan.

Sai kamshi ke tashi na dora daya a saman plate din nakai gaban mum din na aje komai a gabanta harda madaran hollandia na lwali kananu guda hudu.

Ina kokarin dora masa ya sake dagowa yace no ki barshi nawa na cikin mota idan zan shiga zan dauka nakune wanan ya fada kamar a gajiye yake.

Mama matso muci kinji ta fada shidai wanan abin da farin jini yake watau don dai nasan ba,a kwana biyu bamuci kazaba amma wanan din na daban ne na motso kamar yadda tace din.

Na mika hannu ina dan yaga naman takai hannu ta dauka mukaji sallaman daddu ya shigo hakan yasa ya dan sauko da sauri yana gaida daddy din da wuni daddy din yace.

Aliyu dama ka dawone ashe to ya Abuja din da fatan ayi nasaran tafiya dai ya dan sosa kai yana fadin dama yanzu nake son in nagama in shiga ina dakon kagama cin abincine sai inje in maka bayani.

Don yanzu shigowana ke nan gidan dazun munyi waya take fada mjn bata jin dadi shine na tsaya nazo mata da magani har na makara .

Ai nazo mata da wani Hafiz ya fada min nasoyo mata tasha da zanshigo ai kace nazo a makare ke nan ashe ka rigani tallafawa a nan suka danyi murmushi yakai kallonshi ga abinda nakeyi yace uwata babu ko tayi ?

Murmushi nayi ina fadin daddy sannu da dawowa yace naki ai baki ganni ba tunda kina gaban uwarki Allah daddy ina jiran ku gama da yayane ingaida kai na fada ina kumshe kaina cikin kunya.

Yau dadi za acine haka ya kara kallon abincin yana fadi mum tace dadi kan ai kullun kana bamu shi gidan nan munaci wanan danka ya sayo muna yace kada kanwarshi tayi girki yamma yayi .

Ka kyauta gashiko dama idan mutum ya tashi ciwo yana jin kawa kaga wanan abinda matasan yanzu basu ganewa ke nan sai su dauka kudi kawai iyayye ke bukata akullum ba kula ba.

A saka makane mum ta fada da sauri ya Addel din yace no ki barshi bari na dauko masa nawa a mota sai in sayo wani .

A,a ka bar abinka wata rana zaka saya min da sauri ya mike yana fadin a,a daddy ya fice daddy ya kai zaune yana fadin yaron nan tausayi yake ban koda yaushe kamar yana cikin damuwa yake ko an tambayeshi yace ba komai.

Shi sam baya da sakewane shiyasa nake fita zancenshi mutum ya zauna kullun shi kadai yayi ta tunane ka rasa abinda yake tunane kuma lokacin yayi sallama ya shigo da ledan irin namu yake fadin daddy akaima can ne ciki ?

Yace miko min nan kafana kafan kayata fruit din nan yafi min komai dadi a cikin kayan nan don ina sonsa sosai su kuma suna kiuyan hada min shi kullum.

Ayya mum ku dinga hada masa don Allah yana da kyau wanda yakai shekarun ku yana shansa kullum don yana kara lafiya sosai a jiki.

Kai rabu da babankun nan fa mum ta fada a daidai lokacin da wayansa ya dauki kara yana kiciniyar fito dashi daga aljihunsa ya kara akunne.

Mu dai munji yace ina zan tsaya kuwa ina nan part din hjy kubura nazo duba jikinta kome tace mun daiji yaja tsoki ya kashe wayan yana fadin mutum bai girma.

Wanda keda tashin hankali haka gabansa zai tsaya wani fadan shirme inba hauka ba ni wai ko malka tana da tabin hankaline dai.

Wani abu ya farune ya Addel din ke tambaya daddy yace ya faru mana yadda suke so dama in mutum yace iyayye basu isa masa ba shiya iya ai karshensa ke nan wahala.

Sai ya soke kai yace Nafusace dai miji ya sako da ciki dazun shine har uwarta taga wurin fadan shirme yanzu nasu na mata marasa hankali.

Innalillahi ya ambata da sauri yace garin ya haka ya faru kuma yace ba ita tace taji ta gani ba da auren bare ga diyan dangi tako ina duk yawan mu kamar kwaekwata wai ace saita tsalake ta auri bare toga abinda ya biyo baya yanzu ai.

Subbanallahi ya sake ambata ina zaune na soke kai a kasa ina sauraren su na kasa cin komai don daddy dake wajen da ya Addel din.

Mikewa daddy yayi yana fadin abin takaici wai kamar Nafisa miji ya sakota taki fita saiya hada da hukuma an mata koran wullakanci sanan ta fito.

Kai abar zancen yariga ya faru yanzu kuma ai mata uziri don Allah taji da abinda yake damunta yawan surutun nan sai kuma ya kara jefata cikin wani hali.

Ko ance din yana maganine yanzu tunda saki ukune ba gyara subbahanallah wanan wani irin wawane shi da zai saki mace da ciki har saki uku ya Addel ya fada rai bace.

Kaddarace kawai amma tun farko mutumin nan yana da matsala ga duk wanda ya kallesa yasan kuma dacewa amma sam Nafisa bata dace dashi ba gaskita abu daine baya faduwa a lokacin aga bakinka ga banza.

Har daddy yakai kofa da ledanshi a hannu ya juyo yace ai yanzu dai ta kare tunda ba gyara kuma yasa kai ya fice daga dakin yana dan lalabawa.

Ajiyan zuciya na sauke a daidai lokacin da mum ke fadin ai abi ke nan in ce mutum ya bari suce bai waye ba toga wayen nan mungani yanzu Allah dai ya sauwaka Nafisa kan yanzu ta zama abin tausayi ga ciki dole a lalabata.

Shiru nayi ina kara nazari kalami kowansu a raina shima bai dadeba ya tashi ya fita yana tajan tsoki nasan abin ya taba mashi zuciya sosai a lokacin.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[2/3, 07:47] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FAKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

14

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Sosai naji dadin fruits din nako bude ciki na dirka naci naman don bambcin da yake dashi da wanda mukeci saboda wanan dai gadashi akayi dan ruwan kazan na ainihi na jikinsa wancam kuma nagida ai soyashi mukeyi wanan ne vamvamci da mutane ke daukin cin nama kasassa wani lokaci saidai da yake ra,ayi ya bambamta wani lokaci kowa da abinda ransa keso.

Mun danyi kallo don da alaman Mun ta samu sauki tun shan magani da kuma mai dana shafa mata banji ta kara korafin wanan ciwon kan nata ba kuma don so dayawa yana damunta gaskiya zakiji ta kwanta tace kai na mata ciwo.

Saura na dauka nasa a fridge kada ya lalace na rufo ko ina muka kwanta don yanzu a daki daya muke kwana tun bayan barin halimatu wajenta.

Da yake washegari ba school hakan ya bani daman samun yin batcin safe sai karfe takwas da rabi na tashi na soma yan aiyukan gida da nasan ni zanyi don nikan gaskiya ba sai an tuna min aikina ba.

Kafin goma da rabi har wanka nayi na dauki kayan karin Dada da muke kai mata irin wanam raman nakaiwa Dada din kamar yadda muka saba duk weelend idan muna gida.

Sai lokacin na tuna da zancen anty Nafisa din na shiga wajenta zaune take bakin gado ta kurawa kasa ido tana tunane idamuwanta har lokacin sunyi hulu hulu dasu wanda ke nuna alaman bata bar kuka ba.

Gaida ita nayi ta dan dago a sanyayye tana amsa min kafin in samu waje a gefenta nakai zaune kasa na dago na kalleta nace.

Anty kiyi hakkuri nasan akwai zafi hakan don anzalunceki amma inkinyi hakkuri kin barwa Allah lamarin sai ya saka maki kan zaluncin da akai maki din daga baya don kukan nan illane yanzu a gareki halin nan da kike ciki.

Cikin dan tausa murya nake kallonta ina fadin hakan sai naga ta fara sauke wasu hawaye masu zafi a fuskanta nima bansan lokacin da hawayen yazo min ba na fashe da kuka.

Ajiyan zuciya naji ta sauke kafin tace dani haba dai sis ke kuma da nake jin dadin kasancewa dake kin dora da kuka ya kike son inyi ni kuma yanzu ?

Jin hakan yasa na dan tsagaita ina hadiyan zuciya tace min a sake alaman ta dan fara saukowa lokacin tace kina jina sis nace gyada mata kai don ban iya bude baki a lokacin.

Tace can you trust me as i can trust you nan ma da sauri na sake daga mata kai alaman ehh ba tare da nadago kai mun hada ido da ita ba lokacin.

Good sis dake kadai na yarda kaf gidan nan kuma kalaman ki gareni da kike tunatar dani komawa ga Allah yasa nake jin dan sauki a zuciyana tun jiya ba wanda ya bani magana mai dadi irinki gidan nan gashi yanzu kuma kinzo kin kara min wani haske.

Tabbas Habbib ya cuceni ba karami ba koda yake laifinane don sonsa ya makatar dani a lokacin har na kasa gane illan abinda yake yawan fada min din sai yanzu nake tuno komai.

Don gaskiya yasha fadain hakan don yaji dadin rayuwansa dani yasa yake ya aureni yasha fada min hakan amma sai ban daukeshi komai ba idan ya fada min wannan lokacin.

Na yarda dake sister dari bisa dari donke din tayuwanki na dabane kin samu tarbiya daya dace ace mun samu tundaga tasowan amma mummy ta kasa gane abinda daddy ke nufi sai son ranmu take bi.

Don da ace tayi tsa AQye ta hanani auren habib da wanan abin duk bai faru dani ba yanzu akwai wullakanci kamar wanan cikin yau in haifeshi sister ba tare da ubansa ba duk akwai wullakancin daya kai wanan.

Anty kiyi hakkuri hakan na cikin jerabawa daga ubangiji ki daukeshi hakan don Allah ki dinga istigifar da haila sai kiji sanyi a zuciyan ki haka malama mu na islamiya suke fada muna sai tayi murmushi donjin abinda na fada din gareta.

Mummy ne ta fado dakin ta bimu da kallo gani ina sharan hawaye tace ita kuma wanan me take nema a nan anty Nafisa tace wurina tazo mana mummy tunda kin ganta tare ta wani daure fuska na mike ina fadin anty zanje in karasa aiki tace ki dawo fa sis nace insha Allah.

Ina mikewa naji mummy na fadin ta dawo tayi maki me kuma kidai baku da zuciya wallahi ina ke ina wanan karamar yarinya kuma har kina jaddada mata wai ta dawo fa tayi maki uwar me a nan din.

Kilama an aikota leken asirine kike wani cewa taje ta dawo to banson hakana kai mummy do lalacewa mai wanan zata zolayeni dashi kuma ?

Ni natsuwan yarinyar nake jin dadinsa kuma haka Allah ya dora min kaunata a zuciyana don Allah ki barmu karkice zaki saka ido ga abinda mukeyi ni banson haka tunda ba yarinya nake ba yanzu dai.

Na dai fada maki kiyi hankali da yarinyar nan don sani da kikai mata don yanzu an lalatata da makirci in kin kashi kikaganta zauna a ciki indai wanan yarce.

Nikan ko wajen Dada ban tsaya ba part din mu na shiga a falo suke ya Addel yana karyawa a sake na gaidashi da ina kwana yaya duk da nasan ba lalai bane ya amsa min amma sai nayi sa,a ya amsa a lokacin.

Ina kika tsaya kuma nace ina wajen anty Nafisace dama jiya tace in dawo ban samu zuwa ba sai yau ba koma sai naga mum tayi min wani kallo kafin muryan yaya ya katseta ga abinda tayi niyar fadi yace OK ta tashine jiya nashiga ance tana barci.

Caraf nace barci kuwa andai fada ma hakane amma ita kan tana nan tana aikin kuka zancen mukeyi da ita saiga hjy ta shigo nafito ke mama ni dai kibi a hankali don Allah.

Ban sanki da jaye jayen magana ba dai kinsan halin uwarsu dai yanzu ba sai na fada maki ba dai don haka ki kula don Allah.

Yanzu mum harda yara za,a hana mu,amula da junansu kema kinsan halin Nafisa ai in bata yarda da ita ba aiko kusa gareta bataga wajen zuwa ba ai ki barsu kawai suyi abinsu ita wanan bata taba yarda da mutum dama idan ba jininta ba.

Kaida bari in tsawata mata ko banza nasu baizo daya da mama ba nasan ko tunda tana wajena ta dauki tsana ta saka mata don ni itama ta iya badon iya ba ko ganinta batayi part dinta yanzu kuma ga Nafisa.

Kai ya dago ya kalloni yana fadin kisan yadda zakibi dasu a zauna lafiya na amsa da to da sauri ina mamaki ashe yana magana mai tsayi irin haka.

Saida ya gama ya mike zuwa wajenta sun dade suna magana a tsakanin su yana bata shawara a karshe take fadin wallahi daga kai sai zainab kuka ban shawara mai dadi a gidan nan.

Yace wace zainab fa tace zainab din mum mana yarinyar nan dake zama da mum ina jin dadin kalamin yarinyar zakace wata babbace idan tana bawa mutum magana.

Kai haba wanan meta sani banda shirme Allah yarinyar nada hankali sosai ta fada kafin mummy ta fado dakin kamar yadda tayi min haka shima tayi masa amma bai

kulata ba don bai tashi ba cigaba sukayi da hiransu kan aiki ta gaji da zama ta mike ta fita wai tana amsa waya.

Halin rayuwa irin na mummy sai a barta irin mutanen nan ne da basu da yarda ko kansu basu yarda dashi ba balle wani ga korafi da cin zarafi ga dan abu kadan idan ya hadaka da ita idon ta zai rufe ta yankewa mutum kauna nan take.

Yanzu kan ko banje gun anty Nafisa ba ita zatazo har part din mu ta sameni ta zauna nan abu ga mai ciki tace wanan take so wancan takeso a kawo mata.

Mum bata faye zama damu ba a irin wanan zaman don ta kula duk tazo sai an turo yan leken asiri azo aga me takeyi a part din zakiga kwana biyu ta dauke kafanta kwana biyu kuma ta dawo muna.

Idan ta dauke kafanta nima nakan da jaye mata a lokacin sai kuma ta aiko a kirani ranan a gaban yan uwa take fadin kai zainab nifa wanan zaman naki ba waya ya fara isata haka .

Ko mutum yana son kiyi masa abu sai ya aiko ko yazo gashini yanzu nayi nauyi tashima yana zama min wuya wani lokaci don haka ina da karamar waya zan baki ki rika yafi mun sauki hakan.

Wani waya anty badai iPhone din nan naki nada ba Asiya ta tambaya cikin kashe yar nasu da idanu tace meye in shine ba nawa bane kuma zan bata.

Ta mike da kyat ta dauko min wayan a dakinta tabani nan na kama murna da jin dadi taban kuma dubu biyu tace nasayi sim nasa da kati nayi ta mata godiya sosai.

Washegarine muna zaune da Mum falo saiga hjy mummy kamar an jefo muna ita falon ina kusa da Mum na mane mata don dadin da uwata bata ban ba na tajani a jiki yanzu ina samu a wuri mum gaskiya.

Lafiya mum ta tambaya a yadda ta ganta ta fado yace gun yarki nazo ina wayan da Nafisa ta baki jiya nace yana daki dauko ki kawo min ta fada a hasale tana gimtse fuska nace to a daidai lokacin da mum ke fadin jeki ki dauko mata.

Kafin in dawo na samu suna cacan baki a tsakanin su mum na fadin kaiyya dadin abidai badai sata tayi ba bata akayi ke kuna jakkadiyan shedan kin hana yar ki alheri.

Zance kike so ni dai waya nake son a bani ba wani abu ba kiji dadin zuwa kulla min sherin da kika saba to van fada ba waya nace ta miko min kawai ba wani abu ba.

Ina mika mata ta fisge a hannuna kamar mai shirim kwata tafice tana fadin haka kawai ni ba a kawo min iskanci ai ke kuma kinci bashi don nasan nayi kike nema yanzu tana fadawa mum din tace tafican mara ta ido kawai.

Ta dawo gareni tana fadin ke kuma kingani ai saida na fada maki kibi sannu da mutanen banzan nan kina ganin kamar ina son in rabaki da yan uwankine togashi kin gani da idanun ki.

Har kuka sai da nayi don waya akwai shiga rai sosai dan kwana dayan da nayi da ita har na fara sabawa da wayan tun lokacin kuma zancen ya fice min a raina.

Ban kuma nunawa anty Nafisa komai ba kan wayan zata sakani aiki in mata ta kuma shigo wajen mu nan wajen mum tayi yadda takeso ta tafi abinta.

Bayan kamar sati biyu sai gata tunda safe su ya suna zaune suna karyawa ta shigo bayan sun gaisa take fadin ina zeey tana ciki mum ta fada ta nufi ciki sai gani muka juyo zuwa falon da ita.

Nan take fadin wai ashe mommy tazo ta karbi waya a hannun ki ban sani ba kuma baki fada min ba akan me kika bata tunda ba ita ta baki waya ba watace fa don me zata karba taba Asiya Asiya ta fiki garenine ko me ?

To nan tazo muna da tashin hankali a bata waya ni kuma nace ta dauko mata ta bata ta fita tana zage zage ba wanda ya kula tana kallon mum din kafin ta juya wajen yan uwarta tace .

Wai me yasa mummy take hakane for god sake bana son irin wanan abin ta sani daddy ma baya so to ba zan ba Asiya wayar ba tunda ba wani ya saya min ba.

No ki bar mata ita ta bari zan sayo mata waya idan na fita shike nan don Allah abar zancen ya tafi a haka please tayar da zancen yana iya kawo matsala kuma a gidan nan yanzu.

Kinji dan uwanki yace abar zancen nima ban faye son ta rike wayan nan ba yanzu tunda karatu takeyi gaskiya no bari dai a saya mata tunda duk yan uwanta suna da waya itama a saya mata din ya fada.

Sai ta juya ta fita ya juyo gareni yace wani irin wayane mummy ta karba nace ko iPhone nawa karama daice naji su halima na fadi mum tace kaji wata shegiya nan halimatu din nan bansan me kika tare mata ba a gidan nan.

Anyi hakan koda zai dawo sai gashi da waya ya kawo min ina falo ya jefo min ledan saman jikina yace kardai ki biyewa waya ki bar karatu mum tace nina sagartaki da waya ya juya ya fita.

Ihun murna na sake jiki na rawa na fada jikin mum ina rawa tace ohh abin naki ya zama shegantaka yanzu na karbe wayan naga tsiya kuma nan na shiga rokonta murna ya hana bakina rufuwa a lokacin caji nakai na saka wayan.

Anyi hakan da kwana daya saiga mahaifiyar halimatu wai tazo ganin uwarta Dada har part din naje na tareta amsawan da tayi min ba yadda muka saba da ita bane.

Zuwa yamma da mum tashiga saiga mace ta fara yankar kauna tana fadin dama da biyu tazo garin nan ke kubura ki fada min tsakanin Zainab da Halimatu wayafi galihu a gidan nan wajen ku.

Ina dai zariya daya muka fito nida mai gidan nan mum tace hakama aida uban zainab ko don banga bambamci a tsakanin ku ba kai har mu tace ato uwa daya dai ta haifomu dashi ko don haka banga dalilin da za a saka min ya gaba da bakin kishi ba.

Zainab don ta iya makirci da kisisina tabi ta kammale ku babba da yaro kun mayar min da ya saniyar ware a gidan shine nazo in kafa sheda don ku sani ita ma dai nan gidan kawuntane ehh,hey.

Au da kice don ni kikazo ashe tace bake daya ba wallahi dan kowa nazo ke can kin koreta saboda taki yarda ta zamo boyi boyin ki nan kuma data dawo suma sun tasa min ita agaba.

Au abinda ta fada maki ke nan dama to inkin dauka haka din ne saidai ki sani ni ban dogara ga aikin yaro ba gasu nan ki tambayesu kiji mamace dai wanan kamar yadda kika fada kuma nima inada iko da abina.

Jin hayaniyarsu yasa hankalin mutanen gidan ya dawo gunsu har Dada dake waje tana gugan goro da zata watsa a bakinta tana fadin me nake gani nake kuma ji hakane ke Atika ?

Barta hjy tace da biyu tazo gidan nan saboda mu don mun saka mata ya a gaba da wullakanci ehh haka nace ba,ayi hakan bane dama ta fada a gadarance.

Atika ki daiyi da mai kalan diya mata amma bani ba don nawa da Allah ya ban sun isheni tinkaho a ko ina a garin nan don ba sai naje ina karamin murya kwaso wasu diyan ba .

Sai fadan ya rikice masu tsakaninsu su uku kuma Dada tayi rabo har ta gaji ta fashe da kuka sai anty Nafisa ta daga waya ta kira daddy a kasuwa ta fada mai sai gashi yazo rai bace.

Bai tsaya tambaya ba don Nafisa ta fada mai abinda ya kawo rikicin don haka yana zuwa yace Atika ki tattara kayan ki da yarki ku bar min gidana a yau din nan basai gobe ba.

Nan kuma Dada tasa mashi kuka tana fadin sai dai suje tare ina zasu da daren nan ga yara dole ya barsu akan washe gari zasu tafi har halimatu di dake ta kuka wai bata zuwa saboda rashin zuciya.

Ni dai ina part din mu tunda ba abin kallo bane nan aka zauna bayan sallah isha,i daddy ya tambayi ba,asi mum ta mayar mai da komai tun farko tunda itace babba a cikinsu.

Ya juyo kan halimatu yace yau ga ranan magana tunda kikazo gidan nan Kubura ta taba koranki a part din ta ki fadi yau ta girgiza kai yace ba kai nake son ki girgiza min ba ki bude baki kiyi magana.

Tace bata taba ba to meyasa kibar part din bayan kinsan nan na ajeku wurinta yar uwarku ta tsaya ke kuma kika canza sheka dama irin wanan rana nake jira yazo ai .

Sai ta dukar da kanta kasa yace magana zakiyi ko gobe tunda safe in sakaku motar katsina daga ke har uwarki wallahi jin ya ambaci wallahi yasa ta dago kai ta kalleshi tana dan kokarin budan baki tare da fadin dama dama naga tafi son zeey ne yasa kawai nabar part din.

Dole inso mama tunda ke,,,, dakata don Allah banzo gareki ba ya fada sai mum din tayi shiru tanawa yar uwarki wani abune ke batayi maki ba ?

Ta girgiza kai to ya kika gane tafi son mamana dake nan ma shiru tayi to tunda baki da amsa kuma ba koranki akayi ba akan me zakije wurin uwarki kiyi hadi ?

Nifa yaya bashi ba gidan nan kaf an saka mata Ido sai a gaban idon ka ake nuna anasonta har satan nama da kudi da tufafi saida malka da yaranta suka dafawa yarinyar nan.

Gashi kullun hjy malka da yaranta komai zasuci ko susha itake dafa masu amma hakan baisa sun ganewa yarinyar nan ba.

Kutuma wace yarinya ke muna wanan aikin wazaici girkinta ko jagwalgwale amma kin rainawa mutane wayau watau kinzo fada daine akan yarki.

Meya rabata da part din hjy kubura idan ba son jiki da munafunci da kika koya mata bandashi bata iya komai ba a rayuwanta.

Idan kince hakan gaskiya kika fada nazo nan da biyu kai kuyi min shiru gobe ki shirya keda yarki ku koma gida ta huta yiwa mutane bauta a nan shike nan daddy ya fada masu.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[2/9, 09:51] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

An samu an sulhuta da kyat bayan yan kokekoken daya biyo baya tsakaninsu kan cewa zata zauna tare da Dada a part dinsu tunda dama a wajen Dada take zaune din.

Don Dadan ta nuna cewa tashin tashinta idan ya kori Halima din da a yanzu nida Dada muka saura kiranta da halima ita Dada sai tace halimatu din nan niko ina fada ta dinga fada dani ke nan wai ina bata mata suna.

Don yanzu ta koma amsa Sadiya a school su kuma yan gidan daddy din yan gayu suna kiranta da Sady cool sunan da takeso ke nan fiye da wanda ake kiranta dashi da baya.

Ga karyan tsiya tana nuna ita din diyar cikin daddy ce ta dinga shara karyan arziki saidai azo a tambayeni ince ehh hakane din amma kowa yasan ni iyayyena suna katsina don ko a hausa na suna gane cewa lalai daga katsinan na fito.

Saboda hausan namu ya dan bambanta da nasu kanawa kamar yadda hausan kowani dan state ake saurin gane jaharshi don harshe da dabi,u yakan bambanta.

A cikin wanan dan takin mahaifana suka dawo kano da zama a cikin gidan da daddy din ya gina masu wanda wasu yan uwa manya sukayo masu rakiya har zuwa kano din.

Naji dadin wanan abin duk da dai ba,a wajensu zan zauna ba amma munje nida hjy Mum mun dan dade a gidan tare dasu naga kannena sun kara min girma sosai

yayin da baba bai boye jin dadin ganin yadda na koma ba yanzu a hannun Hjy Mum dake rikona.

Don nazama wata babba dani komai ina yinsa cikin hankali da wayewa wanan yasa iyayyen nawa jin dadin ganina din da sukayi a lokacin.

Ana sallah azahar nice ma na matsawa Mum da mutafi saboda ranan mum ce zata bawa daddy abincin dare don haka muna da aiki da zamuyi idan mun koma din.

A bakin Hjy Mum da suke zance da diyata naji irin rikicin da akayi da hjy Mommy da daddy akan dukiyan da daddy din ya warewa mahaifinmu da sunan ya bashi su halal malak har gaban Allah.

Wanda hakan ya tunzurata ta shiga ballawa daddy din miyagun magana marasa daddy har abin ya kaisu ga saki a tsakaninsu sakin ma kuma na tijara da har yasa ta bar masa gida wanda sai a lokacin nasan ashe mommy din wai bata gidan na daddy.

Allah shedata banji dadin jin wanan maganan ba duk da ba,a kan baba kawai ya faru ba amma kusan hakan shine sanadin faruwan komai a tsakaninsu din.

Nan na barsu suna hira na dauki abincin Dada don in kai mata don ina son in dawo in wanke uniform dina da ban wanke ba a ranan kafin dare yayi sosai duk da ina da wanda zan saka a jikina din.

Tunda na doso part din nake jin muryan Dada yana dan tashi da alaman fada takeyi da wani a lokacin har na karasa na kai abincin can ta baya dakunan da su Dada din suke zaune wanda aka gyara mata shi don an saka komai irin su kujeru tv capet da sauran abubuwa wanda a takaice dai daddy ya dauko gyatumanshi ya dawo da zamanta yanzu a kusa dashi ke nan ba zancem komawa katsina kuma a wajen Dada din .

Duk wanan yana cikin tashin hankalinda mommy din tayi da daddy har yaja mata saki a cewan bakunan su wai mommy tace don daddy yaga baida lafiya shine yake rabar da dukiyanshi ga yan uwa don yai masu keta su iyalanshi yana kwasan dukiyanshi yana bawa yan uwanshi da sunan taimako.

Idan ba aikin asiri ba wani mai hankali zaiyi wanan abinda daddy din keyi don haka ita wallahi bata yarda da wanan tsarin daya dauko yi ba.

Saidai in hakane ita ma yayanta ya ware masu nasu kason ya basu tun yanzu kowa ya rike a hannunsa mamaki kwarai daddy din yayi da kalamanta din gareshi.

Har ya dago yana fadin waiko malka kina cikin hankalinki kuwa ko so kikeyi ki konani da gaske ki hana min lahirana a sanadin ki ranta ya baci tace ina ruwanta da lahiranshi ita su dai ya basu dukiyansu kafin asiri ya kara kan mashi ya kwashe komai ya rabar.

Wanan kalman ya harzuka daddy din da ita har yace ke malka kije dai yau na sakeki tunda nagane badon Allah kike zaune dani ba dai.

Dama kowa yasani an fada kuma tunda kika aureni cewa don dukiyana kika aureni tunda da farko aida banda komai kina kikayi sai daga baya dana dan fara dagowa kuka shiga kuka fita har na aureki keda iyayyenki.

Ita kuma tace dashi dadin abin dai ba ita kadaice iyayyenta suka iya shige da fice ba wajen malamai shima nasa iyayyen ai sun iya don suna mata kuma tasan komai kan hakan.

Yanzu ma mommy dince ta shigo gidan ta tayar da zancen tana surfawa daddy din zagi shi da yan uwa da mugun kalamai wanda ran Dada din ya baci na yadda tazo tana aibanta mata zuria har yakai ta tunzura ta biyewa kalaman nata sun rikice.

Ban shiga ba ina ajewa na juya zuwa part dinmu koda naje ban fada ba sai da ta jiyo hayaniya ta fito ta samesu ida Dada ke fadin ko an raba an baki kason nawa zaki samu marka ?

Mai yaya maza a gida ta kyale taja bakinta tayi shiru saike mai gayar yaya mata saboda kwadayi zakice sai an raba dukiya anbaki kar ya kare.

Su yaya matan ba mutane bane Dada diyan suka fada nan dai suka tararwa Dada din da yake ta iya ta biye masu suna maida kalamai a tsakaninsu din.

Anty Nafisa ta fito da tsohon cikinta daga daki tana fadin haba mummy wanan abin kunya da kike ja muna fa daddy fa hakkin zumunci yake kokarin fitarwa yan uwansa .

Ina dai kudin nan nasane shiya nemi abinsa don haka ki kyaleshi kisa masa ido ko duka zai raba masu kudinsane ai mommy.

Kuma ya fada min cewa kwangila yayi mai tsoka ya samu alheri ya roki Allah ya yayi mai mafita dasu har dabaran yin hakan yazo masa.

Don Allah mommy ke ba mai taimaka masa bane wajen yada wanan manufan nasa na alheri a garesu tunda kema harda yan uwanki aikaiwa alherin nan bafa nasa kadai yabawa ba kudin nan har naki yan uwan.

Don daddy yaiwa yan uwansa hidama da dukiyarsa a yanzu shine zai rage dukiyansa kome har kuke wanan abin kunyan kuma a yanzu bakuyi saki a tsakanin kuba a da sai yanzu yanzun ma din ace akan alheri mum kada abinda yan uwa ke fada a kanki ya zamo gaskiya fa.

To uwata imun fada keda kika san gaskiya har kike fada ni kinsan bansan wanan ba ai saikin fada a yanzu zan sani tunda dama yan uwana fadi a kaina .

Ayai kiyi hakkuri mommy ban fada don ranki ya baci ba ai don Allah ku bar wanan abin na zauna yau da safe da daddy akan yayi hakkuri ya barki ki dawo dakinki ki zauna yanzu kuma ki shigo kina wanan masifan ai kinsan ba zaiji dadin hakan ba har ya hakkura din.

Kallon hjy mum tayi datake tsaye yar ke wanan kalamin a gabata sataji haushin hakan nan take ranta ya kara baci ita ko Nafisa din ganinta bai hanata fadan abinda take fadawa uwar ba don hakane uwar taji mugun haushi tayi cikin diyan da zumar dukanta sai muryan danta mukaji yana fadin kada ki tabata mana mommy.

Kinsan dai anty Nafisa ba zata fada maki karya akan daddy ba nima na sameshi ya fada min sun zauna da ita don shi kikaji na kyale zancen hakan .

Alokacin hjy mum ke bawa Dada hakkuri ta fita part din ta koma nata don Allah abar zancen a sasanta a tsakani tunda yara har sunsa baki a zancen.

Wani juyowa da yayi ya watso muna harara hakan yasa da sauri na labe a bayan hjy mum dake kusa dani tsaye ina satan kallonshi ta bayanta.

Ku,kuma me kuka tsaya saurare ya fada a cikin tsawa yana zare idanunsa garemu hakan yasa hjy mum fadin kubar wurin nan na juya da sauri na riga kowan mu fita daga part din ni dai har nakai ina jin muryan mommy a lokacin .

Barcine ya daukeni a fslon hjy mum din ban sani ba wanda har suka shigo suna dan hayani hakan ya tayar dani daga barcin dana samu inayi din a lokacin.

Saidai ban motsa ba illa ido dana bude yayin da nake gane da yaranta take wanan zancen a lokacin don muryoyin su da nake ji na gane hakan tana fadin lalai yanzu na yarda hjy malka akwai jahilci a lamarinta sosai.

Mum ki daina biyewa wanan macen kin dai ji yau metake fada da bakinta yau din ma ni sai naga kamar bata cikin hankalinta babban ya fada yana kallonsu.

Ba dole ta koma haka ba tunda tana ganin hakan ba zai taba faruwa ba kuma ya faru yanzu zata karasa halaka kanta wajen yan bori da yan tsubu tana ganin wani ya saka hakan ya faru gareta.

Ba,abinda zai sameki mum tunda baki mata ba ya fada yana mikewa lokacin wayana yayi kara na mika hannu ina dauka duk suka kalloni danna dauka nayi ina fadin inna ina wuni ta amsa min sai kuma na sake fadan gata na mike ina mikawa hjy mum din wayana.

Ke ki kawo min abinci ya Nasir ya fada a lokacin da nake shirin mike tsaye daga gefe ya Addel ke fadin baka san sunan ta bane yau kuma zaka kirata da Ke.

Baidaiyi magana ba nima ban iya amsa mai ba na shige ciki bandaki na shiga na kewaya kafin na hada mashi abinci nakai mashi wayan nawa har lokacin tana hannun mum tana bincike a cikinsa.

Nasan tana dubane kona saka wani abinda bai dace ba da shekaruna baikai dauka ba a lokacin wanan bashine karon farko da hjy mum takan dauki wayana ba kusan ko yaushe tana dauka tayi bincke a cikinsa.

Alhalin banda komai a ciki sai yan cartoon da film din hausa irin na ibro yan gajeru na ban dariya number kuma baifi na mutum goma bama a lokacin da nake dashi na iyayyena sai nasu mum din dana kawayena shima ba mai yawa ba dai hakana.

Zama nayi ina fadin wallahi wancan mugun ya firgitani mum na dauka dukan mu zaiyi ai yadda ya kallomu din nan tace hauka yayi da zai dukeki kawai bacin raine suma yake damunsu a yau yadda uwar keyi din nan.

Koda yake shi dama yana yarda da haukanta ba kamar Nafisa yake ba don ita tun tana karama bata yarda da wanan shirmen nasu dan dama shi haka kawai yakan dauki fushi dani wani lokaci kamar ba namiji ba.

Ya Nasir daya fara cin abincinsa ya dago yana fadin wai Hafiz take zance dama ai dama ya bal,balaku tunda gulma kuka iya da kunji kyasham ba,a rigaku zuwa kallo.

Dan marairaicewa nayi ina fadin hai ya Nasir ni yaushe nake irin wanan da har kake mun fatan wanan gabjejen katon ya dake shifa yana da saurin hannu hakan yasa nagudu tunkan ya karasa rufe bakinshi.

Suka kwashe da dariya Mum tace wai kin ko san wanan ya mari mutum ai sai jinya nace nima tsorona ke nan yasani shan maganin dole ban shirya ba.

Motsaraciyar banza watau mukika raina dama ko ince ni da bakya tsoro nace kaima ai ina tsoronka yaya na daifi tsoronsu su biyun nan shida ya Addel don ko yaushe fuskansu a daure yakesu.

Ni dai ban kara jin zancen mummy ba gashi har yaranta sun fara ba mutane tausayi a gidan don yadda kallo daya zakai masu kasan suna cikin damu da kewar uwarsu.

Zuwan su baba gidan ranan sun dade da daddy a falonsa ina ta dakon jin yashigo part din amma har yamma saina gane sun gama ganawa da daddy sun tafi don haka na debe rai ga ganinsa a ranan .

Sam mum bata koya min zuwa gidan mu wurin iyayyena ba koda zamuma a tare muke zuwa mu dan dade kan mu dawo gida da tare da ita kuma don haka ban ma samun wani sakewa a yanzu da iyayyena din.

Hjy Mum gaskiya tana kokari matuka dani wajen nuna min kauna da sakani hanya ta yadda ba zan wahala a rayuwa ba nan gaba.

Ma,ana dai ta mayar dani tankar yar cikinta data haifa hakama diyanta sun daukeni kanwarsu sosai ko don ganin yadda uwar ke min ne son basu son suga ko

hjy mum din ta bata min rai balle wani a gidan nasu yace zai saba min sai inda karfin su ya kare a kaina.

Muna hutune don haka ba fita muke ko yaushe ba muna gida sai islamiya da yanzu ni kadai keda kokarin zuwa ko yaushe sauran sai sunga dama suke zuwa tunda daddy ba mazaunin gida bane shi .

Ranan na dawo daga islamiya na samu mum bata gida nayi mamaki don haka naje part din su ina tambaya suke fada min sun kai anty Nafisa asibiti wai zata haihu.

Nayi murnan jin hakan da suka fada din sosai don haka na samu waje na zauna a nan din tunda Dada ma bata nan tare suka tafi da ita donshi na zauna a nan din ina mai mata adduan sauka lafiya a zuciya.

Don nasan hakan tun ina karama a kauye da baffa Ado yayi aure wajen haihuwan farko amaryan nasa mai kyau da ita ta mutu abin ya tsaya min azuciyana don na kasa mantawa da hakan.

Ajiyan zuciya na sauke kafin na mike na fada dakin anty Nafisa anty Nafisa badai kazanta ba kan na fada a raina don dakin ga komai nan a yashe kasa ko ina ka duba kayane datayi amfani dasu ta kasa daukewa zuwa muhallinsu.

Tsab na gyaro dakin har bandaki da ko ina sau daya Asiya ta dan lekoni don jin motsina datayi a dakin taga ko waye a ciki take fadin au kece ashe kina da aiki kuwa indai dakin nan ne .

Don har pant sai kinci karo dashi a dakin nan indai Anty Nafisace zaki ganta a waje tsab amma a gida kuma kazan kazan da ita bata daga hammata ki shaka wanan ya san ban dariya ta fita tana tabe baki wai kazanta ance gwano baya jin warin kansa tunda kusan duk haka suke.

Don basu koyi ko kawar da kara da kansu ba yan aiki ke masu a baya saida fitinan mummy yayi yawa daddy yace ba zai kara daukan masu yar aiki ba kuma kowa ta sallami masu aikinta.

Da farko suna ganin ai hjy mumce zata sha wahalan haka sai gashi sule wahala a yanzu son ko basu saba ba don haka basa iya kula koda muhalinsu a yanzu.

Sunkai awa uku sai gasu sundawo da ita wai ruwa aka kara mata malaria ke damunta ashe haka muka kewayeta a falon mummy muna mata sannu tana amsawa da kyat.

Yayin data yunkura da kyat tana tashi gwanin tausayi ta nufi kofan dakinta duk muka bita da kallo lokacin hjy mum kece min ai ina can ina tunanenki don nasan yanzu kun dawo daga school din zaki samu kofa a rufe.

Nan nazo na bata amsa yayin dana gusa ina karban ledan hannuta wanda lemune ne a cikinsa mai yawa ta sayo don naga an aje wani a part din su anty Nafisa din hakan yasa na juya da zuman in karbi na hannun mum din.

Sister kin shigo dakin nan ko muryan anty Nafisa ke fadan haka nace ehh na zata ai haihuce zakiyi don shi na gyaro dakin kada baby yazo ya samu dakin a haka .

Wai kekan kina da bakin iyayi wallahi kamar tashin kaka duk wani zance da iya fada a bakinki ake jinsa mairo ta fada tana jan tsuki a,a yanzu kuma meya kawo wanan maganan .

Idan ta iya fada a cikin hikima ba kacaba irin daku kuka gada don ku kome yazo a bakin ku haka zaku iya fadawa mutum shi a lokacin.

Don ta gyarawa yar uwarku daki haka kuma laifine ashe don baku raina abin wullakaci ku ko yaushe kuna gadara ana zaune gidan ubanku to uban naku bai iya raba daya biyu ba kamar yadda kuka iya.

Dadace data kai kofa take fadan hakan ga mairo itama kai tsaye nan mairon ke fadin gawa muka gaji hakan agunki ko cikin jin haushin abinda Dada ta fada mata.

Haba don Allah baku bari wanan zancen meyasa kuke hakane ta kallo inda nake tana fadin mujemu kiyi min abu ni dai muka fice muka barsu a nan har Dada don tana gaban mu muna bayanta muka fita daga part din.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[2/14, 11:11] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

17

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Alhamdullahi yanzu dan dawowan mummy din nan zance don ta rage tsiwa da jiji da kai din nan nata a yanzu sosai don haka fitina da yawan tashin hankali ya ragu a gidan yanzu sosai.

Yadda na lura ayanzu hjy mummy din bata da wani power yanzu kamar da datake shimfida ikonta da mulki iya son ranta kamar sunanta Malka.

Don a yanzu daddy kamar bai damu da ita ba a gidan ta zama powerless ga komai yanzu haka zaliki a yanzu na kula komai kamar da hajiya mum yakeyin shawaransa saiko ya,yansa.

Don ko yana kasuwa kan ya dawo zaiyi waya da hjy mum yafi a kirga kan abinda ya shafi rayuwansa na gida dana kasuwa ranan ma ina zaune inawa hjy kitso ya bugo hakan baisa ta tashi don kada inji me zasu fada ba.

Complain yake mata a cikin tashin hankali cewa kaninsa dake Enugu ana fadan kabila a can yanzu haka suna kulle a cikin gidajensu kwana biyu ke nan basu fita ba har iyalansu.

Nan mum kebada shawaran su samu hanya su dawo arewa kawai yafi masu sauki da zaman dar dar a can kullun daddy yace nima haka nagani zan kirasa yanzu na fada mai shawaran dana yanke akai din.

Saidai yayi warning kada abar Dada taji wanan zancen don kada hankalinta ya tashi takuma dagawa mutane hankali ana cikin wanan kuma naji mum tace ina fa ai gara ta gansu kawai sun iso shine kwanciyan hankali a yanzu garemu sukai adduan Allah ya fito dasu lafiya har nima dake tsaye bayanta ina kai tsoron kintson na amsa da amin lokacin.

Kingani ko shiyasa zama a cikin kabilu wani lokaci badai dadi mutum at list ya bar rabin iyalinsa anan arewa rabi kuma na can komai zai faru sai yazowa mutum da sauki amma irin wanan ina dadi duk suna can har shi cikin halin hau,ilahi hannu a gaba.

Washegari kuwa naga an fara gyaran part din dake gefen Dada nasan ko a nan zasu zauna ke nan sai a lokacin nagane hikimar masu kudi da suke gina babban

gida ka rasa me mutum zaiyi a cikin katon gida yanzu na fahinci hikimarsu nayin hakan sai kamar bayan kwana hudu suka iso kano.

Alokacin duk su daddy har matansa sun gama rudewa da halinda dan uwa ke ciki can lokaci lokaci mahaifina zaizo koda safe koda yamma su dade da daddy din nasan suna shirya yadda dan uwan nasu zai fito ne da iyalin nasa.

Allah ya taimaka suka fito lafiya tare da matansa biyu da yayayensu sun iso kano a wahalce gidan daddy din duk sun fice hayacinsu suna bada labari a firgice na irin tashin hankalin da suka gani a can din.

Ni ina school saida muka dawone muka samesu sun iso suna falon mum zaune sunci abinci sun bata waje suna hayaniya da yaransu a sanyaye nayi sallama nashigo.

Duk suka juyo suna kallona gaidasu nayi kafin namike zuwa ciki don in sauya kayan jikina muryan watace ke fadin wanan a nan gidan take itama ?

Ehh diyar Garbace dayazo dazun mana nan take zaune a wajen mai shiyan nan matar tafadawa yar uwarta dake zaune ishishire kasa saman ties din falon mum da alama a gajiye suke lokacin.

Nidai nayi ciki jin motsina da mum tayi yasa ta fito tana fadin kin dawo mama sai kuma kika samemu da baki nace wallahi fa nagansu a falo ai tace matan babangi Ahmed ne dake Enugu sun samu sun fito.

Allah sarki wai munyi barka da suka fito lafiya na fada na shige dakina Allah yagani na debo gajiya sosai ga yunwa a lokacin don haka yasa banson komai ko wani dogon hira a lokacin.

Saida na shiga na tube mafito don in debe abinci inci saidai babu komai duk sun cinye haka yasa na koma ina fadawa hjy mum ban samu abinci ba.

Take fadin abincina yana nan cikin farin kula ta dora sama na koma duk na burkuce kayan kitchen din banga abincin ba na koma na fadawa mum tana jan tsuki da fada ina son na hanata hutawa kawai.

Tana zuwa idon ta yakai wajen abinci yace daukeni inda kika aje salati mum ta saka tana fadin yanzu wayiwa yarinyat nan haka don Allah ko abinci nace za a dafa mata yanzu kafin ya dafu ai wani aikine kuma.

Hjy abu kuke nemane dayan matar baba da sukazo yau ta tambaya sai mum ne ta juyo tana fadi wallahi abincin yar nan dana aje shine ban gani ba.

Au ko shine shamsiya ta dauko a kitchen dazun da tace bata koshi ba kinsan mun jima ba wani cima mai kyau a cikin mu na tsawon kwanaki.

To amma ai da sai ku tambayeni tunda sai kuma tayi shiru ta juyo gareni tana fadin kinga muje ki samu abinda zakici a daki nabi bayanta daidai ina shiga wayata dake dakin mum aje yafara kara na dauka.

Anty Nafisace ke magana tana fadin tana nemana don Allah yanzu a part dinsu nace ganinan zuwa nake fadin antyce ke nemana wai inzo yanzu don Allah.

Kije ba tare da kin samu abinda kikaci ba nace barin dawo mum nafada ina fita daga dakin nata na nufi wajen kiran da ake min din tana zaune a falonsu ta mike kafa kodana shigo tace yauwa sister don Allah magani nake son ki karbo min tafada a kasalance.

Magani wani kala anty dauko min bag dina a daki in baki kudin tun dazun nake neman mai sayo min maganin nan ban samu ba, bag din dana dauko mika mata karba tana budewa yan naira dubu ta miko min tare da kwalin maganin.

Bayan na karba na juyo naji muryanta tana fadin sister meya faru naga kamar ranki a bace mana ba komai anty banci abinci bane abincin da Mum ta aje min wanan bakin wai sun dauka sunci.

Haba dai is undead kashe ki suke son yine don Allah ya zasu daukar maki abinci zo zo nan ta fada tana mika hannu gareni ga cikinta da yai wani kato a gabanta nace cikin yar murya No barshi kawai inje na sayo maki ai.

Ban jima ba na dawo daga sayen maganin har canji na mika mata lokacin kuma yaron dake dan zirga zirga ya dawo daga aiken da tayi mai don bata da aiki sai faman aike da kashin kudi shiyasa bata shiri da kannenta ko kadan a yanzu.

Mika mata Allah yasa dai ki iyaci ta fada tana kokarin bude ledan maganin dana sayo mata din tasha kaina girgiza ina fadin ki barshi No kefa nasa ya sayowa shi dama.

Lokacin na dago kai ina fadin nagode na juya zan tafi take fadin idan kinje can zasu bari kici kuwa don haka suke dama kamar yan yunwasu balle wanan abin ya faru zan shiga daki naci na fada ina juyawa na fice.

Banci ba saidana biya wajen mum na nuna mata tare da mata bayani ta danyi shiru kafin tace jekici ai Nafisa bata da wani manufan sheri akan mutum ita.

Wani lokaci idan Hjy Mum tana irin zancen nan nakanji haushin hakan a zuciyana sai in dauka dukkansu dai suna da bakin kishi a zukatansu kome basu da yarda a kan dan uwa dukkansu din.

Ta ya daga ban abinci zata furta rashin yarda alhalin tana kwance a inda na barta ita bataje nema min abinda zanci ba an ban kuma tace wai tana zargin abincin bayan a gaban idona aka sayoshi ina kallo ko karban ledan take away din batayi ba.

Haka gidan ya koma family house don saida suka share kusan kwana uku a tare damu kafin su koma part din da aka gyara masu din da zama suka barmu da aikin gyaran waje.

Saida hakan ya dan sani zazzabi kwana biyu don komai dagani sai mum keyi daga su har iyayyensu suna zaune suna kallo ko hira kafa mike abinsu.

Munyi barka komawansu wajensu din don yanzu ko hayaniya da koke koke yai muna sauki ko haka kawai zakiga danbe ya kicime a tsakaninsu zakice su din diyan yarene ba hausawa ba wallahi.

Don dabi,unsu sam baiyi kama dana dan bahaushe ba gasu a tsatsaye koga iyyayansu wanan yasa na kara nisa dasu din don ko hjy mum da taga zasu shige min yanzune zata kirani ta sakani wani aikin da zai dauke min hankali.

Don yaro ya zagi uwarshi ko kuma yace yayi fushi yana kaiwa uwa duka itako tana dariya adole ga yaro su iyayyen basu dauki hakan komai a wajensu ba.

Gasu dai tsab a ido amma kan gaskiya halin ba kyau ko kadan suna da saurin fita ran mutane don wanan halin nasu naba kwabo a garesu .

Ranan da suka koma din wuni mukayu muna gyaran part din mu wani abin kn saidai hjy mum din tayi hakkuri dashi don sun halaka mata kaya ko yaro ya dauki abu zai barnata uwa bata iya tsawata mashi sai idan yayi barnan kaji ana fadin kai dan nema kawai zan dukeka/ki fa.

Da yake weekend ne mun gama na dan kwanta don in huta sai barci gashi kuma nayi wanka a lokacin sai kawai kasala ya sauka min shine na buge da barci nayi sa,a kuma hjy mum bata tayar dani ba a lokacin kodan tasan na debi gajiyane ta barni oho ?

Karfe biyar na tashi a gagauce ina duban lokaci a dan zabure na mike ganin lokacin danayi na nufi bandaki na dauro alwala sallah na tayar ranan ba zancen zuwa islamiya awajena.

Falo na fito na leka mum bata ciki hakan yasa na nufi kitchen nan ban ganta ba sai na tuno ranan itace zatayi girkin daddy watakila tana part dinshi kuma tana gyara ga girki dai ta dora amma bata nan cikin part din namu.

Tsayawa nayi saidana tuka tuwon tare da hada miya lokacin tashigo a gajiye tana fadin yar albarka kingani na gama wanan na dan shiga wai in rage aiki bakiga uban aikin dana sama ba kuma a can din.

Taja tsuki tana bude kulan dana kwashe abinci zuwa lokacin ledan yayi sutum sutum ciki ya dauki zafi ga tuwon na kwasheshi yan madaidaita daidai cin mutum daya.

Mama ke kan kin huta mijinki baya shan wahalan abinci da gyaran gida komai da akeson ya mace ta iya kingama iyasa Allah ya baki miji dan albarka irin ki sai na turo mata baki hakan nakanyi a duk lokacin da tayi min zance irin hakan.

Niga nawa watauna na tsani aure ayanzu tun akan abinda ya samu anty Nafisa yadda naga suna soyayya da mijinta amma a karshe suka kuma rabu rabuwa mai muni a tsakaninsu.

Hakan yasa a yanzu nake jin na tsani zancen aure ban ma taba kawowa kaina wani zancen aure ba can balle har naji ina son yinsa din a kaina.

Mun karasa kafin magariba don haka a nan baya na dauro alwala nashige ciki ban kuma sake fitowa ba don nasan ranan kwana ni kadai zanyi a part din tunda Mum kila part din daddy zata kwana.

Kwance nake falon ina kallo sai wayana dake gefe ya dauki kara na dan dago ina dubawa Anty Nafisace don wani lokaci takan kirani hakan tace inzo in karbi wani abu a part dinsu.

Nasan kuma ranan bamu hadu ba ko donshi zata iya kirana a lokacib tayi min korafin hakan tace na manta da ita ko naki zuwa inga lafiyanta.

Na mika hannu nayi receiving ina fadin Ayya anty Nafisa wallahi yanzun nake zancen ki a raina yau aik,,,,, muryanta naji cikin wani yanayi hadi sauke numfashi guda guda tana fadin da kyar.

Sister kina inane kizo yanzu don Allah ki sameni a dakina sai naji ta kashe mikewa nayi tsaye da sauri na dauki wayan na nufi hanyan kofa sai kuma na tuna babu kowa a part din mu a lokacin.

Hakan yasa na tsaya na jawo kofan mum dake bude nasaka key na jawo kofan na nufi hanyan part dinsu sauri nake jikina na rawa ina dan hada hanya don sauri.

Ina tafe inawa kaina tambayoyi barkatai na meya sameta naji muryanta a hakane ina mutanen part din nasu suka tafi kuma da wana tambayan har na isa part din nasu nayi sa,a babu kowa a falon hakan ya ban daman shigewa dakinta kai tsaye.

Ina tura kofan na hangota kasa tayi gurfane ta dafa gado ta dukar da kanta kasa da gani tana a cikin wani hali mai muni a lokacin hakan yasa na karasa da sauri dakin ina fadin Anty meya faru meya sameki kuma ?

Ta samu ta dago kai da kyat ta kalloni yanayinta gaba daya ya sauyawa sanin da nayi mata son lokaci guda naga hallittan ta ya canza min ga gani hakanlina ya kara tashi da gagawa na karasa gab da ita ina kiran sunanta.

Dafata nayi ina maimaita tambaya anty meyake damun ki hakane sai naji ta dan sauke ajiyan zuciya a wahalce t dago kai wani uban zufa naga tayi tana kuma cije baki.

Ta dan kai zaune tana fadin Sister kira min Mum idan tana nan don Allah ko kuma ki kiramin Dada dai don nasan yanzu mum tana wajen daddy.

Da sauri na juya don in kira mum din har da Dada don ina ganin wanan ba zancen kiran mum bane ita kadai na murda kofan in bude naji ta saka wani salati me karfi a wahalce murya na rawa tana son tashi ta dafa gado ta kasa sai murde murde takeyi a wajen ita kadai.

Hakan yasa da sauri na dawo gareta kuma ina faman yi mata sannu hannu ta miko min tana min alaman inzo in taimaka mata niko a lokacin nagama rudewa ko nace bari na kira Dada dai tazo.

Yadda ta ciji kasa ta yunkura ta mike ta dafa gado haka harafin bakinta ya fito da karfi tana fadin sister ki kamani don Allah zan mutune kila da sauri na rike ta ina fadin baki mutuwa anty bari na kira su mum suzo.

Wani nauyi naji tayi min a hannuna wanda hakan yasa nakai zaune bakin gadon ta dora kanta a kan cinyata gami dayi min rikon da kamar karti goma naji sun rikeni a lokacin.

Saida na dan sake dan kara kafin naji tayi wani irin nishi da karfi saiga da ya fito daga jikinta yana callara ihu irin na jarirai wani irin tsoro ya kamani lokaci guda don ko ance nasake fitsari bani mussu.

Ganin ashe haiwace yasa na dan dake ina fadin sannu anty ina kokarin cireta a jikina ta sake wani irin ajiyan zuciya tana amsa min tare da fadin yi sauri sister ki kira wani yazo ya yanke cibi don Allah.

Na fito a gigice ina kwasan gudu zuwa wajen Dada banko kula da mum na wajen ba tazo tambayan ko nashigo wajensu don taje part dinta ta samu a rufe yake ta dauka nazo nan din.

Ke lafiya ga uwarki tazo neman ki kina ina hakane mum ta tambaya ta tare zancen Dada din nace mum anty Nafisace ta haihu yanzu.

Haihuwa a ina nace ina haki tana dakinta salati suka saka suka kwasa zuwa dakin nata dukan su suna rige rige Dada na fadin dazun fa da uwarta zata fita shine tace ita bata zuwa ina mata sheri.

Kusan tare mukai part din dasu saidai a falo na tsaya don sai lokacin naji tsoro kuma ya kamani Dada ce ta fito muka zauna a falon nan muka barsu tare da mum din a cikin dakin.

Dan tsayin wani lokaci saiga mum din ta fito da abinda aka haifa din nade a cikin wani zanin anty din don a lokacin ba zance ga kalan abinda ta haifa ba don ban tsaya duban kome ta haifo ba saboda firgicewa.

Dada ta mikawa da sai fadin take ikon Allah na yarda haihuwa habone don baifi awa ba da muke zaune da yarinyar nan a waje har inawa uwata fadan kwasa su fita haka su barta ita kadai ga ciki tace min ba dadewa zasuyi ba ai a can din.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[2/14, 11:11] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON ,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

16

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Wayan da ya Addel ya kara sai mun ya zama abin hassada ga yan uwana a wanan gidan duk da ba wani dogon shiri muke a tsakanin mu ba wanan bai hanasu sakawa takona ido ba don basu san da wayan ba da farko sai daga bayan nan suka kula da wayan da nake riko din wanda ya Addel ya sayo min din saidai basu san a ina na sameta ba har yanzu.

Don ince a dalilin wayan nan harkal ta da halimatu yayi rauni a yanzu a cewanta ita da uwarta wai asiri iyayyena ke min na farin jini a gidan nake da sa,an mutanen gidan wanda ba haka bane kuma.

Rashin kiuyana da girmama mutane yake jawo min alheri ga kowa a gidan koda mutum bai niyar yimin hakan ba zai mun duba ga irin halina ya kyaleni wanda a lokacin ban masan wanan halin da suke min dubaiya a kansa ba din.

Amma halimatu da uwarta duk sunbi yan uwa suna shelata nida uwayena wai asiri mukewa daddy da iyalinsa yasa baya kallon kowa a cikin dangi saimu a yanzu.

Ga mutane mafi yawa suna yarda da vamfin akan asiri sai kadane suka san gaskiya basu daukan hakan da tasiri a zuciyarsu su dai san hamon jinine bayan hakan kuma daddy din yana fadawa mutane ai uwarsu daya da baba don a hannun maihaifiyar babana ya tasoshi kuma komai da yazama yau itace silar hakan agareshi.

Dawowan anty asibitin nan yasa na zamo mai kula da ita bani kadai ba son har hjy mum da Dada suna bata kula na musamman kamar yadda likitoci suka umurci a bata din.

Sai kuma hakan ya koma hassada don ko yaran hjy mummy sun matsa da kiranta a waya suna mata gulma wai kada hjy mum ta asiceta su juya mata hankali don ko wani irin abu a yanzu bata sukeyi da sunan samun saukin gwiwa wanda hakan ya dagawa hjy mummy hankali sosai.

Nan ta fara bin yan uwa masu fada aji a cikin dangi don sam taki yarda ta koma katsina tun fitanta gidan a nan kano take zama gidan wata aminiyar ta wanda zaman nasu ya fara canza sallo don hjyn ta nuna itafa ta gaji wanan na cikin abinda ya kara dagawa mummy hankali take yawon bin yan uwa abawa daddy hakkuri ta dawo dakin ta.

Tare da alkawarin cewa ta fahinceshi ta daina saka mai ido yanzu ga komai nasa har ta labe ga haihuwan anty Nafisa da take fada masu abin kunyane a gareta Nafisa ta haihu bata gidan nan ai .

Wanan suka duba sukaci karfi daddy din ya yarda hjy mum din ta dawo sai kice wata yarinya karama don ko bata dawo ba saida ta zauna ta gyara kanta irin da mata keyi harsu kumshi da kitso da da bata da lokacin yinsa duk akan daddy ya rude akanta ta tsaya tayishi a yanzu din don dawowanta gidan daddy din.

Saida ta kwana tayini kafin muyi arba da ita koshi anty nafisace ta kirani wai inzo in duba mata abu yasa nashigo part din amma ina jin komai a wajen hjy mum tana fadan yadda mummy din ta dawo gidan tana abu kamar karamar yarinya.

Ina shiga falon mukai arba da ita zaune Asiya da mairo suna gefenta da gani wani zance sukeyi a tsakaninsu na shigo zuwa nayi har inda taken na kai kasa ina gaida ita din da fadin mummy ina wuni an dawo lafiya.

Ta amsa min ciki ciki ba yabo ba fallasa agareni hakan yasa na mike da sauri na nufi hanyar shiga ciki muryan Asiya naji tana fadin ina kuma zaki shigawa mutane haka zikau dake ?

Sallon ki kullawa mutane wani sheri kuma ace ga abinda akayi maki ko don kinga kina da daurin gindi ba dama ayi magana kike zato.

Anty Nafisace ta kirani aida baki gani ba nan na juyo ina fada kafin in kara naji mummy din tace jeki don Allah ina ruwanki da shigowanta ko an hana ta shigo part din ne ?

Nasa kai nashige zuciyana fal da tunane saiga anty Nafisa din mun hade a kofa da ita ina fadin gani anty sai naga ta wuceni tana fadi jirani a daki inzo sister .

Ashe fada tayiwa Asiya din don komai a kunnenta ya faru na gane hakanne don yadda ta shigo tana huci a dakin lokacin tana shigowa tace dani yaran banza kawai suko koyi basayi da halinki su koya basu da auki sai gulma da kisisina da zaman saka ido suna zuga mummy ko yaushe.

Dan dariyan yake nayi mata ina kara fadin gani anty ta kara dagowa har lokacin ranta a bace tace gara da baki biyewa yan iska ai gasu nan komai basu iya ba duk jerabawansu baiyi kyau ba to basuyi karatu ba suna aikin gulma da saka ido mana.

Kiyi hakkuri anty na sake fada a cikin yar murya saita ja tsuki kafin tace barin fadawa yan iska ita mummy din da take biyewa tseguminsu ai tafi laifi.

Wani abu zan makine tace ehh dama wancan jakkar nake son in duba wasu kaya yasa na kiraki don wallahi tun shekara jiya nake son saukesa amma na kasa hakan.

Mikewa nayi na nufi wajen ina sake tambayan wanine a ciki ta nuna min shi da kyar na iya jawo jakar na kawo tsakan daki muna cikin budewa kanin nata ya shigo dakin ban masan yana gari ba sai lokacin.

Gaidashi nayi ya amsa min da kyat kafin ya murde fuska yace mekuma ya hadaki dasu Asiya kedake fama da kanki tace munafunci don basu kaunan a zauna lafiya a gidan nan.

Yarane ai ki barsu zasu bari don yanzu duk fadan da zakiyi masu basu fahintarki sai suce kin matsa masune nayi mamakin jin kalaminsa din ban dauka ya iya kalma mai taushi ba a rayuwansa sai naji tace is Ok ai ya wuce.

Gobe din zaka tafine yace wai haka naso gara nabi file din nan naje ayi komai a gabana zaifi yafi min wanan zaman da nakeyi a nan yanzu tace is better karfe nawa zaka tafi din ?

Yace zuwa dai sha biyu nake son in kama hanya OK ta kara fada tare da furta zan ganka kafin katafi din yanzu muna wani dan aikine da sister nan sai ya dan kalloni inda nake duken idan mun gama zan kiraka a waya kazo mu san yadda za,ayi din.

Ya juya ya fita ba tare da yayi magana ba nidai ina duke da kaina saida ta juyo tana fadin sorry sister na barki da kaya a hannu aiki yake son samu a abuja su kuma sun aje shi a zamfara shine yake so canzawa.

Allah ya taimaka na fada cikin yar siririyar muryana ta amsa min da to Amin abinne akwai wahala mutum ya gama karatu sai kuma aiki yazo yayi tsaye mukaci gaba da gyaran kayan sai kusan magariba na samu kaina kodana fito gun Dada na biya don bamu hadu wunin ranan ba da ita nasan ko sai tayu min korafin hakan.

Gashi kuma kwana biyu bata nan taje gun iyayyena ta zauna dasune tayi kwana takwas da tace sati biyu zatayi amma jin dawowan mummy yasa Dada ta kasa zama ta dawo gida don sa ido.

Aiko ina shiga ta shiga min korafin ba,aganina yanzu ai take zancena da yake halimatu dakilace saita kyaleta bata tanka mata ba sai kuma gani nashigo wurinsu din.

Ina kika shiga hakane ta tare dashi tun jiya dana dawo kowa yazo gaidani banganki ba sai yau din nan har na fara zance ko baki da lafiyane wai ?

Nace lafiyat kalau Dada jiyan dai bana gida ina islamiya kinsan na kusa sauka yau kuma tun safe ina wanki yanzu nagama sai kuma anty Nafisa ta aika inzo tun dazun ina wurinta ina gyara mata kayan ta yanzu nafito.

Ta dan duba kofin tace dada kinga uwarku mara kunya dai ta dawo taga bin boka da malam da kuka a wajen manya saida ta dawo gidan nan don naci Allah ya gani banson zuri,an mahauta gidan nan don ba mutanen arziki bane cikin mu dama tsoho ya fadi tunda isuhu ya shiga dabi,an nan yace zai gurbata masa zuria gashi kuwa hakan yana faruwa yanzu.

Toke Dada ina ruwanki inta dawo tunda ba saman kanki zata zauna ba niko keda ruwa mara kunya tacewa halima data katse zuban da takeyi din tace.

Da ban haifi dan ba zata ganshi ta aureshi har ta nace tana zuba iko da mulki iya son ranta haka au ke kika haifeshi ashe na zata Abu mai gyadace ta haifeshi ai cewa takwarana.

Don naga da ita daddy yake kwantace ai ungo nan ta fada Abu maigyada tayi komai wallahi don yayi alfahari da ita ai baiyi ga banza ba don ya rike amana har bayan ranta.

Niko nasan halima din ta fadi hakane da biyu banko kai karshen tunane na ba sai naji tace wani amana ita kadai ta rike da ai kuma kun rika meyasa ba,a hakan yanzu ?

Kina da wata manufa ke nan ga zancenki diyar nan ke kenan baki son a zauna lafiya kulun kina takalan magana to Abu mai gyada da zurianta dai sunfi karfinki don ki sani don ko suna da abinda baki dashi shine tauhidi.

Nan ko tasa Dada din agaba tana ci mutunci don me Dada zatace mun fita komai a duniya ke nan ita bata arziki a duniya Dada ke nufi kome ?

Nikan nafice na barsu suna rigima a tsakaninsu su biyu a part din na kuma samu mum ta hau fushi dani akan dadewan da nayi saida nace ina gun Dada ne suna rigima da halima na tsaya sai kuma ta koma tambayana akan me kuma suke rigima ?

Na labarta mata abindake faruwa tace wanan yar da tada zaune take yanzu kuma ta bugawa uwarta waya tace ga shirin da akai mata akanki baida wuya a wajenta itako data fita hauka ta hau zancen ta zauna tunda ba kunya garesu ba.

Nasamu hjy mum tagama duk aikin da zanyi a lokacin don haka na nufi dakuna na gyara a gagauce don magariba ban fito ba saida nayi sallah har isha,i na fito don cin abinci faten tsakin masara yaji kayan hadi mum tayi muna shi kuma mukaci matsayin abincin dare a ranan har ina zancen in kwanta ya Nasir ya shigo shine dan farko da mum ta fara haifa a gidan nima sai daga baya nagane hakan.

Don ba zakice bashi ya haifi ya Addel ba gaskiya dubaga irin shakuwan dake tsakaninsu don daddy yafi sonsa da anty Nafisa yana yawan shawara dasu koda kuwa basu kasan zaice ajira Aliyu ya dawo wanda hakan ke batawa hjy mummy rai.

Tayi fadan hakan har tagaji dole ta saka iido a karshe tabar zancen a fili amma tana yawan korafin hakan lokaci lokaci zatace abin yana damunta ga diyasa ya dauko bare ya saka ajikinsa duk da tasan shi din ba bare bane a wajensu mutuwace ta kawo hakan.

Ba wani abu mai wuya bane indomie ne da kwai zan dafa mashi na shigo falon tambayan mum ko kwai nawa zan dafawa ya Nasir din.

A falon na samesu da ya Addel shima yana fadan ba zai iya cin wanan faten da mum tayi ba da daren nan sai gani mum tace ga mama nan saita dafa maku abinda take dafawa Nasir tare dakai ai.

Me take dafa mai ya tambaya yana kallon mum din tace ina zan sani ai gata wai me kike dafawa Nasir ne ta kalloni tana tambayana nace indomei da kwai mum tace shi yafi wanan faten nawa kama ciki ke nan ?

Kwai nawa zan saka mashi mum na tambaya daga bayana naji an bani amsa da hudu muryan ya Nasir ke fadan hakan gareni na dan juya ina kallonsa yayinda mum ke fadin tunda kai kadaine sai a dafama hudun ai.

Draman su bai karewa da Nasir din hakan yasa na juya da niyar komawa kitchen din naji mum na fadin shi baki tambayesa ko kwai nawa zaki saka mai ba nace nasani biyune.

Hakan yasa ya lumshe idanunsa lokacin da mum ke fadin watau har kinsan ko nawa yakecishi nace nasani mana mum naahige na barsu ban fito ba saida naga hada masu komai na kawo masu abincin a gabansu na dire nan na barsu ya Nasir yana zuba masu santi yanaci.

Ban fito ba saida safe nayi duk yan aiyukan da zanyi na koma na kwanta don akwai gajiya a jiki barci na samu sosai nayi lokacin kafin in tashi inyi wanka nafito da zumar in karya don kunun gyada mukayi kuma ina sonsa sosai don haka mum take munashi don itama tana so.

Haka kawai ganinsu yasa girjina bugawa duk da baiko kulani amma masifan tsoronsa nake ji tunda na fahinci baida mutunci ko kadan a fuskanshi.

Masangalin kujera kawai na dafa nace ina kwanan ku wanda jin hakan yasa suka juyo kamar kullun wanan kallom wullakancin nasa ya jefo min sabanin yan uwansa da suka amsa min a cikin mutunci kamar yadda muka saba.

Ai gara da kika fito ki taimaka ki dafa muna wani abu mu hada da kunun gyadan nan zamubi hanya dan anjima kadan don muje da nauyi ya Nasir ya fada.

Saidai kai nikan ba zan tsaya cin jagwalgwale ba in bi hanya cikina ya rude ina tsayawa kai wanan yarinyar ta iya girki harda na indiyawa sarkin barkwanci ya Nasir ya fada yana dan dariya.

Zakace shi ba ciki daya suka fito da ya Addel ba saboda yawan barkwancinsa ga mutum don hakanema nafi sakewa dashi kaf inkin debe anty Nafisava cikin yaran gidan duk ko da dadewan da na danyi a gidan yanzu dasu.

Kitchen din na nufa don in duba abu mai sauki naji wanan ya Hafiz na fasin me zata dafama ta wuce baka fada mata bafa kada tayo muna jagwalgwale don Allah.

Aiba don ka zanyi ba don dan uwana zan dafa amsan yazo min a takaice kuma na fada kowa naji ni kaina amsam yazo min ne a hasale don rainawa mutane wayau da yakeyi.

Kanshi kawai ya girgiza cikon wayencewa ya kuta nashige yake fasin mum wata rana saina karyawa yar nan taki kafa tana wasa dani wallahi ya Nasir yace wayaga ball ke nan.

Abinci lafiyayye nadafo masu kuma suka zauna sukaci harshi miskilin da suke faman cika wasu takardu a part din mum din wanda nasam shiya kawoshi part din dama.

Daki na samu mum kwance na zauna a kusa da ita muna hira take ja min kunne kan na kiyayyeshi don ba hankali ko kunya ke garesu ba insun tashi tsiyarsu.

Haka dai zaman ke tafiya a gidan muka koma hutu don ya kare munsha dogon hutu a lokacin daga komawa aji shidda zan shiga nida Halimatu sai kuma aka samu akasi sunan halimatu ya fito cikin yan repeating dole saita maimaita shekara kuma.

Aikuwa nasha zunde a gidan mu don sheri suka laka min cewa wai ina hurda da malamai a asirce yasa suke passing dina ko wani jerabawa son sunga ina da kyau.

Ita mummy ce wanan karon ta kashe wanan zancen kafin ya fito fili amma duk da hakan saida zancen ya dawo kunnen mu ranan kuwa hjy mum tayi fada saida anty Nafisa tace ai mummy tayi masu fada sosai kan hakan.

Don agaskiya mum tayi niyar kai zancen wurin daddy amma jin hakan yasa ta kyale zancen gashi kowa ya gani zai yaba sai cewa ake nayi kokari na

Wanda hakan yake karaba halimatun haushi sosai don har kyauta daddy yayi min don cin na farko da nayi ya sayo min lace mai kyau da takalma har da hand bag na yan gayu sai murna nakeyi.

Nasan yayi hakan ne don yan uwana suji haushi suyi kokari don tare zamu zauna dasu yanzu su kara zana jerabawan nasu a school din mu din.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[2/14, 11:14] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

18

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN

LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Hjy mummy da mamaki ta dawo gidan tana barazana wai bata yarda yarta ya haihu ba watakila an mata hakan ne donvta dawo daga unguwar.

Wanan yasa tun a mota da daddy ya kirata take yankan sababi dashi ya za,ace ta haihu kuma wai agida abu kamar almara don haka ita bata yarda ba har saida ta shigo gidan .

Ta fara ganin alaman gaskiya don jin hayaniya yan gidan da ake a ciki murna kamar yadda ake taya mai haihuwa da wanda ya shafa fari ciki a kasan hausa.

Nan ta shigo tana fadin wai dagaskene baby ta haihu din abinda ta shigo tana fadawa mutane ke nan a dakin cikin fada tana shigowa falon dake cike da yan gida suna murna da haihuwan don yanzu gidan ya koma gidan jama,a cike yake da mutane don daddy Enugu daya dawo da nasa iyalin.

Kallon mamaki kowa ke mata don basu tsamaci hakan gareta ba farin ciki da jin dadi suka zata a wajenta don Allah ya sauke yarta lafiya a gida kuma.

Mamakinsu bai kare ba saida ta furta wanan ai gangancine dole a dauketa akaisu asibiti daga ita har abinda ta haifa din a duba lafiyansu a can.

Lalai Marka baki da imani kuwa ina wanan zance mara dadi haka ya fito a bakinki kuma ga yar ki ana farun ciki zakizo da zancen banza yanzu kuma ?

Wani asibiti kuma kike zance yanzu Allah ya rabata da talan munta gaban mutane ta haihu daki daga ita sai kanwarta data dafa mata baya lafiya yanzu kizo muna da zancen banza.

Don kudi yaiwa mutane yawa haka kuma kice aje asibiti yanzu don hauka ai wanan ya zama kuwa bayan halri ke nan kuma ai saida aka haihu za ayi zancen asibiti.

Wani kallo mai alaman shock tayiwa rasarkuwar nasu Dada tana fadin wace kanwarta wai badai mama ba don yanzu dole itama da mama take kirana agidan ko uwar masu gida tun ranan da Dada taci mata mutunci a gaban mu kanta kirani da Abuwa.

Wa kuwa inba Abuwa ba itace dai me wanan karfin halin ita ta karbi haihuwar yar uwan,nata sai kiran mu kawai sukayi daga baya bayan sun gama zugansu a dakin su kadai.

Wai baby tana da hankali kuwa Maamah ce zata kira ta kama mata haihu mama dabata ko san inda ke mata ciwo ba tunkun ya Malka ai farin ciki dai zakiyi tunda ta sauka lafiya Allah ya tsare gaba kuma matan daddy enugu uwargidan ta fada daga inda suke tsaye cirko cirko suna kallonta cikin mamaki don basu zaci hakaba gareta.

Fitowan hjy mum da jariri a hannu tana fadin ku shiga mungama tana ciki yasa mummy din juyawa tana kallonta mairoce ta mika hannu da sauri tana fadin hjy mum kawo babyn mu gani me aka samu.

Tace gashi kun samu baby boy mai kama da ubansa sak har dan dingon nan na habib yaron nan saida ya dauko don kara ta fada tana dan dariya fuuuu mummy ta wuceta ba tare data shiga ba sai sauran suka bita a baya.

Nikan wajen su mairon muka tsaya munawa baby din kallon kwam da shawa,awa tare da jin dadin haihuwar yar uwar tamu din a lokacin don abin farin ciki ya samemu.

Kunya nakeji naji ance wai ai zainab ce ta tsayawa anty Nafisa ta haihu don ko kowa haka yake fadi a gida ta haihu ita da maamah ai maamahce ta karbi haihuwan.

Muna part din har yamma na tsaya kara gyara dakin da fiddo mata da kayan da zasuyi amfani dashi ita da jaririnta su daddy suka shigo su ukkunsu dashi da mahaifina da daddy Enugu.

A falo muka tsaya suna fadin ina abokin namu ance mun samu abokin kokuwa mai karfi jin muryansu yasamu fitowa ko maijegon fitowa tayi tare damu don ta gaidasu din.

Muryan mommy data rigamu fitowa tana fadin gashifa mai karfi dashi haka tayi kasadan haihuwa a gida su kuma suka biye mata bayan kowa yasan yanzu yadda haihuwa yake tattare da hatsari gashi kuma na fari.

Sai naji daddy din na fadin Allah ya kawo muna sauki an haihu a gida shine saukin aida ake fata daddy enugu ya fada yan kuda na kwana inji manya yana karban yaron daga hannun Asiya.

Mr Enugu gasadane hakan ai daga ita sai maamah suka haihu don maamahce doctor tayi karban haihuwan don wauta ta fada rai bace.

Daddy dasai murmushi yakeyi yace interesting ashe zan samu likita mace a gidana ke nan gaba kinyi kokari sosai mamana haka ake son karfin hali ga mutum ya koya ya iya Allah ya raya ya fada yana karban yaron a karshe shima.

Hjy mommy bataso jin hakan ba ta juya ta shige tana jininin abin babane ya kallo inda nake yace ku bani dabino da dan ruwan zamzam idan akwai.

Daga inda Anty take zaune don basu girma ta dan kalloni tana fadin kije cikin side drower dina suna ciki ki dauko ashe ita kan ta tanadi komai akan haihuwan na fada a raina lokacin dana juya.

Na dauko na kawo mashi ya karba ya dan saka dabinon a baki yayi laushi kafin ya fitar ya karbi yaron daga hannun daddy din ya gyara da kyau ya dan daga yaron daidai kunnuwanshi yana mashi ikamah duka kunnuwa biyu.

Kana ya dan kwantar dashi ya zuba mai a baki tare da addua a bakinshi ya dauki lokaci yana hakan muna tsaye mun zuba masu ido.

Ikon Allah saiko yaron ya lashe yana tandan baki muka sa dariya ya dade yanawa yaron addua kafin ya mikawa daddy Enugu shima yayi suka mikowa mummy datafito ta tsaya a gabansu.

Ni dai daga nan ban koma ciki ba part din mu na nufa nayi dan gyare gyare kafin yamma ya karasa don ba zancen taya mum girki ranan don nagaji nama samu tayi abinta.

Ban koma part din hjy mummy ba don jikina daya fara dibge min saboda rikon da anty tayi min har bayana nake jin yana dan min ciwo da hakarkarina saboda wuyan da naci a lokacin.

Ko washe gari haka na kwanta baya nayi sallah don gaba daya jikin nawa yayi min tsami ina jin kamar zazzabi iri mai taunan jiki din nan zai kamani.

Saida na dan farka nasha magani jikin ya dan sake haka kuma da nayi wanka sai naji wasai har na samun daman leka maijego ina shiga tana zaune taci kwaliya tayi kyau zakice ba ita bace ta koma jagwal a yan kwanaki.

Har mun dauka ko damuwan rabuwa da mijintane yasa haka saboda ko yawan surutu ma batayi sai yawan jan tsuki da ajiyan zuciya sai idan naje ina damun ta da tambaya takan dan sake har muyi hira wani lokaci.

A Kwana biyu ban samun hutu hankalina ya kasu ga karatu ga jigilan maijego da kusan komai nike mata haka kuma ban yarda na sake abinda nake dan kamawa mum ba a part din mu don gudun zuciya.

Yau ma shiga nayi na atamfar ghana da mum ta dinka min lokacin wani bukin kawarta da sukayi yana cikin wanda tayi min na fitan buki don gaskiya mum akwai kulawa sosai ba laifi.

Kida ke tashi a part din hjy mummy dabi,ansu ke nan da zaran daddy ya fita za,a kure kida kamar gidan kafirao wasu yan gaye har kitchen nabi hjy mummmy nagaida ita ta amsa min ciki ciki kamar yadda ta saba don ba sakin fuska ko annashuwa tsakanina da ita sai agaban mutane niko ban saba sai nake shareta idan tayimin hakan.

Har na dan juya naji tace yauwa maamah taimaka min ki kaiwa yayanku abincin nan tun dazun ya bugo min wai yana jin yunwa niko sai yanzu nagama.

Dan tsayawa nayi ina tunanen wani yayan nawa a ciki take nufi ganin hakan tace yayanku hafiz mana mika masa yana dakinsa kwance.

Jiki ba kwari na karba tare da tunanen zancen mum ko yaushe tana min fadan karna yarda taji ance wani yasani wani aiki a bangaren samarin gidan inba haka ba raina zai baci.

Don shi duk zama a gidan dasu ban taba taka kafana ni kadai a part dinsu ba sai gashi yau mummy din ta aikeni kuma banda halin cewa banzuwa ta tuztuzgi ubana ba wani aiki bane wajenta .

Dole na karba na kama hanya taimakona guda ranan da muka shiga gaidashi wai yayi accident dasu anty Nafisa nasan dakin shi don haka na nufi wajen kai tsaye da kayan abincin.

Gabana sai faduwa yake daga kofa na tsaya ina kwada sallama shiru hakan yasa na kwankwasa tare da murda kofan lokaci guda ina sallama.

Yana zaune dagashi sai gajeren wando ya mike kafa daya ga sigari yana busa ga kwalban giya ya rike da hannu daya idanuwansa da suka kada sukayi jajir ya dago yana fadin.

"Ke ubanwa yace ki shigo min daki haka kai tsaye ashe baki da hankali dama haka ban sani ba ubanwa ya aikoki min daki ma ya fada yana kakafeni da idanuwansa.

Cikin dan rudewa ina i,iniya nace dama hjy mummy ce tace na kawo maka abincinka don Allah kayi hakkuri shout up my friend don kina doluwa shine zaki shigo min ba tare da nabaki izinin shigo min ke dabban inane wai ?

Ga abincin na aje a gabansa don kiris ya rage in fara amai saboda warin giya da taba daya game dakin wanda ko a hanya naji warin taba damuna yakeyi sai kaina ya daure balle wanan dakin daya dauki warin abubuwan lokaci guda haka.

Da sauri nadago na juya don in fice daga dakin naji yace cikin tsawa ina zaki haka dakata kiji wallahi duk naji wanan zancen a bakin wani gidan nan saina kusa kasheki da duka ba kuma abinda za,ayi tunda bakinki mai gulma yaja maki.

Duk da tsoronsa da nakeji haka bai hani fadin ni ina ruwa da zanje in fadawa wani wanan tsakaninka da ubangijinkane ai na fada ciki ciki a zatona ba zaiji me nace ba amma sai naji yace.

Kika ce me ashe baki da kunyane haka zan tatakaki wurin nan yanzu idan kika kara magana ya dan yunkura kamar zai mike na kwaso da gudu zuwa waje ina haki daidai fita dan corridor su mukaci karo da ya Addel dake shigo.

Cikin mamaki da al,ajabi yake kallona kafin yace ke zeey meya kawoki part din nan ina dan waiwaye nace ba hjy mommy bane taban abinci wai in kawowa wanan yayan shine don nashiga na sameshi yana shan taba yace wai inna fadawa wani saiya halakani.

Kallon kofan ya Hafiz din ya danyi kafin yace kinga tafi ina zuwa kar kuma aji wanan zancen a bakinki kindai san halinsu daga yau kuma kowa ya aikoki nan part din kece na hanaki shigowa ko mum ta hanaki na gyada mai kai ina wucewa da sauri ina dan waigowa kada ya biyoni a baya ya shakeni kamar yadda yace tunda na fadawa ya Addel din.

Ban koma part din nasu ba don tsoron da naji kada ta kara turoni kai masa abu don haka na wuce kai tsaye wajen mu mum tana daki lokacin tana barci don haka na shige dakina na kwanta sai tunane nakeyi a raina.

Wai ashe haka dama warin giya yake dama ashe ko dadi baida kuma mutane ke sha bayan Allah ya haramta shanshi me suke ganewa a cikin wanan abin mai wari ?

Ya Addel dayake shigo dakin anty don su gaisa yaga baby yaji anty Nafisa na fadin wai ba muryan Zeey naji ba ina ta tsayene kuma tana tambayan tsohuwar da suke dakin tare don mummy bata yarda kowa ya zauna mata da ita ba ita da kanta ta samo mai zama da yar nata.

Shiya bata amsa da fadin itace yanzu na hadu da ita wai mummy ta bata abinci takaiwa Hafiz daki shine ya korota ta fito da gudu har tana karo dani.

Akan me zata aiketa dakinsa kuma shi baya zuwa ya dauki abincinsa da kansa mummy fake kara bata Hafiz yake iskanci dayaga dama abincin ma ba zai iya zuwa ya dauka ba sai ankai masa.

Haka kawai ajawa yarinya zagi ko duka ga banza haka su mairo suka dauko iskancin nan don sunga tana min abubuwa sukaso su mayar da ita boyansu saida na hana.

Baiyi magana akan zancen ba illa cewa dayayi da ita ya kuka kwana tace sorry ance jiya daka iso ka shigo munyi barci yau da safe ake fada min kazo jiya mun kwanta ya hanya ?

Yace Alhamdullahi ashe an sauka barka da arziki Allah ubangiji ya raya muna yasa dadin musulmine ya tayar muna dashi ta farkin addinin musulunci ba kunya ta amsa da Amin woo bros.

Allah ya nuna muna auren ku kuma matanku su haihu haka ayi dozin dozin yace haba sai kace za,akai kurmi indai andan samu sai a huta zaifi suka kwashe da dariya.

Tace ai haihuwan baida wuya saidai zullumi yace ai ashe me sauki kika samu har kike fadan haka tace gaskiya ka bari abin ba dadi ai nida zainab mukasha tumulun mu dakin nan har na haihu dagani sai ita.

Kai wace zainab din ya tambaya cikin mamaki karara a fuskanshi tace zeey dai tamu zainab din mum aika bari wallahi shiyasa nake son yarinyar nan har cikin raina tanada hakkuri da sanin ya kamata.

Yace amma dai kunyi kasada zainab ce zaki tsaya ta karbi haihuwanki kema Nafisa nan ji nayi da kike fada min kamar ba gwareki a ginan nan wallahi don haushi.

Ta kwashe da dariya suka dauko zancen mahaifin yaro tsohon mijinta nan ta bata rai tana fadawa dan uwanta damuwanta na rashin zuwanshi yaga babyn kuma bai aiko kowa ba.

Hakkuri yake bata yace kiyi hakkuri wata rana ai zai nemesa balle ma dole yazo don daddy ba zai kyaleshi ba ai kodon aiwa yaron nan gata koni aka barni dashi zanyi maganinsane ai balle su daddy balle gasu baba garba akusa da daddy Enugu nasan dole zasu dauki mataki kafin suna yazo ai.

Shigowan mummy ya katse su kamar kullun in suna magana tashigo sai ya fice don baison wani abu ya hadashi da ita bayan gaisuwa tun lokacin da tayi mai tonon sililin a tsakar gida yana karami ya kiyayi kansa da ita.

Taso su shiya amma sam ya Addel din ya kasa sakewa da ita dama gashi miskili sai abin ya taru ya hade yana bada wani ma,ana iyakansu gaisuwa a tsakaninsu.

Bayan fitanshi part din muya nufo don ya karya kummalo hjy mummy kuma taja tsuki tana fadin yaro miskili haka kamar dan wani sai fadin ran tsiya da fankama kamar dan wani minister dashi.

Haba mummy na dauka ko don kaunar da yake nuna muna zaki kyale mutumin nan yanzu ai mahaifiyarshi fa ba danki da take nunawa wani abu a gidan nan.

Ke rufe min baki sakarai da baki gane shigo shigo ba zurfi da ake muna dama ba hakan suke son a fada ba gashiko kema kin fara fada balle yan waje.

No mummy gaskiya ki daina hakan don Allah dama ba yau ba nake son in maki wanan maganan don Allah ki daina nuna masa hakan kuma don Allah kada ki kara aiken zeey part din su,,,,

Au to har karana yake kawowa gunki ashe ban sani ba to ko uwarshi sai in aika ba zainab zanci maku mutunci daga ke harshi agidan nan ki bari a watse taron nan lafiya dani dake ta fada rai bace tana fita.

Yayinda Nafisa din ke fadin niba karanki ya kawo min ba jin muryanta nayi ban ganta ba ahine nake tambaya yace yanzu ya ganta a part dinsu wai kin aiketa.

Ina mummy din ta riga data fice rai a bace ta koma dakinta dama gulma aka kai mata shine ta taso ta tabbatar dako yana nan din sai gashi ta gansu a tare suna hira.

Har ta zauna tana tunane sai kuma ta mike fat kamar an tsikareta ta fito zuwa part din hjy mum din tayi sa,a suna zaune ta fado masu kolarin karyawa yakeyi sai gata.

Fuuu tana shigowa tace Addel Aliyu dama don kai nashigo don banson kananan tsegumi don had ka fadawa Nafisa cewa na aiki zainab takaiwa Hafiz abinci.

Zancen nan ya tsaya iya nan kada ka jawo min wani magana kuma ko hafiz yana dan iska me zaiyi da zainab wanan mara kunya din kallon mamaki mun ta tsaya yi mata kafin tace wa mummy din.

Kai amma wana baiyi ba din na hanata zuwa wanan sashen ban ma jin cewa ta taba shiga sashen nan a gidan nan don ko Alh yaganta fadan hakan zaiyi nasani don shine ma na hanata hakan.

Wani kallo mummy din tayiwa mum tace ba kaji ba dama abinda nakewa gudu ke nan yasa nazo nan din gashi ko tun yanzu ana kokarin juya zancen.

To ku sani kada wanda ya bata min suna ko dana don in zancen nan ya juya gaskiya rayuka zasu baci a gidan nan don ko ba zan kyale ba nima haka kawai daga aike sai abubya zamo dan kari.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[2/15, 17:42] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Tayi jidalinta ta fice don ya Addel dayayiwa mum signal da ido akan ta kyaleta don Allah kada ta biyewa shirmenta na banza su zama daya wanan yasa mum din kyaleta badonshi ba ita ta iya biye mata sosai.

Ga mum irin masu soka magana dayace ya tsaya wa mutum a rai kalma daya biyu zuwa ukku zata fada da zaisa mommy jininin wata da watani agidan.

Batan fitan ta kaina suka juyo ranan mum tayi min kaca kaca saida ya Addil ya kwaceni ya nunawa mum aiba laifina bane tunda bazan iya cewa bazanje ba don ita din ba sa,ata bace amma da akai hakan yafi ai.

Ranan ban koma gun maijegon ganinsu ba gashi tana ta aike da bugo waya nazo amma fir naki na shareta har takaiga bugowa mum waya tana nemana.

Hakan yasa dole da dare na dan shiga na lekasu ban jima ba kuma na sulale tana bayi na fito nadawo part din mu hakan yasa da saffe ina kitchen sai gata ta shigo da kanta tana fadin ina mum ?

Hjy mum nazo naji dalilin dayasa zeey take gudun danta tun jiya mum dake daki ta fito acikin mamaki tana kallonsu.

Tace ina kuka fito haka tace gashi na kawowa uwarshi shine don tun jiya tayi muna yaji bansan abinda mukai mata ba shine mukazo biko.

Murmushi mum tayi tana karban jaririn a hannun uwarshi tace kinsan hjy malka idan ta tashi abinta bata ganin gaba balle baya nan tazo jiya da safe ta kare muna zari.

Mummy din nikan nayi tunanen akwai matsala tace wallahi muna zaune da dan uwanki sai gata walahi Allah dagashi har mama din amma sai gata tashigo da cin mutumci wai yayanki na nufin kada ta saka mama komai ko yana nufin wani abune dayake kokarin kulla mata sheri ta kwashe zancen yadda akayi ta fada mata sai hakkuri take ba mum din.

Karshe dai mum tace ta kyaleta kada taje tayi mata zancen kuma rayuka sukai ga baci ga mutane a gidan ta kare da fadin tana nan zuwa idan ta gama abinda takeyi tana muna breakfasts ne.

Tamike tana fadin kizo kiga dinkunan da aka kawo min mu zabi wanda zan fara sakawa a ciki nace to cikin tashin dadin rai a nan tabar baby din zata fita saiga mairo ta shigo tana fadin mummy tace kizo ga mutane sun shigo ta juya kai tsaye bata ko tsaya gaida mum ba.

Ko yar uwan tayi mata fada sai gata ta dawo tana fadin sorry mum banko gaida ke ba mummy ta azalzaleni nakira mata anty har na rudi karbi dan ki kai tunda ga yan barka sun shigo .

Fuska ta bata kafin tace barshi kawai mum ni banga kowa a gidan ba zancen mummy ne kawai don Allah ta juya ta fice ta bar dan a hannun mum din.

Karshe dau zuwa din akayi aka karbi taron nasan ko ita ta aiko a karbeshi saboda rashin yarda da bata dashi a zuciyanta gudun ai masa wani abin wai.

Saida nagama da kitchen har girkin rana nayi wanka na shiga part din nasu don mu gaisa daita a falon ta take sun baza kaya ni banko kallah ba amma kiri kiri naji tana fadin rufe min kayan nan har anjima nagani.

Ina gaida ita na juya zuwa dakin anty Nafisa din tana zaune ita da wanan tsohuwar da Dada kunune irin na gargajiya a hannunta tana shana shigo.

Wallahi zeey baki da kirki sai yanzu kikaga daman zuwa har tela yazo ya wuce na dai bashi samfur yayi maki dogon buje da riga ko dogon riga kikeso nace a,a ina juyawa don gaida tsofin dake dakin.

Nan Dada take fadin bansan meya samu yar nan ba yanzu da bata son shiga mutane kamar da yanzu ma abin ya kara rikice mata in anyi magana tace karatu kamar al,hudahuda uwarta kuma ta kama mata.

Dada aiko ba zakice min haka ba na fada na juya zuwa wajen yaron yana barci amma haka na daukoshi ina dubawa ina kare masa kallon kwata hilla har uwar ta lura dani tace.

Wanan kallo haka zeey nace yaron nan naga kamar ya rame mun a ido kafin uwar tayi magana Dada tace keko dai yasha iskan duniya ya bazai rame ba.

A,a Dada yaron nan kamar baya da lafiya fa nake gani duba yadda ma yake numfashi a wahale ina dan juya hannun yaron a hankali daya tsohuwar tace mikoshi mu gani na mika mata ta karbeshi Dada sai fadi take wanan yar kamar tashin tsofi take fa.

Gaskiyan yar nan Dada yaron nan baida lafiya ikon Allah amma duk bamu lura ba wanan abinda ba a so gashi duk ya shedo masa a ciki zubur anty Nafisa ta mike tsaye.

Cikin rikicewa tana fadin ina mummy mu kaishi asibiti ke kwantar da hankalim ki abi sannu ina fita tayi daga dakin ko minti biyu ba,akai ba sai gasu tafe gaba dayansu a rikice dakin.

Anty Nafisa sai fadi take badon shigowan sister dakin nan ba ba wanda ya kula da hakan yanzu fa kuka dawo dashi tun dazun yana falo wurin ku ke iya ya akai haka kuma nan Dada ta tare da fadin kamar ya kuma ya akai haka ?

To hjy za ace gaku zaune amma baku gane hakan ba sai shugowan maamah saboda Allah bamu da amfani ke nan ko itako iya sai fadi take ita dai Allah ya turo ta gane muna dama.

Caraf anty Nafisa ta karbe yaron daga hannun tsohuwar tana fadin sister dauko min jakata mu tafi wanan ba zai fissheni ba da sauri na juya saman gado inda jakkarta yake ina kokarin daukowa naji uwar tace mata.

Ke banson rashin kunya kinji dukkan mu nan bamu damu dashi ba ke nan kike nufi ko me ko sai kin nuna muna ke kika haifesa tau gamu ganin ikon Allah dai Dada ta fada tana tashi.

Sai rana naji mummy tayiwa anty Nafisa fada irin gyara kayanka a gabana duk zamana dasu gidan ban kare mamakin haka ba saida naji tace ke mairo kira min hjy kubura.

Nace ashe ko mugu yana da rana ke nan yau ga ranan mum ke nan ashe itama mum a rude tazo hankali tashe part din tana fadin asha meke faruwane kuma ?

A nan dai aka yanke shawaran tafiyansu da mum din asibitin bayan an kira daddy an sanar dashi yace su hadu asibitin gasu nan zuwa suma hankalin gida ya tashi dan Adam mai tsada da kima kan dan jariri hankalin kowa ya daga a gidan mutum ke nan.

Bayan tafiyansu dakin nakoma na gyara masu shi tsab don a karshe hjy mummy itama ta bisu don bata yarda ba hakan ya ban dama tsayawa na gyaro mata dakin na rufo na koma part din muna jiran abinda za ace game da yaron.

Gashi duk aka tashi magana za,ace ai zeey ce tagane hakan ga tsofi basu gane ba sai kuma hakan yake sosa min rai idan na tuna don halimatu a gabana ta fara fadin kwarkwasa ke nan ai tasan komai ita dama.

Watau har abinda ba ai tsamani ba duk na sani ke nan take nufi amma na kyaleta don ba lokacin musayan baki bane ana cikin tashin hankali haka din.

Su mum suka dawo suna fadin an basu gado don an kwantar da yaron wai ya fito da shawara har tayi masa yawa a jiki ta hudu shi wanda suke kira da Jondis.

Acewansu likitocin sunyi fada sosai na rashin kawo yaron da ba,ayiba da wuri akabarshi gida haka ciwo na batun masa illa.

Banda wani aiki don haka mum tace in shirya in bisu naje don hankalina ya kwanta a can muka samu su maito dasu halima da Asiya don banko sanda fitansu bani.

Ina shiga Anty ke fadin ehh sister badon ke dake da kula ba da yaron nan ya mutu muna zaune ana faman surutu a daki ba wanda ya kula da hakan gareshi.

Mum tace haba bai mutuwa ai sai idan kwanansa sun kare wahala dai akewa gudu amma kowa ya mutu dama iya abinda ya debo ke nan a rayuwanshi.

Mun jima a nan take min hira cewa dan iskan uban nasa dazun daddy ya buga mai waya yana sanar mashi gamu asibiti sai cewa yayi Allah ya sauwaka kawai.

Mum ta kara kada baki garemu tace to me zaice Nafisa dole dama ai addu,an samun lafiya zai masa tace ki bari kawai hjy mum habib dan iskane na gaske dama ya fadi ya barmin cikin duk abinda na haifa inje inji dashi tunda nace ban yarda a zubar da cikin ba.

Kinga dan nan dayaki anty idan Allah ya bamu raida lafiya wata rana shine mai tallaban rayuwansa saukin abin agaremu bakece baki kaunar yaron ba ai kuma yan family din mu kowa yana kaunarsa kauna mai tsanani.

Yarone fa amma ki duba daga dakin nan har waje duk yan uwane suka taru akan dan nan insha Allahu sai yaji kunyar wanan abin dayayi wata rana.

Kwatsam ya hafiz ya fado dakin kallo daya nayi masa na dukar da kai ina tuna irin yanayin da naganesa a ciki a dakinsa sai naji girmansa da kimarsa da nake gani yazube min ga ido.

Gashi tsab zakice mutumin kirkine a fili ashe a boye mutumin banzane irin na bugawa a jarida din nan muryan anty nafisa ce yakatse min tunane a lokacin take fadin wai baki gaidashi ba sister.

Firgigit nayi tare da fafin wa hafiz mana ta fada nace ai nagai dashi daya shigo na kara fadin ina wuni tsuki yaja yaci gaba da magana da yar uwarshi ya fita zance na.

Mummy ce ta fado dakin da kawayenta kallon yadda muka hade kai da anty muna magana kus kus kus ga iya zaune a saman tabarma bata ko jin me muke fadi tashigo.

Kallo mu ta sakeyi tana fadin to rakwato aisai ki fita ga bakina nan sunzo duba yaro kar kuma a kaimu haba mummmy please ki dainawa yarinyar nan haka a gaban mutane mana sai a dauka haka halintane ai yar ta fada ciko bacin rai.

Ban san ya sukayi ba don na bi driver nakoma gida sai washegari na sake lekasu asibitin koshi da nace ba zanje ba don mummy saboda nagane dai ta tsaneni a zuciyar ta.

Banje da niyar zama ba muna zaune saiga ya Addel da budurwansa sun shigo wanan gulma ya zaunar dani muna kallon ikon Allah yadda ake soyayya nami sai a barshi kawai akan soyayya don idonsu kan rufene a lokacin.

Donko abinda ya Addel keyi ba zakice shine ba ko don iyamu yarane a wajen lokaci saiko yan tsofin dake zaune daga waje ga yarinyar da alama ba kunya gareta ba.

Don ko garemu katsinawa wanan rashin ta idone mutum yazo gun dangin miji tun baishigo ba yana wanan kaudin haka ba nuna alkunya ga kowa sai nuna sani da iya tun a nan ta sure min a zuciyana.

Shiko yana faman washe baki yana jin dadi nace kaiya anyi ba,ayi ba kenan mutum kamar ya Addil Allah ya hada da wanan kalar macen kuma ?

Yar gayuce ta fada amma hade da rashin kunya ko gayun nasune yake jawo masu rashin kunya oho saidai mazan dake son su basu ganin hakan.

Basu jima suka tafi ina gefe daya lafe ina kallon ikon Allah saida suka tafine kowa ke fadan albarkacin bakinsa kan yarinyar nasa nikan ina tsoro ban furta komai ba nabarwa cikina mamaki.

Aiko labari har kunnen iyayyen mu yakai nan hjy malka aka samu abin fadi don tun mum bata gane ba har ta gano ta tsureni tana tambayana amsa daya na bayar shine kila bayan fitowana sukazo.

Wanan kalman ya rabani da kowa lafiya ana gobe suna aka sallamo su Anty suka dawo gida har lokacin uban yaron bai tako yazo yaga dan nasaba.

Ko hakan yasa anty Nafisa yin sanyi ba kilama don gaskiya abin yana damunta sosai don tun tana boyewa har ta fitar muna da damuwanta fili nida iya da muke dakin wanda ba komai ya dameta sai rashin radawa jaririn suna da uban bai aiko ba.

Nan ta gane lalai furcinshi akansu da gaske yake har dan ya yafe mata ke nan yake nufi wanan nasan yasa hankalinta tashi adaren sunan.

Don ba itaba har mummy lokacin jikinta yayi sanyi da zancen don ta rage yawan rigiman da takeyi da farkon haihuwan sun koma shiru shiru yanzu.

Ashe bamu sani ba daddy yaci masu mutunci daga uwar har yar nata don yakira shi habib din kan zancen sunan ya so gayawa daddu din zancen banza akan anty nafisa din shine shi kuma ya sauke haushin hakan akansu da yadawo gida.

Bayan ya fitane nashigo nan ne take muna korafi nida iyan mai kula dasu shigowan ya Addil gidan yasa muka danji sanyi inda yace suna kan za,ayisa don ba za,abar yaro ba suna ba ai hakan saiya zamo abin kunya ga family tunda yana da ubansa.

Ga daddy yayi rantsuwan cewa bai yankawa yaron rago da kudinsa duk nan takewa yaya din complain yace yaro kan yana da gatansa ai don bai fado a gidan banza ba .

Shi dai da ya mayar da kansa dan iska yaje duniyace ai zata bashi darasi komai dadewa bayan ya gama lalashinta yake tambayanta sunan da take so ta sanyi dariyan yake kafin tace ga uwarsa nan zeey ka tambayeta sunan da sukeso.

Farat nace yaya kasa mashi mohammad don Allah mu dinga kiransa da Amir baiyi magaba ba bayan dan kalloni da yayi sai washegarin suna kowa na zaman darr sai gashi ya shigo yana fadin suna da Mohammed rago biyu manya aka yanka.

Sai akwatina set da aka shigo dasu wai inji uban da wanda komai na baby da uwa ansaka aciki daya kai wajen Dada ta kawo ko mum bata san yayi wana hidimar ba don ya hana yar uwarshi kukan zuci mai yawa.

Albarka yasha shi wurin kowa wanda bakin mummy ya mutu mutus da ganin kayan idan ba dan gida ba yadda kowa ke fadi idan yashigo yaga kayan zasu tambaya wanan kayan sunane ace masu ehh.

Zakiji sunce gaskiya yayi kokari haka akai suna kowa na farin ciki da yamma akai walima anci ansha an raba abubuwa kamar ko wani suna aka watse.

Da daren kuma wanan budurwan nasa ta zowa jariri da nata gudun mawan shake da leda don ko Pampers har hudu nagani a cikin kayan.

Ranan kuma bata tafi ba saida tabi su mum ta gaidasu taba kowa turmi daya daya har Dada wai na fitan suna wanda kowa yasan aiki ya Addil ne hakan.

Sani mum bata so yasa hjy mummy kama zancen kamar da gaske wai danta yayi dace da mace ta gari gaskiya wanda kowa yasan bana Allah takeyi ba hakan da takeyi dayan biyune.

Ko dai don rufawa yarta asirine da yayi ko kuma akwai abinda take kokarin kullawa gareshi nan gaba don danin halin mummy din da kowa yayi.

Mun dora abubuwan shagalin sunan da akayi wanda har ita maijegon ta dora hakan yasa shi uban dan gani a status dinta har yabi bayan kwana kamar ukku da suna saiga yan gidansu sunzo.

Da nasu kayan suna wanda ba wani abin azo agani ciki kuma wai sunan da Sani sunan kakansa Dada ko ta hausu tace su dauki kayansu su tafi yaro ya rigada yaci sunanshi dama mohammadu daga iyayyensa masu kaunarshi.

Mum ce tasaka baki har suka danji sanyi aka karbi kayan da sukazo dashi din daga bangarensu suka tafi tsomai tsomai dasu da kunyan da dan uwansu yaja masu.

Haihuwan nan na anty Nafisa yasa innan mu zuwa gidan akai akai wanda zuwanta kusan uku duban maijego da danta bayan suna kuma suka dauke kafafun su don gudun magana.

Ganin angama shagalin buki lafiya yasa na mayar da hankalina kan karatu na da yanzu saura kiris mu kare gaba daya mu fada wani matakin a yadda nakewa kaina fata nan gaba.

Don ganin yadda su Mairo suka maimaita shekara yasa ko ysushe ina addua Allah ya taimakeni inketare nawa ba tare da tabgardan komai ba

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[2/15, 08:01] Maman K: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

19

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Tayi jidalinta ta fice don ya Addel dayayiwa mum signal da ido akan ta kyaleta don Allah kada ta biyewa shirmenta na banza su zama daya wanan yasa mum din kyaleta badonshi ba ita ta iya biye mata sosai.

Ga mum irin masu soka magana dayace ya tsaya wa mutum a rai kalma daya biyu zuwa ukku zata fada da zaisa mommy jininin wata da watani agidan.

Batan fitan ta kaina suka juyo ranan mum tayi min kaca kaca saida ya Addil ya kwaceni ya nunawa mum aiba laifina bane tunda bazan iya cewa bazanje ba don ita din ba sa,ata bace amma da akai hakan yafi ai.

Ranan ban koma gun maijegon ganinsu ba gashi tana ta aike da bugo waya nazo amma fir naki na shareta har takaiga bugowa mum waya tana nemana.

Hakan yasa dole da dare na dan shiga na lekasu ban jima ba kuma na sulale tana bayi na fito nadawo part din mu hakan yasa da saffe ina kitchen sai gata ta shigo da kanta tana fadin ina mum ?

Hjy mum nazo naji dalilin dayasa zeey take gudun danta tun jiya mum dake daki ta fito acikin mamaki tana kallonsu.

Tace ina kuka fito haka tace gashi na kawowa uwarshi shine don tun jiya tayi muna yaji bansan abinda mukai mata ba shine mukazo biko.

Murmushi mum tayi tana karban jaririn a hannun uwarshi tace kinsan hjy malka idan ta tashi abinta bata ganin gaba balle baya nan tazo jiya da safe ta kare muna zari.

Mummy din nikan nayi tunanen akwai matsala tace wallahi muna zaune da dan uwanki sai gata walahi Allah dagashi har mama din amma sai gata tashigo da cin mutumci wai yayanki na nufin kada ta saka mama komai ko yana nufin wani abune dayake kokarin kulla mata sheri ta kwashe zancen yadda akayi ta fada mata sai hakkuri take ba mum din.

Karshe dai mum tace ta kyaleta kada taje tayi mata zancen kuma rayuka sukai ga baci ga mutane a gidan ta kare da fadin tana nan zuwa idan ta gama abinda takeyi tana muna breakfasts ne.

Tamike tana fadin kizo kiga dinkunan da aka kawo min mu zabi wanda zan fara sakawa a ciki nace to cikin tashin dadin rai a nan tabar baby din zata fita saiga mairo ta shigo tana fadin mummy tace kizo ga mutane sun shigo ta juya kai tsaye bata ko tsaya gaida mum ba.

Ko yar uwan tayi mata fada sai gata ta dawo tana fadin sorry mum banko gaida ke ba mummy ta azalzaleni nakira mata anty har na rudi karbi dan ki kai tunda ga yan barka sun shigo .

Fuska ta bata kafin tace barshi kawai mum ni banga kowa a gidan ba zancen mummy ne kawai don Allah ta juya ta fice ta bar dan a hannun mum din.

Karshe dau zuwa din akayi aka karbi taron nasan ko ita ta aiko a karbeshi saboda rashin yarda da bata dashi a zuciyanta gudun ai masa wani abin wai.

Saida nagama da kitchen har girkin rana nayi wanka na shiga part din nasu don mu gaisa daita a falon ta take sun baza kaya ni banko kallah ba amma kiri kiri naji tana fadin rufe min kayan nan har anjima nagani.

Ina gaida ita na juya zuwa dakin anty Nafisa din tana zaune ita da wanan tsohuwar da Dada kunune irin na gargajiya a hannunta tana shana shigo.

Wallahi zeey baki da kirki sai yanzu kikaga daman zuwa har tela yazo ya wuce na dai bashi samfur yayi maki dogon buje da riga ko dogon riga kikeso nace a,a ina juyawa don gaida tsofin dake dakin.

Nan Dada take fadin bansan meya samu yar nan ba yanzu da bata son shiga mutane kamar da yanzu ma abin ya kara rikice mata in anyi magana tace karatu kamar al,hudahuda uwarta kuma ta kama mata.

Dada aiko ba zakice min haka ba na fada na juya zuwa wajen yaron yana barci amma haka na daukoshi ina dubawa ina kare masa kallon kwata hilla har uwar ta lura dani tace.

Wanan kallo haka zeey nace yaron nan naga kamar ya rame mun a ido kafin uwar tayi magana Dada tace keko dai yasha iskan duniya ya bazai rame ba.

A,a Dada yaron nan kamar baya da lafiya fa nake gani duba yadda ma yake numfashi a wahale ina dan juya hannun yaron a hankali daya tsohuwar tace mikoshi mu gani na mika mata ta karbeshi Dada sai fadi take wanan yar kamar tashin tsofi take fa.

Gaskiyan yar nan Dada yaron nan baida lafiya ikon Allah amma duk bamu lura ba wanan abinda ba a so gashi duk ya shedo masa a ciki zubur anty Nafisa ta mike tsaye.

Cikin rikicewa tana fadin ina mummy mu kaishi asibiti ke kwantar da hankalim ki abi sannu ina fita tayi daga dakin ko minti biyu ba,akai ba sai gasu tafe gaba dayansu a rikice dakin.

Anty Nafisa sai fadi take badon shigowan sister dakin nan ba ba wanda ya kula da hakan yanzu fa kuka dawo dashi tun dazun yana falo wurin ku ke iya ya akai haka kuma nan Dada ta tare da fadin kamar ya kuma ya akai haka ?

To hjy za ace gaku zaune amma baku gane hakan ba sai shugowan maamah saboda Allah bamu da amfani ke nan ko itako iya sai fadi take ita dai Allah ya turo ta gane muna dama.

Caraf anty Nafisa ta karbe yaron daga hannun tsohuwar tana fadin sister dauko min jakata mu tafi wanan ba zai fissheni ba da sauri na juya saman gado inda jakkarta yake ina kokarin daukowa naji uwar tace mata.

Ke banson rashin kunya kinji dukkan mu nan bamu damu dashi ba ke nan kike nufi ko me ko sai kin nuna muna ke kika haifesa tau gamu ganin ikon Allah dai Dada ta fada tana tashi.

Sai rana naji mummy tayiwa anty Nafisa fada irin gyara kayanka a gabana duk zamana dasu gidan ban kare mamakin haka ba saida naji tace ke mairo kira min hjy kubura.

Nace ashe ko mugu yana da rana ke nan yau ga ranan mum ke nan ashe itama mum a rude tazo hankali tashe part din tana fadin asha meke faruwane kuma ?

A nan dai aka yanke shawaran tafiyansu da mum din asibitin bayan an kira daddy an sanar dashi yace su hadu asibitin gasu nan zuwa suma hankalin gida ya tashi dan Adam mai tsada da kima kan dan jariri hankalin kowa ya daga a gidan mutum ke nan.

Bayan tafiyansu dakin nakoma na gyara masu shi tsab don a karshe hjy mummy itama ta bisu don bata yarda ba hakan ya ban dama tsayawa na gyaro mata dakin na rufo na koma part din muna jiran abinda za ace game da yaron.

Gashi duk aka tashi magana za,ace ai zeey ce tagane hakan ga tsofi basu gane ba sai kuma hakan yake sosa min rai idan na tuna don halimatu a gabana ta fara fadin kwarkwasa ke nan ai tasan komai ita dama.

Watau har abinda ba ai tsamani ba duk na sani ke nan take nufi amma na kyaleta don ba lokacin musayan baki bane ana cikin tashin hankali haka din.

Su mum suka dawo suna fadin an basu gado don an kwantar da yaron wai ya fito da shawara har tayi masa yawa a jiki ta hudu shi wanda suke kira da Jondis.

Acewansu likitocin sunyi fada sosai na rashin kawo yaron da ba,ayiba da wuri akabarshi gida haka ciwo na batun masa illa.

Banda wani aiki don haka mum tace in shirya in bisu naje don hankalina ya kwanta a can muka samu su maito dasu halima da Asiya don banko sanda fitansu bani.

Ina shiga Anty ke fadin ehh sister badon ke dake da kula ba da yaron nan ya mutu muna zaune ana faman surutu a daki ba wanda ya kula da hakan gareshi.

Mum tace haba bai mutuwa ai sai idan kwanansa sun kare wahala dai akewa gudu amma kowa ya mutu dama iya abinda ya debo ke nan a rayuwanshi.

Mun jima a nan take min hira cewa dan iskan uban nasa dazun daddy ya buga mai waya yana sanar mashi gamu asibiti sai cewa yayi Allah ya sauwaka kawai.

Mum ta kara kada baki garemu tace to me zaice Nafisa dole dama ai addu,an samun lafiya zai masa tace ki bari kawai hjy mum habib dan iskane na gaske dama ya fadi ya barmin cikin duk abinda na haifa inje inji dashi tunda nace ban yarda a zubar da cikin ba.

Kinga dan nan dayaki anty idan Allah ya bamu raida lafiya wata rana shine mai tallaban rayuwansa saukin abin agaremu bakece baki kaunar yaron ba ai kuma yan family din mu kowa yana kaunarsa kauna mai tsanani.

Yarone fa amma ki duba daga dakin nan har waje duk yan uwane suka taru akan dan nan insha Allahu sai yaji kunyar wanan abin dayayi wata rana.

Kwatsam ya hafiz ya fado dakin kallo daya nayi masa na dukar da kai ina tuna irin yanayin da naganesa a ciki a dakinsa sai naji girmansa da kimarsa da nake gani yazube min ga ido.

Gashi tsab zakice mutumin kirkine a fili ashe a boye mutumin banzane irin na bugawa a jarida din nan muryan anty nafisa ce yakatse min tunane a lokacin take fadin wai baki gaidashi ba sister.

Firgigit nayi tare da fafin wa hafiz mana ta fada nace ai nagai dashi daya shigo na kara fadin ina wuni tsuki yaja yaci gaba da magana da yar uwarshi ya fita zance na.

Mummy ce ta fado dakin da kawayenta kallon yadda muka hade kai da anty muna magana kus kus kus ga iya zaune a saman tabarma bata ko jin me muke fadi tashigo.

Kallo mu ta sakeyi tana fadin to rakwato aisai ki fita ga bakina nan sunzo duba yaro kar kuma a kaimu haba mummmy please ki dainawa yarinyar nan haka a gaban mutane mana sai a dauka haka halintane ai yar ta fada ciko bacin rai.

Ban san ya sukayi ba don na bi driver nakoma gida sai washegari na sake lekasu asibitin koshi da nace ba zanje ba don mummy saboda nagane dai ta tsaneni a zuciyar ta.

Banje da niyar zama ba muna zaune saiga ya Addel da budurwansa sun shigo wanan gulma ya zaunar dani muna kallon ikon Allah yadda ake soyayya nami sai a barshi kawai akan soyayya don idonsu kan rufene a lokacin.

Donko abinda ya Addel keyi ba zakice shine ba ko don iyamu yarane a wajen lokaci saiko yan tsofin dake zaune daga waje ga yarinyar da alama ba kunya gareta ba.

Don ko garemu katsinawa wanan rashin ta idone mutum yazo gun dangin miji tun baishigo ba yana wanan kaudin haka ba nuna alkunya ga kowa sai nuna sani da iya tun a nan ta sure min a zuciyana.

Shiko yana faman washe baki yana jin dadi nace kaiya anyi ba,ayi ba kenan mutum kamar ya Addil Allah ya hada da wanan kalar macen kuma ?

Yar gayuce ta fada amma hade da rashin kunya ko gayun nasune yake jawo masu rashin kunya oho saidai mazan dake son su basu ganin hakan.

Basu jima suka tafi ina gefe daya lafe ina kallon ikon Allah saida suka tafine kowa ke fadan albarkacin bakinsa kan yarinyar nasa nikan ina tsoro ban furta komai ba nabarwa cikina mamaki.

Aiko labari har kunnen iyayyen mu yakai nan hjy malka aka samu abin fadi don tun mum bata gane ba har ta gano ta tsureni tana tambayana amsa daya na bayar shine kila bayan fitowana sukazo.

Wanan kalman ya rabani da kowa lafiya ana gobe suna aka sallamo su Anty suka dawo gida har lokacin uban yaron bai tako yazo yaga dan nasaba.

Ko hakan yasa anty Nafisa yin sanyi ba kilama don gaskiya abin yana damunta sosai don tun tana boyewa har ta fitar muna da damuwanta fili nida iya da muke dakin wanda ba komai ya dameta sai rashin radawa jaririn suna da uban bai aiko ba.

Nan ta gane lalai furcinshi akansu da gaske yake har dan ya yafe mata ke nan yake nufi wanan nasan yasa hankalinta tashi adaren sunan.

Don ba itaba har mummy lokacin jikinta yayi sanyi da zancen don ta rage yawan rigiman da takeyi da farkon haihuwan sun koma shiru shiru yanzu.

Ashe bamu sani ba daddy yaci masu mutunci daga uwar har yar nata don yakira shi habib din kan zancen sunan ya so gayawa daddu din zancen banza akan anty nafisa din shine shi kuma ya sauke haushin hakan akansu da yadawo gida.

Bayan ya fitane nashigo nan ne take muna korafi nida iyan mai kula dasu shigowan ya Addil gidan yasa muka danji sanyi inda yace suna kan za,ayisa don ba za,abar yaro ba suna ba ai hakan saiya zamo abin kunya ga family tunda yana da ubansa.

Ga daddy yayi rantsuwan cewa bai yankawa yaron rago da kudinsa duk nan takewa yaya din complain yace yaro kan yana da gatansa ai don bai fado a gidan banza ba .

Shi dai da ya mayar da kansa dan iska yaje duniyace ai zata bashi darasi komai dadewa bayan ya gama lalashinta yake tambayanta sunan da take so ta sanyi dariyan yake kafin tace ga uwarsa nan zeey ka tambayeta sunan da sukeso.

Farat nace yaya kasa mashi mohammad don Allah mu dinga kiransa da Amir baiyi magaba ba bayan dan kalloni da yayi sai washegarin suna kowa na zaman darr sai gashi ya shigo yana fadin suna da Mohammed rago biyu manya aka yanka.

Sai akwatina set da aka shigo dasu wai inji uban da wanda komai na baby da uwa ansaka aciki daya kai wajen Dada ta kawo ko mum bata san yayi wana hidimar ba don ya hana yar uwarshi kukan zuci mai yawa.

Albarka yasha shi wurin kowa wanda bakin mummy ya mutu mutus da ganin kayan idan ba dan gida ba yadda kowa ke fadi idan yashigo yaga kayan zasu tambaya wanan kayan sunane ace masu ehh.

Zakiji sunce gaskiya yayi kokari haka akai suna kowa na farin ciki da yamma akai walima anci ansha an raba abubuwa kamar ko wani suna aka watse.

Da daren kuma wanan budurwan nasa ta zowa jariri da nata gudun mawan shake da leda don ko Pampers har hudu nagani a cikin kayan.

Ranan kuma bata tafi ba saida tabi su mum ta gaidasu taba kowa turmi daya daya har Dada wai na fitan suna wanda kowa yasan aiki ya Addil ne hakan.

Sani mum bata so yasa hjy mummy kama zancen kamar da gaske wai danta yayi dace da mace ta gari gaskiya wanda kowa yasan bana Allah takeyi ba hakan da takeyi dayan biyune.

Ko dai don rufawa yarta asirine da yayi ko kuma akwai abinda take kokarin kullawa gareshi nan gaba don danin halin mummy din da kowa yayi.

Mun dora abubuwan shagalin sunan da akayi wanda har ita maijegon ta dora hakan yasa shi uban dan gani a status dinta har yabi bayan kwana kamar ukku da suna saiga yan gidansu sunzo.

Da nasu kayan suna wanda ba wani abin azo agani ciki kuma wai sunan da Sani sunan kakansa Dada ko ta hausu tace su dauki kayansu su tafi yaro ya rigada yaci sunanshi dama mohammadu daga iyayyensa masu kaunarshi.

Mum ce tasaka baki har suka danji sanyi aka karbi kayan da sukazo dashi din daga bangarensu suka tafi tsomai tsomai dasu da kunyan da dan uwansu yaja masu.

Haihuwan nan na anty Nafisa yasa innan mu zuwa gidan akai akai wanda zuwanta kusan uku duban maijego da danta bayan suna kuma suka dauke kafafun su don gudun magana.

Ganin angama shagalin buki lafiya yasa na mayar da hankalina kan karatu na da yanzu saura kiris mu kare gaba daya mu fada wani matakin a yadda nakewa kaina fata nan gaba.

Don ganin yadda su Mairo suka maimaita shekara yasa ko ysushe ina addua Allah ya taimakeni inketare nawa ba tare da tabgardan komai ba

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[2/17, 08:02] Maman K: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

20

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Alhamdullahi zance a yanzu don duk wani challenges din rayuwa da nake samu a gidan daddy hakan bai hana in tsaya inyi karatu ba don ko naga abubuwa kuma naji da kunnuwa amma haka na daure na fuskanci karatuna.

Sai gashi Allah ya taimakeni na fito da sakamako maikyau da har daddy din ke alfahari dani akan hakan wanda wanan abin a wani bangare yayi min dadi wani bangaren kuma baimun dadi ba.

Don ko yaja min bakin jini a cikin gidan sai bangaren mune kuma suke nuna min farin ciki sosai a kan hakan suna yabawa.

Mun gama da sati biyu lokacin akai bukin auren ya Addel wanda asha kwama cala a lokacin bukin don hjy malka ta dauka cewa daddy ne ke masa hidima wanda hakan har ya kaisu da zama da manya akan bata yarda da abinda Alh yakeyi ba tunda shima yana diyan daya haifa da cikinsa.

Hjy malka bata da kunya ta ido Daddy baiyi magana ba saida yace a kira hjy mum don abune daya shafi family tazo dashi don haka suka bukaci da mum tazo falon a zauna da ita.

Bayan mum da Dada sun shigo daddy ya kalleta yace hjy kubura ina son ki fadi tsakanin ki da Allah ya mukayi da Aliyu kan zancen aurensa daya nace sai wanan yarinyar .

Kallonshi tayi cikin mamaki tunda abin sirine daya shafi ahalinta a lokacin yace maimaita don Allah mum din ta dan gyara zama tace ehh to kace ba ruwanka da zancen auren iya sadaki zaka biya masa tund yaki bin akidarku na gida sanan bayan hakan yasani zaka kara mai mata muddin ana raye yar gida kamar yadda yake ga al,adan nan gida lokacin zakai masa naka auren kamar kowa .

Hannu ya daga yace ya isa haka kunji ko bayan wanan me suke shiryawa me suka hada wallahi ban sani ba kayama da kike zance nasan akansane ga hjy kubura ta gaya min nazo nagani sungama hadawa nace sukai Allah bada sa,a koba haka akayi ba ke kubura ?

Allah da Annabinsa sunyi gaskiya da sukace zato zunubi koda ya zamo gaskiya a wajen bawa kin daiji hjy malka ba hannun Alh a wanan zancen ashe .

Daddy ya dauka da fadin jiyan nan yazo yana fada min cewa yasai gida a Nasarawa nima da mamakin hakan na kwana a raina.

Saidai banyi mamaki ba duba ga inda yake aiki yanzu a matatan mai na kasa koda yayi hakan zai iya yin fiye da hakan ma idan yaso.

Wani gwauron ajiyan zuciya mummy ta sauke dayan babansu yace ai a haifi da arziki yafi a mutu abarmai gado wanan gaskiyane kowa nan ya sani.

To amma waya dorashi a hanyan hakan ai kaine dai Alh kana da daman yadda ka samu nashi aiki a nan wurin samu suma sauran ka sama masu ai kamar yadda shima kai masa hanyar.

To ban samoba din don bansan inda ake samuwa ba ko kina nufin sai kin jefawa diyana kiyayyana dana dan uwansu a kanmune kwadan ki zai fada.

Bansan ya yayi ya samu abinsa ba illa takarda daya zo muna dashi gidan nan na aikinsa danki dana samuwa aiki ai rainaw kukayi ashe hangen nesa kuke masa wayasan na samuwa hafiz aiki a gidan nan bayan ke ?

Ko ita kuburan bata da dan dana haifa da itane da yake son aiki baga Nasir nan zaune a gida ba shima ya gama nasa karatun ?

Yanzun dai abar zancen tunda angano gaskiyan yadda lamarin take kowa yasan yadda zuciya take bata da kashi ke hjy malka kinyi kuskure ai kafin ki taramu nan yakamata ki tambayi mijin ki yai maki bayanin komai.

Kona tambayesa aiba fada min gaskiya zaiyi ba don haka na kiraku a nan hjy mummy ta fada cikin jin nauyi da kunya da batayi tsamanin zai koma a kanta ba lokacin.

Ba zan fada ba tunda ita yar uwar zaman naki bata taba tsareni kan harkuku tasani a gaba ba duk da tasan ina tauye ta wani lokacin ta barmu ga Allah dani dake.

Baba kun gama dani in tafine mum ta fada tana mikewa don takaicin daya rufe mata idanu lokacin Dada tayi magana tace ina zaki ai ki tsaya kisha labarin irin cin zalinki da sukeyi a gefe daya tunda yau ranan tonon sili a garesu.

Murmushi Mum din tayi tana fadin niga Allah na dogara don shine gatan mu nida yaran nawa duka tana fadin hakan ta juya ta fita nan yan uwa dasu Dada suka hau kan mummy din da fada akan bata kyauta ba tana hassada da dan yar uwarta kan duniya.

Akarshe dai dole taba daddy din hakkuri su babanane suka samu mum a part dinta suka bata hakkuri akan abubuwan da ake mata gidan ana danne mata hakkinta din.

Inda daddy Enugu yake cewa ai gashi duk sukayi sai abin ya koma tsakaninsu duniya tajisu akai ga tonawa juna asiri da sukeyi akarshe kowa yajisu.

Yanzu kan da buki yazo suga irin hidimar da akeyi a part din hjy mum sai bacin ran ya yawalta daga ita har yaranta suna nuna bakin ciki kan abindake faruwa agidan suna kallo.

Saboda basu taba zato ko tsamanin hakan ba daga bangaren hjy kancewa wani daga part din cikin yayanta zaizo ya shayar dasu mamki tun ba,aje ko ina ba a rayuwa.

Allah ke nan kadogara dashi ya jarebaka ta nau,in rayuwa a hanyoyi daban daban akarshe inkayi mai imani da yarda da kaddarace sai ya sakama a ta hanyar da baka zataba haka ubangiji yake lamarinsa a inda yaso.

Abu namu maganin a kwabemu bukin mune bukin part din mu gaskiya ko a sanka wajen daya ashe asalne mai kyau sanina a yar mum kwara daya datakeji dani na zamo kamar igenta inji hausawa yasa min farin jini ga masoyanta dama kowa mai kaunarsu ita da diyanta.

Wanan daman ya haskani a idon mutanensu na arziki inda wasu ke dauka koni din ma diyar cikintane ai wanda suka sani kuma suke daukata da daraja a idanunsu na zamana a wajenta.

Haka zama din ya kulla wani halaka mi girma tsakanin mum da mahaifiyata da yanzu shawaransu guda kasancewan su gari daya da aka fito.

Hakan yana taba zuciyan hjy malka da har yakai tanawa inna tuhumar dabai dace ba kindai san yadda kishiya kan zargi duk wata wace ke tare da kishiyanta koda kuwa tasan ba wani abin asha suke gudanarwa ba ga amintakan amma wanan kishin yakan koma ga aminiyar kishiyan a hada da ita.

Buki yayi kyau sosai anyi program kamar na sauran buki anci ansha an koshi a taron baki sunzo daga gida anyi kara ga hjy mum da mijinta marigayi daya rasu har na da bangaren daddy kowa ya koma gidansa lafiya aka bar amarya da ango da halaiyansu da zasu fahinta a zama yanzu tunda an zama daya.

Kamar yadda manya kance so ya kare sai zaman hakkuri duk wace tayi aure sai an rakata da wanan kalman walau a ciki musulmi ko kirista kalman dai dayace da ake fada kan a zauna lafiya kosu shi aka fada akansu.

Dan anty Nafisa yayi wayau sosai haka yasa ta fara neman aiki da zata dan fara kafin abubuwa su koma mata daidai arayuwa.

Inda tayi sa,a inda ta fara aiki a B U K suka kara daukanta aiki karo na biyu don tana da hazaka sosai akanta lokacin ilimi ake nema ba nasaba ba kamar yanzu donshine bata sha wani wahala wajen komawa aikin ba.

Hakan yasa tunda muna gida bamu fara karatu ba renon danta Amir ya dawo kaina da farko mummy ta hana hakan sai daga baya data kula ana bar mata da a wahalce ta daukoshi take kawo muna part din mu inda bai fita sai idan ta dawo da yamma an masa wanka akai mata abinta washe gari haka kuma idan zata fita zata kawo munashi.

Ni da mum ke faman dawainiya da yaron da yanzu yayi kyau sosai saboda kulan da yake samu a wajen mu din.

Inda yakai har yaron yana neman ya yaye kansa daga nono don ko uwar ta dawo daga aiki bai damu da nono ba tunda yana da koshi hakan yasa itama take neman yayeshi din lokacin.

Nan kuma mummy ta kawo tsurkun cewa a daina dura masa abinci abarshi yasha nononsa ya koshi sai a kama karamin yaro ana dinkira masa abinci har yazo yai masa illa kuma a karshe.

Zance wasa wasa har yakaisu gaban daddy don mum tayi fushi da kalamin hjy malka inda tace daga yau idan anty zata fita ta barshibgun hjy malka din don kada a kashe mata yaro a nan din wajen mu.

Fafir ranane taki karbanshi ta kuma hanenima karbansa tunda kona karbeshi ai dole a part din tae zan zauna dashi ganin irin rikincin da uwar keson jefata ciki yasa kai tsaye ta samu daddy afalonsa ta fada mai abinda ke faruwa ranan.

Baiyi kasa a gwiwa ba ya kirasu suka sameta tsugune da yaron gabanta da alaman har kuka tayi a gaban daddy din kan abinda ke faruwa dasu nan ya bukaci ta kara fada mai matsalan ta kara maimaitawa a gaban nasu.

Kafin takai karshe uwarta cabe zancen da fadin kalai kan angama dake baby ta yarda baki iya fita inbaki arziki ba nan gabama kina iya cewa ni ba uwarki bace.

Zancen banza ke nan ana magana zaki dauko muna wani zance can ki jefo cikin magana ita zancen danta da hjy kubura tace basu karba tazoyi ke kuma kina kawo muna wani zance a nan.

To Alh banda haka tunda tace basu karbanshi ita bata da uwace ko ba masu daukanshi a wajena idan ni banda lokacin hakan yace ballema kina da lokacin me zai hana ki kula da dan yarki kuma.

Tunda kin rai karan da ake masa can sai lokacin ta gano ba goyon bayanta daddy yakeyi ba ashe magana ya fada mata a dunkule ashe .

Yace ke kin gaza masu kula dashi kuma kina kokarin zarga masu sherin ki da kika iya akansu ko nine aiba zan karbeshi ba ko kin manta lokacin da take bar maku yarin kuka tashi illanta matashi ?

To baby abinda kike nema kin samu a tozartani gaban kowa yanzu kin samu ai saiki zuba ruwa kasa kisha ke nan kanki aka fara haihuwane da baki da kunya ko kadan akan danki ?

Ai bata yar ba don tarbiyan data samu ke nan gara itama tana kara da har ta amince tana kaishi wajen su kubura ko kin mantane in fada maki yanzu ?

Abar zancen nan ke Nafisa kiyi hakkuri kibi zancen mahaifiyarki a zauna lafiya nidai Allah ya gani ko ina sheri banga abinda zai kaini cutawa wanan da mala,ikan Allah ba don Amir har meya sani.

Jin mum din ta kira sunansa yasa yaron yasake nonon dayake sha ya taso zuwa wajen mum din ya haye jikinta daddy ya kwashe da dariya yana fadin duba yanzu ki gani don Allah.

Don Allah Dad aba mum hakkuri ina lantti zuwa wajen aiki tayi hakkuri subar zancen nan a karban manshi tunda dasu ya saba anty Nafisa din ta fada tana kallon mahaifin nata.

Ni banda matsala kin sani abin zargi ko tuhumane banso a rayuwana in bashi ba mai zai hana in karbi Amir to ki karbeshi tatafi gun aikinta daddy ya fada a cikin bata umurni a lokacin.

Yace mika mata kayanshi ki tashi ki tafi hakan tayi kamar yadda daddy ya fada din ta mike tana masu saita dawo yaron bai ko kulaba yana jikin mum kamar yadda ya saba yana wasanshi.

Bayan fitan anty Nafisa daddyn ya kallesu yace waike malka sai yaushe ne zaki barmu a zauna lafiya a gidan nan ko sai ranan da hafiz yayi aure kikaga kin kai ga sarakuwa zaki daina hakan .

Ai ba gatse don yadda kowa yayi aure shima din yi zaiyi insha Allahu balle aso fada min magana a fakaice haka niko nasan yi zaiyi tunda nike da dana da ikonsa sai ta kalloshi.

Mun na ganin haka ta mike da yaron tana fadin muje in kaika wajen uwarka ni islamiya zan tafi yanzu bata tsaya jinsu ba tafice abinta nan sukayiwa juna kwal suka kuma shirya.

Nikan ina barci nake jin alaman ana tabani don daga kwanciyan da nayi na boyewa anty Nafisa kar in dauki yaron sai barci yayi gaba dani a dakin mum din.

Na dinga jin ana dan tabani sama sama ga nauyi da dadin barcin safen daya daukeni haka na kama tsinkayo gwalancin yaron a gefena.

Idona na bude da kyat ina fadin kai kuma ina ka fito nan mum dake tsaye tana saka hijab tace dani gashi nan dai maki ai uwarsa bata yarda ba ai takai karab mu wajen daddyn kune.

Da yake uwarta bata da kan gado can na barta tana babatu nafito don kada shirmensu da bai karewa kullum yasa in makara ban fita ba tara ya kusa yanzu.

Zaune na mike ina kamo yaron zuwa jikina nace kai matsalan mum harda yaro duk wanan wahalan ita bata gani sai kuma zargi da sheri ya biyo baya.

In batayi ba ai bata jin dadi munta fada tana daukan jakkar hannunta bata da kunya ko yanzu a falo sai shirme da rashin kunyavtake zuba min wanan ina tausayawa wanda zai zauna da ita wallahi.

Shiru nayi na dan lokaci kafin tace sani nina fita abincin ki yana falo yau dan wake nakecson in mun dawo muyi akwai komai na tanada jiya na sayo kayan hadinsa a islamiya.

Sai kin dawo za,ayi din na tambayeta tace ehh to ai ina zaki iya kwabinsa ko karki manta ki saka kuka dan madaidaici da zai isa saiki kwaba ki bashi madaransa a daina bashi abinci tunda shine basu so.

Kallon yaron nayi ina shafo kansa nace wanan aiko ban bashi ba shi zai saka hannu yaci da kansa indai abincine wanan madaran yanzu bai masa ai sai an hada mai da abinci.

Ai gaku nan dai ta fada ina mata adawo lafiya shima yaron ya daga hannu alaman bey bey a gareta na kamo hannunsa ina dariya tarw da rungumesa a jikina ina jin son yaron yana shiga zuciyana.

Falo muka dawo na karya shima yaci dankali da ruwan tea sosai lokacin kafin in daukeshi in goya a bayana muka fara gyaran gidan da banyi ba saboda shigewa dakin danayi na kwanta da bai mun rana ba kuma.

Koma na gama lokacin yaron yayi barci a bayana na shimfide shi a dakina saman gado na shiga wanka har na fito na shirya yana kwance yana barcinsa hankalin kwance.

Har mun ta dawo ta sameni a kitchen take fadin ina dan naki halan yayi barci ko nace tunda mukayi breakfast yake barci har yanzu dan murmushi tayi ta juya ta fita ta barni a kitchen din naci gaba da aikina.

Na kusan gamawane takawo min shi wai ya tashi ita kuma sallah zatayi na karbeshi na fito nan na cire mai kaya na daurayeshi kafin na canza masa tufafi na zauna bashi abinsa yaci saida ya koshi.

ZAINAB IDRIS MAKAW

[2/18, 19:48] Maman K: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

21

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Fitowan jerabawan mu ya fara jagula komai a rayuwana don ko jerabawa ya fito kowa na kururuwan jerabawan yayi kyau kamar yadda na fada da baya gareki.

Wanan yasa Hjy mum samun daddy akan zancen karatuna tunda jerabawa yayi kyau sosai zan iya shiga jami,a ai dan dagowa daddy yayi zaune kafin yace ina sane da hakan a raina kubura.

Saidai tsarin nawa a yanzu so nake ya canza dubaga lamarin Nafisa agidan nan ko ban fada ba kinsan dai abin yana damuna azuciya zamanta haka a gida babu aure yana cimun zuciya wallahi.

Donshi nake son na koma tsarin iyayye a yanzu bance ya mace bata boko a gidana ba a,a zasuyi amma iya secondary zasu tsaya agidan nan na aurar dasu su karasa karatun su can a dakunan mijinsu idan suna son haka ban hana ba kuma zan taimaka idan ya kama.

Wani ajiyan zuciya Mum ta sauke kafin tace wai akwai matsala yadda mama ta kwallafawa karatun nan rai yanzu kuma ace aure za,ai mata da rana tsaka gaskiya akwai matsala don ita ko irin dan saurayin nan da sukeyi sam bata da ra,ayin hakan ita.

Wanan ba matsala bane don lamarin na riga dana tsara komai azuciyana lokaci kawai nake jira in gabatar maku kudasu ku sani don haka zancen karatu a yanzu a jayeshi kawai sai indan sunyi aure .

Mum tayi shiru a wajen tana faman tunanen abinda zata fada min da yadda zan dauki zancen kafin ta motsa tace duk da hakan Alh ai za,ayi sayen form din kada shekara ya wusu kuma ko ?

Wanan abari sai nayi tunane zan zauna da yan uwana mu tatauna akai muga yadda ya dace ayi din tace Allah yasa muji alheri tana nisawa ya amsa da amin shima.

Sam mum bata fada min komai ba taja bakinta tayi shiru saidai abin yana ci mata zuciya har dai idan ina haukana ko shirme kome aka ban zan boye nace saina fara fita makaranta zanyi amfani dashi.

Nikan bata tausayi da har yakai ta kasa boye hakan azuciyanta don yanayinta kan canza idan ina zancen karatun har yakai nima na fara gane hakan.

A yanzu don nakanyi tunanen ko bata aon nayi karatun ne yasa haka to me zaisa haka kuma bayan itace ta kara karfafamin rai ga wanan karatun har ta zaba min likita take son in zama ba lauya ba kamar yadda nace.

Ranan muna hira da ya Nasir daya samu aiki a world bank branch dake nan Nigeria wanda dan uwansa yashiga ya fita aikin ya samu ta bin hanyoyim ganin manya har abin ya tabbata yanzu suke zance a kai da mahaifiyarshi.

Nikan na huta ai mum idan na kare karatuna ba saina sha wahalan neman aiki ba tunda gani dasu yaya a hannu kalloni mum tayi tana murmushi tace aikan ke ai yar lelece mama don dole su samo maki aikima ko ban raye kuwa.

Balle kina raye mum sai tsufa na futuf zai rabamu insha Allahu sai na kaiki makka da kudi ko in daukeki mu koma wajena ki huta da hjy mummy da fadanta.

Humm wawiya shi mijin naki zai yarda da hakan ai saiki bari sai kinyi karatun kafin ki tsara haka bayan daddy yace baku karatu aure zai maku dukkanku.

Wani zabura nayi don gabana daya fadi lokaci guda nace aure na kallo mum din nace wai mum haka daddy yace ?

Tace rabu dashi kinji ai harshi idan yana ganin ya tsirane to baka tsira ba ai don gaba dayan ku yace zai aurar dakune ba matan ba kawai da kake mata sheri.

Wani abu naji ya fito daga kafana zuwa kai lokaci daya na ji numfashina yana batun dauke min ga mum dake kusa dani ta fara gano hakan nan ta fara kiran sunana da dan karfi tana fadin mama fa ke mama yau ga tsiya.

Kaima Nasir da sheri kake meya kaika fada mata wanan zancen yanzu bayan kansan halinta akan karatun nan yadda ta kwallafa rai na fadama ina son har Alh ya saukone in rarasheshi ko zai yarda ta fara .

Kai kuma yanzu kazo ka fada mata haka kai tsaye baka kyauta min ba gaskiya ka tashi ka fita ka bamu wuri tunda banga abinda kake nema a nan yanzu ba.

Zubur na samu wani karfi yazo min na mike nashige daki sai lokacin na samu kuka yazo mi mai karfi ina toshe bakina kan hakan amma ban iya controlling din kaina dole sauti ya fito waje.

Hankalim mum ya tashi sosai bata iya shigowa dakin ba ranan nayi bakin ciki da nadaman kasancewana a karkashinsu nayi nadama babba a ranan.

Don da ace a karkashin kulawan iyayyena nake saibidan nace boko ya isa a bangarena don baba yai min alkawarin hakan tun ina karama wanan nahau na zauna a kai zancen mahaifina din sai gashi kuma yan zun yadda abin ke nema ya kasance dani kuma.

Haka na dauki tsawon lokaci mai nisa ina fama da kuka da tunane azuciyata har da tambayan kaina nayi towama zan aure ni da a tsawon tarihina ban taba yin wani saurayi ba kona wasa balle na gaskiya.

Wasa wasa har zaxzabi mai karfi ya sauka min ajiki nan na koma dunkule jina shiru da mum tayi ta leko bayan azahar tana fadin wai har yanzu fushin karatunne akeyi.

Rufe ta hangoni cikin bargo a kwance ikon Allah abin har yakai ga rufa hakane takaraso gareni tana fada tare da yaye bargon ido ya kadai min yayi ja sai rawan sanyi nakeyi ina neman taimako alokacin.

Salati ta saka tana fadin yau me zangani haka daga zancen kararu ki fadi ciwo haka meke damunki kuma haka lafiya lau kika tashi fa dazun ?

Aikuwa wani aman kummalone yazo min lokaci guda na yunkura da niyar zuwa bayi ai kafin nakai na sake har da guntun boli a wajen amai sosai nayi dan kunun tofiyokan danasha duk shi na amaye zalla alokacin.

Aiko ba zan gani ni kadai ba ta fada tana danna wayan dake hannunta anty nafisa ce ta kira lokacin suna tare da Dada a part dinta itace suka shigo da sauri tana fadin.

Hjy Mum maman Amir ba lafiya kuma gaskiya banji duriyanta ba yau mum dake duke tana goge aman ta dago tana fadin kedai bari Nafisa.

Lafiya kalau fa muka tashi da yarinyar nan me shegen bakin surutun nan Nasir ana zance yake fada mata wai Alh yace ba zasuyi karatu ba ai aure zai masu.

Shinefa zancem har yakaita da nadewa yanzu haka ni abin mamaki ma ya ban na rude kar yar mutane ta mutu nace barin kira mutanen gida su sheda.

Ai ba a mamaki da ikon Allah Dada dake bayan anty nafisa ta fada sai gani na bude bayin na fito ina makyarkyatan dari da sauri na nemi abin rufa na dunkule kaina.

Sama sama nakejin zantukansu akaina haka baisa na iya mikewa sai tashin hankali da zancensu ya kara ingizani ciki a lokacin donko Dada sai fada takeyi tana fadin.

Akan karatun boko da iyakarsa duniya za ki nemi kashe kanki a banza ki mutu mushe ki mutu kafira yarinya haka da shegen son karatu nagabama da sukai karatun meya tsinana masu ?

Nidai naji anty ta tallabani mun fita sai wajen mota wai ashe har suma nayi me karatu abin zai baki mamaki kan zancen karatu har dasu suma kuma.

Abindaya kara firgitani shine zancen aure wazan aura ko nima irin auren da nake jin labarin cewa iyayyen mu sunayi a family din mune yanzu zai hau kaina .

Wanan ne har ya kaini ga fita hankalina na dan wani lokaci na some harda su zazzabi mai karfi wasa wasa sai gashi an ban gado ana ta karin ruwa.

Da dare su daddy sukazo su uku suka dubani fuskan babana ba sauki kallo daya nayi mashi ban sake ba don na karanci halin babana dole akwai abindake damunsa a lokacin kwana daya nayi aka sallamoni da yamma muka dawo gida wanda anty Nafisa ce ta zauna dani asibitin lokacin.

Kodana dawo gida ban wani kara sakewa ba kamar yadda na saba saidai abinda ke ban mamaki shine har na kwanta na taso asibiti mummy bata lekani ba hakama yayanta.

Sai bayan kwana biyu da dawowana sai gata part din mum din wai sun shigo gaidani mum ke fadin ai mama taji sauki ko saidai dan abinda ba,a rasa ba kuma amma ta mike insha Allahu.

Murmushin yake hjy mummy tayi kafin tace ku dai jaye maganan ku tun kan akai ga hasaran wani acikin su don wanan zance ba mai yuyu bane kuma kun sani.

Meye naw a ciki hjy malka iyakata nima ido Alh ne inya tashi abinsa baijin shawara yadda ya hau din nan waya isa yace masa kar yayi ai gamu gani ta fada ta juya shine gaisuwan da aka tursasata tazo tayi min shi tayi ta fita lokacin.

Haukan baza sai kace dan naki yafi dauran yayane agidan inba dole ba wake son hada zuri,a dake sai dole wallahi mum ta fada a cikin takaici duk ban fahinci me zancen yake nufi ba.

Nidai naga sun canza min dama kuma kusan haka muke dasu wata rana tayi muna dadi ana shiri wataran kuma kowa ya debi iska ya hau a tsakanin mu dasu sunce sun iya nace muje haka zaman namu dasu yake.

Yadda iyayyen mu ke kishi haka nima muke zubawa a tsakanina dasu duk hanyan da zasu nuna min jiji da kai ko wani gani gani nasan shi tun a kauye sun gaza don nima na sanshi.

Ina kwance daki da yanzu na saba dashi duk da nakan dan fito tunda safe bayan nayi sallah na danyi aiyukana irin gyaran part din mu gyaran kitchen ko wanki idan mun tara nakayi saidai baki ganina zuwa rana ko a falon mu zaune saidai daki.

Yanzun ma zaune nake ni kadai a dakin na kurawa kasan dakin ido ina faman tunane mum tashigo tana fadin ga yayanki nan falo yana tambayanki.

Na dauka yaya Nasir ne na dan dago na kalleta nace wai ya Nasir yazone tace bashi ba Addel dai sunzo jiya yanzu suka shigo yake tambayan ki.

Ai nasha ai ya Nasir ne nafada ina mikewa tsaye daga inda nake zaune haka na fito tagal tagal ina dan kako murmushin dole a fuskana nace sannuku da zuwa yaya.

Kafin kuma na banbanta nace anty Safiya sannu da zuwa ya hanya anzo lafiya tace lafiya kalau ke mai tsoron aure akan aure kikayi wanan rama haka sai kace wani mugun abu can.

Zaune nakai da kyat don ta tabo min inda keyi min ciwo watau suma suna da labari ke nan na fada a zuciyana aure ai bashi zai hanaki karatun ki ba zakiyi karatu insha Allahu ina takardun naki suke ya Addil da sai lokacin yai magana ya fada.

Zubur nayi nace suna gun mum yaya sai matar tashi ta kwashe da dariya tare da fadin ke wai karatun kikewa zumudi haka kinko san wuyan dake cikin karatu.

Ai ita talent ce ba irin ku bace masu tsoron karatu wai ashe hakan daya fada yai mata zafi wai ya nuna ita din ba mai kokari bace agaban mu.

Matsalan da yake fama dashi ke nan akanta saurin fushi abu ba abuba yanzune zata murtuke fuska ta dauki gaba dashi na tsawon wani lokaci.

Mum ce ta gane hakan don ko bata kara magana ba har suka fita data mike tana fadin muje ko yace ina tace amma kasan ina da abinda nazo yi dama garin nan in baka tashi ba nika sameni a can zan tafi tana kokarin fita.

Mun dake fitowa da takardan nawa a hannunta ta kalleshi lokacin wai har ta fita ko tace ya haka kuma wani abin kuma ya faru yace kyaleta mum haka nake fama da ita ashe zancen ya fada kunnenta.

Mum ko cewa tayi kayi hakkuri kowa da halinsa ake zama dashi shine kuma laifin mum din a lokacin abin ya taru ya karu ko part dinsu Dada da sauran mutanen gidan bata shiga ba ya fito suka tafi.

Takardun ma nawa nan ya barsu hannun mum yace zai dawo nan zaici abincin dare ya karba sai bayan tafiyansu mum takece min akwai aiki ga wanan fitsararar yarinyar da nake gani .

Dama abinda muke masa gudu ke nan ga irin yaran nan da gata ya huda duk sune su Nafisa ido ya bude tun a waje basu kunyan kowa balle tsoro.

Haka yake son abinsa yar gayene kuma sosai kamar anty Nafisa itama na fada daga inda nake zaune da a bayane banji zancen karatuna ba ko tsinkawa mum din ba zanyi ba lokacin.

Don duk haushinsu nake ji don ina ganin da hadin bakinta itama aka hanani karatu don in zauna inta mata aiki tana morana haka zuciyana ta kiyasta min kanta yasa yanzu ko dan girkin ma na daina yi sosai na fake a rashin lafiya yanzu nako san tagane kawaicine irin nata kawai akaina lokaci .

Mum tace kinjiki da wani shirme ke bakiga yadda yayan naku ya fada bane wanan kila ko abincin kirki bai samu gayune za,aci akoshi kome ?

Mum kinfa san su yan gayune basu son suyi kibane kila taja tsuki donjin haushin magata din tana dorawa da fadin kin daiji yace a nan zaici abincin dare ki tashi ki masa tuwon masara donshine abincinsa.

Ba musu ko na fada kitchen din ina kokarin hada girkin ba wani dogon lokaci nagama na wanke kayan aikin na gyara ko ina nashiga wanka nafito na gyara jikina ganin magariba akwai sauran lokaci yasa naje part din Dada.

Anan na samu matan daddy Enugu zaune suna hira suna ganina suke fadin yau kan yar mum ta fito a,a lalai hjy kubura sai tasha ruwa tayi barci ga yarta ta fito daidai yau.

Dan murmushi nayi ina gaidasu ban kula da Amir ba saida ya fado min ajiki na ganshi kamosa nayi ina fadin Amir dina nayi missing dinka sosai .

Wani kin yi abingasane bayan kina son halaka kanki a banza meye a cikin karatun ko aure da kike wanan fargaban in angon nakine bakiso saiki barmin dama mun saba ai .

Nace ke Dada waya gaya maki hakane wai in anyi magana kice wai karatu ko aure to anki ayi auren don Allah dama ai nasan kune mazuga masu zuwa lahira da ,,,,,

Ni yar nan ni da nake goyon bayanki kuma zakiyi min wanan fatan da sauri nace nabari to Dadana tace yar nema ai baban naku shine maganin ku.

Waini dazun ba Addil bane suka shigo gidan nan matar daddy Enugu take tambayan cikin kallona nace sune zasu dawo wani waje zasu na gajarce zancen a takaice.

Nikan ai nace nan dada ke fadin amma ko suna sauri aita lekomu tace yan banzan nan kuna lafiya dama na kula bata da marmari tun ranan da muka kai mata wuni tasa ya dawo damu gida din nan.

Kai kedai Dada baki mantuwa wallahi abinda akayi tun tana amarya yanzu kike tunawa kuma kedai bari ina zan iya manta abin nan ai yarinyar nan ta iya yankar kauna dama abinda ubanku yai masa gudu ke nan ga auren.

Biyu ke nan na fada a raina mum ta fada yanzu kuma Dada ta fadi wai kodai akwai matsalane ga zaman su nake tambayan kaina a lokacin.

Wai yaron nan shi a dole yayi kewana yake nufi na fada don kawai a kawar da zancen ya Addil din data dauko har Dada ta fara kumdumawa matarshi zagi a lokacin.

Ina gudun in jawa kaina wani matsala yazo yaji yace ya fasa goya min baya naje karatun da nake son zuwa din in kara samun matsala kuma nawa ya sameni.

Nakoyi sa,a sunbar zancen don sai aka kama na yaron ana fadin baijin dadin part din kakansa don basu da lokacin kulashi saboda mummy ba mai zama bace ita.

Irin matan nan ne da suke amfani da daman mazan su idan sun fita nema suma su laga su fita suje nasuyi don har ta saba da hakan daddy yayi fada ya gaji ya barta da Allah.

Haka suma yan gidan sunyi gulma hakan sungaji sun saka mata ido gashi yanzu har diyanta su dauki hannu suna Allah Allah daddy ya fita ko uwar suma suje yin nasu harkan a waje .

Ya Allah ka hada zurian mu da iyayye na gari mun kuma godewa Allah da iyayyen daya bamu Allah ya kara masu daraja yaji kansu badon hakin mu ba Allahuma Amin.

Don koda ake zancen nan sunce tun safe mummy din ta fita sukuma yaran bayan azahar sai bayan karfe hudu kowanin zai dawo anyi daidai da kafin biyar daddy yake dawowa daga kasuwa. Ganin magariba ya gabatone yasa na mike zuwa part din mu na samu mum a falo tana waya gefenta na zauna saida ta gama ta juyo tana fadin ke kuma daga ina hakane ?

Gun Dada naje mu gaisa na zauna kuma muna hira dasu mum ashe dazun dasu yaya sukazo sun gansu shine Dada ke fada wai basuje sun gaisa dasu ba.

Dama nasan haka zai faru wanan yar tana son jamin magana acikin gidan nan haka wancan karon abinda tayiwasu hjy ya kasa fita min a raina.

Aiko yanzu ta fada na amsa mata shiru tayi kamar tana nazarin wani abu a zuciyar ta kafin ta dawo fadin ai bari zaizo ya sameni dole ya taka mata burki akan hakan

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[2/19, 21:12] Maman K: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

22

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Ina daki ina sallah naji shigowanshi har kofan mu ya tsaya daidai kofan mahaifiyarshi yana sallama hakan yasa nagane ya dawo gidan kamar yadda yace.

Baifi minti biyu ba daidai ina idar da sallah naji muryan mum tana kirana daga dakinta shafawa nayi na mike ina amsawa zuwa dakin nata gani mum nace daga inda take zaune take fadin.

Jeki falo kiba yayanku abinci don Allah na amsa dato ai naji muryanshi ina sallahne dama na juya zuwa falon kitchen na fara zuwa na dauko abincin nafito mai dashi dama a shirye yake a kitchen din.

Zaune yake saman kujera yayi shiru ya kurawa kasa ido kamar mai tunane jikinshi yana saye da tufafi baki na dinki irin na maza sai yar hulan maza irin na pakistan

mai gashi daya kafa a kai abinka da farin mutum sai kalan kayan ya amshi jikinshi sosai.

Sallamana falon yasashi dago kai yana amsawa cikin yar siririyar murya nagaidashi tare da fadin akawo nan ne ko in aje a dinning ?

No kawo min nan ya fada dama nasani yaranta basu damu da zama saman dinning suci abinci ba dan table na jawo na dora masa a gaban sa zan juya yace .

Don Allah dauko min ruwa mara sanyi na amsa da to na kawo mai goran faro da cup har da ruwan wanke hannu na aje thanks ya furta tareda cire hannun daya tokare fuskanshi dashi ya motsawa zuwa gaban abincin.

Hannu ya daure kafin ya bude abincin ina jin sautin bissimilanshi a daidai lokacin da zaikai loman farko a bakinshi don ina falon ban fita ba saboda na tsaya tattara kayan da mum ta bari nata watse a falon da muka shiga sallah.

Ina shiga mum din tana fitowa tace dani harkin bashi na amsa da ehh nashige na dan dade ban fito ba don na tsaya dan gyara a dakin kodana fito falo na fito don indan samu abinda naci alokacin.

Yana zaune tare da mahaifiyar nasa da alama wani zance sukeyi hakan yasa ban tsaya ba na shige kitchen acan tsaye na tsaya naci abinci na kusa karasawane naji muryan mum tana kirana na amsa.

Koda nafito ban sameshi ba a falon ashe suna wanan ita kuma Aisha matarsa nata kwala masa kira akan yazo ya dauketa mana baiga dare yayi bane da farko ya fada mata yana wajen mum ne ai.

Bata daddaraba ta dameshi da kira karshe ma fada da masifa ta kamayi masa duk mum najinsu tace ta tashi yaje itama bata da lokacinsa dole ya tashi yaje ya sameta a inda take shine mum ta kirani na kwashe kayan dayaci abincin a falo.

Sai washegari da yamma mum din ke fadin kinga yaronga ko don kada in masa zance akan matarshi son nace ya tabbatar daya daukota sunzo sun gaida Alh da hjy cewa Dada.

Shine shima ya tafi ba tare dayazo yai muna sallama ba yaje ko bace ba gashi gata suje suyi tayi dama abinda kowa ke masa gudu ke nan da auren wa yan nan marasa tarbiyan da boko ya ratsa gidansu ke nan.

Yanzu haka itace ta hanasa zuwa ko aikema kin sani tunda bai taba tafiya baizo munyi sallama ba ko yayako yake sauri sai yazo gidan nan watara zuwa zuwa ma saisu shigo garin bamu sani ba harsu gama abinda sukeyi basu zo gidan nan ba ke nan.

Kai haba mum bari mashi wanan fatan aishi ba zai yarda haka ya faru ba akansa tunda yasan hakkin iyayye yaushe kuma tunda har nace ga abinda zasuyi taki zuwa kuma ta hanashi shima.

Wai dako ta zama sakarai wallahi tunda wata rana itama uwace don haihuwa zatayi ai haka dan zai mata kuwa na fada a hasale raina yana baci da zancen ina maijin haushim yaya din.

Ta yaya mai hankalibda hangen nesa kamarshi zai tsaya mace ta juyashi kamar sakarai wanan tunanen nakeyi a raina sunana da mum ta ambata yasa na kallota.

Tace jinyan da suwaye a wurin hjy suke zancensu nace matan daddy Enugune tace ai sai kowa yaji wanan zancen da hjy ce zance zata kyale sai ranan da suka hadu zatacisu taran hakan amma wa yan nan sushiga mitan hakan ke nan sai kowa yaji agidan nan.

Allah sarki komin fushin uwa da danta bata son yau ace ga laifin danta a waje tausayi hjy mum taban don nasan tana iya kokarinta akan tarbiya.

Amma yau sai gashi mace tana son shiga tsakaninta da danta ta hadasu fada a tsakaninsu saboda son kai banta ganin uwar data shaku kwarai da diyanta ba har suka zamo abokan shawaranta irin mum ba.

A take naji tsanar wanan macen ya fita raina dako ina son ta dongayunta ina ji da ita har ina son koyi da irin halinta ashe kyau dan macijine da ita.

Duk macen dake kokarin raba tsakanin da mahaifiyar shi da sunan aure wanan mace ba karamar shedaniya bace son kanta yana da yawa bata kuma kaunar mijin da take aure din.

Kabari a cutama yafi kayi cuta irin wanan mai girma a duniya basu ganewa matan saboda son kai ya rufewa wasu ido har suke jin hakan aiba zunubi suke aikatawa ba.

Ranan dai gajeren hira mukayi da mum da safen son ko bayan mun gama karyawa ta shige daki bata sake fitowa ba ni kadai nayi ta zirga zirgana har na hada muna abinci nagama.

Mum bata kyale ya Addil din ba donko ta kirasa a waya tayi masa kaca kaca ashe matar na kusa a lokacin nan ta fara yan surutai tana fadin dama aiba sonta akeyi dashi ba.

Idan hakane ita gara kowa ya kama gabansa zaifi a tsakaninsu shigo yaji surukulen mata nan ya shiga bata hakkuri yana ban baki kan tabari zai zauna da mum din suyi magana ai bata fahinceta bane.

Ni dai a yanzu nikan ga mum ta aikeni wani gida da bamu da nisa a layin mu gidan marayune maigidan ya rasu ance yakai shekara kusan ashirin ga gidan babba amma iyalansa ke ciki zaune.

To wanan gidan dama nakan dan kai masu sako saidai na yanzu din yayi yawa don yakai harda abinci dafafe idan zamu dafa mukan kara yawa sai tasa i kwashe daban in dauka inkai masu don irin gidajen su Dad manyan gidaje a layin almajirai basu shiga haka kasafai don suna tsoron yankan kai.

Yauma su zan kaiwa sako data ban shake a ledan vaco har da tufafi dasu sabulu omo man shafi da makaroni da taliya niki niki na dauko kayan zan fito daga cikin gida da katon hijabi na don sai ka kula zaka gane ai duka hannuna biyu dauke suke da kaya.

Anty Nafisace tsaye da wani namiji shi ya bada baya don haka ban gane fuskan ko waye ba a lokacin kai sister me kika dauko haka kike haki kamar zaki fadi ?

Mum ce ta aikeni wancan gidan na fada sai lokacin ya juyo nagane ya Hafiz dinsune a wajen ashe nina zatama tayi bazawarine yazo mata hira yadda suke dashi don zaune take cikin motanta shi kuma yana tsaye ya riko kofan motan suna magana.

Wai amma kayan nan sun maki yawa ta kara fada na danyi dariyan yake sai naji yace da ita maganinta ke nan ai jakace dama abinda ya dace da ita ke nan daukan kaya.

Innalillahi na furta ina runtse ido kamar na dawo in bashi amsa sai kuma na wuce kawai kai tsaye a zuciyana nace na barka ga Allah shi zai aiko mai rama min dan giyan banza kawai .

Haka na fita ina fada cikin zuciyana har Allah ya taimakeni nakai gidan ga gidan da shegen girma kafin ka kai cikima aikine a yadda naji wai bayan rasuwan mijinta anso a cinye masu komai daya bar masu.

Sai matar bata yarda ba mafarin da batayi aure ba ke nan tana ciki zaune da yayanta su kuma yan uwan mijin sunce basu yarda tayi aure wani miji yashigo gidan dan uwansu ba yaciwa yayansu gado.

Rikici dai akace anyi sosai shine ta zabi zama da yaranta a gidan akan taje tayi aure kuma taki yarda da tayinsu na son su aureta da sukayi shine suke cikin wanan bakar wahalan ita da yaran kuma sun hana tasa ko dan haya a gidan ta samu inda abinci zai fito mata mugunta zalla a wajen sukai mata.

Tayi murna kwarai tace tana nan zuwa tayiwa mum din godiya da yamma in yara sun dawo daga school kodana dawo ban samu su anty Nafisa din ba motar tama bainan nasan ta fitane lokacin.

A part din mu na samu Amir tare da mum zaune kin dawo mama mum ta fada na zaune ina wash amir yazo ya haye min jiki na daukeshi ina masa wasa tare da fadin waya kawoka nan ?

Nima gannisa nayi ya fado min yanzu yasan hanya tunda ya samu kafa basai an kawoshi ba ai lokacin nace mum ni bansan abinda nayiwa ya hafiz ba ya tsanani ?

Hafiz kuma yazone yana gari ta tambaya a cikin mamaki nace yana nan tare na gansu da Anty Nafisa a kofan gida zan fita son anty Nafisa tace min kayan dana dauko sun min yawa shine yace dani aini jakace dama shine daidai dani.

Hummm ki kyaleshi baida hankali inbashi ba ka kira dan uwanka musulmi da jaki kaji dadi akan me don Allah ki barshi karkima kulashi don Allah.

Shima mashayi dangiya ai gara da jaki haka Allah ya haliceshi da daukan kaya kar in karaji babu ruwanki inma da gaskiya yana sha tsakaninsa da Allahne wanan babu ruwanki mum ta hanani cigaba da magana alokacin.

Shiru tayi tana tunane kafin nace mum matar nan taji dadi sosai wallahi tace ke mai kyautan yan aljanna ce dan kyautanki nazuwa a lokacin da mutum yake cikin matsanacin hali sai mum di n tayi murmushi tana fadin Allah yasa mu dace ga baki dayan mu na amsa da Amin.

Bayan kona biyu muna zaune abin mamaki wai saiga ya Hafiz ya shigo part din mu da takardu a hannunshi yake gaida mum kafin ya juyo guna yace ke karbi takardun ki yace in fada maki ranan Monday zakije screening.

Yana fadin hakan na mika hannu na karba da sauri ina murna kafin nace nagode na mikawa mum tace takardan kine ai na karatu tun jiya yayaki ya bugo min cewa zai aiko dashi.

Sai kibi Nafisa taje dake tai maki komai a can yafada yana karasa mike zai tafi nan mum ke fadin ashe kuma fita zaka sakeyi yace eh wallahi mum can din yafine don su aiki baida wahala acan din.

To Allah ya kyauta yasa aje cikin nasara ya amsa da amin yafita hankalina yana kan takardun dake hannuna ina karantawa banko kula da fitansa ba.

Na daiji mum na fadin hjy malka bata da tunane yaron nan zata kara turawa kasan waje kuma shi kadai ya zaunacan suna tare da yan uwama bai natsu ba balle yaje shi kadai da sunan aiki.

Sam ban tsaya kula mum din ba a lokacin don bayanan dake cikin takardan ya dauke min hankalina Allah ya gani ina son karatu sosai a rayuwata.

Na dago ina fadin mum sai nayi wani photo kuma barima in duba ko nawa suka rage min a daki na mike na barta a wajen zaune.

Har naje na dauko ban tsaya kallon mum dun ba da gaba daya yanayinta ya sauya lokaci guda ta shiga yanayin tunane mai zurfi dagowan da nayi ina fadin ashe ina da guda biyarma aje.

Nan na fahinci sauyin fuskan mum din saidai ban fahinci kona meye ba wanda ba komai take tunane ba a lokacin sai yadda abubuwa zasuzo su kashe tasan dole a samu sabani don rayuka da dama zasu baci a tsakani.

Saidai yanzu bata da iko ko power magana koda ko ace itace ta haifeni bata da hurumin ketara zancen mijinta ta tsaya musu dashi duk da ko yanzu din banda bambanci da diyar data haifa.

Hakan da za,aimin tauyewane a gareni mai yawa take hangowa don kamar fin karfi da son kai za,a nuna min da iyayyena take gani duk da tasa suma a bangarensu sunfi tsanar hadin fiye dasu.

Ita mace ce bata da karfi ko power da zata tsaya min tace kada ayi hadin nan haka kuma iyayyena suma basu data cewa don Alh shine babba ga mahaifina.

Mum lafiya kalman dana jefo mata ke nan na katse mata tunanen ta a lokacin ta nisa da karfi tana sauke ajiyan zuciya tace bari kd dai mama duniya nake tunane wallahi.

Jikinane ya danyi sanyi a zatona kan zancen tafiyan ya hafiz din ne data dauko min na shareta abin yake damunta sai mm aji tace akwai Allah ya Allah ka shige muna gaban lamarin nan yazowa kowa da sauki.

Na amsa da Amin take fadin sai ki shirya don Nafisa zakibi takaiki ranan Monday din abin ai yazo da sauki tunda ana saka wayewan kai aciki ba irin namu bane da kowa jahilci lokacin bamu ba ba iyayyen namu ba.

Part dinsu ya nufa kai tsaye don ya karya yana shiga Dada na zaune suna hira da Anty nafisa ya samu gefe daya ya zauna yana bata rai.

Dada sai zolayanshi takeyi yace dama ina son ganin ki muyi magana sai gaki Allah ya hadamu a nan yanzu rage fara,an fuskanta tayi don ganin yadda shima yake cikin damuwa tana kallonshi tace ai gani kamar Allah ya turoni meka samo min fadi muji.

Dan furzo da iska yayi daga bakinsa kafin yace Dada akan wanan auren hadin da daddy ke son yai min ne gaakiya Dada kwata kwata banson auren nan kuma yarinyar batayi min ba don ba kalan zabina bace ita.

Ita mace har tana da wani bambamcine a wajen namiji ina dai mace macece ya tsuke fuska cikin damuwa don ya kula zaisha wuya koda zai samo kan tsohuwar.

Dada nasan ke kadaice zaki fahinci me nake nufi ni sam bani kaunar wanan yariyar koda yan uwantaka balle da sunan aure kinga yin aure tsakanin mu hakan

kuntatawane ga gaba dayan mu sai hakan ya kara haifar da matsala har yashafi wanda ba,a zata ba..

Tunda ya fara maganan Dada ta bude baki take masa wani kallon na mamaki wanda shi bai iya tantance ko nameye alokacin.

Haka mummy ma data fito daki da manzafi data daukowa Dada daga daki dama shi Dada din tazo nema a wajensu ta zauna itama kallon mamaki tabi dan nata dashi lokacin don sun riga dasun aje magana dashi don mafita akan zancen.

Kai ashe rashin hankalin naka yakai haka ban sani ba yar uwar haihuwan naka kake fadi a gabana baka kauna koda zumunci balle da aure ?

To ka fara zuwa wurin ubanka daya hada zancen a tsakanin ku kafin kazo wurina watau ni gani tsohuwar banza mai yukan yanke zumunci bari kazo wajena ka laba ayi yankar kauna ko ?

Ke Dada wai bakya ganewane shifa so wani abune kada ku tauye min rayuwata mana don Allah zaku hada baki ku cinna min wanan mahaukaciyar yarinyar in kaita ina don Allah ?

Inda ubanka yakai uwarka nace inda ubanka yakai uwarka Dada tafada a hasale cikin mikewa tana haki kamar zata dokeshi daga inda hjy malka take tsaye ta kwala masa kira tace hafiz bakaji ko zan saba maka idan baka fita part din nan ba yanzu.

Kallon mummy din yayi kafin ya juya a kasalance wurin Dada din yace na dauka zaki taimaka min ki rabani da wanan auren alkakan da daddy keson yi min she duk bakin ku daya ban sani anywhere kuyi karku fasa din ai .

M ummy ce ta karaso acikin masifa agareshi tana rantsuwa idan bai fice daga part din ba zata saba mashi rai fiye da tsanmaninsa.

Lokacin Anty Nafisa ta dago kai ta kalleshi tace Hafiz wai bada kai mummy ke magana ba ka bari a lalaba zancen nan mana tunda ku duka bakwason junan ku.

Wani kallo yayiwa yar uwartasa tace yes kamar yadda baka son hadin nan ko ita sister na tabbatar da bata so don ko bashiri a tsakanin ku .

Shine daidai idan anyi auren sai suje can su shirya a tsakanin su tunda sunfi kusa Dada ta fada cikin daga murya har ya juya ya fara tafiya jin hakan yasashi ya dan dakata yana mai juyowa ya nuna Dada din da hannunsa.

To indai har hakane babu wanda ya isa kaf ya fasa wanan auren acikin uban nan ku muddin ina da raina ya nunata yace aisai ki zauna da ita ki jika kisha tunda kince hakan.

Shege ka fasa tunda kace haka in maka na mahaukata wallahi hafizu idan kaga an fasa wanan auren tsakaninka da Abu tabbatar bana raye a doron kasa ta karasa zancen a cikin bacin rai.

Anty Nafisa ta mike tana fadin saika fita tunda ka bata komai dama haka kakeso ai Dada ce zaka sama ko daddy dayayi ma wanan hadin meye na Dada a cikin zancen nan.

Kai ya girgiza a cikin yakaici yana fita daga falon yakai iya kololowan tashin hankali don yanzu ya tabbatar da wanan auren da daddy ke ikirarin ya zaba mashu mata yar mutunci yar albarka ba fashi sai anyisa.

Idan gaskiyane meyasa ba aiwa ya Addil auren dole bashi saishi da aka raina za a kakaba masa wanan kucakar yarinya da sunan aure wai fa zeey a matsayin matarsa.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[2/21, 14:52] Maman K: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

23

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Yawan jinini da mita irin na tsofi da Dada keyi yasa har zancen yazo kunnen hjy mum matar daddy Enugu take tseguntawa mum din nidai naji mum na fadin wanan abin matsala kawai yake son kawowa a cikib gidan nan da abarshi kawai zaifi amma Alh ya kafe dole sai anyi bai daukan shawaran kowa kan zancen nan.

Nikan ban tsaya ba don nasan cakwakiyarsu gidan ba karewa yakeyi ba sai randa rai yai halinsa garesu ranan da ba dayansu kila zasu daina rigima da baki kishi a tsakaninsu.

Sai gashi bayan magariba an gama isha,i daddy ya bugo yana kiran mum kuma tazo dani falonsa bamu kadai ba kowane ashe nagidan aka kira lokacin.

Kusan mun samesu afalon mune muka shigo karshe nida mum gabanane ya fadi azatona zancen karatuna daddy zaiyi a lokacin na samu waje na tsuguna ina gaida daddy din sai lokacin na kula da daddy Enugu a zaune falon shima nagaida dashi.

Na daiji daddy nafadin kaga abin ko kagani dukkansu nan suka shigo muna sokai sokai dasu don rashin tarbiya amma mama tana zuwa da yake tasan darajan mu ai kaga ta bimu tana gayarwa daya bayan daya.

Su ba yan gata bane su gaida mutane suna kallon sunfi kowa aduniya babu yar banza irin halima wajen nan data dauki rigan aro a yanzu ta yafawa kanta don girman kai.

Ku barta abindata sama anayine agidan daddy ya fada cikin takaici har mummy zatai magana ya daga mata hannu yana fadin dakata don Allah muyi abinda ya taramu a nan mu watse.

Saida ya kallo kowa ko din ya tabbatar da kowa yana fallon ne oho yace nasan ba wanda yasan dalilin dayasa na taraku a nan yanzu ko kuma wasu sun sani dai.

Dazun da safe zan fitane hjy tazo ta sameni da wani zance koda yake bankai ga jiba akai min sallama nafita shine yanzu na taraku a nan ayi zancen agaban kowa dake gidan nan yaji.

Hjy ko zaki maimaita muna zancen mu na dazun dake don Allah idan ba takura saiki kara muna bayani agaban kowa gamu gaba daya anan yanzu.

Dada ta gyara zama tana fadin akan zance da yaron nan ne hafizu na shekaran jiya hankalina bai kwanta da kalaminsa shine nazo na samu mahaifinsa kan zancen shi kuma bai samu saurarona ba sai yanzu da ya kiramu din.

Nan ta kwashe komai tana mayarwa su daddy din yadda ya kasance a garesu ranan saidai bata fito fili ta ambaci sunana ba saida mum tace Allah sarki ai itama mama din bata ko san anayiba wallahi don ban taba fada mata ba kuma ban tsamanin wani ya taba fada mata a gidan nan.

Ko a fada ko kar,afada ai yanzu baida magani boyon don dole dai tasan hukuncin da muka yanke a kansu din ina dai gaba dayansu duk mu muka haifesu don haka ba wani cikinsu da zan kafawa doka ya ketare minshi gaba dayansu ko.

Haka nace zan hada aure tsakanin hafiz da ita mama ita kuma mairo da jafar din salisu dake bauchi ni daddy mairo tace cikin zaburowa da mamaki.

Daddy din yace ko ban isa ba ke kiyi shiru don Allah mummy ta fada yace idan ma ba zatayi shiru ba tunda tana da wani uba bayan ni aisai ya isar mata tunda ni ban isa ba .

Kiyi shiru mairo kinji Nafisa dake gefe ta fada ke kuma Asiya da Nura dan babanku musa dake katsina sai halima da shawaran mahaifanta nake jira yasa abin dan daukan lokaci don sunce a bari suyi shawara kila suna da wani wanda suke son hadata dashine can gida ban sani ba.

Amma su wayan nan shawaran dana yanke ke nan a kansu yanzu don haka kowa a nan yasani aure nan da wata biyu masu zuwa insha Allahu.

Hannun hjy Mum ne a kafadana ta yadda babu mai iya gane hakan tana min alaman kada nayi wani motsi ko magana daga Allah saini sai ita muka sanda hakan na fahinci me take nufi hakan yasa banyi wani koda motsi ba a wajen.

Zaune nake ban motsa ba sai gumi da nake ji adukkan sassan jikina yana fita ina kasa fahinyar bayanin da daddy din keyi a karshe don gaba daya ban cikin hayacina a lokacin.

Muryan anty Nafisace da iyayi ya kaita ga magana tana fadin daddy adai duba wanan zancen don ke rufamin baki mara kunya har me kika dauki kanki a gidan nan ?

Dama ina tafe kanki ai ko baki nuna min kina nan ba kar kiji wai a rana daya zan daura maki aure dasu ko kin kawo miji ko baki kawo ba ina da wa yanda na yaba da natsuwansu da hankakinsu a tare dani zab samu daya daga ciki in daura naki auren da maishi a ranan.

Wani kallo tayiwa mahaifin nata sai Dada ne tayi karfin halin fadin amma kasan bata yaye danta ba tukuna a dan daga mata kafa har tayi yaye.

Hjy yaron nan baida matsala yana da kafansa ko ina yana zuwa ta yayeshi kafin lokacin dana diban masu yayi tayi aure kowa ya huta nagaji da nunani da mutane keyi agari hakana kanta.

Ina fatan kowa yaji abinda na fada suma mazaje na sanar dasu tun wacan satin donsu fara shirye shirye kafin lokaci .

Ya juya wajen mummy yace ke kuma ki fadawa danki bani hukunci in tayar yasani in yana son mu zauna lafiya yabi zabin da naimasa shine alheri agareshi.

Amma Alh bakai mi adalci ba gaskiya Malka na fada hakan kuma za,ayi banga abinda zan tsaya jira da yaran nan ba don ba wanda bai isa aure ba acikinsu.

Ko so kike a maimaita abin kunyar da kukaja min keda yarki a garin nan na zabin ranku da kukayi ba wani dogon bincike ni kuma na biye maku.

To ku sani bazan lamunta da wanan ba yanzu tafarkin gidan mu da muka gada iyayye da kakanni nakoma wanda kuma keda wani magana ko ja sai yayi inji .

But mummy ta mike tafita daga falon cikin matsakaicin tashin hankalin da bata taba tsanmanin zuwansa ba a rayuwanta yaya uku koma tace hudu duk a auren dole har da da namiji sam ba zata yarda ba .

Tana fita daddy ya kallomu yace kuna iya tafiya dan nagama daku idan ba mai magana kuka sosai Asiya tasa Dada sai fadi take lalai zamani akan zabin mahaifiki ke wanan kukan.

Mu lokacin mu har asaka lale akai gidan miji baka taba sanin mijinka sai anyi kwana uku kafin kasan waye mijin kuma haka zaka zauna dashi amma yanzu don jin dadi ai maku gata ku tsaya kuna kukan iya shege.

Ba Asiya ba koni ji nayi kamar in shake Dada ranan saboda bakin ciki kalaminta suna kara min zafi a zuciyana sosai ina jin takar da gaiya take zancen tana kara zuga daddy din lokacin.

Akwai cakwakiya a gidan nan lokaci daya ace za,a aurarwa mace da diya kuma bada saninta ba gaskiya .

Alh ya kamata ka dubawa hjy malka idan na matan za,a farayi kabar namijin ko kuma a farayin na namijin abar matan har muyi shirin mu irin na mata.

Wai dadatace ke wanan maganan tana nufin a fara aurar dani kafin su Asiya din da daddy yayi niyar hadamu a tare ke nan lalai ashe Dada ba kaunata takeyi ba a zuciyanta tunda har ta nuna tafi jin tausayin jikokinta a kaina gaban kowa.

Aiko mum naji tana fadin hjy idan akai hakan kuma ita mama din fa da za,a aurawa hafiz gashi ta kwallafa rai ga karatunta kafin Dada ta bada amsa dake bakinta daddy yace.

Abinda na tsara ke nan ba ruwana da wani shiri don nagama shirya komai akan auren nan ko bayan buki abinda Allah ya hore masu suna iya kaiwa yayansu a dakunan su.

Allah ya kyauta mum tafada ta mike tana kamoni tare da fadjn tashi muji mama ganin ban iya motsawa ba yasa mum din kamo hannuna ta mikar dani muka fice daga falon.

Har muka kai part dinta ta zaunar dani saman kujera kafin tace ki yarda da kaddara mama banson ki nuna komai akan hadin nan don nasan Alh yayi hakane dawani manufa da sai nan gaba za,a fahinci manufarsa nayin hakan akanku.

Duk wani abinda kowa zaiyi koya fada agaban ki kan auren nan banson ki nuna komai ki daure kiyi biyayya ga iyayyenki Allah na sane damai hakkuri baya barin ki tabe insha Allahu.

Mataukar kikaiwa iyayyenki biyayya baki watsa masu kasa a ido ba sai yai maki sakayya ta hanyar da baki zata ba don haka nake son kiyi hakkuri ki rugumi kaddaraki na aurensa da hannu biyu.

Kiyi kokari ki hade komai azuciyanki game da komai da zakiji akan hakan Allah zai saka maki da alherunsa insha Allahu na tabbatar Alh baiyi wanan hadin da wata manufa mara kyau akanku ba sai duba da yayi da yawan alherun dake cikin abin .

Kuka kawai nake haba mama kibar kukan nan kinsan dai bacza a taba hada kai dani a gidan a cuta maki ba abune na magabata bamu da yadda zamuyi akan hakan ki daina kukan nan.

Wanan yasa dan uwanki yayi tsaye saida Alh ya yarda da zancen karatun ki don ya samu dai ki samu karatub da kike buri kada aure ya tauye ki ga murdinki nason yin karatun nan.

Yasha fama da Alh kafin ya yarda da zancen karatun ki duk baki san wanan ba don haka nunawa kowa kedin mai biyayyace ga iyayyenki din ki nunawa kowa hakan bai dameki ba ki tashi maza yanzu ki shiga ki wanke fuskanki kada wani yashigo ya sameki kina kukan nan haka.

Kinsan gidan nan yanzu yazamo gidan tsegumi ba,a raina abin magana yanzune zakiji ana fadin abinda bashi kan haka don haka nake son ki nunawa kowa baki damu da hakan ba .

Da kyar na tashi nashiga ciki don yin abinda mum din tace nayi na shiga na wanko fuska na dawo na zauna samab gadona don hawayen da sukaki tsaya min alokacin.

Ina nan zaune najiyo muryan maman Yusura uwargidan daddy Enugu tashigo a raina nace gaskiyan mum ashe nan zancen ya kawota ba wani abu ba alokacin.

Ranan yadda naga rana haka naga dare barci sai wajajen asuba nasamu don ko mum bansa tayi barci da dadi rainmba a rana kowa zuciyashi ba dadi a gidan.

Washegari monday haka na tashi ina shirin bin anty Nafisa school har na shirya mum tasa na dan kurba ruwan shayi mai zafi don cikina ya walwale don tasan banci komai ba da dare tun abincin safene dana karya acikina na jiyan.

Bata zo sai waya data bugowa mum ajan cewa inna shirya in fito gata waje tana jirana koda zan fita saida mum ta kara ja min kumne kan kar in yarda inyi wani zancen dabai dace ba da wani.

Zaune na sameta cikin motan tana jirana ina zuwa ta bude min gaba gefen drive nashiga na zauna muka tafi mun dan bar kwanan gidan take fadin waike zancen daddy ne har yanzu a zuciyan ki ?

Zancenshi yakeyi kawai don yasan wanan abin da yake sonyi ba abu bane da zaiyuyu haka don wanan zamanin ya shige na auren hadi abin ma babu ko dadin ji ai gara dake.

Asiya da za,a dauka zuwa katsina fa ansan aure yana iya kai mace ko ina amma ace wai kamar Asiya za a hada da wanan don Allah.

Me Asiya tasani fisabilillah gaskiya idan daddy yai haka bai maku adalci ba a raina niko fadi nake wani dama da auren mashayi ai gara zuwa kauyen koda kuwa kauyen kauyayyene.

Itama din danata bacin rai don cewa tayi sister kiji min Dad fa wai zai min auren dole ina karamata haba dai sai kace ku din nan ba aimin auren hadi a daba balle yanzun nan dako mijin nan yaga iskanci.

A gurina mai saukine idan daddy yace na bar mai gidansa kawai saina tattara inbar gidan in kama haya ko in nemi gida aban nan quarters din staff din mu in zauna.

Amma wanan auren hadin gaskiya ba mai min shi a yanzu dai kan koda banyi ba balle yanzu wai kinsan mun taba soyayya na yara da Addil tun lokacin mummy ta sakani gaba saida ta rabamu tun wanan auresu na gida ya fita raina.

Duk da na tabbatar dashi nake aure a yanzu da duk wanan bai sameni ba da ina gidan mijina a zaune don Addil mijin aurene halinsa yana da matukar kyau sosai wallahi amma mummy ta rabamu.

Halin da nake ciki bai barni nayi mamakin zancenta ba don jin abinda ta fada kan dan uwan namu watau wanan yasa dukkansu sukaki auren hadi sukayi na son ransu ke nan.

Muko anki bamu dama mu gwada sa,anmu a wajen mugani koda sa,a sai wani hadin ganbiza da daddy yai muna inani ina ya hafiz mai zuciya kuma dan giya koda yan uwanshi da suke uwa daya ina ganin yadda suke kwasa dasu kullum shi basuyi daidai ba a idonsa.

Balle ni yanzu da zan zauna da sunan aure dashi ya rayuwan zata kaya a tsakanin mu nida yakewa kallon bagidajiya yar kauye kuma fa ?

Nasan akwai fitina kwance a kasa ga aurenki da hafiz tunda hafiz ba zai hakkura ba don yace ke ba kalan macen da yake so bace bayan hakan kin masa karama ga aure nasan da hakan.

Amma naso yayi hakkuri kubi umurnin daddy din yaki ya fahinceni shida mummy yanzu kuma ga zancen auren su mairo ya taso gaskiya daddy baiyiwa mummy adalci ba a nan.

Shi yana duban nawa auren yadda ya kayane shin daddy baisan da kaddara bane dama Allah baiyi zamuyi dogon zama da habbib ba ko kuma dayan mu na iya mutuwa zaman ya yanke ai.

Ban tsamanin shi yake kallo anty amsan dana san na bata ke nan kada tayi ta zuba ita kadai ba tare dana dan tanka mata ba sao naga ta dan girgiza kai tana dukan sitiyarin motan tace.

Baki san waye daddy ba ke nan yadda mukai mai banga da auren habbib shine yanzu yake son ya rama akan yan uwana ya rike zancen a ransa tun farko kuma nasan hakan zai iya faruwa tunda abin nan ya faru tsakanina da habbib din nake fargaban hakan amma ban dauka yan uwana zai shafa ba.

Mun shiga haraban makarantan ta samu waje tayi parking din motan sai lokacin ta kalloni tace nasan kina cikin wani yanayi a yanzu ki daure ki tsaya ki dage da karatun nan shi zai kwato maki rayuwa a nan gaba insha Allahu kin dai gani yanzu a gareni.

Kusan tare mukai komai don bata barni nayi wani wahala ni kadai ba sai wajajen biyu nagama don samun taimakonta da nayi na zama daliba ke nan a yanzu nima .

Don gata yai min komai bansha wani wahala da sauran dalibai suke samu ba yayin cike ciken form dinsu saboda ita don tana aiki a tare dasu wajen.

Karfe hudu duk ina gida part din mu na nufo kai tsaye sai dai ban samu mum ba don haka na nufi daki in rage tufafin jikina har kuma nafito falo mum bata shigo ba hakan ya ban mamaki fitanta tabar part din abude .

Cikin gida na dosa in tambaya ko ta fitane a tsaye na samu matan daddy enugu suna magana suna ganina kuma sukayi shiru gaidasu nayi nake tambayan mum din.

Amaryan ke fadin tana ciki dasu Alh tun safe yau bai fita ba yana gidan nan suna rigima da hjy Malka akan zancen auren yayanta Allah dai ya sauwaka tashin hankali baida dadi wallahi shi kuma Alh ya kafe sai yayi abinda yayi niyar yi.

Hafiz ma yazo dazun nan duk suna ciki suna magana tare da wasu yan uwa da sukazo daga katsina a raina nace Allah yasa a wargaza zancen nan.

Saidai a fili juyawa nayi na koma ciki na kwanta a saman dogon kujera ina faman tunanen abinda zaije ya dawo akan zancen.

Don nasan mahaifina ba zai taba budan baki suyi magana kan hukuncin da daddy ya yanke a kaina ba sai dai Allah kadai zai kwatoni ga hakan.

Na dade wajen sai ga mum ta shigo tayi mamakin ganina a falon zaune take fadin kin dawo ashe na amsa da ehh tun dazun nashigo .

Muna can yau gaba daya abin baiyi dadi a gidan nan ba wallahi badon zuwan su yaya ba da Allah ya gyara gaakiya yau da ban san inda fitinan nan zai tsaya ba gidan nan.

Don abin ya kaisu har da duka da rotse rotse da girman su suna aikin yara ga hafiz yazo shima da nasa haukan shikan ai ban raga masa ba don mahaifi mahaifine ko ya yake kuwa.

Allah dai ya gyara Allah yasa kuma iya fitinan ke nan don gaba akewa gudu tunda abu har yakai ga hukuma ai zance baiyi dadi ba.

Haka tayi ta koro jawabi a gajarce ta yadda ba zan fahinci meya faru ba don dukule zancen da tayi ill takardun resit dana mika mata ta karba sama sama ta duba take fadin anyi komai ke nan na amsa da ehh .

Tace Allah ya bada sa,a yasa ki amfana damu duka da sauran al,umma baki daya wanan yasa ban damuwa sosai don karatun nan da zakiyi din.

Baga Nafisa ba yanzu karatunta ya taimaka mata ga komai har takan manta da abinda ya sameta a baya karatun yana da amfani sosai ga mutum idan ka dage kayisa Allah ya taimaka yaba sa,a na amsa da amin.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[2/21, 21:53] Maman K: DUBA MIN BAYA FOKON,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Me karatu nasan zakiyi mamaki da al,ajabin yin shiruna haka lokaci guda ba tare dana nuna wani bori ko botsewa zancen daddy ba alokacin .

Hakane kwarai hakan kuma ya samo asaline bisa ga gargadin dana samu daga mahaifana dakuma hjy mum dita da sukai min cikin kakausan murya kan yiwa iyayye biyayya don baba ya gargadeni da cewa duk yaji wani rashin mutunci ya fito a bakina in tabbatar dana nemi wani uban bashi a duniya.

Amma ke kina ganina kinsan ina cikin tashin hankalin tsaka mai wuyan fita a rayuwana gashi ansano yin shiru koda kuwa ana min habaici ko cin fuska dole nake jan bakina inyi shiru.

Saidai yanzu gaba daya na daina fita ko ina daga makarant dana fara a yanzu sai zaman part din mu wanda ya zamo sabon hali agareni yanzu din.

Ban shigo ko wajen Dada balle part din hjy mummy da yanzu a kusan haukace ta da kowa agidan don ganin laifin kowa takeyi yanzu mutakat ka zaune a karkashin daddy don tace hadin baki akayi ai mata hakan don aga iyakanta.

Tana zaton da bakin mum cikin wanan shawaran kamar yadda nima na zata fa farko koda saninta akai min haka djn daddy ya rasa wanda zai hadi aure sai hafiz dan hjy malka.

Matar da bata kaunan ko jin sunana a bakin wani balle ace wai nice a matsayin sarkuwarta kan danta data kwallafawa rai a duniya fiye da kowa da komai nata sai gashi haka ya faru yanzu.

Ni kaina nakan zauna wani lokaci inyi tunanen ko meye dalilin daddy na zabana yaba ya hafiz a matsayin mata ko hakan na cikin karin zumuncin da yake ikirarin yanayi da mahaifina ke nan.

Duk rikicin nan ban taba sakashi a idanuna ba saidai inji a bakin mum cewa yazo koya tafi cikin zance don dama ba gwanin shigowa part din bane ya gaida mum shi sai lokaci lokacin daba,a rasa ba can ko wani abu kwakwara ya shigo dashi part din mum din.

Safiyace sauri nake kada in makara don yanzu tafiyan mu bai daidai da anty Nafisa don ita takan dan jima a gida yasa nake rigata fita a yanzu din.

Sauri nake nafito daga cikin gida inata kokuwan gyara hijjab din jikina kamar ance in dago kai ya hafiz nagani tsaye gaban motanshi daga shi sai gajeren wandon maza da taba a hannunsa yana zuka.

Ya harde kafa daya cikin daya yana waya kuma tare da zubo min muggan idanunwans dake daga min hankaki da kallonsu take naji kafafuwana suna hardewa haka na daure na sawa kaina kwazo ko kara kallonwa banyi ba nasa kai nafice daga haraban gidan.

Break muka fito kamar yadda muka saba fitowa don yan lalurorin mu na yau da kullun ban kokaiga fitowa wayan anty ya shigo wayana na dauka.

Take tambayana da ina inane munfito break na amsa da ehh take fadin kizo yanzu ina jiranki office dina na amsa da gani nan zuwa.

Gashi akwai nisa sosai tsakanin department din mu dasu haka na taka ga yunwa dake cina a lokacin har addua nake azuciyana da Allah sa wani abinci zata bani inci alokacin.

Ina isa jerin office din na tsaya tare da nocking naji muryanta tana amsawa da shigo nasa kai zuwa ciki ina mata sallama ji nayi lokaci guda kamar in juya don ya hafiz din da nagani zaune gabata.

Lalai kiran nan yayi sa,a har kin karaso shigo ki zauna dama ga wanda yazo ganin ki ni barin dan je in dawo kafin ku gama kar in zauna ace min surikar zamani kuma.

Tafita tana dariya sam bata kula da yanayin da nashiga ba a lokacin shiko ya hade rai kamar yaga mugun abu a lokacin fuskar nan nasa a tanke kamar kullun duk da yana son kama da daddy ga zubin hallita rashin fara,arshi kamar daddy yasa kaman nasu yana dushewa.

Don daddy mutum ne mai fara,a da son mutane ga sakin fuska ga kowa daya sani komu da muke yaransa yana sake muna fuska wani lokaci daine idan ransa ya baci zaka hadu da fushinsa.

Dan lokaci mai tsawo yaja ina tsaye ina saurarensa yana cike da haushi da takaicin zubar mai da mutuncin da daddy ke shirin masa akaina.

In ba abin daddy na kauyenci ba da wanan karamar yarinyar da bata gama ko fetan majinan yara ba daddy zai hadashi a raina masa wayau kawai.

Iska mai karfi naji ya furzo da iska dakyar maganan ya fito masa yace well, koda yake ba sai kin zauna ba dan baki da darajan da ina zaune kina zaune a guna.

Ina son ki saurareni kiji me zan fada dama shi ya kawoni nan ba wani abu ba don karki dauka ko donki nazo nazo nayi maki kashedine a kaina.

Nima ban fatan ace irin ka yazo zance wurina na tsunci kaina da bashi amsa don raina ya gama baci sosai dashi don yadda yake min maganan da kuma kalamin daya fara fada.

Sai naji yace really yarinya ashe show din zaiba da cita tunda kina ja abin yayi min daidai kuwa toki saurara kiji idan kina son kanki da lafiya ina mai shawaratanki da kiyi gagawan samun iyayyenki ki fada masu baki da baki da baki kaunata kema kamar yadda ban kaunarki.

Wani shu,umin murmushi irin na wullakanci ya subbuce min a lokacin na kallesa a wullakance bandaiyi magana ba yace kwarai abinda nake son kije kiyi ke nan a wajensu.

Don ke kanki kinsani niba sa,an aurenki bane don kawai ajawa mutum abin kunya yasa mahaifinki ya likewa daddy ashe don kawai a manna mani ke in kaiki ina dubeki don Allah ?

Wata kala mace tsaye haka kimkam kamar muciya ko fasali da ma,ana babu irin na mata don zalama nan ma saida kuka biyomu don kwadayi.

Wani malalacin murmushin mai karawa mutum haushi da takaici na sakar masa ina cewa.

Au ashe naku zargin ke nan dama akan mahaifina ya mannewa daddy ko daddy ya manne masa ?

Yadda ya dahewa baba din yana cin riba dashi aimu aka cuta da sunan zumunci akaci amanar mu baku ba.

Ke ni sa,ankine ya taso min kamar zai kaureni kome ya tuna kuma naga yaja baya yana fadin kin daiji menace dake kiyi gagawan zuwa ki sanar dasu tunkan rana yai maki dare a zancen nan.

Au kai baka san hanyar yin hakan bane saini zaka zowa da wanan zancen donnka daukeni sakarai mara tarbiya da bansan darajan iyayyena ba ko to kasani niba hakan nake ba.

Nasan zafin da darajan iyayyena fiye da kowa a duniyan nan saboda nasan zafinsu da darajansu don shine ma kaji nayi shiru tunda aka fara zancen nan daidai da rana daya bani fatan su kwana da bakin cikina a zuciyarsu don haka bani da ja a duk hukuncin da suka yanke akaina koda kuwa nasan abin zai cuta min.

Common ki rufe min wanan bakin naki a nan tun ban masgeki ba ya mike ya nufoni yana zare min ido nace .

Oho dai kaika sani na juya da sauri dama a kofa nake tsaye tunbshigowana tun kan ya karasa fitowa daga cikin kujeran da yake zaune yakai gareni nafice daga office din.

Anty dake tsaye da wani abokin aikintane taga fitowana a office din kira take kwala min ko juyo banyi ba nasa kai na wuce ina share kwallan da yazo min a lokacin.

Ina jin kira a wayata nasan itace banbi ta kan wayan ba na nufi school mosque kai tsaye don gabatar da sallah azahar ko zuciyana zai min dan sanyi alokacin yadda nakeji.

Office din ta koma ta sameshi yana huci a ciki shi kadai tunda ta shigo take fadin hafiz me kaiwa yarinyar nan meyasa kai baka jin maganane don Allah ?

Kaki ka bari abi abin nan sannu kowa ya huta sai kara jagula lamarin kakeyi ga baki daya yanzu me kai mata don Allah nasan halinka da saurin hannu wallahi ?

Lalai yarinyar nan tana da ja meta daukeni da zata tsaya gabana tana mayar min da magana haka watau nine dan iska mara tarbiya take nufi kome ?

Wallahi nama fasa ja akan zancen nan yanzun zan aureta din in koya mata hankali ita da wa yanda ke daure mata gindin badai igiyar auren nasu a hannuna yake ba ya buge table da karfi jin hakan yar uwar nasa tace .

Me kake nufi da wanan kalamin naka hafiz ?

Ya jefo mata wani kallo na bacin rai kafin ya kuta yasa kai ya fice daga office din kiransa yakeyi da karfi bai tsaya ya kallota ba yafice abinsa.

Kai ta dafe tana fadin oho my god me yaron nan yazo yayi a nan yanzu Allah dai yasa ba dukan yar mutane yazo yayi a nan ba yaja min aiki .

Waya ta kara lakuban layina saidai wayan akashe yake lokacin don haka takai zaune tana shawara a zuciyarta kafin dabaran kiran mummy yazo mata ta danna mata kira kai tsaye.

Mummy na dauka tace mummy yanzu abinda hafiz yazo yai min ya kyauta ke nan don Allah nan yazo gun aikina ya sameni yace yana son don Allah nasa a kira masa zeey yana son magana da ita.

Mummy ina ganin fa dukar ta yayi yadda naga ta fito tana hawaye bata ko saurareni ba ,,,,,,,

Ke dakata don Allah nina dauka wata tsiyan ya shuka kuma har hankalina ya tashi inya doketa ai ya duki banza dama haka sukeso ai ita da iyayyenta ki bari in kirasa inji meya ya faru tsakaninsu ?

Sai kuma ta koma fadin ina ma ruwansa da itane wai da zai bita school ya ja maki fitina acan nima mummy abinda ya daga min hankali ke nan ai.

Wai harda ce min yama fasa yanzu aurenta zaiyi yaga iya gudunsu badai auren a hannunshi yake ba ai shike nan yasan maganin su tunda abin tsiyace.

Barshi zai shigo ai ya sameni don shine mani yanzu banson zuwanshi garin nan don inyazo kara caza min kai yakeyi ba kwantar min da hankali ba.

Ina fitowa mosque din kai tsaye gida na nufo dan nasan anty Nafisa zata iya zuwa nemana a lokacin don haka na nufo gida ban koma ajin ba kuma.

Nayi sa,a mum tana falo na shigo bata kula da yanayi na ba sai cewa takeyi yau da wuri kuka dawo haka amma dai kunyi saurin tashi yau din sai sheshekan kukana taji da sauri ta dago tana fadin subbahanallahi meya faru kuma ?

Da sauri ta mike ta karaso gareni tana fadin wai meya farune kin zauna haka kina min kuka ki fada min abindaya faru mana ?

Nace mum ina kamo hannuta don Allah ku taimakeni ku raba aurena da wanan azzalumin mutumin don ba dai kaunar juna mukeyi dashi ba mum.

Wai hafiz meya faru ina kika gansa nace school ya bine office din anty nafisa nan na kwashe komai ban boye mata ba na fada mata tace.

Lalai hafiz yakai dan iska dama wanan zargin sukewa yaya Garba ashe haba gaskiya dai habaici ke zuwa yana dawowa ashe da yaya sukeyi manufansu ke nan dama.

To wallahi bari Alh ya dawo dolene yaji zancen nan kuwa don ba jaka za,a kai masa ba da zai kama ki tin waje yana duka da zagi harda cin zarafin iyayye haka dole ayi wani abin gaskiya akan zancen nan.

Don wanan zancen ba karamin magana bane dole iyayye maza su sani su tsawata mashi tun wuri yanzu waya saura aure da dukan mace kuma ?

Nan dai ta lalasheni da kalami masu dadi tana kwantar min da hankali da kara ban shawara kan yadda zan kiyayyeshi .

Anty Nafisa na dawowa nan part din mu ta dira take tambayan mum ni tace ina ciki dakina ta nufo zaune nake saman gado na mike kafafuna da takardan karatuna a hannu ina faman tunane.

Jin shigowanta yasa na dago kai gareta ina kallonta na samu na bude baki da kyar ina fadin sannu da dawowa anty itako sai wani kallo take min na kinganki ko din nan.

Tace watau shine kika kashe min waya don kinsan zan kiraki kuma kika kama hanya kika dawo gida tun ba,a tashi da kika dawo gidan karatun naki fa sister ?

Kada ki bari kiyi wasa da karatun ki gaki kinsan course din ku bana wasa bane meyayi maki kika fito kina kuka ina dai ba dukanki yayi ba ko ?

Ta fada tana kallona don son jin amsan da zan bata a lokacin hawayene suka fara fito min kafin nace da ita meye ma bai mun ba anty ya dakeni ya zagi iyayyena yaci masu mutunci ya kirasu da yan maula.

Don shi suka asirce daddy don a manna masani suci arzikin Dad din na karasa ina wani irin kuka hannu ta dora akai tana fadin nashiga uku ashe hafiz katon wawane ban sani ba.

Baba Garba din zai kullawa wanan sherin mutumin da kowa yasan irin kauna da amincin dake tsakaninsu da daddy zai tsaya kan shirme yana masa wanan sherin haka ?

Au kema kinji ko kinji abinda Hafiz ya aikata ke nan duk da kema naga laifinki ai tunda kinsan basu shiri me saisa ki kirasa masa ita don Allah.

Wallahi hjy mum na zata alheri ya kawosa wurinta bansan dan iska sheri yazo yayi ba na dauka abin arziki ne wanan babban maganan daga ina yafito masa haka kuma ?

Atoh kila abinda yaji ana fada ke nan shima ya fadi in bashi ba yaya Garba sa,ansane da zai jefa masa wanan kalamin kamar ubansu daya fa da Alh.

Duk da ran anty Nafisa din ya baci da kalaman mum amma haka ta daure tana bada hakkuri ga mum din wai kada zancen yakai ga daddy don laifinta Dad zai gani.

Tace nafisa ke nan wanan abin kema kinsan ba abin a kyale bane tunda har yakai ga dora hannunsa akanta tun yanzu ga kuma cin zarafi ai dole aiwa zancen tufka tun yanzu.

Ni har naje na fadawa hjy tun dazun ai don tayiwa Alh magana idan ya dawo don dole dai su sani wanan abin gara abarshi tun rayuka baikai ga baci ba gaskiya.

Ayi abu don zumunci ya kara a tsakani azo kuma ana da ansani a tsakani ai kinga gara a bari haka zaifiwa kowa sauki tun yanzu.

Kai hjy mum kema kinyi saurin fadawa Dada ai da ki bari in dawo mu samu dan iska muyi masa tas amma duk da hakan bai baci ba ai don zaifi gaskiya a tsawata masa doni dan iska ya tashi jawa magana ai a wajen aiki.

Da hukumar makaranta sun sani wallahi wanan abin zai iyasa su bani quiry ko kuma su koreni ma don hakan dokane a garemu mai tsanani.

Ta kalloni tana fadin kiyi hakkuri don Allah zeey in Allah yaso za,a tsawata masa ya daina ta daga tana fadin bari naje mum kada suga na dade ban dawo ba azata har yanzu ina can.

Daddy kan jin abin yayi kamar al,amara ya dade zaune shiru bai iya magana ba sai bayan tsawon wani lokaci yace me yaron nan yake nufi ne wai ?

Ke nan ya nuna ni ban isa dashi ba ke nan da zance dashi ga abinda nake so har ya tsaya yana jayayya akai haka shike nan yaje ga duniyan nan ai fadi gareta tunda yana da wani uban dayafini.

Yaro in maka gata in hadaka da yarinya ta kwarai kace min ba haka ba shike nan tunda ban isa dashi ba ai koda yake nafi ganin laifin Nafisa ai a zancen nan.

A,a Alh kada kaga laifin nafisa don Allah ita meye nata a cikin zancen nan don Allah na tabbatar Nafisa dai ba zata turashi yaje yayi abin nan da yayi ba maganar gaskiya.

In kasan halin mutum ko bayansa ka fadi gaskiya akansa babu ruwanta cikin zancen nan yaje da sunan hirane yayi hakan ita kuma tayi fada sosai ga yadda yayi din .

Ai gashi ga duniya tun haka uafi masa din aurene dai ba fashi nayi niya sai anyusa kuma ko zai mutune ranan daddy din ya fada rai bace.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[2/26, 07:16] Maman K: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

Rayuwan haka yake tafiyawa bawa da kalubali iri iri wani tun yana karami zai fara fuskantar kalubalin rayuwa wani ko sai ya zama magidancin kansa zai fara karo da hakan.

Nikan kusan sai ince tun ina karama din na fara fuskantar hakan na baro kauye cikin kunci da matsi mun dawo katsina wanda zuwa kano ya zamo min babban kaddaran rayuwa a yanzu.

Don ko yanzu na fahinci shirin buki haikan hjy mum dina keyi don ko duk wani abu daya kamata ace uwa ta tanada nakai yarta aure da zatayi amfani dashi gidan miji hjy mum tana tanadar min shi daidai gwargwadon halinta zakice itace ta haifeni da cikinta abinda take min.

Duk da zaman namu Allah baiyishi da dogon tsayi ba amma haka bai hana taimin komai na sakayya a gareni ba takance nidin yartace ta cikinta don ko dan uwanta ya haifa matani.

Nidai ina kallonta don duk gayyan kayan nan basu burgeni kosu ban sha,awa kawai dai ido na saka zuciya tab da tunanen me zaije ya dawo min.

Karatuna kawai nasawa gaba wanda hakan ke dan sake min zuciya duk da banda kawa da zan nuna ince ga aminiyata yau acikin kano.

Bawai kuma ban samu bane a,a bandai ba hakan muhinmanci bane a rayuwata don akwai mutum uku da mukai karatu tare a secondary da yanzu course din mu daya don suma pepper su yayi kyau sosai an kaisu uni.

Dan dama su wani lokaci zaki ganmu tare muna hira ko muna dan tatauna abinda ya shafi karatun mu na yanzun don sanin da sukai min mai fasaha tun a secondary a sanadinsu sunana ya fara dan dagawa a class din.

Gashi har Saturday nakan shiga school around twelve mu dawo four na yamma don hakane na zama busy sosai a wanyanzun din ban kuma fadawa kowa zancen aurena ba.

Wani lokacin nikanyi mamakin rashin fara karatun su Mairo amma nakan bar zancen da cewa watakila dai don result din su baiyi kyau bane daddy din yaki kaisu ko kuma ni na samu daurin gindine a wajen dan uwana daya tsaya min har yaga na samu na fara karatun a yanzu kar a tauye min rayuwa gaba daya.

Ranan na dawo school din rana na samu part din mu cike da matan gidan ina shigowa da sallamana Anty Nafisa dake duke ta baza zannuwa tana kallo ta dago tana kwala guda tare da fadin kunga amare fa.

Yan gatan daddy aini wallahi daddy ya nuna min banbanci irin wanan lefe haka gaskiya yaran nan kun taki sa,an daddy ba kadan ba gabana yayi wani irin mumunan faduwa lokaci guda na dan daga kai na kalli kayan sau daya na shige daki.

Zaune nakai don gaba daya wani irin duhu nake gani lokaci guda saida mm a dade zaune a wajen kafin na rage jin muryoyinsu a falon da alaman sun fita kenan part din.

Hakan yasa na daure na mike lokaci guda na fara rage kayan jikina motsin mutum ya shigone yasa na dan juyo inga maishi Antu ce dai still ta shigo dakin nawa.

Haba sis kayan lefe ba abin wasa bane balle ku da daddy ya kashewa wa yan nan makudan kudin wajen hada wanan lefen komai iri daya daddy ya saka maku saidai ya banbanta kala don kowa da kalan nasa haka kuma,,,,,

Sai naji tayi shiru don fahintar da tayi ba ita nake sauraroba a lokacin tace gaskiya banso ki da haka ba zeey zaki biyewa Hafiz ne ku sabawa daddy ga baki daya ku ?

Bayan duk kokarin nan da daddy keyi akanki kada ki bari shedan ya rudeki har a gane hakan akanki bayan kowa na yabon yadda kikayi biyayya ga iyayyen mu din yanzu kuma ki bata rawanki da tsale.

Gaskiya kada ki yarda wanan labarin ya kai ga daddy din yadda yake fama yaba hankalinki a wajen kowa ko mairo fa Auwal yazo daga bauchi sun shirya yanzu duk ta rage wanan iskancin data dauko yi kinsan guy din hadadene ga kuma ilimi.

Asiya daice da take bin zancen mummy wai ba zata katsina ta zauna ba har yanzu nake dan ganin kanta yana hayaki itama dai din ta rage ba kamar farko ba don na zauna dasu nayi masu nasiha sosai.

Kuma na lurar dasu gatane fa daddy yayi maku zeey ke mace ce zeey duk wani iskancin Hafiz na dan lokacin nan ne kina shiga gidan na tabbatar da zaku shiya dashi.

Abu dayane zuwa biyu shine nasan Hafiz dan karyane na gasken gaske don haka sai kin zage sosai kin koyi kwaliya girki don kamar Addil yake shima su biyu keda

rayuwan tsada da jin kyama a gidan nan bako ina suke shiga ba ba kuma ko wani abinci suke ci ba haka kasafai.

Kinga nan ma sai kin kula haka kuma nasan hafiz da son jiki da son jan girma kuma kamar yadda kika sani kowa kuma yasani kinga ke nan a nan sai kin hada da hakkuri.

Hakkuri kuma bana wasa ba don nasan kinsan komai basai na fada maki hafiz yana shaye shaye ba duk da mummy tana ganin ba wanda ya sani a gidan nan nasan kin sani a ranan da mummy ta aikeki kai masa abinci part dinsu kuma munyi zancen dashi.

Don haka kinga nan ma akwai matsala na zauna nayi tunane da hikima daddy yayi wanan hadin naku keda shi zeey don ke din ta gidace zaki iya rufawa dan uwanki asiri ba kamar wata bare ba ta waje da zata iya tona mashi asiri ga abinda yakeyi din.

Zuwa lokacin na kasa boye hawayen da nake faman riko a idona kuka sosai nakeyi a dakin naji ta dafani tana fadin wallahi zeey da hikima sosai cikin wanan auren Daddy bai hadaku ba saida yayi nazarin hakan ya hada kowa da daidai da ita.

Kada kiyiwa daddy mumunan zato a wanan hadin naku kice ya manna masa dansa dangiya alhalin su yayansa ya zaba masu masu kirki .

Ba haka abin yake ba zeey wallahi na fahinci daddy a yanzu duk wanan hadin da daddy yayi yayisane akan hikima da basira ko wanen ku ya hadashi da wanda yasan zai gyara rayuwansa amma ba kowa zai fahinci hakan ba sai nan gaba.

Idan kun daure gaba dayan ku zakuji dadin auren nan naku jin meta fada yasa na dago kai na kalleta tace Yes iam telling you zakice na fada wata rana insha Allahu.

Hannunta ta dauka ta dagwara a nawa tace ki jajirce sosai zeey ki zamo jaruma a gidanki zainab ki mayar da mijinki abin alfaharinki abin kuma so ga kowa daya gansa.

Kuka sosai nake har ban iya gane mum na dakin ba saida naji tace kukan na meye haka don kawai kijawa kanki ciwo duk abinda Nafisa ta fada gaskiya ta fada maki.

Don ba karya acijin zancenta nima abinda na hango Alh yayi ke nan kikaga ina faman baki hakkuri da kike dauka duk bamu son kine wanan shine gata da kaunan da zamu iya nuna maki ai mama.

Itama mum dafani tayi acikin sanyin jiki tace mama kiyi hakkuri ki daina kukan nan don Allah ki yarda da hukuncin da Allah ya kaddara a gareki.

Ki yawaita kiran Allah ya sasauta maki abinda kikeji a zuciyarki insha Allahu abin zaizo maki da sauki ta hanyar da baki tsamani ba da yardan ubangiji.

Tana kaiwa nan ta juya ta fita zuciya ba dadi agareta ta barni da Anty Nafisa din dake fadin haba sis ki kwantar da hankalinki mana ki dauki shawaran da muke baki nasan kowaye hafiz idan kikabi sharan mu zakiyi maganinsa hafiz zai dawo a hannunkine wallahi.

Haka kuma sai kin daure da mummy don rayuwan Hafiz gaba daya bisa tsarin mummy yake don hafiz ko wanka yayi saiya kira mummy wani lokaci yana tambayanta kayan da zai sauya saboda sagarta data koya mai wai so.

Don haka ki dauri kibi shawaran nan namu insha Allahu zakice nace dake ni zan koma don in gyara wancan kayan nasu mairo dake part din mu don nasan mummy ba zata tabasu ba idan bani naje na kawar ba a yanzu don Allah ki natsu kamar yadda hjy mum ta fada maki.

Daga haka kuma tafice daga dakin ta barni a wajen saida na dan dauki lokaci kafin in mike nashiga bandaki na fito don la,asar ya shigr ko ana batun magariba ba daman ayi nafila a lokacin yasa na wanko fuskana na fito abinci na sama mum ta kawo min har daki na zauna naci kadan don kada tace banci ba na kwashi kayan zuwa kitchen.

A dakin kwananta ta jera akwatinan auren nawa da daddy ya gabatar masu a matsayin lefen mu wai ashe duk da fitinan mummy bayan Dad ya kirasu saida ta saka matar daddy enugu ta bude ko wani tagani ta kana tace a musaya a dauki wanda daddy yace shine nawa shi kuma ya fito yace bata isa ba kowa da sunansa yasaya mai ya kuma saka komai iri daya aciki don yasan kalan da kowan mu ke so ai.

Nan kuma ta kwashi fushi ta hau bakinta daddy din yace idan son kai nayi kece dai naiwa son kai din don matar dankice na cikinki zata daura kayan don haka ake nayiwa son kai din ke nan .

Wani kallo tayiwa daddy kafin tace matar danka dai amma ba dana ba in gaskiyane ita mama din abin kwaraice ka hadata da Nasir ko Addil mana amma ba jini naba.

Tunda kasan ko a rarihi ba aure tsakanin zauren gidan mu da nasu ke nan ashe ba aure a tsakanina dake ko ?

Tunda hakane tayi shiru ta juya ta bar wurin rai bace yace sakaran banza zan koya maki hankali a gidan nan tunda ke kulun yarinya kike zama baki girma kafin ki tauna zance.

Dada da abin duniya ya dama a lokacin kallon hanyar da hjy malkan tabi tayi tana dadin wai ko anya kan marka daya kuwa kodai marka ta tabune ba,asani ba ?

Lafiyanta kalau tsaban iskancine da rashin sanin ciwon kai data iya take nunawa wanda bai gama sanin halinta ba a yanzu wai ita marahankali.

Bayan kamar kwana biyar ya Addil ya shigo garin sai washegarin asabar ya shigo gidan muna zaune falo don ranan ba zamuje karatu ba kowa na gida saboda dan tafiyan da mai course din yayi muka huta gida a ranan.

Yana saye a cikin wani yadi fari daya kara masa kyau sai wata yar hulan maza dagani mai tsadane mai kalan dan ruwan toka akansa duk da akwai rama a jikinsa hakan bai hanashi yin kwarjini ba a idanuwan mutane.

Part din Dada ya fara shiga dana daddy Enugu ya gaidasu suna tambayarshi matarshi Aisha duk da tare suka shigo kanon amma saiya saya yace tana lafiya kawai ba ambata tare suke ba don gudun korafi a wajensu.

Ya gama dasu har part din mummy kafin yashigo nasu part din ya samemu zaune da mum din a falo muna kallo mum kuma na waya da mai kayan kamshi da tayi Oder a kawo mata wata yar maiduguri.

Lah ya Addil ashe kazone na fada cikin yar fara,ata ina kokarin dagawa inda nake zaune yace amarya gaki duk kin rame mana ko duk rakin auren ne haka kika fada tun yanzu ?

Fuska na dan bata tare da fadin haba dai ya Addil har dakai kuma kaine fa share hawayena kullun inawa ya Nasir gorin hakan don yaji haushi .

Zance kuma a gaskiya karo na farko ke nan duk zamana gidan da wani kalman wasa ko zolaya ya taba shiga tsakanina da yaya din don baya magana balle inga fuskan tsayawa wani wasa dashi can yadda mukeyi da ya Nasi da sai mum ta koresa wani lokaci .

Mun din ta gama wayan ta dago tana fadin ashe kun samu shigowa yace ehh aina fada maki zanzo kafin buki na ganku ya sauko saman kujeran ya tsuguna yana gaida ita a cikin ladabi ta karba masa ni dai hakan na ban sha,awa wallahi.

Ruwa da abinsha na karaso masa dashi har na dire a gabansa yace nagode mum yarki ta rame da yawa wallahi ko tayi ciwone wai don raman nan yayi mata yawa gaskiya.

Aiba ita daya ta rame ba har kai don haka ashe aure ramar da mutane yakeyi ke nan ba kiba ba kana zancen mama kai kaga yadda ka rame din kuwa ?

Halan ko abinci bata baka balle wajen kwana kai ya kamata aiwa wanan tambayan a yanzu ba mama da har yanzu tana dakin uwarta bako .

Meke sakaka wanan rama haka har ya ja maka dushewa hasken ka ya dushe sosai a yanzu mai sunan malam ta kirasa da sunan da akasarin yan family suke kirashi dashi din don sunan kakansa malam Ali da yaci .

Dan shafo kai yayi zuwa fuska yana murmushi yace mum don daidai kin dade baki gani bane kike ganin na rame amma ai jikina nan da haskena kuwa.

Allah yaya ka rame ka fada sosai kayi baki ka rage tsayina ya dago ya harareni nayi saurin nokewa a bayan mum yace kika karajin ana min magana kin sani ai zan fasa shegen bakin nan naki a wajan nan.

Ba zaka dukar min diya ba son gaskiya ta fada ai duk mai kaunan kako zai fadama sauyawan nan da kayi Addil da alama dai auren nan abinda mukewa gudune ke faruwa da kai dai ke nan ?

Dan murmushi yayi yana fadin mun kin fa san yanayin aikina yanzu ba kamar da bane mum aiki yai min yawa a yanzu ga kuma nauyin iyali akaina.

Tareshi mum tayi da fadin au kace min kun samu karuwa ashe kunfi ku biyu yanzu gidan to Allah ya raba lafiya ya bamu mai albarka da sauri yace ba abinda nake nufi ke nan ba mum muna dai fatan Allah ya kawo ya fada yana dukarda kai kasa cikin ladabi .

Shiru kowansu yayi kafin shi ya kawar da shirun da cewa Dad ya buga min waya yace saura sati uku yanzu daurin auren yaran nan da sauri na kallo mum din ina fatan tace yafi hakan ai sai naji tace insha Allahu ga yadda yasa lokacin ba saidai uwar yaran ai ta nemi da ya kara mata lokaci ta kara shiri ban sani ba ko zai yarda da hakan data bukata don Alh bahagon mutum ne idan ya tashi abinsa.

Ko naka ba haka bane daga zuwa nema ya saka rana mikewa nayi tsam na barsu a wajen hankali tashe ya Addel din yace nasan ba zai canza wanan ranan daya saka ba ai.

Don yanzu ma kiran da yai min akan hafiz ne wai yace baya son wanan gidan daya gina masu saidai a canza mashi wani mum fara zancen dashi a waya shine yace idan na samu lokaci inzo.

Yanzu canza masa wani zaiyi ke nan yace to bamu kaiga magana ba shima bansan dalilinsa nakin wanan gidan ba ai gashi baya da nisa sosai da gida kuma ginan gidajen yayi kyaiu sosai wallahi.

Sagartane irin nasa kawai da neman magana yana son ya bullo da duk wani hanya da rayuka zasu kaiga baci in bashi ba ina ba zama nan din zasuyi ba na dindindin meye nasa na tsaya zaben gida inba neman na yiba.

Zanje na gani yanzu ai kafin daddy din ya fita muyi magana akai Allaj ya kyauta ta fada tana kawar da kai gefe cike da takaicin abubuwan dake faruwa a gidan cikin dan lokacin.

Shin tunda ba Allah yace sai anyi hakan ba abari mana amma kan yaro daya har ciwo na batun kayar da Alh in anyi magana kuma suce saboda taga ba danta bane.

Koda ya Addil din yaje wajen daddy ya sameshi yana shirin fita baiyi magana saida yasa aka kira anty Nafisa razo yake kara gaya masu matsalan da dan nasa ya kawo kuma yanzu.

Anty Nafisa ce ta fara magana tana fadin wai meke damuwan hafiz ne haka wanan ai iskancine kawai yakewa mutane wanine zai zauna masa da matar ?

No ba hakana bane ke Nafisa kinsanfa halin hafiz sarai idan da hali a canza masa kawai a wuce wurin hakan zaifi sauki kafin yakai karshe tace.

Amma kana bani mamaki wallahi ta nasa za,abi koshi ya haifi mutane da zaice sai yadda yakeso za,ayi masa Dad ka fita zancen kawai muga tsiya shidin banza zai tsaya yana juya mutane haka.

Dakata hakana naji zancen kowan ku ai magana ta gaskiya a yanzu banda halin yin hakan bandai sanarwa gaba ba idan rai ya kaimu lafiya.

Ko gaban ba za ai masa ba daddy ai ba shi kadai ka haifa ba su sauran yan uwasa fa idan akace sai abinda yake so za,ai masa kada ya zauna mana.

Da dai kin bari mun roki Dad din ayi masa yadda yakeso din zaifi sai a gaba da babinsa ba shike nan ba ya Addil ya fada cikin ladabi .

Aliyu nasan meyasa kakeson hakan to ba zanyi ba yaje yayi duk abinda yayi niyar yi kada ya fasa idan ban canza masa gidan ba koba shike nan ba donshine ma na kiraku ku manyansu kuji .

Dad din ya shiga masu dogon sharhi akan rayuwan dan nasa yace ya kuma sani ko zancen giidan nan da hadin bakin uwarsa ya furta hakan cewa sai a canza masu wani don bai zama kusa da dan uwasa a waje daya.

Nan dai suka tashi a hakan bayan sun fito sun dan jima a waje suna zancen kafin ya Addil din ya tafi wajen matarsa data kirasa don tana gidan iyayyenta a lokacin.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[2/28, 06:27] Maman K: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Duk wanan badakalan da akeyi iyayyena basuce uffan ba duk ko da zagi da cin mutuncin da mummy keyi kamar a gabansu take fadinsa don komai sunaji amma sun taushe zuciyarsu saboda zumunci.

Akwai sauran imanin zumuci a lokacin dan uwa na iya bugun gaba da dan uwashi ako wani lokaci ya yanke hukunci akansa ba tare daka daga kai kace don me akayi hakan ba.

Duk dadai har duniya ta nade akwai masu imanin gaskiya da biyayya bisa ga tsarin musulunci don sai ince duk yawancin al,adun malam bahaushe kadan ne yake tsarin al,ada duk koyine da addini bahaushe yake abinsa.

In banda yanzu da boko ya sauya wasu suke ganin tsarin na farko ba tsari bane akwai tauyewa acikinsa yasa karfin zumunci da bahaushe yake girmamawa ya rage a zukatan mutanen yanzu sosai bisa ga mutanen baya da suka kwanta dama.

Allah ubangiji ya jikansu da rahama ya gafarta masu albarkan kalman shahadan da suka rike a bakunansu Allahuma amin.

A kwana a tashi hasaran rayuwa inji malam bahaushe buki dai ya karato kowani bangare sai shiri akeyi inda hjy mum gwaggona uwar dakina itama ba,a barta a baya ba wajen shirya yarta da zata kai aure watau ni ke nan.

Don ko wani tsimi wani gunba wani hayakin jiki dana tsuguno da siracin irin na shuwa duk nashashi a wajen hjy mum don sai dare yayi kafa ya dauke zata tasani

agaba da wa yanan abubuwan tun ina sha ina amai har ya fara zama min aciki saidai idan nasha zuciyana ya dinga tashi inyi ta barci.

Sai yanzu nake tuna abubuwan nan don tun ina karama muke shiga daji debo wasu ganyewa matan gidan mu na kauye wani lokacin muke hada masu kafin yan sari suzo daga birni suna saya.

Wanda sai na mahaifiyata ya kare kafin saura su samu shigar da nasu don ita tasam hadi don hakanema nima na koyi hadin ina taimaka mata wajen hada abubuwa.

Sai yanzu tunanen hadin yake dawo min arai naga ai nima nasan dame dame ake hadawa ya zama gumba ko hayaki ko gari da sai sauran haki irin na yar mai ganye .

Tabbas sudin ne don na tuna da dandanonsu hakan yasa na fara tuhumar wasu daga ciki sun fito hannun mahaifiyata ke nan.

Saboda nasu hadin na El,sutura daban ne dana saura ba irin hadin neman kudi bane kawai hadine na sahihi da masana tasirin ganye a jikin dan adam suke hadawa mata don amfaninsu.

Hadine mai inganci dake saukarwa mace da ni,ima da gyaran jiki ki koma abin sha,awa agun kowa duk wanda yasan asalin yar mai ganye yasan yadda maganinsu yake da kyau da tasiri agun manya da yara don ita yar mai ganyen asali bata tsaya iya gyaran mace ba kadai har yara da masu lalura tana taimakawa da magani cikin yardan ubangiji kuma a dace harma da maza wani lokacin suna dace idan sun samu yar asalin yar maiganyen na ainihi.

EL,SUTURA TANA SOKOTO YANZU HAKA ZAUNE GA DUK MAI BUKATAN MAGANIN TA NA AINIHI HAR GOBE AKWASHI KU GARZAYO KUSHA MAMAKI DA IKON ALLAH .

Saura kwana hudu bukine anty Nafisa ta turasasa min binta zuwa wajen gyaran jiki inda ta kaini wani shagon gyara na mata suka fara gyara min jiki tun daga kaina zuwa tafin kafana basu barshi a baya ba .

Don bayan dilka ga kitso ga kumshi ga kuma turaren jiki bayan wanda hjy mum ke banka min din itama ta dora nata akai don hakane duk inda nazo na tsaya zan bar wajen da kamshi.

Duk da ba fita nakeyi ba ina dakina ko dakin mum in kafa ya dauke kuma a falonmu .

Saidai hakan bai hana halimatu yawo da sunana wajen classmates din mu da sunan raba chewegun din buki tana tallana cewa auren hadi za,amin ai.

Mijin baisona amma ni sai rawan kai nakeyi dan naga dan maikudine tun yanzu na dara dagawa mutane kai shine ita tace bari tazo ta kawo masu IV don kar,a manta juna.

Wanan dalilin yasa Anty Nafisa daukana kowa bai sani ba gidan takaini wajen gyaran jiki don ta fahinci irin makircin da sukeyi suna son bambanta sha,anin da wani manufa.

Sai gashi suna ganin gyaran da akai min sai kuma ya koma tsone masu ido ni ina ta kaina su kuma suna hassada dani bansan dalilin wanan abin ba nasu akaina koda yake ba abin mamaki bane don mummyce uwarsu fa.

Hakama kawayen da halimatu ta gayato sai sunzo zasuga aiba gaskiya ta fadaba don yadda suke samuna cikin rashin dadin rai a lokacin zasu fita suna gulma nan dai Allah zai wankeni akan zargin su gane gaskiya a take.

Nida kaina na fadawa wayanda muke courses tare yanzu gaskiyan abindake faru dani sun kuma tausaya min jin zanyi aure da fara karatun mu ta hanyansu suka kara walwalewa kawayen namu gaskiyan al,amarin sabanin abinda halimatu ta fada masu kaina.

Ban taba ganin mahaifina ya shigo wurin hjy mum ba harsu kebe su dade suna magana sai a yau da ya saura kwana biyu daurin aurena da yaya Hafiz ba alamansa nasan wanan maganan kodai wani daya shafi rayuwanane ya kawo baba wajen hjy mum din har suka dade irin haka suna tataunawa a falonta dashi.

Daddy ko ance kallo daya zakai mai kagane hankalinsa ba a kwance yake ba don ance ya fada sosai don tashin hankalin abinda dansa keson yimasa na bashi kunya ga yan uwa da mutanen arzikinsa ga kowa sunan hafiz ya sani a cikin yayansa don haka sunajin auren Hafiz ne ai zakiji mutum yace insha Allahu muna nan zuwa damu za a daura auren.

Wanan ganin da nayiwa baba da mum ya kara daga min hankali sosai da har na kasa fitowa washegari ina kwance a daki sai da mum ta leko tana fadin wai ke lafiya kin shige daki tun safe baki leko ba.

Zaune nakena mike kafa saman gado dake nuna alaman lafyata kalau illa da dumuwa kawai ke damun zuciyana lokacin na dan dago da zuman kallonta saiga hawaye ta ko ina idona sunyi hulu hulu saboda kuka da naci.

Kai haba mama yanzu kuma don Allah damuwa ko kukan nan meye kikeyi hakane don kawai ki tonawa kanki damu asiri mama.

Ya kamata ace kinsawa zuciyanki dangana game da zancen nan don kin gani a zahiri tun ainda aka fito har kawo yau din nan babu alaman canji ko gezau ga Alh gareku.

Aiya kamata ki dauki hakan a matsayin kaddara ki yarda ki amince da hakan kaddarakice mama yin biyaya zaisa kiga Allah ya sakawa rayuwanki ba zaki taba tabewa aduniyan nan ba insha Allahu.

A hankali na iya dago kai na kalli mum din ina fadin mum badon wanan nake kuka ba ni ko waye daddy zai ban ya bani amma ba ya hafiz mashayi dangiya da,,,,

Haba mama kul na sake jin wanan kalamin a bakinki kin taba jin inda hannunka ya rube ka yanke kayar wanan dalilin na cikin nacin auren ku da Alh keyi don yasan irin tarbiyanki yana fatan ta dalilinki hafiz ya shiryu nan gaba.

Mum ta ya ni zan iya shiryashi bayan Allah daya haliceshi yakewa sabo ga kuma daddy da mummy aisu ya kamata ace sun gyara abinsu bani ba ni har wani hikima nake dashi da zan gyarasa.

Addinin ki da tarbiyanki mama dasu zakiyi amfani ki gyara dan uwanki dashi ke dai kawai banda garaje kinsan halin hafiz sai kin bisa a sannu.

Ba kuma ance da zuwanki ki fara masa zancen shaye shayenshi ba a,a cikin hikima da basira da saka wa,azi da kuma addua idan da rabo sai kiga kinyi babban jahadi kin kwatoshi daga wanan mumunan dabi,an.

Ki tashi maza ki wanka ki gyara jikinki kamar kowa don gida ya fara cika da baki ko tun yanzu don yan katsina na nan sun fara isowa kuma suna tambayan ina kike ki kuma adana duk wani abinda kikeso cikin wardrobe dinki ki kulle ki miko min key din na rike a hannuna tana kaiwa nan ta juya ta fita daga dakin.

Jin hakan dole natashi nashiga bayi nayi wanka na fito na samu wani yadin material da akaiwa dogon riga na saka a jikina.

Mum ce ta kwala min kira daga dakinta na amsa nashiga take fadin in dauki abinci inci itama shi takeci a lokacin ban jaba na dan diba a plate nan na zauna ina tsakura saiga anty Nafisa ta fado dakin.

Lah ke kina nan zaune a daki ba zaki je wajen event din naku ba kai na dukar kasa kafin nayi magana mum tace bamu tsara wani event ba don walima kawai.

zamuyi a bangaren mu.

Haba mum ina tare da yan uwa zatayi komai ko ?

No Nafisa kinsan halin yaran nan don Allah barshi a yadda muka tsara zamuyi walima hade dana saukarta shike nan itama idan mijinta nason suyi event idan ya iso saisu tsara abinsu amma barsu can suyi abinsu don Allah mun ta kakabe zancen.

Ta danyi shiru kafin ta juya tana fadin Allah kyauta mum don dai kinkine amma ina wajen ai waya isa yai mata wani abin bayan gani wajen a dai bar zancen har mijinta ya iso garin.

Mum kina ganin wai hafiz zaizo garin nan ko bakiji irin kwasan rikicin da sukeyi da daddy bane tun shekarajiya kan zance guda.

Ban tsamani zai shigo don ko mum yau naji ta kirashi da safe tayi masa kaca kaca ko zaiji yazo ban sani ba dai ni har mamaki yake ban wallahi waima baki san wani abuba mum ?

Mum din ta kalleta tayi mata signal da ido ta daina zancen a gabana saita juya tana fadin barin dawo mum yanzu ina sauri sister mum ta hanaki zuwa ko ?

Dan murmushi nayi bayan fitan ta mun ta juyo tana fadin nasansu yaran banzane basu da kwabo sai kunje wajen taron nan su nemi su wullakantaki a can gara dai ki zauna gida kawai.

Mum nima ba zanje ba don ban ra,ayin wanan event din da zasuyi yau ai yanzu dai na fada mata taje can ta sanar dasu na hanaki duk wani program nasu da zasuyi.

Washegari yan katsina suka shigo kusan mota uku na mata bada maza ba wai wasu suna baya tafe ashe yan uwan inna ma sun shigo a ranan su da yan kauyen mahaifin mu baba.

Wanan kauyen da muka fara zama a cikinsa suma sunyo gaiya sunzo don sheda aure da za,aimin a lokacin suyi kokari sosai gaskiya yadda suka kashe lokacin su zuwa har kano wurin bukina din.

Saidai duk a gidan iyayyena suka sauka basu sauka a gidan daddy din ba don haka ko gidan mu basu huta da jama,a ba don an taru a can din ma.

Daddy da kansa ya sauke abinci a can duk dako mahaifina yayi nasa kokarin ya tanadi abinda zasuci har su koma amma duk da hakan saida daddy yayi nasa kokarin.

Washegaru mum ta tura akaje akai min jere duk da daddy yai muna komai amma kuma saida tayi nata na fannin uwa a waje an gyara gidan tson kowa ya dawo yana yaba kyawonsa da tsari.

Yayin da bangaren mummy sunje su tun saura sati daya buki sunyi nasu gyaran dakin wa diyansu acan garuruwan da za,a kaisu din .

Don sun fara tsegumi akan mum wai dama ai sunsan ba zata taba yimin wani abin kwarai a rayuwanta ba tunda bata da alheri bautar dani kawai tayi.

Balle ba zata kai min abin kwarai ba ai tunda tasan hafiz zan aura don kawai tana bakin ciki da hassada dashi yana dan mummy haka dai suke ta tseguminsu .

Sai gashi sunji cewa mum ta tura an gyara mun daki aka shiga lissafo irin abin arzikin da tayi min mummy sai baki ya mutu kuma ta koma fadin ai dole tayi min hakan.

Dama ta rikenine don ganin iyakar mummy din don ta nunawa duniya ita ba kowa bane san nan ai sun san komai duk abinda aka gani daddy ne ya bada kudi a boye akaimin shi son kawai ya farauta muna rai.

Niko nace ashe mummy tasan dan nata abin banzane ke nan tunda har take iya zaton daddy ya hada muna dacin hanci don a zauna dashi ko ?

Da yamma muna zaune ana hira gida ya cika saiga Dada ita ta saka min lale ta shammaceni banyi aune ba ta zuba min akafa har zuwa sawayena da hannayena tana guda.

Wani irin zabura nayi ina hawaye tare da furta ta faru ta kare ke nan na dai tabbata matar hafiz ke nan na fada a zuciyana na mike zuwa babdaki.

Kuka nayi sosai kafin nabawa kaina hakkuri na wanke nafito don kada mum ta gane cewa kuka naje nayi saboda nayi alkawarin ban sake yarda inyi kuka kuma kan auren.

Nan buki ya fara ga jama,a ko sai zuwa sukeyi daga garuruwa don su sheda kawai su nunawa iyayyena farin cikin ganin wanan lokacin kamar yadda yake a al,adance.

Kamar ko wani buki kuma ko wani gida aka hada bukin yayan daki biyu ake samun yan tsegumi da gulmace gulmace wanan ma namun hakan aka samu.

Hakan yafi faruwane kuma abangaren mummy din hakane ma a asirce mum taba da girki da za a dinga yo mata daga wani gida ana kawo mata nan gidan kawai saidai aga ana shigowa da manyan kuloli na abinci apart dinta.

Sai hakan kuma ya tsonewa mummy ido sai gasu har gaban Alh wai bata yarda da tsarin da mum ta dauko din ba nan daddy yake fadin baki yarda ba sai kije kiyi yadda tayi din mana kema.

Ni dai nasan Kubura bata tambayeni kudi wai zatayi girki ba haka kuma nima ban dauki kudi na taimaka mata tayi girkin nan ba ina duk abinda tayi tayine da sunan taimaka muna dai a cikin sha,anin nan .

Tunda dani dake keda bukin nan ba dole bane sai kubura tayi wani abin bajinta da har zai tsone maki ido idan kina da tunane mu tayi wa wanan karan ai a nan.

Duk da haka mummy bata fahinta ba don bata yarda ba kishi ya rufe mata idanu a lokacin sai cewa tayi dama ai bakinsu hadene gashi ita din dake cewa mum tana da rowa .

Itace irin halittan nan ne da komai sai sunci riba dashi kudin ba bata samu bane wajen miji bata dai iya fitarwa ne akashewa jama,a ta zata daddy zaicewa mum a hada a dinga kawowa ko wani part ga nata wautan.

Sai daren da za a daura aure hafiz din dasu yaya Addil daya shawo kansa suka iso garin cikin dare sosai bayan mum tayi ta korafin rashin zuwan nasu akan lokaci.

Tana cewa rashin zuwan matarsa da wuri yaci mata rai ace tana bukin kanwarsa amma ace wai ba matar Addil a wajen don tana yar rainin wayau.

Wanan yasa washegari da sukazo mum din taki tsayawa ta basu lokacinta tana nuna masu fushinta ga hakan da sukayi na basu kyauta mata ba son gaba su gyara.

Amma sai gashi itama Aishan wai tayi fushi don mum bata nuna tana da muhinmanci ba a wajen ta ga idon jama,a din haka ta sulale ta fice daga gidan ba tare da kowa ya sani ba.

Saida mum tace akirata tana kitchen shine ake fadin ai bata nan a zaton mun ta shiga wani part na gidan ne sai gashi ana fadin anga fita ai tabar gidan.

Ita kuma mum nata matsala ke nan daya fara bullo mata shine matar danta bata da mutunci balle kirki don sam bata da tarbiyan bin nagabanta uwar miji da take tankat uwarka ga me tunane amma ita ko gaban dan sai ta nemi ciwa nasa mutunci.

Don hakanema gaba daya gidan ba wani mai dogon shiri da ita baya ga gaisuwa da za a tsaya a danyi sama sama don gani take ta girmi wayewan kowa a gidan don haka babu sa,anta take daukankai

Sai dai ita a wajenta kuma gani takeyi kawai dai ba,a sontane don hakane bata nemi hanyan gyarawa ba sai iskanci da takeyiwa mutane tana kara bata kanta a zuciyan yan gidan mijin nata.

Don ko hakan datayi ba wanda baiji wanan labarin ba kowa na tir da halinta a cikin taron nace kinga bone kowa ya zageki Allah yasa mu gane gaskiya mu gyara ba sai ana son mu zamu kyautatawa uwar miji da yan uwan miji ba halinmu zai muna alkalanci a gidajen auren mu mata.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[2/28, 06:27] Maman K: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Duk wanan badakalan da akeyi iyayyena basuce uffan ba duk ko da zagi da cin mutuncin da mummy keyi kamar a gabansu take fadinsa don komai sunaji amma sun taushe zuciyarsu saboda zumunci.

Akwai sauran imanin zumuci a lokacin dan uwa na iya bugun gaba da dan uwashi ako wani lokaci ya yanke hukunci akansa ba tare daka daga kai kace don me akayi hakan ba.

Duk dadai har duniya ta nade akwai masu imanin gaskiya da biyayya bisa ga tsarin musulunci don sai ince duk yawancin al,adun malam bahaushe kadan ne yake tsarin al,ada duk koyine da addini bahaushe yake abinsa.

In banda yanzu da boko ya sauya wasu suke ganin tsarin na farko ba tsari bane akwai tauyewa acikinsa yasa karfin zumunci da bahaushe yake girmamawa ya rage a zukatan mutanen yanzu sosai bisa ga mutanen baya da suka kwanta dama.

Allah ubangiji ya jikansu da rahama ya gafarta masu albarkan kalman shahadan da suka rike a bakunansu Allahuma amin.

A kwana a tashi hasaran rayuwa inji malam bahaushe buki dai ya karato kowani bangare sai shiri akeyi inda hjy mum gwaggona uwar dakina itama ba,a barta a baya ba wajen shirya yarta da zata kai aure watau ni ke nan.

Don ko wani tsimi wani gunba wani hayakin jiki dana tsuguno da siracin irin na shuwa duk nashashi a wajen hjy mum don sai dare yayi kafa ya dauke zata tasani agaba da wa yanan abubuwan tun ina sha ina amai har ya fara zama min aciki saidai idan nasha zuciyana ya dinga tashi inyi ta barci.

Sai yanzu nake tuna abubuwan nan don tun ina karama muke shiga daji debo wasu ganyewa matan gidan mu na kauye wani lokacin muke hada masu kafin yan sari suzo daga birni suna saya.

Wanda sai na mahaifiyata ya kare kafin saura su samu shigar da nasu don ita tasam hadi don hakanema nima na koyi hadin ina taimaka mata wajen hada abubuwa.

Sai yanzu tunanen hadin yake dawo min arai naga ai nima nasan dame dame ake hadawa ya zama gumba ko hayaki ko gari da sai sauran haki irin na yar mai ganye .

Tabbas sudin ne don na tuna da dandanonsu hakan yasa na fara tuhumar wasu daga ciki sun fito hannun mahaifiyata ke nan.

Saboda nasu hadin na El,sutura daban ne dana saura ba irin hadin neman kudi bane kawai hadine na sahihi da masana tasirin ganye a jikin dan adam suke hadawa mata don amfaninsu.

Hadine mai inganci dake saukarwa mace da ni,ima da gyaran jiki ki koma abin sha,awa agun kowa duk wanda yasan asalin yar mai ganye yasan yadda maganinsu yake da kyau da tasiri agun manya da yara don ita yar mai ganyen asali bata tsaya iya gyaran mace ba kadai har yara da masu lalura tana taimakawa da magani cikin yardan ubangiji kuma a dace harma da maza wani lokacin suna dace idan sun samu yar asalin yar maiganyen na ainihi.

EL,SUTURA TANA SOKOTO YANZU HAKA ZAUNE GA DUK MAI BUKATAN MAGANIN TA NA AINIHI HAR GOBE AKWASHI KU GARZAYO KUSHA MAMAKI DA IKON ALLAH .

Saura kwana hudu bukine anty Nafisa ta turasasa min binta zuwa wajen gyaran jiki inda ta kaini wani shagon gyara na mata suka fara gyara min jiki tun daga kaina zuwa tafin kafana basu barshi a baya ba .

Don bayan dilka ga kitso ga kumshi ga kuma turaren jiki bayan wanda hjy mum ke banka min din itama ta dora nata akai don hakane duk inda nazo na tsaya zan bar wajen da kamshi.

Duk da ba fita nakeyi ba ina dakina ko dakin mum in kafa ya dauke kuma a falonmu .

Saidai hakan bai hana halimatu yawo da sunana wajen classmates din mu da sunan raba chewegun din buki tana tallana cewa auren hadi za,amin ai.

Mijin baisona amma ni sai rawan kai nakeyi dan naga dan maikudine tun yanzu na dara dagawa mutane kai shine ita tace bari tazo ta kawo masu IV don kar,a manta juna.

Wanan dalilin yasa Anty Nafisa daukana kowa bai sani ba gidan takaini wajen gyaran jiki don ta fahinci irin makircin da sukeyi suna son bambanta sha,anin da wani manufa.

Sai gashi suna ganin gyaran da akai min sai kuma ya koma tsone masu ido ni ina ta kaina su kuma suna hassada dani bansan dalilin wanan abin ba nasu akaina koda yake ba abin mamaki bane don mummyce uwarsu fa.

Hakama kawayen da halimatu ta gayato sai sunzo zasuga aiba gaskiya ta fadaba don yadda suke samuna cikin rashin dadin rai a lokacin zasu fita suna gulma nan dai Allah zai wankeni akan zargin su gane gaskiya a take.

Nida kaina na fadawa wayanda muke courses tare yanzu gaskiyan abindake faru dani sun kuma tausaya min jin zanyi aure da fara karatun mu ta hanyansu suka kara walwalewa kawayen namu gaskiyan al,amarin sabanin abinda halimatu ta fada masu kaina.

Ban taba ganin mahaifina ya shigo wurin hjy mum ba harsu kebe su dade suna magana sai a yau da ya saura kwana biyu daurin aurena da yaya Hafiz ba alamansa nasan wanan maganan kodai wani daya shafi rayuwanane ya kawo baba wajen hjy mum din har suka dade irin haka suna tataunawa a falonta dashi.

Daddy ko ance kallo daya zakai mai kagane hankalinsa ba a kwance yake ba don ance ya fada sosai don tashin hankalin abinda dansa keson yimasa na bashi kunya ga yan uwa da mutanen arzikinsa ga kowa sunan hafiz ya sani a cikin yayansa don haka sunajin auren Hafiz ne ai zakiji mutum yace insha Allahu muna nan zuwa damu za a daura auren.

Wanan ganin da nayiwa baba da mum ya kara daga min hankali sosai da har na kasa fitowa washegari ina kwance a daki sai da mum ta leko tana fadin wai ke lafiya kin shige daki tun safe baki leko ba.

Zaune nakena mike kafa saman gado dake nuna alaman lafyata kalau illa da dumuwa kawai ke damun zuciyana lokacin na dan dago da zuman kallonta saiga hawaye ta ko ina idona sunyi hulu hulu saboda kuka da naci.

Kai haba mama yanzu kuma don Allah damuwa ko kukan nan meye kikeyi hakane don kawai ki tonawa kanki damu asiri mama.

Ya kamata ace kinsawa zuciyanki dangana game da zancen nan don kin gani a zahiri tun ainda aka fito har kawo yau din nan babu alaman canji ko gezau ga Alh gareku.

Aiya kamata ki dauki hakan a matsayin kaddara ki yarda ki amince da hakan kaddarakice mama yin biyaya zaisa kiga Allah ya sakawa rayuwanki ba zaki taba tabewa aduniyan nan ba insha Allahu.

A hankali na iya dago kai na kalli mum din ina fadin mum badon wanan nake kuka ba ni ko waye daddy zai ban ya bani amma ba ya hafiz mashayi dangiya da,,,,

Haba mama kul na sake jin wanan kalamin a bakinki kin taba jin inda hannunka ya rube ka yanke kayar wanan dalilin na cikin nacin auren ku da Alh keyi don yasan irin tarbiyanki yana fatan ta dalilinki hafiz ya shiryu nan gaba.

Mum ta ya ni zan iya shiryashi bayan Allah daya haliceshi yakewa sabo ga kuma daddy da mummy aisu ya kamata ace sun gyara abinsu bani ba ni har wani hikima nake dashi da zan gyarasa.

Addinin ki da tarbiyanki mama dasu zakiyi amfani ki gyara dan uwanki dashi ke dai kawai banda garaje kinsan halin hafiz sai kin bisa a sannu.

Ba kuma ance da zuwanki ki fara masa zancen shaye shayenshi ba a,a cikin hikima da basira da saka wa,azi da kuma addua idan da rabo sai kiga kinyi babban jahadi kin kwatoshi daga wanan mumunan dabi,an.

Ki tashi maza ki wanka ki gyara jikinki kamar kowa don gida ya fara cika da baki ko tun yanzu don yan katsina na nan sun fara isowa kuma suna tambayan ina kike ki kuma adana duk wani abinda kikeso cikin wardrobe dinki ki kulle ki miko min key din na rike a hannuna tana kaiwa nan ta juya ta fita daga dakin.

Jin hakan dole natashi nashiga bayi nayi wanka na fito na samu wani yadin material da akaiwa dogon riga na saka a jikina.

Mum ce ta kwala min kira daga dakinta na amsa nashiga take fadin in dauki abinci inci itama shi takeci a lokacin ban jaba na dan diba a plate nan na zauna ina tsakura saiga anty Nafisa ta fado dakin.

Lah ke kina nan zaune a daki ba zaki je wajen event din naku ba kai na dukar kasa kafin nayi magana mum tace bamu tsara wani event ba don walima kawai.

zamuyi a bangaren mu.

Haba mum ina tare da yan uwa zatayi komai ko ?

No Nafisa kinsan halin yaran nan don Allah barshi a yadda muka tsara zamuyi walima hade dana saukarta shike nan itama idan mijinta nason suyi event idan ya iso saisu tsara abinsu amma barsu can suyi abinsu don Allah mun ta kakabe zancen.

Ta danyi shiru kafin ta juya tana fadin Allah kyauta mum don dai kinkine amma ina wajen ai waya isa yai mata wani abin bayan gani wajen a dai bar zancen har mijinta ya iso garin.

Mum kina ganin wai hafiz zaizo garin nan ko bakiji irin kwasan rikicin da sukeyi da daddy bane tun shekarajiya kan zance guda.

Ban tsamani zai shigo don ko mum yau naji ta kirashi da safe tayi masa kaca kaca ko zaiji yazo ban sani ba dai ni har mamaki yake ban wallahi waima baki san wani abuba mum ?

Mum din ta kalleta tayi mata signal da ido ta daina zancen a gabana saita juya tana fadin barin dawo mum yanzu ina sauri sister mum ta hanaki zuwa ko ?

Dan murmushi nayi bayan fitan ta mun ta juyo tana fadin nasansu yaran banzane basu da kwabo sai kunje wajen taron nan su nemi su wullakantaki a can gara dai ki zauna gida kawai.

Mum nima ba zanje ba don ban ra,ayin wanan event din da zasuyi yau ai yanzu dai na fada mata taje can ta sanar dasu na hanaki duk wani program nasu da zasuyi.

Washegari yan katsina suka shigo kusan mota uku na mata bada maza ba wai wasu suna baya tafe ashe yan uwan inna ma sun shigo a ranan su da yan kauyen mahaifin mu baba.

Wanan kauyen da muka fara zama a cikinsa suma sunyo gaiya sunzo don sheda aure da za,aimin a lokacin suyi kokari sosai gaskiya yadda suka kashe lokacin su zuwa har kano wurin bukina din.

Saidai duk a gidan iyayyena suka sauka basu sauka a gidan daddy din ba don haka ko gidan mu basu huta da jama,a ba don an taru a can din ma.

Daddy da kansa ya sauke abinci a can duk dako mahaifina yayi nasa kokarin ya tanadi abinda zasuci har su koma amma duk da hakan saida daddy yayi nasa kokarin.

Washegaru mum ta tura akaje akai min jere duk da daddy yai muna komai amma kuma saida tayi nata na fannin uwa a waje an gyara gidan tson kowa ya dawo yana yaba kyawonsa da tsari.

Yayin da bangaren mummy sunje su tun saura sati daya buki sunyi nasu gyaran dakin wa diyansu acan garuruwan da za,a kaisu din .

Don sun fara tsegumi akan mum wai dama ai sunsan ba zata taba yimin wani abin kwarai a rayuwanta ba tunda bata da alheri bautar dani kawai tayi.

Balle ba zata kai min abin kwarai ba ai tunda tasan hafiz zan aura don kawai tana bakin ciki da hassada dashi yana dan mummy haka dai suke ta tseguminsu .

Sai gashi sunji cewa mum ta tura an gyara mun daki aka shiga lissafo irin abin arzikin da tayi min mummy sai baki ya mutu kuma ta koma fadin ai dole tayi min hakan.

Dama ta rikenine don ganin iyakar mummy din don ta nunawa duniya ita ba kowa bane san nan ai sun san komai duk abinda aka gani daddy ne ya bada kudi a boye akaimin shi son kawai ya farauta muna rai.

Niko nace ashe mummy tasan dan nata abin banzane ke nan tunda har take iya zaton daddy ya hada muna dacin hanci don a zauna dashi ko ?

Da yamma muna zaune ana hira gida ya cika saiga Dada ita ta saka min lale ta shammaceni banyi aune ba ta zuba min akafa har zuwa sawayena da hannayena tana guda.

Wani irin zabura nayi ina hawaye tare da furta ta faru ta kare ke nan na dai tabbata matar hafiz ke nan na fada a zuciyana na mike zuwa babdaki.

Kuka nayi sosai kafin nabawa kaina hakkuri na wanke nafito don kada mum ta gane cewa kuka naje nayi saboda nayi alkawarin ban sake yarda inyi kuka kuma kan auren.

Nan buki ya fara ga jama,a ko sai zuwa sukeyi daga garuruwa don su sheda kawai su nunawa iyayyena farin cikin ganin wanan lokacin kamar yadda yake a al,adance.

Kamar ko wani buki kuma ko wani gida aka hada bukin yayan daki biyu ake samun yan tsegumi da gulmace gulmace wanan ma namun hakan aka samu.

Hakan yafi faruwane kuma abangaren mummy din hakane ma a asirce mum taba da girki da za a dinga yo mata daga wani gida ana kawo mata nan gidan kawai saidai aga ana shigowa da manyan kuloli na abinci apart dinta.

Sai hakan kuma ya tsonewa mummy ido sai gasu har gaban Alh wai bata yarda da tsarin da mum ta dauko din ba nan daddy yake fadin baki yarda ba sai kije kiyi yadda tayi din mana kema.

Ni dai nasan Kubura bata tambayeni kudi wai zatayi girki ba haka kuma nima ban dauki kudi na taimaka mata tayi girkin nan ba ina duk abinda tayi tayine da sunan taimaka muna dai a cikin sha,anin nan .

Tunda dani dake keda bukin nan ba dole bane sai kubura tayi wani abin bajinta da har zai tsone maki ido idan kina da tunane mu tayi wa wanan karan ai a nan.

Duk da haka mummy bata fahinta ba don bata yarda ba kishi ya rufe mata idanu a lokacin sai cewa tayi dama ai bakinsu hadene gashi ita din dake cewa mum tana da rowa .

Itace irin halittan nan ne da komai sai sunci riba dashi kudin ba bata samu bane wajen miji bata dai iya fitarwa ne akashewa jama,a ta zata daddy zaicewa mum a hada a dinga kawowa ko wani part ga nata wautan.

Sai daren da za a daura aure hafiz din dasu yaya Addil daya shawo kansa suka iso garin cikin dare sosai bayan mum tayi ta korafin rashin zuwan nasu akan lokaci.

Tana cewa rashin zuwan matarsa da wuri yaci mata rai ace tana bukin kanwarsa amma ace wai ba matar Addil a wajen don tana yar rainin wayau.

Wanan yasa washegari da sukazo mum din taki tsayawa ta basu lokacinta tana nuna masu fushinta ga hakan da sukayi na basu kyauta mata ba son gaba su gyara.

Amma sai gashi itama Aishan wai tayi fushi don mum bata nuna tana da muhinmanci ba a wajen ta ga idon jama,a din haka ta sulale ta fice daga gidan ba tare da kowa ya sani ba.

Saida mum tace akirata tana kitchen shine ake fadin ai bata nan a zaton mun ta shiga wani part na gidan ne sai gashi ana fadin anga fita ai tabar gidan.

Ita kuma mum nata matsala ke nan daya fara bullo mata shine matar danta bata da mutunci balle kirki don sam bata da tarbiyan bin nagabanta uwar miji da take tankat uwarka ga me tunane amma ita ko gaban dan sai ta nemi ciwa nasa mutunci.

Don hakanema gaba daya gidan ba wani mai dogon shiri da ita baya ga gaisuwa da za a tsaya a danyi sama sama don gani take ta girmi wayewan kowa a gidan don haka babu sa,anta take daukankai

Sai dai ita a wajenta kuma gani takeyi kawai dai ba,a sontane don hakane bata nemi hanyan gyarawa ba sai iskanci da takeyiwa mutane tana kara bata kanta a zuciyan yan gidan mijin nata.

Don ko hakan datayi ba wanda baiji wanan labarin ba kowa na tir da halinta a cikin taron nace kinga bone kowa ya zageki Allah yasa mu gane gaskiya mu gyara ba sai ana son mu zamu kyautatawa uwar miji da yan uwan miji ba halinmu zai muna alkalanci a gidajen auren mu mata.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[2/29, 06:30] Maman K: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

27

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Rana bata karya saidai uwar diya tayi kunya to Allah ya gyara kamar kullum wanan uwar diyar batai kunya ba kamar yadda kow keyin abinsa cikin rufin asiri haka Allah ya rufa wanan asirin don an daura aure kamar yadda kowani aure aka saba daurashi lafiya an kuma samu jama,an da suka sheda hakan bila,adadin wajen taron.

Karfe hudu bayan daurin aure masu waliman da hjy mum ta kira sukazo suka cika unguwa da lasifika suka hau sharfi akan aure da biyayya ga iyayye suna kuma kwatance da irin kokarin daddy wajen tada zumunci da zamanin nan yake neman gagara a tsakanin yan uwa ko makwabta.

Anyi an watse lafiya an raba gifts wani mai hoton amare mu uku wani kuma hotona da ya hafiz ne a manne duk wanan kokarin mum ne datayi na aurar da yarta.

Sai washegari za,a tafi da mairo da Asiya garuruwan mazansu saini dake gari da za,a aje gaba da unguwarmuce za,a akai ranan.

Duk dako angon ya fada masu cewa komawa zaiyi washegari don matsa mashi da daddy yayine ya dauko pass yazo halartan bukin ba don wani abu ba can.

Duk da jin kalaminsa hakan baisa daddy ya girgiza ba ga abinda yayi niyar yi haka mahaifina ni dai sai ince tu ranan da yazo wajen mum sukayi magana ban kara ganinsa ba duk ko da kaini gidansu da mum tasa akayi ana gobe za a daura muna aure a can na wuni cikin yan uwana tare dasu.

Sai yamma akaje aka daukoni amma banga baba ba ko a idona haka mahaifiyata akwai damuwa sosai a fuskanta amma saboda kawaici irin nasu batace dani uffan ba har lokacin dana barsu din.

Ana gama walima muna zaune saiga Dada ta shigo part din mum tana fadin ina amaryan hafiz din ina jin hakan na bata rai take na hade fuskana .

Take fadin ki taso iyayyenki na jiranki waje iya abinda ta fada min ke nan dole na tashi nabi bayan ta bayan na nemo mum na fada mata.

Mukaje da Samira don tare muke sai dawowa samira tayi ita kadai tana fada masu cewa su daddy sun wuce dani ai sun tafi su kaini gidan mijina.

Nan take gida ya rude da mamaki mum kasa hakkuri tayi daidai motar su ya tsaya saiga kiranta tana tambaya hankali tashe da Alh wai kunje kai mama dakinta yace gamu har mun iso gidan ai ya kashe waya.

Su daddy Enugu suna gaba su biyu daddy kano yana rike dani har zuwa cikin gidan yana saman bakinshi da nema muna kariya daga sheda da sauran abin ki ga musulmi.

Gabana yayi wani irin faduwa a daidai lokacin da muryan hafiz ya daki kunnena ashe yana gidan yana sana,arshi kiran da daddy yayi mai yasashi tashi ya feshe gidan da air fresher gidan ya dauki kamshi lokaci guda.

Nasiha sukai muna sosai saidai na daddyn mu nasihan shi kamar wanka da jurwaye yayi muna don nasihace ta gugar zana garemu daga shi har ni kan zaman takewa.

Har kofa ya rakasu bai dawo ba saida yaga motarsu ya daga daga wajen ya juyo zuwa ciki ina nan rakube a inda daddy ya barni zaune sai tsukinshi naji hakan ya sanar dani shigowanshi daga rakiyan da yai masu din.

Banza ukuba yanzu kika shigesa duk wanan barnan miyau bakin da daddy keyi akanki zai kare bani ba don ki sani daga yau kin shiga tashin hankalin rayuwa ke nan a rayuwanki zakice nace.

Tunda har kukai sanadin mai dani bazawari bazanyi ni kadai ba koda ace maza suna zawarci saidai muyishi tare dake saina bar maki mugun tabon da gobe ko ance maku ga kwadayi dake da iyayyen ki makwadaita zakuce yana wari.

Ke dasu sai kunce,,,,,,

Knocking din kofan gidan da akeyi ya hanashi karasa abinda zai fada yaja wani ubab tsuki yana fadin kawai kawai mutum yana zaman zamansa a dauko masa masifa a sarkafa mashi a habasa shakat da rayuwansa wanan wani irin masifane wai a hana mutum hutawahasale.

Yana bude kofan a hasale anty Nafisace ke fadin dama nasan kana ciki tunda naga ba,a bude da wuri ba ko har ka fara shan angoncinne kai ni basu Dada waje su shigo don Allah ka wani rdakin kofa kamar baka son mu shigo yan kawo amaryane sukazo.

Ido ya waro waje yana fadin wace amaryan ke nan kuma ya tambaya cikin mamaki.

Dada tace naka mana ko an kawo maka itace dama tana zolayanshi ido ya waro waje yana kallon kofan dakin daya barni a zaune cikin razana .

Gudan da yajine ya kara firgitashi yana fadin wai da gaske Nafisa ita wacan na zaune a dakin fa ita din wacece Dada ta amsa data karfece wanan kuma amaryan danko muka kawo maka yana bin samira dake rufe da kallon mamaki.

Kaje dakinka don Allah kada mata su sameka wajen nan su dauka koka fara bita zauzaune tun yanzu nafisa ta rada masa a kunnensa.

Wani haushi da takaici ya kara rufesa wajen wai ana nufin mata biyu daddy ya aura masa lokaci guda koko dayan daya saninece data zamo mashi alkakai a yanzu ?

Nan yaji tururuwan jama,a suna shigowa da guda da ihu abinda yayi hating duk mata sun ruda gidan ga koke koken yaransu yana tashi duk da ya rufe dakin amma yana iya jiyo muryansu a nan din.

Sai bayan wani lokaci ya daina jin muryoyinsu tare da jin tashin motocinsu suna barin gidan duk da hakan bai fito ba sai sha daya da wani abu yazo ya rufe gidan ga baki daya yana jan tsoki.

Yar gatan amarya yar lele itace angonne ke zuwa sayen bakinta don nikan bayan wucewan yan uwa mikewa nayi na nufi kofa na saka key na dawo na rage kayan jikina na shiga bandakin na dan watsa ruwa tare da dauro alwala.

Na dade zaune ina addua kafin na mike na hau gadon saboda zuwa lokacin zuciyana ya dake ya bushe ina jin kaina kamar bani bace kamar ban iya kai safe lokacin.

Allah da ikonsa ina gama addua na kwanta bansan lokacin da barci ya daukeni ba sai falkowa nayi na ganni kwance cikin hasake sai kuma lokacin na tuna da inda nake kwance din.

Zabura nayi ina salati nakai duba ga kofa na tuna nayi masa key kafin in kwanta na samu na mike da kyar na koma bandakin na sake dauro alwala nazo na sake tayar da sallah.

Hannu sama ina kuka nake rokon Allah daya hausheni kan duk wani mugun nufin da hafiz kedashi a kaina na zama matanshi danayi yanzu din.

In nayi adda in tsaya inyi kuka in kara kuma daga hannu ina rokon Allah in kuma koma tunanen duniya a haka wani barcin yayi gaba dani ba tare dana sani har gari ya waye sosai kafin na zabura na mike ina sallati na sake shigewa bandakin na dauro alwala.

Haka na koma kamar zautata a ranan ni kadai a daki gashi ba motsinkowa a gidan koshi azzalumin banji motsinsa ba na kuma kasa bude dakina ina jin tsoro don bansan da wace zaizo min ba lokacin kuma .

Ga ba waya a hannuna wayata na dakin mum saman akwati na aje lokacin da zan saka abayan zuwa wajen walima tun lokacin ban kara bita kanta ba wayan samirace a hannuna kuma karama ita nake ta jagula tunda nazo.

Sai wajajen karfe daya naji anata dukan kofa hakan yasa na daure na bude wata gwaggon mune yar mum ce ita take fadin tun dazun ake zuwa ana fadin kofa a rufe.

Uwarki nacan ta rude dole ta taso damu muzo mu dubaki ko wani abune ya sameki gashi yanzun muke jin wai mijin naki ya koma tunda safe inda yake aikinsa.

Wani dadi naji duk da ban cikin yanayi mai dadi a lokacin amma jin hakan yasa zuciyana sanyi lokaci guda nace Allah sarki mum nasan ta damu sosai ga wayana na barshi a dakinta tun jiya din.

Gwaggo Rahinatu tace ai mun gani tun jiyan ta dauka ta boye maki shine ga abinci can a falo tace zuwa yamma zata lekoki ta ganki ai yanzu ma munzo duba ko lafiyane anata zuwa kofanki yana rufe.

Basu tsaya suke fada min ai an wuce da amare tun safe yanzu ai kila sunkai don gobe zasu dawo masu kai amaren nikan duk sama sama nake jinsu.

Saida suka wuce naga abincin ganin kayan abincin yasa nagane daga hjy mum suka fito ba part din mummy da yanzu ita keda alhakin ban abunci don ina karkashin danta da zama yanzu.

Sai lokacin na samu daga kai na kalli tsarin gidan gidane mai kyau nagani na fada don ba inda wanan gidan yake da maraina gaskiya a wajena nikan.

Abincin na bude na dan tsankwara nace bakina ba dadi don haka banci wani abin kirki ba na aje cokalin na zauna nan ina tubane hakan yafi mun na fada a raina.

Da zaman dan cin mutuncin da baisan daraja iyayyenmu ai gara yayi gaba hankalina yafi kwanciya da hakan da zamansa don bansan iya abinda zai iya min ba idan yana nan.

Allahne ya karbi addua na dana kwanayi a dakin ya iza min shi gaba na fada a zuciya shigowan su Samira ya kara dauke min hankali nan suke min hiran abubuwan daya faru bayan bari na gida din.

A bakinsu nake jin wai yace next week zai dawo ba dadewa zaiyi ba dama bai samu hutu ba yadai zone kawai ayi buki dashi ya koma.

Ni dai ban tsuka ba shigowan su mum dina ya dauke min hankali saidai mum din a yarda na ganta ranan duk ta zabge tarame kamar wace tayi ciwo a dare daya.

Abubuwa sin ma rayuwanta yawa don bata saba hakan ba sai gashi da zaizo mata yazo mata da tashin hankali kowa najin abinda ke damunsa har daddy uban gaiyan.

Sunyi min nasiha sosai wanda duk cikin nasihan hakkuri da biyayyan aure shine kan gaba duk wani kalami na kowa da zai fada shine inyi hakkuri wata rana sai labari insha Allahu.

Ta ban wayana tare da fadin duk da nasan baki da kawayen banza amma zan kara ja maki kunne don Allah ki kula akwai hakkin aure akanki yanzu mamana kada ki yarda ki canza rayuwan ki nan gaba don Allah.

Da kuka muka rabu yan uwa suna bata hakkuri take fada min su samira zasu kwana tare dani in Dada ta dawo kai amarya daga bauchi zatazo ta zauna dani a gidan.

Muka rabu cikin rashin dadin rai ranan tare dasu samira muka kwana wanda tun karfe takwas da wani abu na kwanta barci saboda barcin gajiya dake idona.

Washegari bamu jira an kawo muna breakfast daga gida ba mu muka girka abinda mukeso tunda akwai komai da aka kawo min nagara na dauka ya Addil zasu ratso kafin su tafi .

Sai gashi samira na fada min ai sun wuce tun safe yazo ya sallami mum cewa yana da aiki zai koma a raina nace kowani al,lazi da nasa amanun shi kuma yaya matarsace nasa matsalan rayuwan.

Don nasan itace zata matsa mashi su koma a ranan bawai son ransa bane zaisa ya koma dama shi ya Nasir bai samu zuwa ba yana wajen course din aikin daya samu na world bank.

Ranan ma dasu Samira din muka wuni muka kwana gashi washegri zasuyi sammako su koma don su Dada sai dare sosai suka dawo kuma bata da lafiya koda suka iso.

Haka washegari tunda safe aka turo su samira suka fit suka barni ni kadai a gidan kamar manya sai gidan ya dan fara ban tsoro ganin ni kadaice a ciki.

Sai maigadi dake can ta wajen gidan yana aikin gadinsa ba ruwana dashi kuma haka na kwana don mum data kirani tana sheda min Dada jiki yaki har ssibiti aka kaita da sunyi shawara a turo min halimatu ko ya nagani nace su barta zan iya kwana ai saboda karfin hali.

Tun daga wanan rana na kama kwana ni daya a gidan tsoron haka kuma ya fice min a raina zansha barcina da safe tunda muna hutun boko a lokacin.

Saina gaji zan tashi indanyi abinda zanci daga nan kuma sai dare zan dan nemi abin da zanci in kwanta sai hankan ya fara kwantar min da hankali.

Kwatsam saiga mummy da kawayenta wani safiya wai sunzo ganin amarya don basu samu zuwa ba saboda gajiyan buki suna wani dan yatsune yatsune da mede baki kamar sunga kashi.

A cikin ladabi na taresu na kawo masu ruwa don shi ke gareni gidan lokacin to ba maigidan balle ya sawo min wani abu ko ruwan nice naba maigadi kudi ya sayo min bag biyar na ruwan don masu zuwa ganin amarya duk daba wasu jama,a ke zuwa ba sai in wuni ma wani bai shigo gidan ba ranan.

Yo ga tsiya mune zaki tara da ruwan leda ko haka uwar naki kikaga tana taron baki inda kika baro ?

Koda yake ba mamaki hudubar da tayi maki ke nan kike gwadawa a yanzu ai in ba rashin tarbiya ba munyi maki kama da masu shan ruwan yaku bayine a nan.

Sai naji dayan matar tace ki barta muko takawo ba zamu shaba ai ruwa na gida mun bari ke dai yarinya dauke ruwanki a nan dama mu ganin gidan dan mu mukazo muyi ba wani abu ba.

A take idona ya kawo kwalla dakyar na iy furta kuyi hakkuri mummy shi kadai nake dashi a gidan nan bansan zakuzo ba danayi maku tanadi ai.

Lah yar nan ke kuma da sherin da kikazo ke nan batawa dan mu suna kan bai kula dake kome ?

Rudewa nayi lokaci guda ina basu hakkuri daba haka nake nufi ba iya gaskiyata na fada amma suyi hakkuri don Allah sai naji mummy din taja wani uban tsuki ta mike tana fadin.

Kunga irin abinda nake fada maku ko dama nasan yarinyar nan ba karamin makirci aka kulla mata ba da zatazo tayiwa mutane gashi ko tun ba,aje ko ina ba har ta fara.

Don Allah ku tashi muje da wanan abin haushin da muke gani a,a hjy malka ba,a hakana yanzu me yarinyar nan tayi kuma wata daga cikinsu ta fada .

Ku tashi muje don Allah da wanan bakin takaicin da muke gani a nan din dama abinda Alh ke so ke nan inga bakin ciki ya dauko wanan yar tsiyar ya mannawa hafiz don bakin ciki ya kasheni gashi kuwa .

Ai hafiz din zai dawo koshi yaji wanan rainin wayau da kikai muna ba zai kyale ba ai mune zaki wani tara da ruwan leda kamar kinga gayyan yan kauye.

Da kuka na kira mum ina fada mata ashe lokacin suna tare dasu Dada har da anty Nafisa hakkuri mum din ta ban tace wanan shine auren ai mama.

Mun fada maki sai kinyi hakkuri ina jin muryan anty Nafisa tana tambaya meya ya faru mum din tace ba komai ta dai ban magana muka kashe waya .

Halan mummy ko don naji suna waya dasu hjy Ramatu yau zasuje gidan suga gida na mantane wallahi in kira ta in fada mata zuwansu din nan mum ta labarta masu abunda ya faru tsakanin mu.

Anty nafisa tace sai tayiwa mummy din magana hakan nan dai sukace ta barta dama sai an samu haka ai tsakanin mu kafin a shirya take fadin don me mummy zataje gidan yarinya suci mata mutunci.

Toke Nafisa aiyin maganan naki zai kara rura wutan abin tsakaninsu kawai dai kije kikaga mama din ki bata magana in ma wani abune dole ta kyale akan cewa zatayiwa mummy din magana da tayi niyar yi da farko.

Ita ko mummy hafiz din ta kira inda take shiga ba nan take fita ba ta kwashi karya da gaskiya ta fada mashi ya hau yana batsewa yana fadin i can't mummy ba zan iya zama da wanan yarinyar ba gaskiya.

Kece wai har yarinyar nan zatayiwa wullakanci tace ba dole tayi min ba tunda tana ganin Alh ya daure mata gindi zama da kai dolene ko bamu so ai dole tai muna haka taga gidan mike kafa a dole.

Wani shu,umin murmushi yayi kafin yace a ina fa mummy kawai ta bari inzo in sameta gida zata raina kanta wallahi mutane kamar mayu duk wanan bai isheta ba sai ta gwadawa mutane ita yar dajine ko zanzo zanyi maganin yar iska ai.

Hutun mu har ya kare na sati uku don hakane ranan na bugawa daddy waya ina sheda mashi ya danyi shiru kafin yace dani to uwata ba zan tauyeki ba a gida in hanaki zuwa abinda zai fisheki ki shirya kawai ki koma school din ki kici gaba da karatun ki tunda shi haka yaga yafi mai.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[3/2, 21:07] Aishatu Aliyu Musa😀: [3/1, 07:51] +234 706 511 1949: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

28

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Zaune take a falon tana katatun littafin da take kai a Islamiyansu yayi sallama ya shigo falon nata ta dago daga karatun tana amsa mashi.

Kallo daya tayi mai ta fahinci akwai matsala koda bai fadi ba tasan akwai matsala a wani bangare hakan yasa ta rufe littafin da take duba din ta fuskanceshi.

Zaune yakai har tsawon wani dan lokaci kafin ya dago yace zancen hafiz ne dai yake damuna don ban fahinci me yake nufi da yar mutanen dake gidanshi zaune ba da muka tauye.

Dazun ina shago ta bugo min tana fada min cewa hutunsu ya kare tana son ta koma karatun ta watau hakan ke nan yana nufin bai waya da ita tun tafiyansa ?

Dan murmushi mum ta sake a fuskanta kafin tace ai kaima ka sani Alh ban tsamanin cewa hafiz nada number mama a wayarshi.

Kuma hafiz bai yarda ya karbi auren mama ba kamar yadda kake zaton ka shawo kansa daga baya har ya yarda ya amince nina sani saidai sanin baida amfani a gareni .

Tunda banda power din da zan dauki mataki alokacin da nasan haka din wayar yarinyar nan samira dake hannun mama din a cikinsa mukaga irin yankar kaunar da yai mata ranan da kuka kaita kuka fita.

Mikewa ta tashi tayi ta dauko wayanta data tura ta kunna mashi yayi shiru yana sauraren rashin mutuncin da yake shuka min a lokacin har lokacin da aka fara nocking kofa ya fita da dan hiran mu dasu Anty da suka shigo take fadin har yanzu kukan rabuwa da mum nakeyi ne ?

Nisawa daddy yayi kafin ya dago kai ya kallo mum da idanuwansa da sukai ja jajir dasu yace lalai yaron nan yakai dan banza yana ganin banda sauran amfani a garesa yanzu ko ?

Tunda nagama masa wahala ya girma yana ganin yanzu kafansa shi sun kama kasa sakaiyan da zai mun ke nan kafin ta kiraka ni ta fara kira ai mum ta katse mashi magana don luran da tayi ya fara fita hankalinshi lokacin.

Cikin hikima ta fara canza zancen da fadin tana kirana ta fada min wai tana jin tsoron fadama shine nace dole saika sani ai wanan yasa ta kiraka.

Alhamdullahi ai tunda ita yarinyar bata bijire muna ba har yanzu tasan a karkashin iyayye take tana kuma biyayya ka kyaleshi kawai shida kansa zaizo ya gane cewa yayi kuskure abinda yakeyi a yanzu.

Yin shirun ka shi zaidaga masu hankali zasu shiga tashin hankali don basu san me shirun ka yake nufi dasu ba amma idan kai magana abinda suke nema ke nan dama rayuka sukai ga baci a yanzu ka kyalesu kawai ka saka masu ido zaifi.

Illa iyaka ita mama mu saka ido akan al,amuranta a bata kula yadda ya dace ta yadda damuwan hakan bazai dameta ba ni shawarana ke nan .

Ya shafo kai yana fadin neman maganane nina sani kuma da hadin bakin uwarsa yake hakan duk abinda hafiz keyi malka tana da labari don hakan shawaran ki ya kawo min mafita a cikin zancen nan yanzu ya mike ya fito daga dakin nata .

Ranan monday da safe bayan na shirya naji horn direban dake kaimu school ne yazo daukata shiya kaini makaranta a ranan da aka tashi kuma yazo ya daukeni .

Anty nafisa bata san da cewa nashigo ba don bamu hadu ba ban kuma nemeta ba don banba office dinta ba har na dawo gida don a yanzu ko waya bamayi da ita tunda aka kawoni gidan dan uwanta halakar mu ya danyi rauni tsakanin mu.

Bansan dalilin hakan ba amma tun lokacin buki ta fito da wasu abubuwa gareni mum tace a shareta kawai nikan badon mum ba gaskiya da bansan ya rayuwana zai kasance ba a cikinsu.

Hankalina kwance nake karatuna ban sakawa zuciyana komai ba inci mai kyau insha maikyau ba abinda ya dameni saboda kurciya har mantawa nake da nayi aure a lokacin don wauta.

Sai wata ranane malam isah ya daukoni zamu dawo gida muka hade da ita a daidai get tabi motan da kallo don sanin motar gidansuce wanan .

Sai lokacin ta ganni ciki zaune a baya malam Isah yana jana zai mayar dani gida mamakine ya rufeta a lokacin tabimu da kallo har muka bace mata.

Malam isah din ke fadin ga hjy Nafisa can ko mu tsaya ne nace a,a mu wuce kawai illa iyaka ya danyi mata horn ta mayar masa itama muka tafi.

Mamaki tayi sosai har takai inda zata kafin ta dauki waya ta kira mummy tana tambaya dama ashe yarinyat nan tana zuwa makarantane mummy yanzu naga malam isah ya daukota zai mayar da ita gida.

Wace yarinya ke nan mummy ta sake tambayanta tace Zeey mana ta nan gidan matar hafiz ta fada kai tsaye sai uwar tace kika ganta ina tace school mana mummy na dauka aitamooiu n dainane yanzu don auren nan.

Kima daina zancen nan don Allah bari nakira hafiz din inji sai yar ta katseta da fadin to meye mummy idan taje school tunda dama tana karatunta ba sai a barta tayi ta zuwa ba.

Wai meyasa ke baki gane abinda ake nufine baby wanan fa anyi hakanne da wani manufa sai yanzu nake gane nufin dan iskan yaron nan me dadin bakin tsiya da har ya bada shawara kan taje karatu zaifi.

Watau ita tayi karatu su mairo ko suna gida zaune wai suna aure ba damuwansu bane su kinga abinda nake sha fada maki ke nan baby amma kin kasa fahintana dake ke nan suke son jayayya a gidan nan tunda hjy kubrah bata da diya mace sai wanan yarinyar.

Haba mummy ni kuma Zainab fa har yaushe zainab zata iya kaini balle su tsaya kwatantawa dani don Allah sai dai idan suna da wata manufa dai ta daban akan karatun nata dai.

Shiko hafiz din data kirashi bai dauki waya a lokacin ba sai data masa da dare ya dauki wayan suka gaisa ta fara fadin kai ka umurci yarinyar nan da tafita zuwa school ?

Wace yarinya ke nan mum ya tambaya tace matarka mana zeey dazun baby ke fada min ta ganta malam isah driver ya daukota daga makaranta.

Mummy akan zancen yarinyar nan kika kirani don Allah kibar kirana kanta mummy don banson ai min zancen wanan yar iska don nabarwa daddy ita shida ya matsa sai anyi auren nan to anyi din ban bashi kunya ba sai su zauna da ita din mugani.

Wai dama har yanzu tana gidan a matsayinane kota koma gida tace kai hafiz ka natsu ka saurareni kaji me zan fada maka akanta.

Don na rarasheka ka yarda ka aureta hakan ba yana nufin ka fita zancenta yadda kayi din nan gaba daya bane don akan zancen nan na tabbatar da Alh zai iya saba muna gaba dayan mu daku.

Koma yayane akala ka dan kula da ita a matsayin matarka kana dan zuwa baka share haka ba har ana neman kwasan wata baka leko ba me hakan da kayi yake nufi ke nan ?

Gaskiya mummy i can't ban taba jin wani feeling akan yarinyar nan ba kwata kwata wallahi mum banko son in ganta a rayuwana wallahi kai kadakata da wanan shirmen ka saurareni kaji me zan fada ma.

Nan dai ta koma lurar dashi abinda ya dace yayi har ya fahinceta don a yanzu ta fahinci Daddy ya juya mata baya itama duk da bata san dalilin hakan ba saidai ta fahinci akan zancen dan natane da yake ganin bakinsu daya ya kawo sauyin nan tsakaninsu.

Don yanzu iyakan daddy da ita ina kwana ya amsa mata a daure ko kuma inta kawo abinci daga part dinta zai zauna ya danci wani lokacin wani lokacin kuma ko kallon abincin baiyi zai barshi a wajen.

Bata saba da irin wanan rayuwan ba sai abin yazamo mata sabon ak,amari don hakane tayi shawaran cewa dole sai tasa dan nata ya natsu kafin ta fahinci inda Alh ya dosa da ita.

Bawai tana nufin ya zauna dani dole bane a,a suyi nasu irin takon suma su nunawa Alh din ai suna tare dashi da hakane zata fahinci me yake nufi da canzawabshi.

Duk da dai bai sake mata magana ba akan dan nata amma tasan shirun shi a yanzuma din maganane bawai ya kyale zancen bane akan a tafi a haka hakan na nufin shima da nasa shirin akansu ke nan.

Anty nafisa bata dadara ba saida ta dauki waya ta kirani bayan sjn gama waya da mummy tana fadin sis ashe kina shigowa school shine baki taba nemana ba sai yau dana ganku din nan ?

Ina zuwa anty iyakaya department din mune kada nayi wani laifi kuma ace ina yawo donshine ban zuwa ko ina idan nashigo amma kiyi hakkuri don Allah na fada a karshe.

A,a aiba komai nafahince ki amma ki sani dake da hafiz din dukkan ku kanne nane don kinzo waje na bashi zaisa a jefiki da wani zargi ba sai dai idan dama kina da wani manufa akaina.

Na danyi murmushi na sake fadin anty kiyi hakkuri ba haka bane na fada maki gaskiya kawai don ki fahinceni bayaga school a yanzu babu inda nake zuwa kuma.

Gidan na bude nashiga ina sauke ajiyan zuciya tare da zama ina bin ko ina na gidan da kallo kafin in sauke ajiyan zuciya ina lumshe idona na fada bayan kujera na fara tunane.

Wayana dake aje gefena dana aje yake dan haske alaman kira yana shigo min a lokacin na dauka ina kallo number kasar wajece Canada na gani a rubuce.

Na sake maimaita sunan garin har kiran ya tsunke ban daga ba don ina tsoro banda kowa dake kasan waje da zai kirani nayi tunane a zuciyana lokaci guda.

Saiga kiran ya kara shigowa again nayi karfin hali na dauka na kara a kunnena ba tare da nayi magana ba sai naji muryanshi yana fadin.

Keda wullakanci ana kiran waya kina share mutane me kike daukan kankine wai ko kin dauka kina da wani matsayin da za,a kirakine wai ?

Muryanshine ba tare da sallama ba yatareni da fadin hakan daga daukan wayana kafin ya koma fadin ke ina kika fita kikaje ba tare da sanina ba ?

Wai waye hakane don Allah kamar ba musulmi ba daga daukan waya sai bakar magana kamar mara hankali to wrong number naja tsuki na kashe waya kai tsaye.

Ina jin yana fadin kika kuskura kika kashe min waya wallahi dip na kashe wayan ga baki daya ina jan tsuki nace wawa dab giya kawai kafin in koma fadin.

Lalai mum tayi gaskiya da takece min na kula da Anty Nafisa don yanzu a matsayin yar miji take a gurina watau dan ganin nan da tayi min har ta buga masa waya kai lalai mutum abin tsorone duniya.

Wasu zafafan hawayene suka zo min lokaci guda suna sintiri a fuskana har sai yaushe wanan zai fahinci iyayyenmune na tambayi kaina ina runtse idanuwana a cikin takaici.

Wanan kila ya kora tsiyar nasane yake son ya karanto min hauka daga kawai fita zuwa school inba abin dan giya ba zaka kirani kana zagina.

Na dade zaune a wajen kafin na mike zuwa dakina na sauya kayan jikina zuwa na shan iskan gida banso yin girki ba amma dole nayi saboda maigadina tun lokacin da yace min shi bakone daga kauye yazo neman abinci kano ya samu gadi nake tausayinsa.

Dadina guda shine Allah baiyini da yawan magana ba don haka ban fadawa kowa abinda ya faru ba balle a ban shawaran na dakata da karatuna dana kwallafawa rai.

Don hakane washegari na shirya na nufi school duk da zancen ya tsaya min a raina ni kadai nake hade abina tunda banda abokin shawara a lokacin.

Ina nan zaune da yake ina fashin sallah naji sallama a gefena na dago ina amsawa watace tsaye a gefena take fadin ko zan iya zama ni bakuwace a department din nan bansan kowa ba asalima dai ni ba yar gari bace transfer akai muna muka dawo kano daga Lagos.

Zaki iya zama mana na fada ina kawar da kaina gefe daya takai zaune tana bissimillah sai hakan ya burgeni amma ban dago na kara kallonta ba duk da kamshinta dake shiga hancina a wajen.

Itama din karatunta takeyi hankali kwance har lecturan da zai dauke mu ya shigo ajin muka mayar da hankalin mu ga abinda yake koya muna din.

Ya dade kafin ya fita lokacin ta juyo ta kalleni tana fadin gaskiya ban fahinceshi sosai ba da zan samu karin bayani zanso ni dai banyi magana ba sai kokarin bin abinda ya koya muna nakeyi.

Tana kokarin jana da hira duk da basar da ita din da nayi a lokacin bai hana taci gaba da magana ba dani sai amsa da nake bata a takaice take fadin in taso muje wajen motarta mu karya don lokacin break yayi.

Sai lokacin na dan dago ina fadin nagode ban tare da yunwa saida na karya na fito ke dai yar uwa naga kamar baki natsu dani ba niko kaf ajin nan dake hankalina ya kwanta.

Nagode na fada tace kinsan komai gamon jinine na hango natsuwa a tare dakene sunana hauwa Garba daga Niger state muke aiki ya kawo mu garin nan duk da mijina uwarshi yar garin nan ne ita.

Sai lokacin nayi dan murmushi a fuskana ina dagowa nace surname din mu daya dake ashe nima zainab Garba katsina nake bearing a takarduna.

Tace shike nan mun zama sisters dake ashe shine mafarin sakewana da wanan bakuwar da yanzu take dan sakani magana koda ban son ba kuwa.

Don irin mutanen nan ne masu son asani nan halinmu yasha bamban da ita amma ba laifi tana da son naci ga karatu ga yadda na fahinta idan an koyar bata gane ba zatayi ta nacin da sai ta gane kome ake nufi wanda nima ina kara fahinta ga hakan.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[3/1, 07:51] +234 706 511 1949: *_GUDUN ƘADDARA_*

H U G U M A

PAGE 13

Waya ta sameshi yana yi. Dogon wando ne fari qal a jikinsa da singlet fara itama,sai ya ajjiye wayar yana duban tanja data tsaya nesa da falon

"Mainasara bibi ce take kira"

"d'accord" ya amsa can qasa da muryarsa me sanyi.

Ko daya baiyi niyyan shiga sassan bibi din ba,ya sanyama ransa ma sai tayi cigiyarsa kafin ta sake ganinsa,saboda yana ganin cewa suna da tagomashi wajen lalacewar ginin da ya fara yiwa rayuwar sultana. Saidai kuma bibi din ta wuce ta kirashi yaqi zuwa,don haka ya sauke qafafunshi dake saman table qasa yana ajjiye wayarsa saman kujerar ya wuce zuwa bedroom dinsa.

Kaftan abaya budaddiya ya zura navy blue,kalar data fidda sigar kyawunsa matuqa,haskensa ya fito sosai,ainihin zallar hasken cikakken ba'abzine.

Kamar yadda yake dabi'arsa hannayensa zube a aljihun kaftan abaya din yana qissima abubuwa da dama cikin ranshi. Iskar bayan azahar tana kadawa

kadan kadan me cakude da sanyi maras tasiri. Ire iren wannan yanayin suna masa dadi sosai kasancewarsa mutum ras son zafi ko kadan. Hatta da sutura ba kowacce yake sanyawa ba saboda baison abinda zai takura jikinsa.

Da nutsatstiyar sallamarsa ya shiga parlor din bibi. Ta amsa masa tana karantar nazarinsa sanda yake basarwa ba tare daya kalli fuskarta ba,daya daga cikin alamun fushinsa kenan.

"Samu waje ka zauna" bibi ta bashi umarni kai tsaye,ita dinma yau fuskarta ba'a sake take kamar yadda ta saba ba.

Kaman bazai zauna din ba sai kuma ya matsa sofa din gefanta ya zauna a kai bayan dukka wadanda ke zirga zirga a falon sun kau,don basu waje.

"Aliyyu" bibi ta kirashi da sunansa na asali kai tsaye. Sexy eyes dinsa ya daga ya kalli Bibi sannan ya motsa bakinsa

"Kada kace komai maina,mamaki kurum yanzu kake bani" ta fadi tana qare masa kallo tamkar tanason hange meye abinda ya canza a tattare dashi da ya sauya launin mu'amalarsa da sultanan tashi

"Gaba daya ka canza maina,kamar ba kai ba,ka tashi daga mainan sultana ka koma aliyyu haidar,ka tashi daga frèren sulty ka koma wani abu na daban,kana neman zamewa yarinya kamar wani dodo,kamar ba kaine ka raineta da hannunka ba?,kamar ba kaine kaci kashi da fitsarinta ba?,kamar ba kaine kake hana idanunka bacci saboda sultana na kuka ko tana rigima ko bata da lafiya ba,dukka ina wannan kulawar?,tsakaninka da ita yanzu sai kyara sai hantara sai tsangwama,sama da tsangwamar da kakewa kowa cikin gidan nan" bibi ta qarashe fada tana sauke maganganun nata hade da fitar sirrin numfashi,da alama daga qasan zuciyarta maganganun suke fita

"Me yasa bibi?" Ya jefa mata tambayar,idanunta kadan ta qanqance tana dubansa alamun neman ba'asin tambayar da yayi matan

"Me yasa bibi zaku barta ta sangarce bayan kowa cikin gidan nan tarbiyya bai daya ake musu,waye tafi cikin yaran gidan nan bibi?,sai abinda sultana ke so?,sai abinda ya kwanta mata a rai yayi kuma dai dai da raayinta?,bibi wannan ba soyayya bace sam ba qauna bace,ita din diya macace,gidan wani zataje,baki tsoron ta tashi a haka taje masa da dabi'ar da bazai iya ba a dawo muku gida da ita?,wala'alla ni din bana kusa da ku,kune zaku fini jin ciwon hakan,kuma kafin ni na gani ku zaku fara gani kune zaku fara karbar sakamakon"

"Auzubillah.....haidar me kake cewa haka?" Bibi ta fada fuskarta na nuna girman da zancan yayi mata. Ba komai saman fuskarsa kaman ma baisan me dame ya cewa bibin ba ya dage dukka girarshi biyu

"Oui(yes)"

"Dukka maza ne zasu iya daukan halin banzanta?"

"Subhanallahi,da gaske ka sauya maina,ka canza,na tabbatar frèren sultana bazai taba fadin haka a kanta ba.....to bari kaji,kai din yaro ne da har yanzu bai wuce shekara ashirin da biyar zuwa da shida ba,a dukka matakan tarbiyya banjin kasan wani abu me yawa,bata haka ake yiwa yaro tarbiyya ba,tsanani da matsi basa kintsa yaro ko kadan,ka sanyawa sultana zafi da yawa,kana amfani da irin zafinka na halitta,ita diya mace kwata kwata bata buqatar zafafawar namiji,bare kuma yaran mata da yanzun suke tasawa tarbiyyarsu nada matuqar sulbi da santsi,don Allah maina.....banajin dadin canzawarka kwata kwata,ka koma frère din sultanansa na baya".

Idanunsa ya lumshe sannan kuma ya budesu, muryarsa a lanqwashe yace

"Bibi na fiki jin rashin dadin dabi'un sultana,na kuma taras da ku ba masu goyon baya na ba wajen maidata hanya,bazan canza ba indai sultana ba zata canza ba,dole ta koma kamar kowanne yaro dake gidan nan" kai bibi ta gyada,tun ba yau ba tasan irin nasa halin. Yana da tarin kafiya da taurin kai akan dukkan abinda ya sanya a gaba ko ya furta zai aikata. Fadin zaiyi abu yana da wuyar ji daga bakinsa,amma muddin ya furta din to babu sauyi,komai dadi komai wuya.

Sake gyara goyon school bag dinta tayi dake bayanta,tana jin kamar ta fada dakin ta rufe yaa maina da duka,ai ita batasan haka yayi nisa wajen qinta ba,batasan haka zuciyarsa tayi zurfi wajen son quntata mata ba,lallai Allah baya bacci da har kunnuwanta suka jiye mata komai. Indai yana tunanin iya tsare gidansa,daci da baqin ransa,fada da hararraminsa zai bashi abinda yakeson yaga ta koma din to tabbas zata tabbatar masa ita din ba tsoronsa takeyi ba,kuma bai isa tabuka komai ba

"Sultana kibi a hankali,kinfi kowa sanin waye frère" wani sashe na zuciyarta ya gaya mata sanda take qissima da irin salon da zata shiga falon

"Idan garwashi ne shi ni wuta ce" ta baiwa kanta da kanta dama zuciyar dake gargadinta amsa,bata kuma sake tsayawa sauraron kowacce shawara daga zuciyarta ba ta sanya kai falon da waqar data zame mata madadin sallama.

Idanunta saman fuskarsa tana nazarin furucinsa daya bayan daya,dai dai sanda siririyar muryarta dake cike da tsiwa ta isa ga kunnuwansu tana rera waqar ado isa gwanja

Allah ka aika munafukinmu qarshen nesa,tafiyar qasa koda lafiya ko babu,kaishi garin da ko kuyanga babu,barshi a can da arziqi ko babu,ni nasha tabara nasha yasin,kuma nasha rigakafin alatsine . Sai ta juya zuwa waqar wani mawaqin qasarsu ta nijer

Munafuki Alla kasheshi,koda safe koda rana ko ma dare ne

Tana maganar ne kanta yana kallon lobby na dakunansu tana kuma nufar can,tamkar batasan da zaman mutane a wajen ba.

Mutuwar zaune bibi tayi,ana kukan targade ga karaya ta samu,ana neman gyara ga sabon ruwa ya ballo. Ko waye kai,komai girmanka muddin ba iyayensa ba baka isa ka ratsa waje bakayi masa sallama ba,kamar yadda duk yadda yake da buqatar shiga guri muddin ba'a amsa sallamarsa an kuma masa izini ba yana

juyawa ne ya koma inda ya fito. Wannan ya samu asali ne daga cikakken karatu da tarbiyyar daya samu daga islamic school din da yayi masu kyau a Nigeria.

Har ta kusa shigewa ya kirayeta cikin tsawa,kaman ta wuce ciki sai narkakken tsoronsa dinnan da take qoqarin binnewa ya motsa mata. Tunga taja ta tsaya kana ta waiwayo tana dubansu ba tare data iso inda suke ba

"Koma ki yima mutane sallama" idanunta masu kama da digon zaiba ta dan juya tana bata fuskarta,ta motsa qaramin bakinta dake cike da tsiwa tace

"Nifa na riga nayi sallamata ehe" daga wannan ta juya tana shirin wucewa dakin tare da sake maimato waqoqinta a sarari sosai saboda saqon ya isa gareshi.

Wata baqar zuciya ce ta motsa masa,tabbas sultana dashi take,shi takewa wadannan waqoqin. Uwa uba yau shine zaiyi mata magana tasa qafa ta shure?,tama maidashi mahaukaci?.

Daga sultana har bibi babu wanda yasan lokacin da ya isa dakin. Dai dai sanda take wurgi da komai na makarantarta kamar yadda ta saba tana sake sakin waqoqinta cikin harshen faransanci,ranta fes tana jin ta fara samun nasarar rage haushinsa cikin ranta.

Cire hijabinta yayi daidai da dauketa da marin da yayi,babban dukansa shine marin,bai iya wani duka ba idan ransa ya baci bayan shi. Sanin darajar da fuska take da shi ya sanya bai cika yin dukan ba,zaiyi wuya kaga ya daki wani cikin qannensa,amma wajen iya bada horo su kansu sun tabbatar babu na biyunshi kaf cikin family.

Wata irin gigitacciyar qara ta saki tana dafe kuncinta da hannayenta bibbiyu ba tare data fuskanci meye ya sameta ba. Sautin muryarsa saman kanta kwanyarta tayi saurin ingizo mata me yake faruwa da ita,saidai kafin ta gama daidaita tunaninta ya sake aje mata wani Marin hade da qatotuwar tambayar da batasan da wanne zataji ba,marin ko amsa masa tambayarsa

"Saikin gayamin wanene munafukin cikin gidan nan" yayi maganar yana zare belt din dake jikinsa. Dukka jikinta rawa ya fara yi,saboda ganin fushi muraran saman fuskarsa,uwa uba tunda take bazatace ga ranar da aka sanya madoki aka daketa ba,shine ma mutum na farko kaf fadin rayuwarta da ya taba taba lafiyarta tunda tazo duniya,wannan ya sanya take matuqar razana duk sa'ilin da ya shimfide mata dogayen yatsunsa saman fuskarta

"Waye munafukin nace?!" Ya maimaita tambayarsa yana ware mata lion eyes dinsa da suka sake gigitata,sai ta ware dukka muryarta tana qwalawa bibi da tanja kira

"Wayyo Allah na bibi,zai kasheni,zai kasheni,wayyo na shiga uku"

Yatsansa ya dora saman lips dinsa yana sake fidda mata idanunsa dake danqare da bacin rai

"Kika sake buda bakinki a nan sai na miki dukan da ba zaki qara iya daga yatsarki ba,tais toi idiot(shut up idiot)!" Ya qarasa fadi a tsawace. Dole qanwar naqi ta sakaya ihunta,duk da tana jiyo bibi na bugun qofar hadi da kiran sunanshi da bashi umarnin ya bude,saidai kuma bata da ikon cewa komai.

Stool dinta ya jawo ya zauna a gabanta,ta qanqame jikinta guri daya tamkar me jin sanyi. Ba sanyi takeji ba,tsantsar tsoro ne ya sanya jikinta ke shivering,amma batason yaga hakan daga gareta,hawaye kwance saman fuskarta,ilahirin fuskar tata radadi take mata

"A frère dinki kika sanni ko?,to daga yau ki saka a ranki maina nake a wajenki kamar yadda nake a wajen kowa na gidan nan,zan fiddo miki ainihin kalata tunda na fuskanci kin zama graduate a fannin rashin kunya

[3/3, 20:08] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Haduwana da hauwa a yanzu yasa na dan sake wani lokaci har banson mu rabu don tana sakani dan walwala idan muna tare kobaka so hauwa saita saka magana ko dariya.

Sannu a hankali wata yar sokoto itama ta hade damu saidai ita auren ta ya mutu a lokacin duk da tana cewa damu zata komawa mijinta ai don ko yaushe tana maganan hakan haihuwanta daya dashi suka rabu ta dalilin kishiya sai yayanta ya daukota zuwa kano ya kadata karatu a nan kano din.

Sai Fatima kawata ta secondary da wani lokaci tana zama damu itama don haka ko ina mu hudun zaki ganmu a tare don department din mu daya ba yawa ke garemu ba kuma dama hakan yasa muke tare da juna.

Duk zaman mu basu taba sanin cewa ni matar aure bace don ban fada masu komai ba akaina sun dai san cewa ni yar jahar katsinace kawai .

Su a zatinsu ina zama da yan uwanane kawai a nan kano din duk da suna ganin malam isah driver na zuwa daukana kullum amma basu kawo zancen aure a gareni ba.

Don a lokacin bamu da lokaci karatun mu yadau zafi zamuyi jerabawan canza ajine ba wani wasa ko shiririta agaremu gashi sun gane ina da fahinta don haka suka kara like min muka hade sosai dasu.

Ban kiran kowa a gida yanzu saidai su kirani don tun ranan da nakira mum ta furta min kunyanama take ji a yanzu don bata san me zata iya furta min ba na daina kira saidai su idan sunjini shiru daddy kesa ta kirani mu gaisa.

Ya ban hakkuri yace na kara hakkuri akwai abinda yake jira yasa ban jisu ba amma insha Allahu komai zaizo daidai a garemu nikan ban damu ba don yanzuma da nake zaman kaina nafi jin dadin karatuna tunda banda wani takura .

Bamai sakani aikin komai gidane ni kadai ke cikinsa don haka kwana bibiyu nakeyi na bata lokaci tunda safe na gyara gida kafin malam isah yazo daukana.

Dan abinda zanci kuma wani lokaci a waje muke tsayawa hanya in saya in dawo gida dashi ba sai nayi girki ba a ranan gashi ban saka damuwa ba yadda mutane suke zata sai wani haske da kyau dana kara a yanzu din.

Ma,ana dai sannu a hankali na fara gogewa ina ganin kwaliyan gayun makaranta yadda suke dresse dinsu don haka nima ban bari an barni a baya ba duk damu kayan mu da lap cort a sama don a bambantamu da sauran dalibai.

Da farko nayi rakin karatun nawa saidai yanzu ina jin dadinsa yadda muke samun shawara da kulawa yadda ya kamata sai nake jin kara son karatun likitan a yanzu.

Mahaifana da suka haifeni kuma kusan ko yaushe da dare idan na dawo nakan kirasu a waya mu gaisa mukan dade da baba yana ban magana har banson ya dauko min zancen auren hafiz dake kaina duk lokacin daya dauko min wai yana ban hakkuri nakan shiga wani yanayi na daban a lokacin.

Muyi hutu da kyar duk da hutun ba wani mai yawa bane dai amma mun samu dan sauki a lokacin saida nayi sati daya a gida ban leko ko get ba iyakata da waje in nafitowa maigadin gidan da abincinsa shine fitana.

Ranan na shirya don in kai masu ziyara gida a karo na farko ke nan wata shidda da auren mu kuma ke nan don a gaskiya nayi tunane kada wanan auren ya tabarbare muna zumuncin mu da iyayyena.

Tsab na shirya nayiwa malam isah waya tunda dare yazo da safe ya daukeni saiko gashi don inason inyi sammako in samu daddy a gida kafin ya fita kasuwa.

Don har zazzabi daddy din yayi amma yace kada a fada min shine baba ya kirani yana sanar dani don haka na shirya don zuwa gida din bayan nayi tunane akai.

Cake da zubo da kunnu ayyah mai dadi na hada nasa a basket sai gida da anty Nafisa na fara haduwa wani kallo take min zakice ranan ta fara ganina muka gaisa na shige part din hjy mum.

Ashe fasa fita tayi taje tana fadawa mummy shigowana dani da basket din ban ko zauna ba mum ta daukeni takaini falon daddy mu gaisa dashi muka gaisa ya nuna jin dadi da ganina din ba cikin mugun kama ba da sukayi zaton ina ciki.

Mun dan dade dashi muna hira kafin na mike don yafita don ba komai bane illa nasiha da saka min albarka kan biyayyan da nayi masu da suke min shida mum din har ya bada basket din yace a kaimai a mota kafin ya fito shida abokansa zasuci a kasuwa.

Yanawa mum sheri da cewa saidai ajin kamshin wanan hadin amma ba mai lasawa a gidan nan tunda diyana tayo min part din mum muka koma a can muke hiran karatuna da mum kafin na mike ina fadin mum bari nashiga nagaida mutanen gida.

Part din Dada na fara shiga inda na sameta a zaune ita kadai tana kallon tv na fado dakin ina fadin halan kina jin abinda suke fadane kin kurawa tv ido haka ?

Saida ta dago ta kalleni da kyau tace ja,ira yau kece a gidan namu ko angon naki ya dawone kuka shigo na kai zaune ina fadin ai kunfi kusa idan ya dawo kece zaki fara sani ai.

Watau Dada harke kika shareni kuka barni ni kadai kamar banda kowa ina rayuwa agida kamar manya kiri,kiri kikaki zuwa mu zauna tare ?

Tace bari yar nan karma kiyi magana don Allah nasan kaf gidan nan mu masu laifine a gareki ai amma don Allah ki yafe muna .

Da sauri na tareta da fadin haba Dada kin taba jin inda iyayye sukaiwa yarsu laifi kome kukai min ai a cikin gatane wata rana sai labari insha Allahu.

Allah dai yai maki albarka yau da ace ba jinin Abu kike ba watace da ba,asan yadda rayuka zasu baci ba da zancen nan lalai hakurima da kawaici gadonsa akeyi na yarda da hakan akanki.

Don kin nuna muna ke jinin Abuce da malam na cikin gida yadda suke kiran kakan mu dashi ke nan lokacinsu dan muskutawa nayi ina murmushi.

Tace yau abin nan da badon ke da iyayyenki masu hangen nisa bane bansan iya inda zancen nan zai tsaya ba ja,iri dan banza zai gama haukansa ya dawo hanya ai.

Bayace wai course ya tsayar dashi ba to wata shidda yanzu ai ya cika sai mugani wanan dan anyi la,anane a cikin zurian mu wallahi duk halin su Marka ya dauko babu halin zariya da dan nan ya dauko namu.

Bari na gaida mummy in dawo Dada na fada ina mikewa tsaye tare da gyara mayafin kaina da kyau na fice daga wajen Dada din.

Har nakai kofa na tuna da halimatu da ban ganta ba na juyo ina fadin wai halimatu fa Dada tace ke dai bari wata yar banza ke nan ai.

Tana katsina kusan wata ukku ke nan yanzu daga zuwa ta dubo iyayyenta taje can ta samu waje ta zauna ni banmasan ko sun rike abinsu bane can.

Sallama nayi har sau biyu ba a amsa min ba hakan yasa na zata basu falon a lokacin sai nasa kai nashiga amma sai ganin mummy nayi zaune tana cin abinci hankali kwance sai anty Nafisa dake fitowa daga daki.

Ban daddaraba na sake sallama a gareta ta amsa min a dakile na zube kasa ina gaida da ita kamar ba zata amsa min ba tadai amsa din tana fadin .

Ashe ina da darajan da zaki shigo gaidani na dauka ai ba za a barki ma kizo ki gaidani ba tunda nina haifi hafiz ai da sauri na dago na dan kalleta daga inda anty Nafisa take tsaye tana sauraron mu tace haba mummy haka ba kyau fa.

Ke ki min shiru don Allah ko yanzu ta shigo gidan nan watau ni banda darajan da zata fara zuwa wajena ta gaidani sai kubura ko don bata daukeni da muhinmanci ba a rayuwanta.

Koda yake ai dolene kiyi hakan tunda yadda akeso ba,a samu ba kinga ko dole ki hakan ina dai duke ban dago ba a yadda nake.

Taso sis ya exam anty Nafisa ta fada tana kama hannuna zuwa part din dakunan su mummy data bini da kallo taja uban tsoki tana hade rai tare da kawar da idanunta kaina.

Hijjab na rufawa mata asiri don haka hijjab din dake jikina ya hana mummy ta fahinci yadda na koma a lokacin sai take ganin ina nan yadda nake ai ban karu da komai ba sai bakin ciki da takaici kawai.

Na kasa sakin jiki da ita duk yadda take dan jana da hira akan exam din mu wai idan ina da matsala in fada mata tabi min case din nan na nuna mata banda matsalan komai ga karatuna ban jima ba na koma part din mum.

Kwatsam muna zaune muna hirane sai ganin mummy mukayi kamar an jefota tana shigowa take fadin hjy kubura yanzu ma din da zainab take matsayin sarakuwa a gareni ba zaki bari mu zauna lafiya da ita ba ?

Dan abinda ta kawo kin karbe kin tura daki koda yake ba mamaki ai don kinyi hakan dama donshi kikai dumu dumu a cikin rayuwanta ai.

Kaiya Allah waddan naka ya lalace inba lalacewa da rashin sanin ciwon kai ba har yaushe zakizo nan ki tsaya kina fada akan abinda mama ta shigo dashi gidan nan.

Au to haka kikace kina da wani manufa ke nan ashe watau lalacewane don na nemi sanin hakkina don yanzu mama a matsayin karkashin dana take ba karkashin ki ba ko wani a gidan nan.

Amma tunda hakane shike nan zan gwada maki baki da wani power yanzu akan yarinyar nan ke kuma makira zaki gane cewa kina wullakantani baki daukeni matsayin uwar mijinki ba ko kadan ko ?

Na dukar da kaina banyi maganan komai ba har tagama fadin maganganunta ta juya ta fita ban jima ba mum tace in tashi in koma gida wunin da banyi ba ke nan a gidan kuma.

Nayi niyar inje gidan mu sai na tuna da sharadin mahaifina akaina daya haneni da zuwa gida in dubasu sai idan mijina ya dawo yace inzo zanzo gidansu.

Wai ashe hakan bayan na tafi mummy bata bar fitinan akan zabcen zuwan nawa ba , acewanta wai nazo masu da abu mum ta boye a part dinta ita kadai don zalama.

Dole har gaban daddy dake zaune saida ya gama sauraron korafin mummy din ya dauki waya ya kira malam isah yace ya bude boot din motan ya dauko kayan nan da mama tazo mashi dashi da safe.

Nan mummy ta fara wiki wiki da idanu kafin malam isah ya shigo da kayan yana fadin Alh ayi hakkuri na manta inshigo dasune yace ya aje nan gabansu ya aje ya fita.

Lokacin daddy ya kalli mummy din yace bayan wanan tazo da wasu kayane gidan nan ina tace ani tayowa cake din da abinsha na kumace ba zan ba kowa ba a cikin ku na fita dashi kasuwa mukaci koba haka ba hjy kubura ?

To ni me zance Alh mum ta fada tana dan murmushi amma ai kasan ba,a kyauta min ba ta yaya yarinyar nan zatazo da abu gidan nan amma ba zan sani ba.

Ke Malka kada ki manta har yanzu ba dan nakine ke ciyar min da ita ba saiki bari duk ranan da dan naki yazo ya dauki abinda mukai masa da muhinmanci sai kiyi wana barazanan naki a kanta.

Ya dai tawace nike da iko da abina kuma ta nunawa duniya na isa da ita ni yarinyar ta gama min komai a duniyan nan don haka ki dauki zancen ki na shirme ki nade ke yanzu bakiji kunyan fadan wanan maganan ba.

Lalai mlka baki da kunya da har kikazo fada kan wanan abin don da kinada kunya da bakiko daga kai kin kalli wanan abin ba.

Ni dama nasan don a cuta muna akai wanan hadin bawani abu ba yaron nan yace baison hadin nan amma ka nace akan hakan yanzu kuma nayi magana kace ina na fito ?

Ta mike ta fice ta barsu zaune a wajen kowa imani ya kashe masa zuciya sai mum ne tayi karfin halin fadin inba shirme ba keda kika iya wanab kika gazaki saka danki yaiwa mahaifinshi biyayya.

Ta mike itama ta fice don lokacin har mijin nasu takaicinshi take ji ganin ya gaza daukan mataki akan iya shegen da matar nasa da danshi sukeyi ya zuba ido kawai ya kasa magana.

Tun rana kuma ban koma gida ba haka na hakkura na zauna gida ni kadai don in maida kaina busy na fara karatu a lokacin kan abinda mukayi a baya ko kuma in kuna kallo ina bin episode.

Har hutun mu ya kare muka koma makaranta nan karatun mu yaci gaba bani marmarin zuwa gida saboda fahintar da nayi cewa zuwan nawa yana haddasa masu fitina.

Don Allah ya gani a lokacin ba, zan iya zama part din mummy na tsayin wani lokaci ba saboda ban saba hakan ba a rayuwana zama a part dinta don bata da dadi ko kadan.

Karatu muke babu kama hannun yaro don haka inna fita tun safe ban dawowa sai yamma lis cikin irin hakane ranan na dawo a gaji bakin get nake sauka don ban shigo ciki don kada in wahal da malam isah din.

Sai dai idan ina da kayane zai shigo dani ciki in sauke sai ya tafi duk da umurnine na daddy nima akwai kyautatawa a tsakanin mu don ina mutunta dattijon sosai saboda ya dan girmewa mahaifina ga shekaru.

Ina turo get din gidan na shigo na hango mutum zaune saman mota ya kurawa kofan idanu ga karan sigari a hannusa sai hayaki ke tashi a wajen baiko gudan yaja matsala wuta ya tashi.

Gabanane ya fadi rasa don ban taba kawo zuwanshi ba sai ganin nan da nayi masa da alama ya dan dade a wajen zaune don guntayen taban da nagani a warwatse a wajen.

Cikin karfin hali na karaso ina furta sannu da zuwa makin ya amsa min sai dirowa da yayi daga kan motan yana jan tsuki tare da kakabe hannayesa.

A zuciyana nace kazamin banza Allah ya kara nisantaka dani mugu kawai azzalumi na nufi hanyar kofan falo na dauko key ina budewa.

A daidai lokacin wani mugun warin taba ya shiga hancina saida na zabura na dan juya shine ke hawowa step din daidai inda nake fuskan nan murtuk dashi kamar abin tsoro.

Gashi yayi baki ya dushe gashi kuma kananan kaya ya saka a jikinshi rigace mai dan hannu daya fito masa da damtsen hannusa waje sai wando jeans na maza dark blue ni bama idona ke mun gizo ba sai ince harda wani katon sarka da yan iskan maza ke sakawa idan sun kosa da iskanci a wuyansa.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[3/5, 08:43] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

30

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Da kyat na samu kallaman sannu da zuwa ya sake fito min daga bakina don kaina daya fara juyawa a lokacin ina jin kamar zan amaye yan hanjin cikina lokaci guda.

Hasaran rayuwa ko kana da rai baiyi ba wallahi don ga mutum har mutum tsayayye a zahiri amma ga idanuna bai cika mutum ba a wajena don raunin shi dana rifa na sani na boye.

Don hakane bani iya kallonsa da kima ko daraja a wajena yadda na taso da tsanar mashayin giya tun ina fuciciyata sanin da mukayiwa yan giya shine irin fulanin daji din nan dakan fara tambadewa suke shan giya a cikin garin.

Zasu biyo hanya suna tambele suna faduwa suna fitsari a wando da amai yara nabinsu da jifa suna masu waka sunyi marisa sunsha kwaya .

Sam ban taba dauka akwai yan birni dake wanan rayuwan hasaran ba ashe abin badaga nan yake ba kowa da tasa kalan kaddara a rayuwa abin masiface in Allah ya nufa kana ciki zaka tsunci kanka a cikinsu din din gani nima yau abin ya shafi rayuwata.

Shine zama da dan giya dan giyan kuma miji a gareni kuma dan uwana kaiconi da wanan rayuwan dana tsunta a kaina na fada cikin abinda baifi second ba na gama wanan tunanen lokaci guda.

Key na murda hannuna rawa na mude gidan ban ko tsaya juyawa ba na shige ciki kai tsaye Allah ya taimaka akwai wutan Nepa a lokacin da sauri nayi dabaran zuwa wurin fanka na kunna don ya kore abinda nake ji kafin na juya zuwa dakina.

Jakka na aje ina kaiwa zaune bakin gado dan tunane nayi dashi din akwai hakkin aure atsakanin fa kada Allah ya kamani da laifin hakan akaina wanan tsakaninsane da ubangijinsa.

Da sauri na daga daga wajen na fito na nufi kitchen din mu ruwan roba na dauko mai sanyi tare da cup na dora saman wani dan ture na nufi falon dashi.

Haba warin taba sigarine daya kunna still ya tareni a lokacin hakana daure har kafana na hardewa a waje daya don rudewa na nufi ida yake zaune ya mike kafa yana waya yana zukan taban a cikin harshen turanci.

Dago kai yayi ya jefeni da wani kallo mai kama da muguwar harara wanda hakan ya janyo min faduwan gaba, gaba daya sai naji na rude a wajen lokaci guda.

Wani irin tsorone da farganansh suka ziyarci zuciyana jikina har rawavya dan somayi na aje cikin karfin hali ina fadim ga ruwanan cikin wani kyarman murya da ban taba sanin ina dashi ba a rayuwana.

Na juya da sauri don in bar falon ai bankai ga dagawan ba naji tsukin shi yana fadin uban wa zai sha maki wanan abin da kika aje ko nayi maki kama da kazaimai ne wai ?

Maza ki kwashe kayan tsiyarki a nan jaka kazama kidahumar banza kawai wai ku wasu irin dabbobine da baku da zuciya hakane ?

Shin wai auren nan dolene kome da zaku nacein kamar ni kadaine a cikin dangi inba kwadayi ba da naci irin naku nagado ke baki zuciya ki koma gidan ubankine wai ?

Ko ina kwadayin mace sai a rasa wace za a hadani da ita saike kucaka haka mutum da zubi kamar kara koda yake ba laifinki bane naci gadansa kikayi ai don haka ba abin mamaki bane idan kinyi.

To ki sani akai kasuwa idan nine badai hafiz ba mata masu ajima ban kalla ba balle ke din nan da banga abin gani a wajenki ba har aba ko kun zata wanan farin naki zai iya rudanane wai ?

To fararen suna can suna mutuwa akaina saina zaba make hole rayuwana dasu ba banza irin ki ba ya karasa da sakar min wani uban tsuki.

Kada ki dauka donki nazo garin nan nazo don uwata da munafukin ubanki ke son kashewa aurene don in kwatar mata incinta ga kowa ba zuwan mutunci nayi ba da kika ganni nan a yau don haka na fara dake din kafin,,,,,

Ina tsaye na bashi baya kamar an dasani a wajen a fusace na juyo kafin yakai karshe nasan zagin mahaifina da suka dafawa laifin hakan akansa zai komayi kafin nace.

Ina sakin wani murmushin takaici a fuskana mai nuna takaici ga kalaminsa nace aikin banza dama hausawa sunce gwano bayajin warin kansa ai.

Ni da ka ganni na tsagwaron biyayya ga iyayye ya zaunar dani gidan nan don in nuna masu sun haifi diyar da suka isa iko da ita a duniya kuma ako ina.

Har ina abin kwadayi ga mai mumunan rayuwa irin naka a nan kadubeka ka dubeni in ba fin karfin iyayye ba nayi maka kama da zama da dan giya ?

Wani zabura naga yayi dayasani ja da baya kadan don ganin bai taso ba naci gaba da fadin babu hayar jirgi data mota wanan dai uban nawa daka raina kuka mayar dashi asuwakin bankiku saboda daukan alhaki ya gama maka komai a duniya ai tunda har ya haifeni nakuma zamo matarka a yau kowa ya sheda hakan .

Ba mamaki kila lokacin kana a cikin mayenka koda hakan ya faru amma wani gyatumin ya daura hakan don da son ran mune ba hadin kifi da kaska ko a hanya kuwa.

Wani zabura yayi yana nufo ni tare da fadin ke kina nufin ubana shine wani gyatumin nace ashe ka gane ina kaiwa dakin na rufo kofa da karfi na saka key ina hakki.

Tare da godewa Allah daya ban ikon fadin hakan koba komai yadai ji zafin zancen ai tunda ya taso hakan a kaina bada dan giya daga zuwanka sai masifan tsiya haka ?

Wanan abin dame yai kama dama ashe haka matan yan giya suke famane da tarun hakkuri da takaicin rashin zaman lafiya indai hakane gaskiya daddy ya cutawa rayuwana da aura min dansa Hafiz da yayi.

Baby kina ina ne mummy gani nan hanyar gidan hafiz daga nan zan wuce office ta fada bata tanka mata ba ta kashe wayan nata tana jan tsuki a daidai lokacin da mai gadi ya bude mata get din gidan ta tura hancin motanta ciki ke nan.

Don hankalinta bai kwanta ba ga wayan da taji mahaifiyarsu nayi da dan uwannata daya kira uwar yana masifa sai ya halaka yarinyar nan ko ya bar mata shedan da ba zata taba mantawa dsshi ba har abada.

Tun a waya ta fara surfa masa zagi ya kashe wayan haka ta kwana da zancen a ranta ta tashi dashi hakan yasata sammakon fitowa daga gida ta nufo gidan hafiz

din tun misalin karfe shidda da wani abu na safe shinr uwar ta kirata ganin tayi sammakon fita haka.

Tayi mamaki data samu kofan gidan a bude hakan ya nuna a budema gidan ya kwana ke nan ba,a rufe ba har gari ya waye haka kofan yana bude kai tasa ta shiga ko ina shiru a gidan .

Hakan ya bata daman fara kiran sunan kanin nata daga inda take tsaye din ga kayan ruwan daya watsar wanda na kawo masa da tiren da cup har goran ruwan duk a watse cikin falon.

Sai guntayen taban daya zuka ya warwatsar a kasa da kwalban yar mitsitsiyar giya duk a falon watse jin bai amsa ba yasa ta nufi kofana tana nocking tare da kiran sunana a lokacin.

Can nake jin muryanta sama sama a inda nake zaune wajen dana idar da sallah ina addua tare da tunanen makoma a yau tunda yace sai ya halakani idan ya kamani kuma dan giyane ba hankali garesa ba zai iya hakan dayace yasa na kasa fitowa daga dakin.

A hankali na bude dakin tana tsaye a kofan ta bini da kallo tare da fadim bai maki komai ba dai ko na girgiza kai a cikin takaici ina bata hanya don ta karaso dakin tace ki biyoni falo.

Iya abinda ta fada ke nan ta juya zuwa falo din nabi bayanta din muna isa yana isowa wajen yake fadin zanyi maganin kine yar iska mara mutunci.

Hafiz har a gabana kake gwada rashin mutuncin naka kome ka zauna kema samu waje ki zauna ta fada in a serious voice ga kowan mu kusa da ita na zauna a darare don kada ya taso yai min dukan dayace a banza.

Dan shiru tayi kafin ta dago tace dani yau baki zuwa school ne da har yanzu kina daki da sauri na dan kalli inda yake zaune din ba tare da nayi magana ba sai cewa yayi wata tsiya takeyi a schoolbdin koda taje tace ban tambayeka ba malam kafin kace min komai ka kwashe wanan kayan kazantan naka daga nan kafin mummy ko daddy su iso gidan nan.

Tunda kai baka da hankali ka rasa inda zakayi shaye shayen ka sai tsakiyar falon matarka don hauka hafiz kako san alhakin hakan ba zai barka ba hafiz wanan wani irin cin fuskane haka wai ?

Anya hafiz kana tunanen gaba kuwa kashe mummy kakeson yi da bakin cikin ka kome an maka auren nan na gida don ka natsu ka dawo hankalinka amma ba a huta ba duniyace fa hafiz tsawo da fadi gareta hafiz.

Komai shakiyancin mutum ba zai iya ganin iyakarta ba saidai taga nasa hafiz sai yaushe ne zaka natsu kaiwa kanka fada akan irin halaiyan nan mm akane hafiz ?

Yanzu ka duba don Allah wani mai mutuncine zai shigo gidan nan haka ya kalleka da daraja ko ita din tayi daraja a idon mutane an samu gidan ku a haka ?

Saidai ita matarka da yanzu ya zamo mata dole dole kuma tayi hakkuri dakai tunda kaddaran aure ya hada duk shaye shayen baban boy bai taba yinsa gabana ba asalima bansan yanayi ba sai bayan rabuwan mu nake jin hakan amma waya sani kaga koni matarsa bansan da yanayi ba sai a bakin abokin iskancin nasa yanzu nake ji.

Ki bar hadani da wanan kucakar yarinyar da sunan matana a gidan nan wanan fitsararyar kucakan zaki kira da matana ?

Au matar waye a yanzu in ba naka ba kana da sauran ja ke nan ashe har yanzu baka fahinci manufar daddy na hadaka aure da yar uwarka ba to bari in warware maka idan zaka fahinta.

Jiya daka dawo a mayenka ka fada min idan wata kake aure ba ita ba idan iyayyenta basu ji wanan haukan dakai mata ba jiyan nan amma ita gata ta shige daki tana hadiyan bakin cikinka.

Yadda kake ganin an manna maka ita itama din hakan take gani tsaban biyayya ga iyayyene kawai kaganta a nan din zaune dakai wani kallo ya watsa min daga inda yake zaune din.

Tace kwarai kuwa don a rufawa juna asiri daddy ya baka wace yake ganin zata iya hakkuri dakai a cikin dangin ko dangin aiba kowane zai iya yin hakan ba.

Enough don Allah kina fadin haka saita dauka ita din wata tsiyace ai nifa ban kaunar yarinyar nan a rayuwata don ku sani.

Anji a yanzu baka kaunarta itama bata kaunar ka ai amma yadda tayi hakkuri ta zauna kaima ka danne duk abinda kakeji game da ita a zuciyar ka yanzu ku zauna lafiya kada kuba iyayyen mu kunya.

Keda kike ta zncen iyayye su zo su zauna da ita mana kosu ba wani a cikin dangi tunda bani kadai bane namiji ai ko it mum bata da diyan da zata hadata dasu sai ni ?

Hafiz ta fada da karfi tare da mikewa tsaye tana fadin ka iya bakinka kada kazo ka fadi abinda zai zamo maka dana sani a gaba.

Bani dana sanin komai ko agaban akan wanan mai zubin wawayen zan dawo ina dana sani kome nazone ayita ta kare a daina damuna da zancen wanan yarinyar ana katse min aiyukana dake gabana.

Au haka kace ba zaka saduda ba ke nan ta kalloni tace ki tashi kije ki shirya ki wuce school kada ki makara wanan bai san ida ke masa ciwo ba tukun shima ya mike yana fadin idan taje ta tsaya can kada ta dawo gidan nan .

Ni dai nashige ina fadin dayafi nono fari a zauciyana a gurguje na shirya na fito na samesu yabini da mugun harara yana jan tsuki ta mike tana fadin mu zamu tafi kaiwa kanka tunane akan hakan.

Ban tunanen komai wallahi indai akan wanan yarinyar ne ta gama zama a gidan nan tace muje kyale mahaukaci idanta dawo ka koreta ina shike nan dai ?

Motan ta bude muka shiga muka barta ciki har lokacin fada take kwasa dashi tana fadin banda haukan giya a aura maka mace kamar wanan ka tsaya kana bura uba da hauka wai kaiga dan iska ?

Baki dai tsaya ya dakeki ba ko ta juyo tana tambayana hakan da kyat na sauke numshi na girgiza kai tare da furta a,a gareta ina hawaye .

Kiyi hakkuri don Allah haka yake tun farko da bakin zuciyan nan nasa na banza balle ya fada harkan drugs yanzu shine iskancin nasa ya karu haka.

Zancen yakeyi a yanzu baisan babban kuskuren da zai tabka ba a nan idan ya sake aka raba aurensa dake ba baki nayi masa ba wallahi sai yayi kuka da hawayensa ba yana muzantaki a yanzu ba nan gaba zai raina kansane a kan hakan.

Ina dai baki fadawa kowa wanan zancen ba zeey don fadan zancen nan zaizo ya shafi kowankune don mutuwan aure baida dadi wallahi ko wani irin aurene kuwa saiya tabawa mutum zuciyansa.

Kiyi hakkuri duk wanan haukan shirme yakeyi duk ranan da kuka zama daya dole ya sauko daga duk tsiyar da yakeji avyanzu balle komr hafiz yayi baya sa laifin hakan saboda yana da daurin gindi.

Both mummy da daddy suna da hannu cikin lalacewan hafiz

Don sun gwada masa gata fiye da tsamani yanzune daddy yake son nuna masa matsayinsa na uba agaresa an riga da an makara ga hakan ko .

Nidai ban ma jin wasu zancen nata saboda hawayen dake zuba min duk da na dan makara ranan bata yarda na wuce class ba saida taga dan natsuwa yazo min ta rakoni har bakin ajin don ta daukar min excuse ga malamin dake ciki lokacin kada ya hanani shiga.

Ranan haka na wuni a cikon bacin rai sai faman sake sake nakeyu a zuciyana kan yadda zamu kwashe dashi idan na koma din tunda ya furta kada in dawo masa gida a lokacin.

Kamar yadda mukazo tare itace tazo ta daukeni don komawa gidan sai naji dan sanyin hakan datayi min sai dai koda muka isa gidan arufe muka samu gidan da katin kwado ya saka ta baya.

A gabana ta kira mum tana fada mata abindake faruwa mummy din tace wai hafiz yana da hankali kuwa ko sai na bata mai rai akan zancen nan ne wai ?

Kafin tace yanzu ina mama din tace gamu tare da ita gaban gidan tsaye sai mummy din tace ku dan jira yanzun zan kirasa ya bude maku.

Amma anty dakin bari na koma gida kawai zaifi don karki tafi yazo yai min wani wullakancin daya wananbdin kuma tunda yace ba bar mai gidansa.

Ki koma ina zeey baki yarda da zancena ba ke nan komawan ki gida ai shine babban illa kuma kikoma kice masu me tunda ba sakinki yayi ba balle kije da tushe.

Gun baba zan tafi ba gidan daddy zan koma ba na bata amsa da hakan sai naga ta dago ta kalleni kafin ta girgiza kai tace shi baba garba din shine baisan tashin hankali ba ko ?

Ai kina zuwa gida zance ya baci harma in ba ai hankali ba sai zumuncin su ya baci da daddy kan hakan don wanan ba karamin zance ba.

Jan bakina nayi ban kara magana ba saboda tunane sa bakin ciki dake cina lokaci guda nine yau namiji kewa koran kare haka kuma ina lake saboda iyayye.

Baifi rabin awa daya ba sai gashi da mota fuuu ya shigo saida maigadi ya kauce mai da sauri kadaya take shi muna kallonsa ya fito yana busan iska cikin tafiyan kasaita.

Yazo dakey din baiyi maganan komai ba ya bude gidan zai juya ya tafine naji tace dashi abinda kayi ka kyauta ke nan hafiz kai me kake son ka zamane wai ?

ZAINAB IDRIS MAKAWA

[3/7, 10:17] Aishatu Aliyu Musa😀: DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

31

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN

LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Tare muka shiga ciki da ita bata zauna ba sai bin ko ina da kallo dayi nagidan ga falon sai warin taba sigari da wani tsami da nake zaton na giyane .

Daki na juya zan shiga don ban iya jure jimirin wanan takaicin a idona da hancina naji muryanta tana fadin hakkuri zakiyi zeey ki fito ki gyara wajen nan don dan iskan baisan inda kansa ke masa ciwo ba har yanzu shi.

Dole ke zaki zage ki gyara gidanki kada wani bakon kunya yakai ga shigo maki gida na hankan ga kinga akwai nauyi da kunya sosai don wanda bai sani bama sai ya sani yanzu ga halin da mijinki yake ciki ai.

Cikin kuka na juyo ina fadin anty bazan iya wanan abin ba gaskiya kuyi masa magana idan zaisha ya tsaya waje don Allah yasha abarsa warin abin nan yana sa kaina juyawa sosai wallahi.

Nasani zeey ko baki fada ba nasan hakan tare da ita muka tsaya muka gyaro ko ina tana fada min muddin yana gari kada in sake inyi wasa da saka kamshi ako ina a gidan.

Bata bar gidan ba saida nayi muna girki mukaci tare ga mahaifiyarsu nata kiranta a lokacin don kira yakai ukku tana fadin tana gidan har yanzu muna gab da kammala cin abincin ya shigo.

Ban dago kai nako kalleshi ba yana fadin wai ke har yanzu dama kina gidan nan tace to ina zani hafiz kana son kajawa mutane wani tashin hankali kuma inya kama in kwana a nan yau har kwana zanyi gidan nan ai.

Dariya ya kwashe dashi yana fadin zakiko hadu da daddy yau ajiku don yanzu nasan ya dawo gida by this hours bai kai dare a wajeshi ashe kasan da hakan kai ina kafito yanzu ?

Cikin gari mana ya fada yana zama kusa da ita yace naga mum da boy ai gidan hjy Binta na fito wurin salis acan nagasu zasu shiga islamiya,Ooh abokin tabaran ka ko ta fada tana hararansa.

Kajiki da shirme salis din ne abokin tabarana kawai sako naje in karbo a wajensa wai meyasa kuke zargin salis ne haka sosai lokacin na mike ina fadin.

Anty zanshiga ciki idan zaki tafi kiyi min magana na fada ina tattara kayan da mukaci abinci da ita a wajen ta dago ta dubeni tana fadin me kuma zakiyi a daki mu muna nan falo zaune ?

Akwai assignment din da nake son dubawa na mrs buhari data bamu gobe take son assignment din nata kuma shi zan duba na fada tace dani to sai nashigo kinsan mrs buhari kuwa kuna kuka da ita department din nan don yar kaifice ita.

Nasa kai na nufi cikin dakin ba tare dako juyowa ba zan shiga ke nan naji muryanshi yana fadin ba zaki ban abunci ba ke nan saina rokeki ko ?

Kunga irin abinda nakewa ke nan mutum ya shigo gida mace tayi maka kimkam kamar icce wai kuce dole sai na zauna da wanan gaskiya nidai ancuceni wallahi.

Ta bangarena tsaye nayi na kasa motsawa a wajen na kasa motsawa saboda banyi tsamanin zai bukaci girkina ba kodon yaji zanyi karatune yasa yake son making dina busy oho ?

Muryan antyne ke fadin jeki zubo masa ina dama kin aje masa ai dauko masa ki kawo masa na shige kitchen din na tsaya na hada kamar yadda muke hadawa daddy nasa abincin.

Da ace zaman lafiya mukeyi da ba wanda yaikaishi samun gata a waje don nidin training din mum ce banda matsala a wajen aiki don na iya komai na aikin gida tun ina gidan mu kuwa.

Na dauko abincin zuwa falo a gabansa na dire kayan abincin na juya na dauko ruwa na aje ina jira inji cin mutunci da diban albarkan da zaiyi min a lokacin har na gama na kwanta banji hargowansa ba ma,ana baiyi wani cin mutunci ba.

Anty tayi masa kur da ido tana kallonsa ko zaici abincin dayasa nakawo masa din ga mamakinta bayan tafiyana sai taga ya bude kulan abin ya kurawa tuwon semo din ido na dan lokaci.

Ko harda abincin nata ba zaka iya ci bane naga ka kurawa abincin idanu kamar mai tunane ya dago yana sauke ajiyan zuciya yace to ya na iya naga kun hada min kai akan yarinyar nan har daddy na batun yi min baki akanta.

Da murmushi ta sake tare da jin tausayin kanin nata ya kamata a lokacin hakan kuma ya kara tabbatar mata cewa ya fara saukowa daga abinda yakeji akansa kan auren.

Yunkurawa tayi daga inda take zaune zuwa kusa dashi da kyau ta zauna tana fuskantarshi tace hafiz ina son muyi magana dakai na fahinta kadai san banda kowa duniyan nan bayan ku don haka kamar yadda ba zaka yarda a cuceni ba nima hakan ba zan yarda a cutama ba kasani.

Hannu ya tsoma cikin ruwan dana aje mai don ya daureye hannun nasa ya soma daureyesu yace ina jinki ai ta kallesa lokacin da ya yanko abincin yana kaiwa bakinsa ta dan murmusa taci gaba da fadin.

Ka fada min meye BC damuwanka akan yarinyar nan ko kuma auren ne baka so ga baki daya ka kasa tsayawa kayiwa mutane bayanin komai har yanzu.

Don girman Allah ka fada min koma meye kada kace zaka boye min damuwan ka a yanzu don Allah kaga sai mu san meye mafita ga auren nan ?

Abincinsa yake ci hankali kwance ya mata bayanin daba zai iya tsayawa yaiwa kowa shiba bayan ita da Addil yanzu ko ko yasha giyar wake ba zai samu Addil da zancen nan ba ai.

Anty ta kura masa ido tana kallon yadda yake cin abincin kuma yana fadin zancen cikin kwanciyan hankali da iya gaskiyansa ke nan har kasan ransa baidai kaunar yarinyar nan zeey a rayuwansane.

Cikin tashin hankali da sauri ta dafe kirjinta tana fadin Hafiz kasan me kake fada hakane kuwa yarinyar nan fa yar uwarmuce ta jini ko banza muna alakan da zaisa kasota a ranka.

Yace kwarai kuwa na sani ai sanin da nayi din yasa ban taba jin ina son taba da kowa nata kuma bani fatan wanan ranan ma yazo da zance wai ni hafiz ina son ta

Kai ta sunkuyar kasa tana sauraronsa don tasan akwai wuya yasoni koya nuna kulawa a gareni nan kusa ta dago tana fadin hafiz wai baka hango babban kuskuren da kake kokarin tabkawa rayuwanka nan gaba.

Nifa haba Nafisat ya kira sunanta kai tsaye yana girgiza kai tare da fadin don Allah ki bari inma har kina tsamanin nan gaba yarinyar nan zata zamo wani abu har insota ki sani fa shi so a nan yake ya daki kirjinshi yace ba a goshi ba.

Na fadawa daddy wanan maganan dazun don mun zauna dashi munyi magana sosai yau kuma ya fahinceni don iyakar gaskiyana nafada kema kuma shi nake fada maki yanzu.

Amma ko ka tafka babban kuskure daka fadawa daddy wanan zancen haka kai tsaye don kafi kowa sanin laluranshi ta fada tana mikewa don barin gidan alokacin.

Har anty ta tafima ban sani ba don ni ina daki bansan wainar da suke toyawa ba a lokacin saboda nasa daya fitar suka gani doni nafishi jin duk abinda yake ji a kaina.

Don a rayuwana gaba daya yanzu na tsani in bude ido in ganshi ko inji an ambaci sunansa a gaba don shine mutumin dana fi tsana fiye da kowa a yanzu din.

Jin karan tashin motocinsu ya tabbatar min da sun bar gidan a lokacin kuma hakan na nufin ba mutum daya ya fice da mota ba a lokacin na dan jima kafin na mike na fito falon .

Tsaye nayi ina bin ko ina na falon da kallo kafin nayi ajiyan zuciya na taka na tattara kayam da sukai amfani daahi din saida na gyara tsab na saka kamshi na jawo kofan gidan na rufo da kyau na koma dakina na saka key.

Zan iya cewa na samu sasauci daga hattaranshi a yanzu don kowa harkan gabanshi yakeyi a gidan tsakanina dashi ballema idan na hada mai breakfast tun safe na fita bansan ya yake karasawa ba.

Haka zan dawo in samu gidan kaca,kaca in gyara da yamma ma zanyi abincin in aje masa in shige dakina amma haka zai dawo ya zauna ba kunya yaci ya koshi yabar min kayana a nan saina fito da safe in kwashe in wankesu.

Duk da haka rashin haduwan mu yana min dadi sosai don hakane damuwa da fargabana ya rage min don ko da zaran na fita su hauwa da karatuna zasu dauke min hankali sai idan na dawo kuma gidan zan shiga fargaban kada ya dawo ya sameni a waje.

Wanan yasa nake godewa Anty Nafisa don ina ganin cewa itace ta taimaka min har yake min hakan a yanzu don kafan da ya daga min.

Gashi kamar hadin baki yan uwa bamai zuwa wajena balle kira har baba idan na kirasa a gyrguje zamu gaisa dashi yace yana aikine banda dogon hira dashi balle inyi masa korafi.

Inda na gane bai gari wajen abincin daren dana kawo masane yadda na aje haka na samu abincin nawa na kwashe na gyarawa maigadi nayu masa dumamensa .

Da zan fitane na kula da motarshi baya gurin da yake ajeta maigadi na tambaya shike fada min yana ganin kamar yayi tafiya don ya gansa da yar jakka ya saka a mota.

Hakan yayi min dadi sosai saidana dawo school na bata lokacina na tsaya nayiwa gidan kwal na goge kujerun da ties din kasan har kitchen ga irin watauna don ina ganin kamar ina cikin kayan giyane a zaune.

Rana sati kuma har lokacin bai dawo ba na kara bin gidan nayi mai gyaran gaske saidai da kuskure ban yadda na taba bangaresa ba don gudun sheri irin nasa.

Hankalina kwance nake gudanar da komai don ji nake kamar ancire mun kaya ajikina ga rashin zamansa gidan kira,a na kunna ina zaune falon ga tashan African tv three na aiki a lokacin naji sallaman mum kamar a mafarki.

Da murna na tashi na tareta sai bayan nagama rugumantane kuma na saketa ina fadin mum wallahi nayi fushi mum kamar kin manta kina ya a nan ?

Dariya tayi tana fadin ja,ira kin taba ganin uwar data manta da yarta inba shirmenki ba ko yanzu ai son in ganki yasa yau na roki Alh daya barni inzo in ganki don nasan yau kina gida.

Mum dama daddy ke hana kowa yazo gurina ke nan tace to inya hana ai daidaine tunda mijin ki yana gari yanzu ko da bainan ai kinga nazo da kaina ban aiko kowa ba.

Mum wani miji kuma don Allah ?

Ni ban masan baya nan ba wallahi nidai na daina ganinsa kawai hakan yasa nayi tunanen ya kara gaba ke nan kuma.

Wani irin zance kike fadi mama kina matarsa har yayi tafiya tsawon kwanaki kice baki san baya garin ba wanan wani irin rayuwa kukeyi a gidan naku ?

Shiru nayi don ganin ta kura min ido tana son taji wani abu a gareni hakan yasa na dukar da kaina kasa na daina kallonta.

Tace yanzu shi da zai tafi bai fada maki zaiyi tafiya bane kome toni mum ina ruwana dashi mutumin daya fada gabana ya fada a bayana bai kaunan ya bude ido ya ganni balle a kirani wai da matarsa .

Mama kina son Allah ya konaki ne akan hakkin aure kome ta fada tana lafeni da idanu cikin canza yanayin fuskanta lokaci guda na dan turo baki gaba ina dukar da kaina.

Tace komeya fada ai ruwansa ke dai ki tsare hakkinki duk abinda kikasan mace nayiwa miji kada ki fasa ki masa sai ya saura gareshi amma ba ku taru ku halaka kanku haka ga banza ba .

Mum ina fa girki dashi kuma yana ci ai nayi kokari ban fita gidan nan sai nayi masa girki na aje mai kuma koda zan dawo zan samu yaci haka kuma ina gyara gidan nan sosai ko yaushe,,,

Ke arr rufe min bakinki wurin nan kada inzo in mamareki an fada maki yin girki kiba miji shine kawai abinda mace zatayi ta burge mijinta ?

A gabanki nake shiryawa na wuce dakin Alh kin sani ba baki sani ba zaki min wani zancen girki can da da baki auresa ba an fada maki baya cin anincine kome ?.

Gaskiya kin ban kunya dama nasan harda laifinki cikin wanan abin don da acebkin nuna masa ke mace ce kinsan kanki dole ya sauke wanan iskancin nasa.

Kafin nayi magana saida na daga na kalli kofan dakin nasa kamar zaifito yaji mezan fada a lokacin nace mum cikin shagawaba anty Nafisa bata fada maki furcinnsa a kaina bane wai sai hawaye .

Furucinsa waina banza mama sau nawa akayi irin wanan muna gani kuma ana tare an hayayafa a tsakani idan zaki natsu ki nasu mama ki maida kanki mace tunda ba haka zaki tabbata ba har abada kuna wasan boya a tsakanin ku.

Watanku nawa da aure yanzu na takwasa kuke nemafa ke nan a yadda naji Asiya tsohon cikine da ita niki niki hakama mairo ance cikine itama da ita.

Sai kece zaki zauna haka don baki san ciwon kanki ba kowafa hakkuri yake da auren nan da yaran da manya kuwa duk auren aiba wani dadi garesa ba kowa yasani amma haka ake daurewa da wullakancin dana miji don kowa raminsa yakewa dama.

Sai kawai naga ta mike tsaye a cikin fushi tana fadin inzaki gyara ruwanki mama ni kinga tafiyana tasa kai ficewa daga gidan da sauri na mike ina bin bayanta tare da bata hakkuri kada ta tafi.

Saida muka kai kofan fitane ta juyo tace min saurara kiji muddin kina son mu shirya dake to kibi maganata ko hafiz na dukanki kiyi masa biyayyan aure yadda Allah ya hallata muna yi mu mata kinga tafiyana.

Ta fice ta barni tsaye sororo ina binta da kallo har saida naji tashin motanta na sauke ajiyan zuciya ina tambayan kaina anya mum tana min son gaskiya kuwa ?

Idan ba hakaba tayaya zata umurceni da zuwa wurin wanan kaskantacen da baisan darajan ya mace ba baisan na iyayyenshi ba balle na wani kila dai so take a kwasoni a karye ranan.

Haka kawai naji gaba daya na koma wata kalla nayi tunane iri iri a zuciyana ta ina zan farane da zancen mum kai ni dai gaskiya sai ince banyi dacen zuwa duniya ba a gaskiya.

Kuka sosai nayi ranan don tun ina na zuci har na koma yi na fili ina maganganu ni kadai kamar tababa a cikin gida ko abinci ban iya tashi na girkawa kaina ba.

Monday na shiga school tun haduwan mu da hauwa take korafinnko nayi ciwone during weekend don na fada sosai lokaci guda murmushi kawai na iyayi bancewa kowa kome ba na barwa cikina zancen yana cina.

ZAINAB IDRIS MAKAWA

DUBA MIN BAYA FOKON,,,,

ZAINAB IDRIS MAKAWA

32

GA MAISON BANI HAKKINA ZAI IYA TURA KUDI DUBU DAYA KACAL A WANAN LAMBAN 2254380105 ZAINAB IDRIS MAKAWA ZINETH BANK KO A KIRA WANAN LAYIN WAYAN 08036959257 NAGODE ALLAH YA BADA IKON BIYA MUN GODE NAKU HAR KULLUN YAR MAKAWA, , , , , ,

YAR UWA KADA KI RAINA NAUYIN HAKKIN WANI A WURIN ALLAH DOMIN AMANACE HAKKI,WANI A WAJENKA , , , , , ,

HAKKIN MALLAKAN JUYAWA AUDIOVISUAL S ZARIA TV KEDA WANAN HAKKIN KADA WANI KO WATA YAYI GANGANCIN JUYASHI ZUWA AUDIO.

Zaune nake nayi tagumi na zurfafa a tunane bayan fitar malam dake daukan daga ajin don cewa da tayi zamu fita practical cikin wanan satin.

Ajin kowa na surutunsa akai ni kuma nayi shiru ina tunanen a zuciyana wanda ya shafi rayuwata a yanzu dama kowa da bukin zuciyasa akace.

Dafani da hauwa tayi yasa na sauke ajiyan zuciya mai dan karfi ina kallonta take fadin kaga manya ba tana can tana tunanen yadda zata fara fida.

Dan murmushi na sauke a saman fuskana ina fadin fidan me kuma anty na tambayeta alaman dai bani tare dasu tace yau ga tsiya me mrs buhari ta fada yanzu kafin ta fita nace ai banjita ba anty .

Banma san tafita ajin ba tace akwai matsala dama na fadi tun Monday yanayinki yake ba daidai ba zainab niko meke damunki hakane har kina batun fita yanayinki lokaci daya?

Lekowan da Rashida tayi tana dan kallon fuskana tace nifa na gane yariniyar nan aure take so ai mata duk kaga yarinyar na irin wanan raman manya sunce aure take so.

Dan wal nayi da ido ina fadin aure kuma Rashida aure na nawa kuma za aimun yanzu lah kinji ko ban fada maku ba ta fada cikin zolaya.

Murmushi nayi ina kawar da kaina gefe daya nace ni ai na dade da aure Rashida ko bakiga alaman aure bane tare dani na fada ina mikewa tsaye don bana son dogon magana a lokacin.

Bangaren mum kuwa a yanzu tana cikin damuwa kan zaman danta Addil da matarsa Aisha wace zamane na zamani mace ke juya miji yadda ranta keso agaban kowa kuwa zata bashi umurni .

Shiko bai dauki hakan komai ba zai bi umurnin nata a ganinsa duk cikin sone da kauna yake hakan gareta wanda su kuma mutane suke ganin ya koma mijin hajiya a lokacin.

Dayawan maza haka suke da sanyin rai amma mutane yan gaza gani zasu fassara hakan da an gama da miji don baida nacewa sai abinda mace ta umuceshi dashi kawai.

Wanda zancen har ya dawo kunnen iyayye ba kunnensu kadai ba don ko a gabansu sunsha ganin hakan sai abin ya fara damun mum don yawan tsegumin da akeyi kan hakan.

Missalin abubuwan kuwa shine agaban kowa zaice su bari adan kara time su tafi zatace No katashi mu tafi yanzu dai sai yabi umurnin ta din ya tashi a lokacin.

Ko kuma yace daga nan zamu wuri kazane sai matar tace ni bazanje yanzu ba hakan kuma zai tabbatan don ba za,aje gurin ba kamar yadda tace abubuwa da dama suke faruwa irin haka wanda su basu daukeshi komai ba a wajen su amma gun mutane hakan ya zama abin magana a garesu.

Sauda yawa hakan yana faruwa tsakanin ma,aurata sai a dauki hakan fin karfine kawai ga matar tashiga gaban mijinta ke nan sai abinda tace za,ayi a gidan .

Don hakane akeson sayawa agaban mutane don hakan ba wayewa bane zubarwa miji mutumcine agaban mutane kome zakiyi kiyishi a tsakanin ku biyu amma matan yanzu basa gane hakan yana ja masu illa ga aurensu sai suyi tunanen kome sukayi sunyi daidaine su.

Amma mutane saisu dauka cewa magani ko asiri matan sukewa mazan su gama dasu sai abinda sukace shine za,ayi duk da akwai dayawa masu hadawa da asirin don su mayar da mazajen nasu haka.

Ita kan Aisha wanan rayuwan yacita don ko babu kauna ko so tsaksninta da yan uwan miji datakewa gani gani a yanzu tana ganin dafisu miji mussanman anty Nafisa da sukasha soyayya dashi a baya na yarinta.

Gashi sun camfata cewa bata son yan uwa su rabesu don zata nuna bataji dadin zuwan dan uwasa garesu ba ko ta nunawa bakon mugun halin da zaisa ya bar gidan ba shiri.

Idan ana irin wanan maganan abin yana konawa mum rai sosai har wani lokaci takan kira dan nata ta fada masa maganganu aka matar nasa wanda baisan dalilin hakan ba.

Abu goma da biyu ya taruwa mum akanta ga zancena da hafiz ga kuma zancen gidan ya Addil dake son yafi karfinsu a yanzu don irin korafin nan yasa yanzu ya dauke kafanshi da kano tun bayan aurena da duka zo sau daya yazo bai kara zuwa ba har wanan lokacin.

Dama ance idan gida yai kyau hakan na samo mafarine daga jajirtatan uwar gida ko mai gida dole sai daya ya jajirce zakiga gida ya kafu har ya tsaya bisa tubali mai kyau.

Dayawa sukan dace da hakan a da zamanin baya namiji zai jajirce ya tsaya a gidansa yayin da mace ita kuma zata tsaya ta kafu ta taimaka masa wajen ganin gidan ta tafiyu a yadda tsarin yake.

Saidai a yanzu zamani yazo da wani nau,in da mata ke mulkin gida da kansu ciki da waje sai abinda mace ta tsayar ne umurni an kaucewa tsarin addini da karfi da yaji saboda boka mata sun koma juya gidajensu ba maza ba.

Wanan yake yawan kawo baraka a cikin al,umma inda dangin miji zasu shigo hakama wani lokacin dangin macen ba za,abarsu abaya ba sai zaman ya koma gashi nan dai agidan ba wani tsari maikyau da za,ai koyi dashi a wani gidan.

Wanda hakan yana cikin abinda ya taimaka wa yawan sakin aure a yanzu zakiga an koma tsarin zaman waje yafi dadi ga ma,auratan an rabu ana son juna bisa kan son zuciya da kaucewa ubangiji akarshe a koma a zaman waje kuma ana yadda badala a cikin al,umma.

Ya ubangijin Allah kasa mufi karfin zuciyar mu mu zauna a saman tsarin addani yadda ubangiji Allah da Annabinsa suka sharada muna muyi damu da zuri,an mu Amin ya Allahu.

To ankai dai inda ba,aso don ko har yakai Dada ta kwashi kafa zuwa gidan ya Addil din dake Abuja da sunan zuwa asibiti saidai ba,asha da dadi ba a zuwan nasu don ko sun sha tarin takaici da bakin ciki a gidan.

Ga rashin kulawa fa kuma yunwa ba zasu karya ba sai shadayan rana lokacin data gama barcin safen ta rafito lokacin zata tsaya girka masu abinci su karya hakama na rana zasu dawo asibiti a wahalce amma ba zasu samu abinci a gidan ba.

Sai dan kayan kwalaman zamani acewanta mijinta baya zama a gida don haka bata girkin rana da dare kuma sai wajajen tara za,a kammala abincin da zasuci.

Wanda suka dawo kano da takaici da bakin ciki wace ta je neman kafiya wani ciwon yunwa kuma yana son kamata a can sun dawo baki na fadi cewa ga abinda akai masu agidan.

Har yakai daddy ya kasa hakkuri ya dauki waya ya kira yaya din yai masa kaca kaca inda ya nuna baisan hakan ya faru ba don shi ba mai zama bane a gida.

Karshe da yaiwa matar magana fada ta hauyi tana fadin wanan yasa bata son yan uwansa suzo don basu zuwa sai sun samu sherin da sukaiwa mutum idan hakane kada wanda ya kara zuwa mata gida tunda gulma ke kawosu gashi yanzu anzo an mata munafuncin da akasaba kulla mata duk kokarinta akansu.

Tas,tas ya kwasheta da mari saida takai ga shirin faduwa a karo na farko daya taba lafiyan jikinta yace ahir dinki wallahi yana fadin ashe baki da mutunci Aisha kakantawace munafuka ko matan babana kike nufi ?

Ashe baki da mutunci da ake fadin baki dashi a gabana zaki kira kakata da munafuka ke wata irin mara mutuncine da har zaki iya kallon idona ki fada min haka ?

Tana dafe da kumatunta ta kalleshi tace honey nika mara yau akan yan uwanka dama ashe sunzo su kashe min auren da basu so Allah yayi tsakanina da kaine ban sani ba ?

Kika kara fadin maganan banza akan wani nawa zan maki abinda yafi hakan a rayuwanki don ban hada yan uwana da komai ba a duniyan nan haka kema naki koda yarone karami ina kokarin mutunta makishi sai nawane keba zaki iya daraja min suba har kina fadin magana a gabana haka don baki da kunya ?

Ta dan sake masa kallo mai nuna zaka san ka mareni ai ta juya a fusace zuwa dakinta ta barshi a wajen tsaye yana huci ya rasa me zaiyi akan hakan saboda bai saba hayaniya da yawa bashi.

Kwana biyu zaman tsami suke agidan kowa na harkan gabansa don ko Aisha ta dau zafi dashi akan zaisan ya mareta ai yayin da shi kuma yake mai matukar jin zafinta a zuciyarshi cewa tayi mai cin fuska bata bashi hakkuri ba.

Hakan ya jawo rashin jittuwa agaban shi ga mum ko zai kwana kiranta a waya bata dagawa har gwada kiranta yayi a wayan Dada amma taki karba don tana son nuna masa fushinta kowa na kokarin nunawa dan uwa darasi akan abinda yayi.

Wanan yasa ya soma tuna yar mum don da tana gida haka ya faru zatayi kokari ta shawo masa kan mum din har ta dauki waya don ko sa,an aurensu ba karamin gudunmawa yarinyar ta bayar ba ya sani kuma yanzu ko ta kara gaba tayi aurenta ko ya suke can da hafiz ma oho ya tambayi kansa.

Ke nan ko dan karema yana da ranansa son ko wani mutum da inda yake amfaninsa a sanaiya da wani ko a zama don hakane yake da kyau ka zauna lafiya da kowa a rayuwa.

Neman number na ya fara yi yayi sa,a number ya shiga lokacin na mike zuwa daki don haka ban samu dagawa ba har ya tsunke saidana dawo naga miscalled dinsa cikin mamaki na danna masa kira.

Yana zaune yana aikin a laptop dinsa kirana ya shigo ya daga yana fadin bari zan kiraki ai ya kashe Aisha dake daukan jakarta data bari falon ta kallosa.

Baima san tanayi ba ta juya zuwa ciki a fusace ita a zaton ta ya sauya rayuwanshi har ya fara harka da yan mata a gabanta hakan yasa ta cika tana batsewa har taje daki ta kasa zama ta juya ta fito tana cika da batsewa.

A daidai lokacin daya dauka yace yar mum aure ya boye ki a shagwabe nace dashi hai yaya wani aure kuma bayan kun mata da yar kaunar ku ya kwashe da wani dariyan da bansan yanayi ba yace.

Haka rayuwa yake ai zainab ke dai ki zauna da mijinki lafiya ki kara hakkuri nasan halin Hafiz zai zo ya sauko komai ya wuce insha Allahu ki dai kara hakkuri kinji.

Hakan yasa Aishan data kawo gab dashi dakatawa tana huci tana kallonsa ya dan dago ido ya kalleta kafin ya sauke yaci gaba da fadin karan mum na kawo maki yasa na kiraki jin hakan yasa ta juya ta koma daki tana tambayan kanta metaso ta aikata haka ba tare da tunane ba wai ?

Canko falon ya fada min abinda ke faruwa na nisa nace ita mum din haba dai meyasa zata dauki zancen wasu akan ka ka bari da kaina zanje gidan gobe muyi magana duk yadda mukayi zan kira in fada maka .

Yai min godiya ya kashe wayanshi yana furzo da iska tare da tunanen akan mum tasan halinsa da saninsa ai ba zai bari matarsa ta wullakanta kakarsa ba haka don ko har shiri yayiwa zuwan Dada din tunda daddy ya kirasa ya fada mai zancen zuwansu din.

Ko driver daga wajen aikinsu ya dauko yaje masu don zirga zirgansu tunda shi baida lokacin hakan wanan yasa ma bai yarda da zancen ba ya dauka don basu son matar nasa ne suke kokarin mata sheri.

Sai gashi ta gwada masa kalan tsiyan data tsula masu din agabanshi ya gani wanda ko waye yaso muzanta masa yan uwa ba zai dauka ba balle matarsa da yake aure.

Naje gidan washegari tun ban dauko zancen tana fadin mama dake da yayanki kuna son kasheni da bakin cikin ku na dauka kunyi aure zan huta ta karkashin ku sai gashi abin ashe ba haka bane ?

Mum Allah na fada maki na daina zan gyara kuma wallahi mum ina iya kokarina duk da zagi da muzantanin da yakeyi mum ya zagi iyayyena duk na shanye ban fadawa kowa ba ranan badon anty nafisa datazo ta ceceni dukana ya tashiyi ya kulleni a daki saida,,,

Nasan zai aikata hakan mama amma ki kara hakkuri ki basa duk wani hakkinshi daya rataya akanki shifa lamarin Allah wuya garesa ga sauki kuma yi nayi bari na bari sai ka samu takarda maikyau a gobe kiyama.

Duk abinda akace min hafiz yai maki nasan zai aikata hakan don ni kaina sai yazo gidan nan gani gashi ba zai gaidani ba don yana dauka da hadin bakina aka bashike .

Ya zamuyi kana da magabata kuma sha,anin aurene baka zagewa dole in baki hakkuri mama don kowa da kike gani hakkurin nan yake adakinsa auren sunane kawai ba wani dadi garesa ba.

Shi nake son matar yayanki ta gane hakan amma ta kasa gane hakan wai ace hjy ce zatayiwa wullakanci a gidansu ta hora tsohuwa da yunwa ga wullakanci kuma ?

Da ace ya daukemu da muhinmanci ai bataga wajen yin hakan ba ban yarda na goyi bayan su ba saida na nuna bacin raina kafin nace amma mum kinsan dai yaya ba zai yarda da hakan ba agansa sherin matane kawai yasa tayi amfani da rashinsa gida ta dinga muzanta masu nan dai nayi ta kare yaya din har ta dan sauko tana fadin ai dama nasan bayan dan uwanki zaki goya mama.

Nadai bata hakkuri kuma naga ta sauko din sosai don ta koma yabon halinsa kuma tace dani ai inya kira zata dauka don tasan yana cikin wani hali a lokacin ban jima ba na gaida mutanen gidan na fito zuwa gidan iyayyena don banson mu hadu da baba yai min fada tunda ya hanani zuwa gidan idan hafiz bai gari.

Na dan jima a gidan kafin na barsu zuwa gida na dawo banjima da shigowabane naji mota ta shigo get din gidan da karfi kafin naji kashe motar ashe shine ya dawo a lokacin .

Ina kitchen ina kokarin hada girki da zanci don ban tsaya ba can balle inci abincin dare a gida saiji nayi mutum ya shigo don karan rufe kofan gidan da naji a lokacin.

Hakan yasani fitowa daga kitchen din na nufo falo shine da kaya niki niki yake shigowa ciki da sauri na hada kalman sannu da zuwa ina kokarin karban kayan a hannunsa.

Kaucewa yayi tare da fadi don't try torch my belongings iam worning you kada ki soma taba min kayana ya shige ya barni wajen tsaye sororo ina binsa da kallon mamaki tare da furta mai hali baya barin halinsa dai.

Nikan kamar yadda na saba na hada girki na dora masa saman table na koma dakina na zauna ban sake fitowa ba sai washegari koda na fito na samu ya ci abincin dana aje masa.

Na kwashe kayana na wanke na kawo masa na safe dana rana nagirke na shirya na fita nabar gidan kai tsaye sai school tun da nagansa na kama kaina tashin hankalina ya karu a lokacin da dawowanshi.

Don nasan dawowanshi gidan wani tashin hankaline agareni tunda gashi ya fara yaushe da zuwanka mace taje taron ka da kaya zaka kogeta ka fara fada mata maganan banza.

Nikan nasan da wuya zancen mum ya shiga son ko ba inda yake ban dama har na samu nashigar da kaina yadda ta fada a wurin shi zan daiyi kokarina naga na cusa din kamar yadda suke so amma ba zan zake da yawa ba insha takaicinsa.

Don haka ban fasa masa yan aiyuka ba kamar yadda na saba kula mashi kamar bashi abinci idan ya dawo ya zauna in kawo masa ruwa zan masa sannu da zuwa koda bai karba ba.

Zan dai gaidashi din in aje masa ruwa kuma zai dauka yasha din idan na aje zan kawo mai abinci da drinks duk dana kula bai damu da shan drinks bashi amma nakan aje saidai na kula yana shan hadin gida don haka na zage wajen hada mashi irin drinks din hausa kamar su zobo fruits salad kunun ayya pineapple juice da sauran hadi har kunun zagmkin dawo da ake sayarwa wani shago nakan sayo na gyara masa.

ZAINAB IDRIS MAKAWA